*_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#ZafafaBiyar
#BlackMoneyLove

Littafin da labarin Ameenatou Wanda ni mamuhgee na rubuta gabaki dayansa sadaukarwa ne ga irreplaceable Besty na AMEENAH ABDULMALEEK (Meenal Maleek)□□

1
BismillahirRahmanirRaheem.

Kaman yanda yake a tabbacen zance Salati baya hana ɗaukar rai, Hakama Kasar kabari bata shuka sedai ta binne binnanne,
Itadai ƙaddara yashi ce ko an dunƙulata bata dunƙuluwa,
Rayuwa da kaddara a tare suke tafiya tamkar Yan uwa Daya sbd haka kowace rayuwa take tafe da tata kalar kaddara duk wanda ka gani yau to yabiyo ta jiya.

****Cikin tsananin sauri da rawar jiki me tsananin gaske dattijuwar dadahnsu ta fito daga dakin da suke ba tareda ta damu da tsananin ruwan saman da akeyiba masu karfin gaske da iska ga Kuma duhu me.

Runfar madafarsu ta girki ta nufa tareda Saka hannuwanta duka biyu ta share ruwan Dake sauka kan fuskarta sbd ta Gani da kyau.

Madafar data gama jiqewa tsaf ta zubawa idanuwanta da sukai jajir cikin nauyin zuciya da tashin hankali Amma Kuma halinda suke ciki a yanzu ya wuce taji radadin baqin ciki ko wanne iri Dan haka ta qarasa inda murhun wutarsu yake ta fara kokarin gyara Yan sauran itatuwan Dake gurin tana hada kansu Dan hura wuta kota Yaya duk da ruwa da iskan da ake zubawa me karfin.

Motsi taji a bayanta sedai Bata iya juyowa ba sbd kokarin hada wutar cikin sauri dan tasan ba kowa bane face babbah mahaifin 'yayan nata mijinta.

Zagayowa yayi ta gefenta Shima a jiqe kayansa na tsiyayar ruwa sosai hakama rawanin Daya zagaye kansa dashi sbd ruwan Shima ya jiqe sosai Yana tsiyayar ruwa.

Duk ruwan Nan da akeyi akansa aka farasu Yana tsaye kofar dakin da suke Tin safiyar ranar har zuwa yamman sallah kawai ke matsar dashi daga kofar dakin har hadarin ya Hadu Yana tsaye duk karfin iskan da aka fara aka fara

ruwan Yana tsaye a gefen dakin Yana jiran tsammani ya zauna ya tashi tsaye,yaje farkon Bango ya dawo Babu abinda yake fata Se Allah ya kawo musu wannan lamarin a cikin sauki ko Dan jarabawa da kaddarorin da suka ringa haduwa dasu a rayuwar Nan.

Tayata hada kan itatuwa gurin da hura wutar yafara kokarin yi Yana Dan rife idanuwansa dasuka manyanta sosai tsufa yafara saukar musu sbd ruwan Dake shiga cikinsu,
Ita kanta dada kokarin kunna ashana takeyi amma ruwa da iska Baya bari Amma takasa Dena kokarin kunnawar hannuwanta na kakkarwan sanyi da mutuwar jikin damuwan Dake dabaibaiye da ita Mai hade da tsananin tsoro.

Shi kansa babba dayake tayata kare iska da ruwan da hannuwansa Dan ta kunna wutar yasan wura wuta a wannan lokacin ba abune da zai taba yiyuwa ba har abada sbd ita kanta ashanar tsiyayar ruwa takeyi Amma dukkaninsu sun kasa yarda da sallamawa sbd Babu Wanda zuciyarta take a daidai da tinanin nutsuwa a cikinsu abu Daya ne a ransa shine bazasu iya rayuwa ba idan wani abin ya samu wadda ke cikin dakin gurin haihuwar abinda yake cikinta,

Itace duk wani karfin zuciya da karfin halin dasuke dashi na ci gaba da rayuwa bayan masifun dasuka ringa shiga,
Babba shine shugaban gidan Kuma gatansu Wanda ya kasance jigonsu,shikuma babba itace hasken zuciyarta Kuma nasa jigon Dan idan Babu ita baida jarumtar cigaba da zama shugaba a cikin Iyalin nasa.

Hannuwansa Dake Dan rawa Shima ya miqa ya karbi ashanar hannun nata yafara kokarin tayarwa Amma kwalin ashanar narkewa ma kawai yafara yi a tafin hannunsa sbd ruwan Daya gama jiqasa..

Qurawa tafin hannunsa idanuwansa dasukai jajir yayi Yana kasa motsawa bare cewa komai zuciyarsa na daukan wani irin nauyi da dumi a lokaci Daya.

Dadah ma da jikinta ke mutuwa dagowa tayi da jajayen idanuwanta ta kallesa zuciyarta na yankewa da ganin yanayinsa,
Yanda yake tsananin son mahaifiyar Ameenatou da Ameenatou haka take tsananin sonsa Dan haka bazata bari ya sake dandana radadin rashin da yayi a Baya ba na rashin ganawa da Rabin jikinsa Dan haka jikinta na rawa ta juya ta nufi inda tasan akwai wata ashanar ta dauko tafara kokarin wura wutar da idan har gawar Dake Rami zata fito tayi magana to tabbas tashin wuta a wannan lokacin zai yiyu.

Ahankali babba ya Bude idanuwansa dake rintse ya Kalli dadah Daketa aikin abinda bame yiyu bane Amma taqi denawa Se qarawa takeyi kaman batasan

ruwane ke tsiyayar daga shanar ba.

Hannu ya miqa ya karbi ashanar ahankali tareda saikinta qasa ya kamo dadan suka bar gurin zuwa kofar dakin da ake komai a ciki sedai kafin su iso matar Dake ciki ta fito dakin gabaki dayanta itama a jiqe da zufa jikinta duk a sake.

Zuba musu idanuwanta tayi kaman yanda suma zuba mata nasu idanuwan suka zuba mata kafin babba ya dauke kallansa daga kan matar ya mayar kan kofar dakin Yana kalla cikin sanyi da wani irin zuciya dayaji Yana saukar masa Yana barinsu.

Dadah ce ta iya samun karfin halin Bude Baki cikin sanyi tace

"Ameenatou ta....??? Kasa qarasawa tayi sbd batasan amsar da Za'a bata ba idan ta qarasa tambayar.

Numfashi matar ta sauke ahankali tareda kallansu su biyun cikin nutsuwa da kaucewa matsala tace,

"Bazan iya ba dole ayi gaggawar kai ta asibiti kafin wata babbar matsalar data fi wannan ta biyo baya."

Shiru dukkaninsu sukayi jin abinda ta fada,
Ruwan dake sauka kansu kawu ya kalla Dan baisan tayaya zaa fita da mara lafiya a cikin wannan ruwan me karfi ba zuwa asibiti yanzu yanzu ba.

Dadah data kasa cewa komai dakin kawai ta shige tana hadiye hawayen dasuke ciko idanuwanta Dan gano 'yarsu.
Babba Kuwa juyawa yayi Shima batareda yace komaiba Dan Nemo abin hawan tafiya asibitin cikin gaggawa duk da Samun abin Hawa acikin ruwa me qarfi irin wannan tamkar shige ruwa neman allura.

Tsayuwar dadah akanta bayan shigowa dakin yayi daidai da fara jijjigarta Dan haka take jikin dadah yadauki rawar discon da Bata shirya ba,murya rikice a karye ta kwada kiran Hafsatu datake wajen tana kamo 'yarta jikinta tana rokon kada Allah ya dauki ranta a yanzu yabarsu da ita.

Hafsatu data shigo dakin a rikice idanuwanta na dauka akan yanayin ta qaraso a cikin sabon rikicewa tana cewa,

"Innalillahi wainna ilaihirrajiun,
Shikenan, shikenan, innalillahi wainna ilaihirrajiun.."

Dadah da kunnuwanta suka dauke ji a take dago jajayen idanuwanta tayi tana kallan Hafsatu kaman wawuya takasa furta komai sbd Jin komai na 'yarta ya tsaya cak a jikinta.

MAFARI
SHEKARUN BAYA!!!!!!

SEELAH'S shine karbabben sunan Aminai biyar da suka taso tamkar uwa Daya ne Uba Daya ya haifesu,
Kauna,shaquwa,AMINCI,yarda,hakuri da tsananin son juna da sukeyi shine ya samar da sunan SEELAH a tsakaninsu Wanda yake dauke da maanar karfin daukaka.

A farko su din bayi ne da suka taso cikin wahala da bauta tareda leburanci a babbar taskar gino danyen zinarin gwal.,

A rayuwar Gina ramukan Nemo zinari suka taso suka girma har Suma suka gada 'yayansu ma suka gada daga garesu,
Basada lokacin iyalansu sbd wasu lokutan idan suka shiga ramin da tsawonsa da zurfinsa tareda duhunsa da azababben zafin da yake kashe wasu da dama aciki sukanyi kwanaki da Basu fito ba.

Ahaka suke rayuwa wadda babu ranar da baa samun mutuwa a cikin ramin Dan kuwa ginar zinari Yana tafiya ne da ginar kabarin binne wainda jininsu yake tafiya a cikinsa.

MAMMAN SEELAH,OMER SEELAH,LAMEENU SEELAH,KASIM SEELAH da JAMIL SEELAH sune Aminai biyar da suka taso a tare cikin tsananin shaquwa da tsananin hadin Kai tamkar iyayensu da suka taso a Hakan tare tin kuruciya har girma har suka rasu Daya bayan Daya duka a harkar zinari Dan haka suka a tare suka taso tamkar iyayensu dauke da sunan SEELAH Wanda aka shedasu da shi gabaki Daya kauyensu da zagayenta.

Da farko su din sun banbanta da iyayensu sbd halayensu dasuke a Dan banbance tareda raayoyi Amma duk da Hakan kusan su kansu sun shedan da Babu wata kauna ko shaquwa bayan tasu shiyasa da yawa baa San ba iyayensu dayaba a idanuwan mutane su din yayane na uwa Daya Uba Daya.
##MAMUH#
#BLACK MONEY
#BEST LOVE STORY
#ZAFIN KAI
#JAMAAL JEEY SEELAH
#DEEP

#AMEENATOU
#2024ROMANCE

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_* _Mamuhgee_

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#ZafafaBiyar
#blackMoneyLove

2
Kaman yanda suka Saba duk zasu shiga Rami a tare suke shiga basa yadda su shiga ba tareda Dan haka Basu taba shigar ba tareda junansu su biyar din ba.

Gyara tsayuwa mamman yayi Yana Dan gyarawa daurin jakar kayansa a qugunsa Yana kallan omer da kusan shine koyaushe me zama karshen Shiga Dan ya yaddarwa kansa idan kullum suna shiga su fito wataran yasan idan

suka shiga bazasu fito din ba.

Shiga sukai da karfin gwiwansu tareda qarfin zuciya Dan kuwa ginar zinari Se me taurin zuciya da rashin tsoro,

Rami ake ginawa me zurfin gasken da idan ka shiga zafinsa da duhunsa kadai zai iya kashe me qaramin karfin jini ko me tsoro,
Da fitila ake shiga tareda batiran fitila da ruwan Sha duk a jikinka daure sbd idan ka shiga bawai Kai tsaye kake fitowaba wasu sai suyi kwana Daya a ciki wasu fiyeda kwana Dayan da kwanaki ma duk sunayi a ciki sbd ba wai Rami ne da zaka ringa shiga Kai tsaye kana fitowa ba,
Idan wainda suke ciki suna ciki to ko magana zaayi musu Saida loudspeaker sbd sunyi Nisa a cikin qasar da ba zasuji magana Kai tsaye ba.

Aduk lokacinda zaa samu zinari ko ginosa to tabbas jinin rayukan mutane da dama zasu salwanta sbd hadarin Dake ciki tareda wani irin son zuciya me qarfin gaske,
Rijiyar Gino zinari bawai Rami ne na qasa ba zaa ringa ginawo Rami ne dazaa ringa ginawa a cikin qasar tareda dutsina masu karfin gaske Wanda shiyasa hadarinsa yakeda yawan gaske sbd wani dutsin kana bugosa a cikin ramin zai rufeka gaba Daya ya zubo ya danneka ba iya Kai Daya ba zai iya zubowa ta koina yayi sanadin Rai fiyeda adadi Wanda da yawa ana ji ana Gani za'a samu Ciro wasu wasu kuwa qasa ta ciny shikenan sbd bazaa iya cirosu ba alokacin,
Idan zaa haqo rijiyoyin zinari a gurinda ake da tinanin akwaisa ana haqo akalla rijiyoyin da fadinsu da zurfinsu bamai misaltuwa bane a gurin akalla daga rijiya goma Sha biyar zuwa sama har dari biyu Wanda jiri ma zai iya Kamaka idan ka tsayu a gurin.
Zinari nada wani Sirri Wanda shine a duk lokacinda jinin wani ya zuba to takan qara yaduwa ne tamkar Shukan da ake bawa ruwa.

Su mamman tin iyayensu na raye suke yawon nahiyoyi daban daban dan Gino zinari Wanda idan suka bar gida akalla sukan shafe watanni da yawa basu dawo ba sunacan cikin daji da Sahara da yawon kauyuka masu Nisa da hatsarin gaske Dan Neman zinari Amma har Allah yayi musu rasuwa Daya bayan Daya duk a harkar Basu samu komaiba bare Tarawa Dan haka yayansu suka dauki Niya da damara tareda alkawarin ko da dadi ko ba dadi,Koda jinin wasu ne saisun samu bazasu qare a wahalce kaman yanda iyayensu suka qare a daji da nahiyoyin nesa Dan Neman zinari ba.

Mamman a cikinsu shine Wanda yafi kowa karfin hali da rashin yadda Koda wasa a tauyi haqqinsu Dan haka suke Dan samun na abinci a harkar duk da Suma har lokacin Allah Bai Basu tasu nasarar ba Amma Basu cire Rai ba Dan yanzu suke matasansu.

Omar a cikinsu Kuma shine Wanda yafi kowa sonsu,
Yana tsananin kaunarsu fiyeda kansa sbd shi Kuma duk abinda ya samu su yake miqa Se yanda Akai dashi duk da Suma sauran suna tsananin kaunar junansu.

Dukkaninsu dai marayu ne tinda Babu me Uba a cikinsa hakama iyayensu mata biyu rasu, mahaifiyar Omar da mahaifiyar mamman,
Tinda suka fara Dan tasawa Suma idan suka bar gida suka kutsa nema saisu share watanni fiyema da yanda iyayensu ke dadewa batareda sun dawo ba sedai duk inda dayansu ya Saka kafa suna nan a tare kaman kashin awaki a manne da juna shiyasa kusan ake da saurin saninsu a duk inda suka yada zango sbd Yan biyar seelahs da ake kiransu.

Shekaransu bazasu wuce Sha takwas zuwa ashirin ba a lokacinda Allah ya bayyanar musu da babbar sa'ar rayuwarsu Kuma babbar musibar rayuwarsu ba.

A babban dajin kauyen ashalawa Dake wani yankin Daya raba shiga nijar da Nigeria suka yada zango kusan shekara Daya har sun zama Yan gari Yan gida Dan kuwa duk kusan da yawan jamaa sun Sansu Kuma suna Jin dadin aiki dasu Dan kuwa sunada karfin halin gaske da taurin zuciyan neman arziki ido rufe Dan kuwa sun dauki alwashi sun duqufa bazasu koma gida ba batareda arziki ba Wanda kusan zuciyar kowannensu ta sauya kudin arzikin zinariya kawai kota yaya.

A ashalawa wata babbar duniyar Neman zinari ce sbd asalinta ba gari bace bare kauye,
Tarin matafiya da Yan kwadago da Yan cin kasuwar gari gari tareda asalin buzaye masu harkar danyar zinari da Yan Nigeria Suma masu harkar rijiya da Kuma danyar zinari ne suka taru suka Maida asalin dajin da aka Gano tarin arzikin zinariya acikinsa gari guda,
Sun Maida dajin ya koma kusan babbar garinda kasuwar duniya kawai akeci a cikinsa,
Ashalawa baida dare baida Rana bare asuba,
Kowanne lokaci su a gurinsa lokacin harka ne Dan haka Koda yaushe a hargitse yake kowa na abinda yake gabansa,
Babu Mai auren da zaka samesa da iyalinsa a ashalawa sbd gurine da babi yiyuwar kawo iyali Dan kuwa Babu kalar kaddararrun mutanen da babu masu rayuwa daban daban,

Tarin karuwai masu aji da masu saukin kudi Babu kalar wadda babu a ashalawa,
Idan Maza kake so kayi muamala dasu akwaisu,

Akwai matasa akwai manya,
Hakama ta bangaren yare da kabila kusan Babu kalar Wanda Babu,

Babu wasu gine gine a ashalawa sai runfuna da tinti da kusan sune suke cikewa ashalawa sunfi dari biyu zuwa dari hudu ma,
Gine ginen Dake ciki ko dozin bazasu kaiba Suma na wainda suka riqa ne suka samu zinariya sosai suka Gina suka zuba karuwansu da suka koma tamkar matayensu Dan kuwa duk Wanda ya jiqa a ashalawa bazai rasa akalla karuwan kansa kusan guda shida zuwa sama ba,
Marasa karfi sosai sune suke da karuwai bibbiyu haka ko Daya zuwa uku Amma dai sauran har me goma akwai.

Masu siyar da abincin ashalawa dukkaninsu Suma kaman mata Maza suke wasu kuwa karuwan ne Dan kuwa idan baka bazaka iya kashewa ko illatawa ko zama busashiyar zuciya bazaka taba iya zama a ashalawa ba.

A garin ashalawa Babu ranar da zinariya Bata kisa hakama Babu ranar da wani Baya illata wani ko kashewa,
Idan baka zuciyarka bata bushe qamas ba Kokuma Daman Tim farko Kai din me busashiyar zuciya ce zaka iya komai Dan ka tsira to bazaka rufa sati Daya a ashalawa ba batareda ka Isa kofar barzahu ba Dan kuwa rayuwa ce akeyi ta ko ka kashe ko akasheka Dan haka zinariyar ashalawa take sake habbaka da yaduwa koyaushe sbd jininda babu ranar da Baya zuba Kuma jini irin Wanda takeso wato me zafi na fitar rashin Imani maana jinin kisar gilla.

Tafiya me tsayi ta kwanaki da satika harma da wata ce ta kawo su mamman Ashalawa inda sukaga duniyar da Basu taba Gani ba Dan kuwa ashalawa wata duniyar ce ta daban me zaman kanta.

Da farko sunsha wuya sosai daqyar suka tsira suka Kai lokacinda suka fara gane kan rayuwar tsira ko mutuwa akeyi a Ashalawa Dan haka mamman ne ya fara tsayuwa ya jefar da tausayinsa gefe ya dauki rashin imaninsu da rashin tausayinsu ya tsayawa Yan uwansa suka fada harkar haqar rijiyoyin zinariyar ashalawa wainda akalla akwai rijiyoyin da aka Tona a gurin sunfi dari uku Kuma Babu wadda idan ka tsaya gefenta zafin ciki kawai idan ya huro Maka zaka iya Yanke jiki ka Fadi sbd tsananin zufinda zaka share fiyeda awanni masu yawa baka Isa kasanta ba.

Duk bulayin yawon shekaru masu yawa da iyayensu sukai harma dasu wanda sukai sai da suka iso Ashalawa suka San sun iso inda ya kamata ace sun samu isowa tin lokacin iyayensu Dan haka gabaki dayansu su biyar din Babu Wanda baisan a yanzu duniyar dasuke buqata ce suke.

Tinda suke a rayuwarsu tin daga lokacinda suka fara takawa da kafafunsu

Basu taba zuwa koina ba batareda juna ba har suka girma wanka ne kawai yake rabasu Shima ba koyaushe ba sbd a ruwan gulbi suke wanka a tare sai Kuma su share kwanaki kafin su sake samun wata damar wankan sai zuwansu Ashalawa suka fara abubuwa ba tareda Shima shiga rijiya ne kawai sukeyi Hakan Wanda idan sun shiga sukan kwana Basu fitoba Dan haka kowa ya dage Dan kuwa yanzu kowa arzikinsa na hannunsa idan ya dage musamman Omar Dake da burin bawa kansa ilimin boko sosai da tasa dukiyar sabanin sauran da babu me dogon alkhairi a ransa.

Shekaransu Daya a Ashalawa sun goge sun zama gaba gaba acikin matasan da ake ji dasu a harkar,
Ba wasa ko tausayi aharkarsu,
Mamman kaf ashalawa bayan Yan uwansa seelahs babu Wanda bazai iya zubarda jininsa a qasar Ashalawa.

Kaman yanda kowa arzikin da Allah yayi masa daban haka Allah ya fara bayyanarda arzikin Dake tattareda kowannensu sbd sun fara Tara abin kansu suna samun zinariya sosai Dan yanzu zubar jinin a ashalawa yawa yake sake yi Kuma kullum samun baqin da Suma imanin Bai ishesu ba akeyi suna zama Yan gari Suma.

Turawa da labawa dakuma wakilansu sosai suke shigowa ashalawa wasu ma da helicopter ake kawosu suyi huldan su hau helicopter din su koma.
A taqaice ashalawa headquarter ce me zaman kanta ta huldar danyar zinariya wadda ake hadawa da gudanarwa cikin rashin gaskia Dan haka turawa da labarawa sosai suke Hulda da Yan Ashalawa Kuma Suma Yan ashalawa sunfi Hulda dasu sosai Dan baka iya fita Ashalawa da danyar zinari idanma ka hada sbd ta kowanne dajin da zaka fita masu jiran ka fito su kasheka su karbe suna Nan suna Jira.
#MAMUH#
#BESTLOVE
#ZAFIN KAI
#BLACKMONEYLOVE
#ROMANCE
#JAMAAL JEEY SEELAH
#TOOTOOHOT
#ZAFAFABIYAR

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOUH_*
Mamuhgee
#ZafafaBiyar

3
Da yamma ne sosai suka fito daga rijiyar zinarin bayan kwanaki da share a ciki,
Lameenu ne yafara fitowa da kyakkyawar sa'arsa ya samo zinariya me Dan yawa,

Murnarsa kasa biyuwa tayi duk da jikinsa Dake rawa sosai na tsananin wuya da wahalar Daya debo a ciki.

Mamman ne yafito na biyu Sedai shi Kam Bai samo wani abin arziki,
Jamilu da Omar da kasim ne suka fito karshe Wanda abinda suka samo Saida ya girgiza kusan mutane da yawa Dan kuwa sun samo abinda aka Dade babu Wanda ya samo irinsu.

Hayaniya Ashalawa ta dauka sosai Wanda tini aka fara kokarin nuna musu fin

karfi sedai mamman Kara rayuwarsa yayi akan Babu Wanda ya Isa duk da akwai wainda suka fisa karfi da girma Amma zuciyarsa kusan zata iya fin tasu qarfi da soyewa idan har rashin imanin sukeji.

Turawa Dake Ashalawa da larabawa masu siyan danyar zinari tini suka firfito suka kama zasu siye da tsabar kudin dollar ko naira duk Wanda akeso Kokuma ta banki.

Wanke qasar da tacewa aka hau yi Dan fidda zinari daga cikinta aikuwa nan ashalawa ta sake rikicewa da tsananin mamaki Dan kuwa zuciyoyi da dama sun shiga tinani kala kala akansu Omar da kasim da jamilu.

Su kansu manyan Ashalawa a tsaye suke ana aikin wankin zinariyar Dan kuwa kowa ya kasa tafiya Dan yawanta ya tabbatar musu da sai an rasa rayuka akanta Dan Hakan suka tsaya.

Kasimu Dake murna da nasa da Allah ya azurtasa dashi Wanda zai ishesa Gina rayuwarsa cikin rufin asiri da wadata tareda rayuwa me kyau Jin yayi gaba Daya jikinsa ya mutu murnarsa ta koma ciki sbd abinda yake kalla a abinda su Omar suka samu shine har yayansu da jikokinsu Inshallah bazasuyi talauci ba,
Wani zufa da sanyin jiki yaji ya rufewa a lokaci Daya ya juyo a hankali ya Kalli mamman wanda yayi Nisa Shima a nasa tinanin.

Dan goge zufansa yayi da hannuwansa Dake cikeda qasa da ruwan qasar sbd daga qasansu har samansu koyaushe a cikin qasa suke sbd yanayin rayuwar da akeyi a Ashalawa din.

Matsowa yayi gefen mamman ya tsaya Yana Dan sake kallan mamman Wanda har lokacin mamman Bai juyo ya Kalli lameenu dinba idanuwansa da suka Dan sauya suna kansu Omar da kasim da jamilu Daketa farin ciki suna rungume juna Dan kuwa taskar arzikinsu dasukaita yawo tsawon shekaru suna nema Allah ya hadasu da ita.

Numfashi mata sauti mamman ya sauke ahankali Yana dauke idanuwansa akansu ya Maida kan zinariyar da aketa wankewa cikin ruwanta da ake wanketa dasu.

Wani numfashin ya Kuma saukewa Yana kallan tarin daruruwan Jamaar Dake gurin anata ihun zinarin,
A kaf ashalawa duk wani Mai Rai a cikinta idan ya samu dama yanada niya ko kudirin danne su Omar ya karbe zinariyarsu ko a ta sauki ko ata daukan Rai.

Daga yanxu dasu Omar suka samu wannan taskar arzikin rayuwarsu tana Bakin bodar mutuwa da rayuwa Dan kuwa Allah ne kadai ya Isa ya fiddasu ashalawa a raye matiqar ba sune zasu zama masu kashewar ba Dan tsira da arzikinsu Daman cikin Dayan biyun ne ko ka kashe din ko a kasheka.

Tinaninsa tsayawa yayi cak Dan kuwa duk yanda yake tsananin son seelahs dinsa baisan tayaya zai Basu kariyarda sukai alkawarin bawa juna ba har mutuwa.

Shima juyowa yayi ahankali ya Kalli lameenu Wanda daidai lokacin Shima juyowa yayi ya kallesa kowannensu da abinda yake ransa daban,
Kallan juna sukai tsawon mintina Babu Wanda ya furta komai bayan zuciyoyinsu da kowace da abinda take tattauna.

Mamman ne ya fara dauke Kai Yana sake Maida kallansa kansu Omar yayi musu kallan daqiqu kafin ya daga kafafunsu Yana washe bakinsa ya nufesu Yana bayyanarda farin ciki da murnarsa sosai,
Shima lameenu takowa yayi ya taho Yana bayyanarda tasa murnar suka rungume juna suna wani irin ihu da farin ciki Mai tsananin gaske.

Suna gama murna kan harkar tace zinarin suka koma sai alokacin su mamman ke sake tantance tsananin yawan arzikin dasu kasim din suka samu.

Ahankali yaji wani abu me nauyi na tasowa daga cikinsa zuwa kirjinsa Yana dannewa.
Dago idanuwansa yayi ya Kalli kasim dake sake shiga farin ciki Yana rungume Omar hadda sumbatarsa a gefen fuskarta yana cewa

"Ahhh Omar ahhhhh Omar burinmu na ratsa ilimi me kyau zai tabbata,
Zamuyi Tarayya da ilimi a cikin wadatar Ubangiji da rufin asirinsa."

Wani farin ciki me sanyi dayake fitowa daga qasan Rai yake bayyana a kan fuskar Omar din Yana sake rungume kasim da mamman Wanda yake washe Bakin dole Shima.

Jamilu kuwa gaba Daya hankalinsa baa kwance yake ba idan ba ganin yayi dukiyar zinariyar ya shiga hannuwansu ba sunbar Ashalawa zuwa rayuwar arzikin Dake jiransu a duniyar wajen Ashalawa Dan kuwa Ashalawa kamar duniyar kafiran da ko sunan Imani ba Basu sani bane,
Ashalawa kamar wata qabilace me zaman kanta da Babu kalar zunubin da baa aikatawa a bayyane cikin izgilanci Dan haka shi a matse yake da barinta a yanzu Daya samu Arzikin da zai wadatar da duk zuriar da zai Tara har tsawon lokacinda Bai saniba.

Lameenu duk yanda yakejin murnar nasa samun a farko gabaki Daya ya dakushe Baya murna ko yar kankanuwa,
Daci da nauyi yakeji a zuciyarsa fiyeda yanda yayi tsammani Dan Bai taba dauka zaiji qyashin samun Daya daga cikin seelahs dinsa ba.

Har dare har safe suna aikin cire arzikin zinariyarsu ba har kusan wata yamma kafin suka samu aka gama cireta gaba Daya aka narka aka ajiye a jere wanda nauyinsu ya sake girgiza Ashalawa.

Sai a Daren su kasim suka samu kansu suka dawo rumfarsu bayan sunyi magana da masu Siya,
Na Omar wani bature ne zai Siya,
Na kasim da jamilu kuwa balarabe ne zai Siya Dan haka Basu baro tent na turawan Dake gefen manyan Ashalawa ba dayake da masu tsaron gaske na samudawan Ashalawa.

Karfe Daya da Rabi da wani abu suka shigo rumfarsu inda mamman da lameenu ke kwance suna bacci Dan haka Basu tayar dasu ba suna cikin tsananin farin cikinsu Daya dadu Dan kuwa wannan Daren shine darensu na karshe a Ashalawa washe gari zasu bi turawan zuwa sabuwar rayuwar Dake jiransu Kuma zasu tafi ne da Yan uwansa lameenu da mamman Dan kuwa dukiyarsu ta seelahs ce gaba dayansu.

Jamilu kaf rayuwarsa Bai taba samun kansa a cikin asalin farin ciki ba irin Daren Dan kuwa mahaifansu mata zasu samu rayuwar kulawa da tattalin da mahaifansu Maza Basu samu damar Basu ba suna gurin yawon nema har suka rasu.,
Zai Tara Iyalin kansa su taso cikin Hutu da wadata ba irin tasa rayuwar Daya taso tin qanqani a yawon duniya ba.

Omar da kasim ma kwantawa sukai kusa da juna suna kallan juna kowannensu zuciyarsa kaman zata zage sbd farin ciki da murnan samun rayuwar nutsuwa da Kwanciyar hankali da ilimi da suka Dade suna buqata da fatan samu.

Omar ne me tsananin burin son rayuwar nutsuwa da ilimin dayake tattare da Kwanciyar hankali da rashin damuwa,
Ahankali raayin Hakan da tsananin so da burin Hakan ya shiga kasim sbd tsananin kaunarsa da Omar Wanda sunfi kusanci sosai sbd kasim din Dake matiqar son Omar tin suna qananun kaunar Omar daban take a zuciyar kasim duk da suna son junansu duka su biyar din Amma Omar ya samu qarin matsayin da babu wanda ya samu a Aransa.

Tsakiyar dare guraren karfe uku bayansu da zagayensu yayi tsit Babu motsin komai da kowa sbd runfarsu tana daga baya Baya sosai inda dagasu sai daji.

Dukkaninsu sunyi Nisa a bacci me karfi sbd wahalar dasuka Sha ta shafe kwanaki acikin tsananin zafin Rami da duhu da wahala shiyasa idan ka fito kake bacci sosai sbd wuyar da gangar jiki Tasha.

Ahankali mamman da idanuwansa biyu bacci ba yaji motsi na kusanto runfarsu Wanda motsin yake cikin sanda.

Bude idanuwansa yayi ahankali daga kwancen dayake batareda ya motsa ba Yana sake saurarawa.

Tabbas motsin tahowa ne gurinsu
Tashi zaune yayi ahankali cikin qaramin hasken dayake gurin na farin wata Yana kallan inda lameenu yake kwance Shima idonsa biyu baiyi bacci ba yanajin motsin mamman din.

Wajen rumfar ya juya ya kalla daidai da isowar mutum uku Bai iya ganin fuskokinsu ba sbd ba haske sosai
Sharbebiyar wuqar Dake hannun Daya daga cikinsu idanuwan mamman suka sauka wadda yasan kaifinta Bata fitowa cikin mutum idan an soka batareda ta yanko kayan cikin mutum ba.

Da sauri mamman din ya miqe Yana Ciro tasa wuqar Dake karkashin pilon Kwanciyar sedai kafin yayi yunkurin Isa gurinsu lameenu yayi saurin riqesa daga kwancen dayake Yana kallansa cikin wani irin kallan Daya Saka mamman din kallansa Shima duk da duhu ne.

Zuciyoyinsu bugawa sukeyi sosai da sosai kaman zasu faso kirjinsu daidai lokacinda mutanen sukayi kansu Omar Dake kwance sedai kafin su afka musu kasim ne yafara tashi yayi saurin tarewa Yana ambar sunan Omar da karfi.

A rikice Omar da jamilu suka tashi lokaci Daya suna miqewa tsaye kowannensu na lalabo wuqarsa da wasu irin gora masu qarfin gaske.

Kokawa me qarfi ce ta kaure tsakaninsu suna ambatar sunayen su mamman da Basu ga tashinsu ba Amma Sam Babu motsin su,

Kokarin kashesu mutanen keyi sosai cikin rashin Imani ko kalilan hakama ga duhu basa ganin juna Amma sunqi yadda Dan haka fadan yafara Muni sbd jini ne ke zuba Tako ina a tsakaninsu sbd kaifin makaman hannuwansu bana wasa bane.

Ba qaramar yanka jikin kasim Dana Omar yasha Amma Sam sun qi yadda a kashe su,
Jamilu yanada karfi sosai Dan haka shi Bai jiqata kaman su ba sedai Shima yasha yankan har a fuska.

Mamman da zuciyarsa ke wani irin rawa da jijjiga daga inda yake yasan ko baa fada ba kashe su Omar zaayi to Amma meye amfanin lafewansu Dan akashe Yan uwansu su gaje zinariyar bayan idanma an kashesu din wainda suka kashesun zasu kashesa su tafi dashi su anbarsu a biyu babu an kashe musu Yan uwa Kuma an tafi da zinariyar.

Idan har Yan uwansu zasu mutu to gwara su mutu a hannunsu su su gaji zinariyar Dan kosu da zasu mutu sunfi son su Yan uwansu su mallaketa.

Abinda yake cikin ransa shine yake yawo acikin zuciyar lameenu Dan haka juna suka kalla a lokacinda suke Jin kasim na ambatar sunansu cikin rauni sbd tinanin ko an Riga an kashesu ne basa motsi.

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#ZafafaBiyar
#Arewabooks@Mamuhgee

4
Hankalin Omar tashi yayi mummunan yi rashin Jin motsin mamman da lameenu Dan haka ya fara sarewa Dan kuwa idan har an kashe mamman da lameenu anyi musu mummunan raunin da seelahs zasu bace gaba Daya Dan Suma ba tsira zasuyiba.

Jamilu da Shima yafara gabalaita bazai iya taresu ba ya juyo inda su mamman din suke zai ambaci sunan lameenu kawai lameenun ya daga wuqarsa Dake wani irin daukan ido a duhun ya kutsata gabaki Daya a cikin jamilun take jamilun ya dago jajayen idanuwansa da sukai jajir ya Kalli fuskar lameenu,

Shima lameenu jamilun ya kalla tareda zaro wuqar ta sake kutsata a gefen cikinsa tareda cirowa jinin jamilun na gangara a hannunsa har qafafunsa,
Jajir idanuwansa sukayi wasu irin hawaye masu tsananin zafi suna cika a cikinsu dukkanin jikinsa rawa yakeyi hakama.

Mamman ma tasa wuqar ya Ciro ya daga sama tareda warawa da qarfi zai kutsata gefen cikin Omar kasim da acikin duhun idanuwansa suka sauka akan abinda yake Shirin faruwa yayi saurin karawa da niyar ture mamman din sedai tini wuqar ta kutsa gefen cikinsa ta shige gaba Daya.

Kafin ya zare wuqarsa acikin matune ukun wani ya sake sokawa kasim wuqar daga bayansa take mamman yayi saurin cire tasa wuqar Yana ja da Baya sbd juyowar Omar Yana ambatar sunan kasim da karfi.

Ihun Omar da sunan kasim dayake kira ya Saka aka juyo hayaniyarsu kafin su lameenu suyi kan Omar tini mutane suka yo runfar kowa suka juya kan fadansu kan wainda suka kawo musu farmakin suka illata su sosai Dan haka Koda aka taho da fitilu masu yawa ana duba mummunan lamarin dayayi Munin da Babu me iya kalla Dan kuwa jini ne na kowa da kowa da aka zubar Amma na kasim da jamilu da suka mutu a take shine yake gangara kwance a qasa hakama Omar yaji rauni sosai.

Su kansu mamman yajiwa kansa rauni sosai sbd fita daga zargi duk da a duniyarsu duk Wanda yasan seelahs yasan bazasu taba illata junansuba koda kalmomin bakinsu ba kuwa bare irin wannan mummunan kisan Gillan rashin tausayi da Imani tareda tashin hankali.

Acikin wainda suka kawo musu farmakin Daya Shima take ya rasu sbd raunikan Daya samu dagasu mamman da lameenu sauran biyun ma sunji raunin sosai Dayan har idonsa Daya ta tsiyaye.

Duk tsananin halinda Omar ke ciki kuka yakeyi sosai kaman ransa zai fita da ganin gawar kasim a gabansa da jamilu,
Su kansu mamman da lameenu kuka sukeyi suna ambatar sunan Yan uwansu cikin tashin hankali da dacin zuciya.

Fada ne ya sake kaurewa akan gawawwakin uku sbd zinariyar dasuka bari take aka fara kokawa ana fidda makamai ana ihu batareda ko gawar an dauke daga gurin ba.

Hankalin lameenu Dan mamman tashi yayi suka Kalli juna Dan kuwa bazasu yarda ba bayan uban sukan bayan da akwai aminansu Yan uwansu na alkawarin har mutuwa duk akan wannan zinariyar Kuma suxo su rasata.

Omar gabaki Daya ya fita hayyacinsa sbd tsananin tashin hankali da girgizan wannan balain Dayake shedawa na mutuwar Rabin jikinsu biyu a lokaci Daya Kuma kisan rashin Imani.

Dayasan samun zinari zaiyi sanadin ran yan uwansu daya raki Allah ya hanasu samunta har karshen rayuwarsu.

Fada sosai kaman yaqi ya kaure a take gurin inda har an sake illata wasu mutum biyu an cinnawa rumfar wuta.

Omar da sauri duk rauninsa ya miqe ya dauki jakar zinariyarsu da shi kadai yasa inda suka ajiyeta ya daure a jikinsa tareda Jan gawar kasim ya fara fitarwa su mamman suka kamo ta jamilu suka fito da ita har lokacin kuka Omar keyi sosai Yana kallan gawarsu Yana juya ta yanda zaiyi rayuwa ba kasim hakama yanda zaije ya sanar da mahaifiyar kasim din kasim ya rasu ya barta hakama mahaifiyar jamilu.

Irin kukan dayake yi ne sosai ya Saka da yawa dakatawa daga tashin hankalin manyan Ashalawa din suka iso gurin ana haskawa da fitilu ana ganin Munin lamarin.

Akan gawar su kasim aka tsaya tareda wainda suka mutu duk akan fadan.

Gefe Akai dasu aka rufe Saida safe zaa musu sallah a rufe.

Omar kuwa dole dashi suka tafi Dan basa kariya idan ba Hakan ba Shima kafin safiyar ba samunsa zaayi ba Dan haka Suma su mamman duk tashin hankalin da suke ciki na yanda komai zai kasance Bai hanasu bawa Omar din kulawa ba daga raunikansa ba.

A rayuwar Omar bai taba tinanin zasu samu kansu a irin wannan mummunan yanayin ba duk yawonsu da hadarukan da suka Saba shiga,
Sun dauka zasu samu kyakkyawar rayuwar da iyayensu Basu samu ba Ashe zasuyi mutuwar kaskanci ne wadda iyayensu su Kam basuyiba sunyita ta rufin asiri daidai gwargwado sbd su a cikin rijiyar zinarin suke mutuwa.

Zazzabi ne take me karfin gaske ya rufesa Babu inda Baya kakkarwa a jikinsa gashi jikinsa har lokacin jini na zubar masa.

Mamman ne ya Kalli lameenu
Shima lameenun shi ya kalla kafin suka fara kokarin cigaba da tattalinsa suna basa kulawa da share masa jinin fuskarsa suna kukan rashinsu jamilu.

Duk da antaho dasu Omar din bangaren manya kafin safe fadan Ashalawa din be kwanta ba saima qara girma yakeyi Daman lokuta da dama karamin fada ko fada kadan sai a tayarda fadan da fitinarsa zatai babbar illa ga kowa sai anyi rashin rayukan da dama shiyasa koyaushe zinariyarsu Bata karewa habbaka takeyi.

Fatinar Bata lafaba ko kadan take ta zama babba Ashalawa ta dauki hayaniya,
Koda asuba tayi sallah kawai Akai turawan sukace tafiya zasuyi sbd tashin hankalin dayaketa sake rikicewa.

Tini sukai waya helicopter zai taho ya daukesu ya fidda su dajin.

Babban tashin hankalin Daya Saka mamman da lameenu kusan Yanke jiki a gaban manyan Ashalawa da turawan da zasu siye danyar zinarin shine Sanar dasu gabaki Daya tarin danyar zinarin kasim ya bawa Omar tin a daren jiyan da Akai rubuce rubuce komai sunan Omar aka Sanya sbd Omar shine zai riqe musu dukiyarsu dashi dashi din Dan haka gaba dayanta ta Omar ce gashi kaf acikinsu ukun da suka samu me yawan gasken ta kasim din tafi ta kowa yawa hakama ta Omar din Dan haka lissafinta ma da aka hada din hankali bazai taba daukaba.

Wani mummunan hayaqin tashin hankali ne mamman yaji Yana fita

kunnuwansa Yana gurbata numfashinsa dake fita da daqyar.

Lameenu kuwa manyan idanuwansa ya fiddo waje suna sauyawa zuwa jajir hannuwansa na daukan rawar tashin hankali yayi saurin qanqame hannuwan Yana kasa boye firgicinsa duk yanda yaso.

Juyawa yayi ya Kalli inda mamman yake zuciyarsa na dauka wani irin radadin zafi da 'dacin baqin cikin da Bai taba sanin da akwaisa ba.

Akan Omar dukkaninsu suka mayar da kallansu lokaci Daya zuciyoyinsu naci da wata irin wutan tafasar zuci.

Me kenan?
Omar sukaiwa kisan su kasim din kenan tinda shine yafi kowa arziki a Ashalawa kenan yanzu ko me?
Me Hakan ke nufi da cewan kasim ya bawa Omar taskar arzikinsa gaba Daya?

Lameenu a tasa zuciyar kuwa abu Daya ya sani shine tinda suka riga suka kawar dasu kasim akan zinariyar to kowama yayi musu shamaki da ita inda suka aika su jamilu can zasu aika koma waye,
Sun Riga sun fara aikinda Babu tsayawa sai sun mallaketa,
Omar bazai taba hanasu mallakarta ba Dan zai musu zarran da bazasu taba kamosa ba har abada Kila,
Tayaya zasu kallesa a samansu su suna qasansa bayan sune sukai dirty work din Daya basa Arzikin dukiyar.

Sake kallan juna sukai shida mamman har lokacin Babu Wanda zuciyarsa ba tafasa takeyi cikin tashin hankali da tsoron tabbatuwar abinda aka fada din ba.

Omar kuwa har lokacin Yana cikin halin rashin lfy Daya rufesa da kukan rashinsu kasim Daya kasa dawo dashi daidai.

Zinariyar kuwa baa tsaya komaiba aka ware ta Omar da kasim aka ware masa abarsa shine zai kula da mahaifiyar kasim Daman tamkar itace ta haifesa yake.

Ta jamilu kuwa batareda tinanin komai ba ko bin tsarin Daya kamata ba haka aka Kara rabe musu su uku,mamman da lameenu Da Omar din Wanda yace ya yafe musu aka barmusu su biyun.

Kason da suka samu ba qaramin kaso bane da zai ishesu Gina rayuwarsu cikin wadata sosai da Kwanciyar hankali tareda samarwa Kai suna da wani

matsayin ma Amma duk wannan Bai saukar da mummunan nauyin Daya Riga ya danne zuciyarsu ba data rikide a dare Daya Takoma wata sabuwa daban da kadan Baya isarta.

Gabaki Daya baqin cikin duniya ba basusan dandanonsa ba shine dabaibaiye da zuciyoyinsu akan mahaukaciyar arzikin da suke kallan Omar dashi Wanda basajin zai taba sauka matiqar ba sune suka kasance mallakinta ba Kokuma rabinta ma.

Tafiya zaayi da Omar sbd baturen dayayi musu alkawarin Basu irin rayuwar da suke so shi da kasim kafin rasuwar kasim din Dan haka ana rufe su kasim tashin hankalin Omar ya qaru sbd Kai tsaye su mamman sukace ba zasu bisu ba su zasu zauna anan su sake samun zinariya kafin su biyosa.

Su biyar din basu taba rabuwaba tinda suke a rayuwarsu sai wannan ranar da biyunsu suka bar duniya gaba Daya sai Kuma yanzu da zaa tafi da Omar abarsu Badan sunso ba sai Dan ana son nuna musu fin karfi.

Mr Jaden da tin farko Allah ya Saka masa kasim arai sosai fiyeda kowa a Ashalawa sbd ladabinsa da nutsuwarsa data fita daban haka kawai yaji bazai iya barin Omar ba a Nan bayan rasuwar kasim Dan yariga yayi musu alkawari hakama zuciyarsa Bata yardar masa barin Omar a tsakanin mamman da lameenu ba Dan haka baiyi tsaiko a tafiyar tasu ba duk yanda Omar ke cikin tsananin tashin hankalin rabuwa dasu mamman Amma Shima yanason cika burinsu shi da kasim na rayuwar Kwanciyar hankali da nutsuwa tareda wadatar ilimi Dan haka yabi Mr Jaden din tinda su mamman din zasu biyo Daga Baya.

Mamman da lameenu tamkar tsokar jininsu ce ake yanka ana rabasu da ita sukeji a lokacinda suke kallo Omar zai tafi da tarin arzikin da suke ganin sunada cikakkiyar haqqi akanta tinda sune sukai aikin kawar da me ita din Dan haka kukansu da baqin cikinsu na tafiyar akan Hakan ne sedai zuciyoyinsu ne kadai ke kika Banda idanuwansu da suka bushe Babu komai Dake cikinsu bayan radadin Jan bacin Rai suna kallo har Mr Jaden Dake riqe da hannun Omar ya jasa suka nufi filin da helicopter din dazai daukesu yazo ya daukesu suka bar dajin Ashalawa.
##MAMUH#
#TOOTOOHOT
#JAMAAL JEEY SEELAH
#AMEENATOU SEELAH
#ZAFIN KAI
#LOVE
#DEEP

#ROM

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#ZafafaBiyar
#Arewabooks@Mamuhgee

5
Lagos suka Isa da Omar Wanda tini zazzabi da ciwo me karfin gaske ya rufesa Wanda idan suka so a lokacin Mr Jaden zai iya karasa illatasa ya gudu da dibbin dukiyar Amma Sam har cikin ransa bayajin zai iya Hakan Dan take kaunar Omar din ta cikesa musamman da a bayyane mutuwar Rabin jikinsa ta tabasa wadda ba zai taba mantawa har abada ba,Dan ko Babu kauna irin

shaquwa da rashin rabuwarsu tin haihuwa dole kowannensu ya rabu ciki kuwa harda su mamman duk da babu Wanda yasan sune sukai kisan.

Mr Jaden na da gidan kansa Daya mallaka a cikin garin Lagos me girman gaske Dan haka ba asibiti ya nufa dashi Kai tsaye ba gidansa dayayi kama da Akira mansion suka nufo bayan yasa ankira likitan da zaizo ya duba Omar cikin gaggawa.

Isarsu Babu Bata lokaci aka shige da Omar har Daya daga cikin dakunansa Dake sama har cikin toilet take manyan yaransa biyu Ahmed da Aron suka gyare Omar din tsaf suka tsaftace sa daga datti da jinin jikinsa da duk ya bushe.

Kusan Omar din Baya hayyacinsa Dan haka suna gama gyarasa kusan gajeran wando sabo kadai suka Saka masa sai aka kwantar dashi a lafiyayyar gadon Dake dakin tareda ragewa AC karfi suka fice daidai isowar likita da nurse namiji Daya sai Mr Jaden.

Bude musu dakin Ahmed yayi Yana matsawa gefe suka shiga.

Kallansa Dr yayi ya raunikan jikinsa sai Kuma zazzabin gaske me qarfi dayake Saka jikinsa wani irin jijjiga.

Babu Bata lokaci ya fara dubasa cikin sauri sbd ganin Yana buqatan taimakon gaggawa.

Da farko akwai inda yake buqatan dinkuna sosai a jikinsa sbd deep yanka Daya samu sosai Dan haka su aka fara duk da an masa allura Amma Yana cikin azaba sosai sedai ko motsi Baya iyawa har aka dauki tsawon lokaci sosai aka gama.

Ruwa da wasu alluran akai masa tareda rubuta maganin da zai buqata Sha suka fito akan zaa daukarwa Omar din nurse me kulawa dashi.

Bayan tafiyar su Dr sai alokacin Mr Jaden ya samu kansa Shima yaje yayi wanka yaci lafiyayyar abincin da aka jere masa su a dining ya koshi ya kunna wayoyinsa ya ringa wayoyi tsawon lokaci kafin ya shige yayi Kwanciyarsa yafara baccin Hutu.

Omar Bai farfado ba sai bayan kwana Daya da wuni Wanda har hankalin Mr Jaden yafara tashi sai gashi ya farka Kuma lafiya kalau Babu zazzabi ko wani ciwon sai raunikansa da Suma zasu warke a hankali.

Kulawa dashi sosai nurse dasu Ahmed sukai harya samu damar yin wanka da

kansa yayo alwala yazo Ahmed dayake musulmi Dan uwansa ya nuna masa gabas yayi ramakon sallolin dasuke kansa duk da ba wani ilimi ko sani akan Addini suke dashi sosai ba Amma dai sunsan sallah Kuma basa tsallaketa.

Ko kafin ya gama sallolinsa tini aka shigo da abinci aka jere masa su lafiyayyu masu Kara lafiya da drinks masu sanyi kadan.

Aron ne ya shigo Shima da wasu sabbin kayan sakawar bayan wainda aka kawo masa kafin ya fito wanka.

Yana idar da sallan abincin ya kalla tareda juya idanuwansa Yana sake kallan dakin dayake ciki din Wanda Basu taba sanin akwai tsari irinsa ba duk yanda suke hararo rayuwar kudi da Jin dadi Basu dauka haka abin yake ba a zahiri.

Tamkar mace haka yaji idanuwansa sun ciko da wani irin Hawaye masu tsananin zafi da radadin rashin su kasim a duniya daidai lokacinda ya kamata su ji dadi,
Bai taba sanin samuwar arzikinsu zai tafi da jini da rayuwar Yan uwansu Rabin jikinsu ba da tini ya Dena rokarwa kansa arzikin.

Su kasim sun bar duniya basa tareda shi hakama su mamman dasuke raye a yanzu basa tareda juna,tayaya zai fara rayuwa Babu su,Suma su mamman din tayaya zasuyi rayuwa Babu shi din.

Share hawayensa yayi yana daga hannuwansa yayiwa iyayensu dasu kasim adduar dacewa da Rahama Suma su mamman yayi musu adduar Allah ya Basu abinda sukai burin samu acan Ashalawa din kafin su baro.

Miqewa yayi daidai shigowar Ahmed Wanda kaman shine Mr Jaden ya bawa Ragamar kulawa da Omar yanda ya kamata tinda sune suke Addini Daya da juna.

Kallansa Ahmed keyi Yana Dan sake fuska cikin kulawa ya sanar dashi ya taso yaci abinci sbd lokacin Shan maganinsa yayi.
Ba musu Omar din ya taso sbd su Ahmed din sun girmesa sosai Dan alama Dan zasuyi shekaru talatin su zuwa sama shikuwa a lokacin ne suke shekarunsu na ashirin zuwa da Daya.

Abincin kudi Kai tsaye zai kira abinda yake kalla a gabansa da sunan abincin, Brown basmati rice ce da aka dafa da abubuwan da bama zai iya gane me dame bane a ciki Se brown chicken breast a jere cikin wata glass bowl daban.

Ahmed ne ya basa kwari gwiwan fara cin abincin Wanda Yana fara Kai spoon

na farko bakinsa idanuwansa suka ciko da Hawaye zuciyarsa na karyewa da tino Yan uwansa su mamman ko sun samu sunci abincin Daren kuwa kokuwa ma kila suna can cikin azabar duhu da zafin ramin gurin Gina.

Ahmed Dake kallansa Yana tinanin Allah me bawa Wanda yaso,
Gasunan dai sunata Fadi tashin nema Amma ga yaro qanqani kaman Omar Allah ya basa Arzikinda zasu lalace a karkashinsa gurin bauta masa kaman bayi.

Harya ci abincin ya gama Hawaye ne ke tsiyaya daga idanuwansa da sukai jajir Babu farin ciki ko kadan a ransa Dan kuwa rayuwar da zai fuskanta Babu seelahs ko Daya a cikinta bazai taba farin ciki ba duk Jin dadin dazai samu acikinta.

Bayan gamawarsa Ahmed da kansa ya kwashe kayan ya fice dasu tareda dawowa sukai sallahn ishai a tare dakin tukuna ya fito ya sauko ya barosa ya sake samun hutawa kaman yanda Mr Jaden yace abarsa ya huta sosai ya dawo daidai tukuna.

Zaune yake shiru har kusan dare sosai kafin ya kwanta bacci ya daukesa Bai farka ba sai asuba.

Bayan sallan asuba da baisan time ba yasan dai lokaci yayi
Yana idarwa sake kwantawa yayi sbd maganinsa akwai masu Saka bacci sosai Dan Mr Jaden ya sanarwa Dr Omar din kaf rayuwarsa Baya samun baccin Daya kamata musamman a wannan lokacin shiyasa aka rubuta hadda maganin bacci.

Washe gari ma haka ya sake wuni daga cin abinci sai sallah Se bacci,
Daga Ahmed Se Aron ne kadai suke Dan shigowa Dan su Dan debe masa kewa Amma Sam Babu walwala ko farin ciki a tattareda shi.

Mr Jaden baya zama kwata kwata sbd komawa da zaiyi qasarsa Poland Kuma duk yanda yaso tafiya da Omar abin bazai yiyuba a yanzu Dan haka dole zai barsa yaje ya dawo kafin can anyiwa Omar din komai da komai na id cards da sauransu.

Kafin tafiyar Mr Jaden cikin kwana biyu yayi kokarin ganin Omar yafara sakewa sosai Dan yanason inganta rayuwarsa fiyeda yanda ake tinani,
Yanason mayarda rayuwar Omar abar alfahari ga Yan uwansa Da Kuma duk Wanda zaiyi muamala dashi,
Yanason Omar ya samu ingantacciyar rayuwar da har abada bazai taba tinani ko shaawan komawa Ashalawa Koda kuwa ziyara ne bare Dan wani abin daban Dan haka Babu Bata lokaci ya nema lawyernsa na Nan Nigeria me

zaman kansa qwararre Akai rubuce rubuce akan zallan tsananin dukiyar Omar wadda kusan yawanta takusa ta dukiyar Mr Jaden din Dan haka a rubuce Mr Jaden da Omar abokanan kasuwanci ne da dukiyarsu ta Hadu tareda adadin ta kowa.

Omar ya amince da Mr Jaden dari Nisa dari sbd kasim ya yarda dashi sosai da sosai kafin ya rasu Dan haka Shima ya miqa dukkanin yardarsa ga Mr Jaden batareda Jin komaiba aka basa takardu duka ya Saka thumbprint nasa aka sealing.

Kafin tafiyar Mr Jaden duk wata sutura tin daga kan underwears da singlet da qananun kaya da manya har turaruka da mayukan da Omar zaiyi amfani dasu da takarman da zai Saka da duk wani abin buqata na rayuwa Saida aka siyosu tsadaddu masu kyau da tsari aka zuba a dakinsa Wanda yake sama babba da toilet dinsa.

Abu na farko daya bari shine zasu fara da basa ilimin Daya kamata Dan haka babban Dan amanansa Ahmed da Aron sune yabarwa komai a hannunsa Dan haka bayan tafiyarsa Id cards aka fara yi masa da passport da banki da komai sai da Akai masa kafin aka tanada malamai biyu masu kyau aka daukar masa Dan karatun da aka fara Babu kama hannun yaro.

Tin tinanin Yan uwansa na dauke masa hankali Yana rabuwa gida biyu har su Ahmed suka Bude masa wuta sosai akan karatun Wanda yakejin kaman bazai iya ba sbd Bai fara ba tin Yana kankani harya zo yafara Maida hankali sosai da sosai Baji ba Gani Dan kuwa Aron Sam Baya masa da sauki akan karatun Dan Mr Jaden ya Basu tabbacin akan karatun karsu masa da sauki ko kadan sosai yake buqatan Omar ya San kansa ya tsayu da kansa.

A bangaren Addininsa ma sosai Ahmed ke taimaka masa Dan haka ya sake zaucewa akan karatun ba wasa ko kadan.

Ahankali ahankali ya fara Bude kansa sosai komai na shiya yanda ya kamata Dan kuwa tamkar hannun sojojin koyan aikin soja aka miqasa a hannunsu Aron Babu wasa ko kadan akan lamarin nasa.

Babu ranar da Baya kewansu mamman da lameenu dasu yake kwana yake tashi a ransa sedai Babu yanda zaiyi tinda baimasan ta yanda zai ji daga garesu ba bare ganinsu dole sai ranarda Mr Jaden ya dawo shine kadai yasan Wanda zai kira a ashalawa a hadasa dasu a waya suji junansu hakama shi kadai ne Wanda yasan yanda zaiyi yakaisa ashalawa din idanma ganinsu yakeson yi gashi Mr Jaden kullum sukai waya basa tabbacin bazai dawo daukansa ba sai yafara fahimtar karatu ya iya turanci Dan haka ya sake Maida hankali sosai akan karatun.

Bayan kusan watanni masu Dan yawa rayuwarsa ta sauya cikin kankanin lokacinda baiyi tsammani ba shi kansa,
Ya sauya sosai ya samu Kwanciyar hankali da nutsuwar rayuwa duk da akwai kadaici a tattareda shi sbd daga shi sai su Aron da masu aikin gidan ne suke rayuwa,
Baya muamala da mutane sbd koyaushe Yana gida sai Kuma idan sun fita yawon Shan iska ko siyayya ko kallan ball da sauransu Wanda sosai ake kokarin yin duk abinda zai sakashi Jin walwala ko makamanciyarta.
#MAMUH#
#AMEENATOU
#DEEP
#JAMAAL JEEY SEELAH
#BLACKMONEY
#LOVE
#CRAZY
#LAHOT

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee
#ZafafaBiyar

6
*_ASHNA BEAUTY SKINCARE_*
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

****
Babban abinda yafara sauyawa sosai a rayuwar Omar shine harshen yare,
Daga Aron har Ahmed dayake musulmi basa Jin Hausa Daman tin farko da dubaru suke magana dashi Dan haka da karfi da yaji yaren turanci ya fara kama bakinsa Dan kuwa ko Ahmed dayakewa kallan nasa ba bahaushe bane yaren igala ne da aka haifesa a Lagos ya tashi a Lagos Dan haka tini Omar ya sake ya fada yaren turanci Shima Yana cabawa.

Sabo da shakuwa dole ya shiga tsakaninsu duk da Yana girmamasu a matsayin wainda suka girmesa su Kuma suna kulawa dashi kaman jininsu Dan kuwa Babu abinda bazasu iyawa Mr Jaden ba ko Yana kasar ko bayanan Dan shine gata da rufin asirinsu da iyalansu.
Mutum ne shi Daya inganta rayuwarsu sosai yanada alheri baida rowa Sam shiyasa suka zama Yan amanansa Dan ya dade a Nigeria shekaru sosai anan yake huldodinsa da yawansu.

******Lokaci yaja Omar tini ya kwana biyu da shiga makarantar da ake kira yaqi da jahilci wadda kusan acan kansa ya qarasa budewa yanzu ba laifi Yana iya abubuwa wa kansa da da sama wainda su Ahmed suka koyar dashi da Kuma iliminsa Daya fara basa,

Shine yake zuwa da kansa yaje ya dawo da mota batareda ankaisa ba hakama Kuma Yana zuwa banki ya cire kudi da kansa batareda wani ya raka sa ba hakama siyayyar abubuwan buqatansa,

A rayuwarsa yanzu abu biyune ya rasa masu damun zuciyarsa kowanne dare shine rashinsu mamman da lameenu a tareda shi sai Kuma rashin Mr Jaden da kusan zuwansa biyu Yana komawa batareda shi ba Amma yanzu Kam da komai nasa na tafiya ya kammala haka yayi bankwana dasu Aron ya tafi yanajin kaman ya rabu da Dan uwansa na jini
Amma Ahmed dashi suka tafi sbd shi har lokacin baiyi aure ba Bai da iyali sabanin Aron yanada family Dan haka shi aka barsa da kulawa da gidan suka koma Poland kwata kwata.

Da farko yaso ganawa dasu mamman kafin tafiyarsu Amma ba lokaci Dan haka dole Mr Jaden yayi masa alkawarin zaa kawo su Suma Nan Lagos su samu Dan ilimin shigowa mutane kafin akawosu Poland inda yake su hade suyi karatu kamansa.

Wannan alkawarin ne ya kwantawar da Omar hankali Wanda har sai dayayi magana dasu mamman da waya daga can Ashalawa suka basa tabbacin suna Nan tafe Suma sun shirya tsaf.

Farin ciki da nutsuwan zuciyar Daya samu da Jin Hakan ya Sanyashi kwantar da hankalinsa daga Dan tsoron Daya shiga na samun kansa a wata qasar wata duniyar da baisan da ita ba Dan haka gaba Daya yanzu ya kwantar da hankalinsa ya Maida akan karatunsa dayake Dan cimma buri ya samu dawowa yaje dubo mahaifiyar Kasimunsa da mahaifiyar jamilu.

A bangarensu mamman kuwa wata sabuwar duniyar rayuwar Baji ba Gani suka Bude a Ashalawa Dan kuwa gasu da kananun shekaru Amma Kuma suna cikin yan lamba Daya na rashin imanin Ashalawa da bushewan zuciya.
Duk abinda suke son samu sunata samunsa da nasu da Wanda na karfin hali ne duk sun hada sun mallaka Dan haka suka Tara wata irin danyar dukiya da Suma basusan ya zasu sarrafata ba,
Jini da rayukan da suka tafi Dan Saka hannunsu sunada Dan yawa a ashalawa Dan haka sunansu ya sake habbaka duk da Babu sauran Amma sunan seelahs Kam a Ashalawa yasake samun daguwa.

Basuda niyar barin Ashalawa sbd so suke ahankali ahankali sai sunkai sune manyan Ashalawa da zasu kwantar da Wanda sukeson kwantarwa su take su kashe.,suna son sukai sune manyan da acikin Ashalawa ko digon zinari bazata fita ba batareda izininsu ba da Kuma kasonsu.

Zuciyar mamman da lameenu ta rikide daga seelahs ta koma wata abar daban da babu Wanda ke iya gane Menene a cikinta ba sai su kadai da yanzu sunfi kowa sanin zuciyoyin junansu.

Dukiyar hannun Omar Bata taba fita daga zuciyarsu ba Kona sekan Daya Dan kuwa itace har yanzu a qasan zuciyoyinsu da basajin har abada idan ba mallakarta sukai ba zasu ji abinda yake kirjinsu ya fada.

Duk wani mataki da sukeson takawa a rayuwarsu Dan mallakar dukiyar ne wadda duk yanda suke daukan Rai baa bakin komaiba yanzu suna mallakar zinariya haryanxu Basu samu abinda yayi Koda Rabin na Omar din bane Dan haka suke sake nutso a duhun zuciya.

A ranar da sukai waya da Omar ya sanar dasu kyakkyawar rayuwar dayake gudanarwa tareda nutsuwa da tarin wadata Jin sukai gabaki Daya hankalinsu ya tashi daga Ashalawa ya koma akan samarwa kansu ilimin da zai Basu ikon mallakar abubuwa da dama daga Omar din Dan haka take suka amince da tahowa inda yake din.

Abinda Basu sani ba shine Omar yariga yabar qasar Mr Jaden ya tafi dashi Poland Dan haka bayan isowarsu sunji ciwon Hakan sosai Amma dai sunsan koman Daren dadewa zasu hade dashi Kuma abinda suke son kota halin yayane sai sun mallaka Koda abubuwa da dama zasu faru.

Aron ne mutum na farko daya fara banbance halinsu Dana Omar Dan kuwa su Babu sauki ko kadan a kulawa dasu kamanshi,
Tinda suka zo yaketa iya kokarin kulawa dasu da karatunsu sedai kwata kwata Babu sauki.

Saida suka shafe watanni suna cin banza a mansion din akai musu komai kaman yanda akaiwa Omar tin daga Id cards da passport da acct suka fara wayewa da harkar kafin Mr Jaden ya hadasu da abokan huldansa da lauyoyi na daban suka fidda dukiyarsu me yawan gaske ta danyar zinariyar Akai huldarta anan ne suka Hadu da Mr Owolowo bayaraben da shima ya goge a harkar danyar zinari ta gurbatacciyar hanya Dan haka tini ya janyesu daga Mr Jaden suka koma gurinsa acan suka fara gogewa da karatu da harkar zinari ta hanyar ilimi da wayewa tini suka bar qasar suka gaba Daya suka bisa Angola acan suka fara karatunsu sosai Kuma suna kasuwancin zinarin sosai tareda wasu huldodin na kasuwancin Daya kamata sabaninsa.

Ahankali ahankali Suma dukiyarsu tafara habbaka kaman yanda iliminsu da wayewarsu ke habbaka tareda sunayensu.

Kaman yanda rayuwa ke tafiyar musu daidai haka rayuwa ke tafiyarwa Omar daidai Wanda nasa ilimin yafi nasu zurfi sosai hakama gaba Daya shi tasa rayuwar tamkar Dan gata yake gudanar da ita Dan kuwa Mr Jaden ya zama tamkar uban Daya haifesa sbd tini ya qara masa da sunansa akan nasa Dan ya zama asalin Dan qasar Kuma kaman yanda da yawa basu San Mr Jaden ya taba haihuwa ba sai suke dauka Omar din dansa ne Daya Haifa a Nigeria sbd zaman da yayi acan sosai.

Matar Mr Jaden da farko ta qyamaci Omar Amma da shekaru suka fara ja ya goge ya koma tamkar baturen Shima hakama nutsuwa da tsananin son dayake wa mr Jaden kamar asalin Dad dinsa ya Sakata itama amincewa dashi a matsayin 'da.

Dukiyarsu Babu Haram Babu cuta ba cutatarwa kasuwanci akeyi da ita sosai tini ta qara haukacewa da habbaka ta bangare Daya Omar ya fara tsayuwa sosai a business ga bangare Daya ya musuluntar da iyayen nasa Mr and mrs Jaden Dan haka suka sake samun nutsatsiyar rayuwa.

****Bangaren su mamman rayuwa tayi musu yanda suke so Tako ina daukaka suke sake samu da qananun shekarunsu Dan haka suna cikin matasan Dake tashen arziki me yawa,

An wayi gari abokin huldansu Mr Owolowo ya mutu sanadiyar bugawar zuciya ake tinani sbd jinin da aka samu ta hancinsa Yana fita da kunnuwansa Amma dai baa tsaya wani dogon bincike ba aka rufesa aka bar maganar daga Nan suka tattara suka bar Angola suka dawo Nigeria suka Gina kansu Amma dai basa wani zama suna gurin Omar Wanda gabaki Daya idanuwansu da zuciyoyinsu sake shiga tashin hankali sukeyi idan suka ga rayuwar dayake ciki da irin mugun tashin da arzikinsa keyi.

Shekarar da Omar yayi graduating daga karatunsa tareda su Akai biki na burgewa da Mr Jaden ya hada masa Wanda ya Tara manyan abokan huldansu da families nasu.

Su kansu su Omar din cikin farin ciki suke sosai sbd burinsa ya cika ayau ya samu kansa cikin ilimi me yalwa da Kwanciyar hankali tareda wayewa tamkar bashine me yawon kauyuka da daji ba.

Su kansu mamman sauyinsu a bayyane yake Dan ma sunfisa budewan ido sbd sunfisa yawon qasashe yanzu tinda kusan su dasu ake yawon duk business dinsu musamman yanzu da Babu Mr Owolowo sune akan dukiyarsu da tasa da suke cinye fiyeda Rabi.

A gurin dinner din mamman ya kalla idanuwansa akan baturiyar qasar data dauki hankalinsa Badan komaiba sai Dan sanin mahaifinta akan sunan dayayi akan harkar zinarin kasar Amma ya tsufa sosai yanzu hakama ko gida baa fitowa dashi mahaifiyarta ce Akai itama mahaifiyar tata ta tsufa.

Da farko lamari ne da bazai taba yiyuwa garesa ya samu baturiyar Amma Kuma duba da Shima kudin ne dashi sosai ba laifi hakama yanada iliminsa da wayewarsa tareda kayansa Dake Jan raayin mata da yawa sosai akansa yasa Hakan zata iya yiyuwa.

Babban abinda yabawa kowa mamakin bayan kwana biyu da dinner din shine soyayyar mamman da Aleena wadda Mr Jaden da mahaifiyar Aleena din da Omar sukai alkawarin hadasu aure Amma Omar na ganin yanda mamman ya mutu akanta take ya Hana Mr Jaden sake tada maganar aurensa da Aleena sbd yayiwa Dan uwansa mamman farin cikin samun mace kaman Aleena duk da ba musulma bace Amma zuciyarta nada kyau musuluntar da ita bayan auren abune mara wuya.

Lameenu dayafi kowa sanin zuciyar mamman Baiyi mamakin farin ciki da tsananin son da mamman din kewa Aleena ba da yanda ya ringa sakin dukiyarsa kaman baisan zafinta ba wadda bawai damuwa Aleena tayi da dukiyar ba sbd shi takeso Kuma duk abinda mamman yakedashi tanada abinda yafisa fiyeda a kirga.
#MAMUH#
#JAMAAL JEEY SEELAH
#AMEENATOU
#DEEP
#ROM
#TOOHOT

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee*_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee
#ZafafaBiyar

7
*_ASHNA BEAUTY SKINCARE_*
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

****
Iyayen Aleena sunada wani irin qyanqyami da kabilanci ga Wanda basu sani ba Sam duk da suna kallan su mamman din a matsayin family na Mr Jaden sedai Sam Sam Basu aminta da mamman ba duk da Shima fari ne sosai kaman Omar Kuma kyakkyawa daya kusa ma yafi Omar din kyau amma dai

hankalinsu yafi Kwanciya dari bisa dari akan Omar dasuke ganin kaman a taredasu ya taso duk da basusan yarinyartasa ba Amma ai a tinaninsu a hannun Mr Jaden ya taso Kuma dansa ne Daya haifa acan.

Aleena a zuciyarta mam kaman yanda yanzu ake kiransa ya kwanta mata dari bisa dari sbd yakai duk mataki da tsarin datakeson namiji yakai mata,
Yanada kyau sosai da wayewan da baya shakka ko tsoron kowa,
Hakama yanada class Wanda taku ne Daya iya abinsa tinda ya samu kansa sabuwar duniyar datafi wadda suka fito,.yanada ilimi da dukiyar kansa da bazai taba damuwa da tata dukiyar ba hakama ya Bata tabbacin shine zai tattaro ya dawo qasar da zama bazai taba daukanta zuwa koina ba Dan haka taji Hakan ya mata.

Omar Bai taba tinanin akwai Kokuma wata manufa zata shigo cikin maganar auren mamman da Aleena ba dan haka yafi kowa farin ciki
Su kansa su mum dinsa sunyi farin ciki daga baya Daya nuna musu Yanason su nuna farin cikinsu da Hakan.

Ansha fitina da damuwa sosai akan iyayen Aleena su amince Amma suka qi musamman mahaifinta Sam Sam Bai amince ba.

Har Aleena ta cire Rai sai kwatsam Dad din nata aka wayi gari ya mutu a dakinsa kwance Yana Yana bacci.

Sun shiga tashin hankali sosai sbd Aleena na tsananin son Dad dinta fiyeda mum din shiyasa ma ta hakura da maganar auren mamman bawai Dan shekarunta basu Kai tayi abinda ranta yakeso ba sai dan Dad din kawai.

Jadens family sun shiga tashin hankali da firgicin mutuwar Mr Harris sbd kusancinsu da zamtowansu family friends tin tsawon lokaci me tsayin gaske.

Omar dasu mamman sun shiga damuwa sosai sosai Dan haka Omar ma yaji Yana sake son auren Aleena da mamman Dan ta samu musulunta ita da mum dinta kafin Suma su rasa wannan damar kaman Mr Harris.

Shi kansa mamman yasan yanzu Kam Babu wata shamaki da zata shiga tsakaninsa da auren Aleena musamman yanzu da nauyin komai na kamfanin Dad dinta da uban dukiyarsa zasu dawo kanta.

Mutuwar Mr Harris ya taba Aleena da mum dinta sosai musamman mum din da Bata sake lafiya ba
Ba Bata lokaci Aleena ta sake amincewa mamman sbd tsananin kulawansa da tattalin dayake nuna musu ita da mum dinta.

Sunyi register na aurensu da komai hakama auren musilunci suka fara yi wedding dinner Daya sukai bayan daurin auren da kwana Daya anan
Duniya ta sake sheda auren nasu Wanda da yawa manyan mutane da respected families Dake tareda su kusa da nesa duk sun samu halartowa.

Babban sa'ar da mamman yasake tsintar rayuwarsa a ciki shine gabatar dashi da Mum din Aleena tayi ga abokanan huldansu na business da sauransu,
Da yawa ta gabatar dashi take ya nutsu ya fara samarwa kansa matsayin da suna a cikin manya ta hanyar nuna nutsuwa da tinani tareda sanin ya kamata harma da bayyanarda tsananin kauna da son dayakewa Aleena da mahaifiyarta da yanzu shine zai tsaya musu.

Da yawan mutane sun yaba dashi Dan take take aka ringa recognizing nasa shida lameenu Wanda yake gabatarwa a matsayin Dan uwansa Kuma abokin tasa huldar.

Omar Baya buqatan gabatancin kowa sbd shi din sananne ne a cikinsu tini Kuma duk yanda suka yaba dasu mamman Omar ne a ransu da idanuwansu fiyedasu.

***Bayan auren mamman da Aleena ya nutsu ya duba ya karanta da kyau yaga duk inda yake tinanin dukiyar Aleena abin ya wuce Nan Dan haka ya sake iya takunsa Dan kuwa son dayake nuna mata tini ya qarasa gamawa da ita da mum dinta take suka Dorasu akan dukiyarsu sbd ita Aleena batada time sbd karatunta na likitanci da saura kadan ta kammala.

Lameenu ya koma Nigeria sbd gudanar musu da ayyukansu na can Kuma Shima Yana komawa Babu Bata lokaci yayi aure Wanda daga mamman har Omar sun halarta angama sun dawo.

Bayan dawowarsu ba jimawa Aleena ta fara aiki a Special Care hospital din data Gina me tsarin Daya dauki kudi masu yawan gaske da hankalin mutane tareda zuba qwararrin doctors da qwararrin nurses da ma'aikata.

Fara aikinta yayi daidai da bayyanar ciki a tareda ita Wanda ya Saka mahaifiyarta da ita murna sosai kamar me
Sedai duk murnarsu basukai ko Rabin ta mamman ba da Daman haihuwar yake Jira dukiya ta tabbata tasa Dan kuwa abinda zata Haifa shine zai gaje dukiyar to Kuma ai shine uban abinda zai Haifa din.

Omar yabar Poland Yana UK gurin qaro ilimi akan harkar business sosai Wanda Shima acan ya Hadu da tasa matar yar asalin kasar Jamaica tin Yana

can suka Kai karshe sedai shikam a Jamaica din sukaje Akai aurensu Kuma kowa ya samu halarta hadda Aleena da mum dinta duk da auren musulmai ne sun halarta.

Bayan auren daga Omar din har Nur dinsa a UK suke sbd itama karatun takeyi Amma ita yanzu ne ma ta fara a matakin farko take.

Lameenu na Nigeria,
Mamman na Poland
Omar na UK,
Haka kowannensu yake gudanar da rayuwarsa bisa tsari da yanda yake Sonta Dan kuwa kowa takai masa iya iyakar yanda yakeson.

Haihuwar Aleena ce ta sake hadasu guri Daya sbd farin ciki Mai tsananin gasken da suka samu rayuwarsu a ciki da karuwar seelahs,

Duk wani Wanda yake Hulda ko yasan seelahs Saida ya sheda farin ciki me tsananin gaske da sukeyi da samun haihuwar farko a cikinsu Kuma Allah a Karan farko Saiya albarkace su da samun 'yan biyu duka Maza.

Mam Bai taba dauka ma zaiji irin farin ciki da tsananin kaunar yayan fiyeda komaiba Saida aka haifosu ya rungumesu jajaye dasu kaman wasu taurari.

Mum din Aleena har hawayen farin ciki ta ringa yi tsabar murna kusan tata dukiyar mallaka musu ita tayi a matsayin will dinta idan ta mutu a Basu 60% na dukiyarta sauran 30 a bawa Aleena din.

Wannan will din ba qaramin dadi yayiwa mam ba Dan haka soyayyar 'yayansa ta ninku a ransa Dan kuwa ya tabbatarda sune mukullin arzikinsa mara adadin dabai samu riqewaba sai yanzu,
Sune sa'arsa Daya Dade Yana jira ta shiga hannunsa,
A yanzu Daya samesu yasan dukiyar Aleena tasa ce itama tinda ta mahaifiyarta ta zama tasa burinsa Daya ne ya rage a rayuwarsa shine mallakar dukiyar Omar wadda duk abinda zai mallaka idan ba ita suka mallaka ba bayajin zai iya numfashi me dadi.
#MAMUH#
#AMEENATOU
#LIFE
#ROM
#JJS
#THE SEELAHS

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!
#ZafafaBiyar

8
ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

****

Bayan haihuwar Aleena Omar yasake yiwa mam magana sosai akan musuluntarta Amma Sam mam Baya wani takurawa ko damuwa da maganar sbd ganin yakeyi duk lokacinda taso zata iya musuluntar tinda dai shi yasan yayansa musulmai zasu tashi a hannunsa.

MUHAMMAD HAROON HASSAN SEELAH da MUHAMMAD JAMAAL HUSAIN SEELAH shine sunan da 'yayan sukaci Wanda daga Aleena har mum dinta Babu Wanda ya musawa sunan kawai dai suna kiransu da Haroon and Jamaal wani lokacin Kuma little seelahs.

Jamaal da Haroon identical twins ne da ko farcensu baka iya banbancewa bare wani abu nasu,
Kamanninsu sunyi mummunan yawan da dole ake banbance musu kalan tufafin sakawansu Dan gane waye Jamaal waye Haroon.
sun taso cikin tsananin kulawa da gata tareda asalin rayuwar da ake kira luxurious life,
Sun taso a cikakkun halfcase Dan kuwa kana kallansu zakasan baturiya da baqar fata ne suka Hadu suka haifesu sedai Allah yayi musu arzikin tserewa dauko gashi irin na mahaifiyarsu hakama hasken Basu wani dauko nata ba na Dad dinsu ne sedai sun fisa haske sosai duk da mam seelah ya Dade da komawa tamkar baturen a harkar rayuwarsa gabaki Daya.

Omar ya dawo Poland inda yake riqe da komai yanxu na nasu dukiyar da kamfanin sbd Dad dinsa ya huta Dan haka yanzu kwata kwata Mr Jaden ya aje aiki sbd manyanci hutawa kawai yakeyi a gida shida mum din Omar ne akan komai Kuma kaman yanda kowa yasani yake Gani Omar Jaden seelah ya wuce ajin su mam ta bangaren ratsawan ilimi da qwarewa a aiki ga class din ma ba Daya ba.

Sun tashi daga inda suke sbd dawowansa kwata kwata da matarsa Dan haka sun koma wani Sabon mansion din daban da suke rayuwa a ciki shida iyayen nasa da matarsa wadda har lokacin Allah Bai Basu haihuwa ba.

Jamaal suna cika 17 years a duniya kakarsu Dake tsananin sonsu fiyeda komai da kowa ta rasu bayan ta musulunta a hannun jamaal wanda shine yafi kusanci da ita sosai fiyeda kowa a gidan nasu Kuma itace tafi ganesu fiyeda kowa a family duk da halayensu sosai suketa banbanta Dana juna tin suna fara tasowa,
Raayoyinsu suna Dan banbanta Amma dai halayensu shine abinda Kai tsaye ya banbance Jamaal daban Haroon daban.

Rasuwar Granny ya Saka Dr Aleena shida damuwa sosai harta koma koyaushe tana gida sbd a bayan Sam batada time na gidanta da 'yayanta mum dince ke kulawa dasu tana nuna musu kauna kaman ta hadiyesu.

Rasuwarta duk wani hali na mam ya fara fitowa Wanda yafara bawa Dr Aleena mamaki me tsananin gaske Dan kuwa Kai tsaye ya nuna mata Nigeria zasu tattara su koma gabaki dayansu.

Da farko ta dauka ba da gaske yake ba Amma daga baya ya rufe idonsa da Babu Imani ko Daya a ciki ya Bata zabi ko ta bisu ko ya dauke yayansa ya tafi dasu yabarta.

Bata taba Shiga tsoro da tashin hankali ba rayuwarta irin wannan sai a wannan lokacin.

Omar tafara nema ta sanar masa komai yayiwa mam din magana Amma Sam mam Bai yadda ba daga karshe ma rashin fahimtar akansu yaso qarewa Dan haka ya fita a zancen.

Su jamaal Basu San meyake faruwa ba sbd karatu sukeyi sosai basa wani zama gida musamman jamaal da shine yake karatun medicine kaman mum dinsu Haroon ma yaso medicine din Amma Yana Shan wuyar karatu ba kaman Jamaal ba sai mum dinsa ta sakashi karantar law.

Duk yanda Dr Aleena taso riqe yayanta abin gagara Yayi gashi batason tayi kararsa sbd tana tsananin son mijinta Dan haka ta Yanke shawarar binsa Amma ba zaman can dindin ba zata dawo Poland tanayi tana Dan Kai masa ziyara itada yayanta.

Da zasu koma kwata kwata Nigeria din dukiyar su Jamaal ta Dade da shiga hannunsa Dan haka tata dinma da yawanta sun kwashe sun taho da ita kusan 70% sun baro 30% a Poland din.

A Lagos suka Bude sabon Babin rayuwar masu hannu da Mai a makeken mansion gidansa Dake manne Dana lameenu hakama na Omar na manne da nasa Shikuma sbd tin suna can suka Aiko da kudaden da aka zube masu tarin yawa aka Gina musu shi a anguwar security dinta kadai zai baka nutsuwa da Kwanciyar hankalin da duke me kudi yake buqata.

Matar lameenu ta haihu yayanta har so biyu duk mata ta Haifa Fadeela seelah da Aysha seelah.

Daga anguwar har cikin mansion din da suke rayuwa a cikinsa Babu abinda ya banbanta Dana rayuwar luxury da suka baro a Poland Dan haka su Jamaal Basu wani samu damuwa ba hakama mum dinsu ba laifi taji she's ok sedai hidimominta na can data baro tanajin damuwarsu musamman asibitinta Data karbu tana cikin manyan asibitocin Poland din.

Anan din ma lafiyayyar tsadaddiyar asibiti Alh mam seelah ya budewa Dr Aleena me tsadan gaske aka zuba doctors da kwararrin ma'aikata tafara aiki ahankali ahankali harta fara sabawa tafara sakewa.

Su Jamaal kuwa Basu wani jimaba suka koma Poland makaranta Amma Basu wani jima ba Haroon yafara shiga damuwa da hadda su ciwo sbd baitaba rayuwa Babu iyayensu ba
Kai tsaye Dad dinsu ya dawo dashi Nigeria karatun sbd Daman yafisonsu a kusa dashi.

Jamaal tin farko shine Wanda yafi Jin mahaifiyarsu a ransa fiyeda Dad dinsu sbd tausayin datake basa sosai kan rashin hutun datake samu ga tinda granny dinsu ta rasu mum din ta sake shiga damuwa gashi Dad yakaita Nigeria bataso sbd Bata sababa Dan haka koyaushe mum dinsa itace a gaba cikin ransa kafin dad.

Tinda Haroon ya dawo Nigeria hankalinsa ya kwanta sbd Yana tareda iyayensa,.ita Kuma mum dinsu bataso Hakan ba ko kadan Dan haka ta sake shiga damuwa sosai sosai Dan har gobe batada shiri ko niyar zaman tabbata a Nigeria musamman data fara fahimtar dukiyar Alh Mam din sake babbaka takeyi sosai fiyeda tinani sbd mummunan business din dasuke gudanarwa a bayan fagen business din gasken da akasan sunayi Dan kuwa suna cikin wainda sunansu yafara yaduwa Yana karadewa sbd kudinsu Dake magana.

A nata tsarin data yankewa kanta dukiyar ma bar masa zatayi gaba Daya ta tattara ta komawarta kasarta ta riqe 'danta Daya tinda shi Haroon sosai yanzu yaketa samun shaquwa da Dad dinsa fiyeda Jamaal Wanda shikuma acan wata irin kauna Mai karfi da shaquwa ce take shiga tsakaninsa da Dad Omar Wanda haryanxu Bai samu haihuwa ba.

***Shekaru sun Dan Kara ja Dan kusan Haroon Dake Nigeria karatunsa yafara Nisa Wanda Dad dinsa ke tsananin alfahari dashi Dan kuwa kusan a matakin dayake Kai yafara sanin huldodin Dad dinsa da Dad lameenu Wanda duk da basa Ashalawa a yanzu Amma suna cikin masu fada a cikinta Dan kuwa Babu huldar da zaa kulla a gama a Ashalawa batareda saninsu ba ko kasonsu,
A matsayi da matakin da suka Kai jini da rayukan da suka kawosu matsayin bazasu kirgu ba Dan haka Allah yake sake musu talalan yanda sukeso suke samu Dan a jere da layin masu kudin gaske idan zaa ambata Seelahs na Daya daga Yan farko farko.

Sunada money and power fiyeda yanda ake zato,
Sunada tarin girma da mutunci a idanuwan mutane sbd suna cikin masu

bugun gaba su Bada tallafi da taimako duk lokacinda zaa buqaci Hakan sbd son sake samun matsayi da mutunci a idanuwan mutane talakawa da manyan mutane.

Duk tarin daruruwan arzikin da Allah yayi musu haryanxu Omar ne a gabansu Dan kuwa takowanne bangaren haryanxu shine a gaba kafin su,
Baya Nigeria Amma yanada tarin dukiya da kadarori da suna a Nigeria musamman haryanxu dayake tareda Aron da Ahmed Yan amanar da suka zama tamkar wasu Yan uwansa na jinin musamman Shima nasa dangin suka koma sirkin Muslims da ahlulkitabi Dan zuriar mr Jaden gaba dayansu sun Dade da amsarsa a matsayin nasu kaman yanda Shima Jamaal nasu familyn yake a sirke.
#MAMUH#
#JAMAAL JEEY SEELAH
#DEEP
#HAROON SEELAH
#LOVE
#CRAZINESS
#ZAFIN KAI
#AMEENATOU

ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee
#ZafafaBiyar

9
ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

****
Kwatsam labarin rasuwar Mum din Dad Omar ta riski familyn seelahs Dake Nigeria dole suka tattara suka tafi gaisuwa da Alh Lameenu seelah da matarsa harma da yayansa sai Alh Mam da Dr Aleena wadda batada niyar dawowa matiqar ta tafin.

Haroon seelah Bai samu Daman binsu ba sbd tarin karatun Dake gabansa,
Duk yanda mum dinsu taso ya aje karatun ya bisu su tafi tare ya qarasa acan Sam Bai aminta da Hakan ba Dan a rayuwarsa Babu wanda yakeson burgewa

da son sakawa farin ciki irin mahaifinsa hakam shi kansa Dad Yana son dansa ya riqa sosai ya qware a harkar sharia Dan tsayawa ga duk abinda ya shafi ahalinsu.

Dr Aleena tin kafin ta tafi Kai tsaye ta sanar da Mam idan ta tafi bazata dawo ba Kai tsaye Shima ya Bata zabin idan ta tafi zai rabu da ita
Ba musu ta aminta da Hakan tinda tasan 'danta Daya Yana acan tareda ita Dan haka ta amince a ranar da zasu tafi ya saketa suna Isa can kasar ma suka shigar da divorce dinsu take Akai komai aka gama batareda yayansu sun sani ba hakama Kai tsaye Bata buqaci komai na sakin da ake bayarwa ba a kasarsu ta yafe masa
Dukiyarta datake hannunsa tabar masa akan ya kulawa yayanta sbd bataga alaman zai Bata ba Dan kwata kwata Babu sunanta akan komai na dukiyar duka ya cire ya mallake.

Jamaal ne kadai yasan iyayen nasa sun rabu Haroon Bai saniba Dan haka Jamaal sosai yaji tausayin mahaifiyarsa yaci gaba da Bata kulawa Dan tashiga damuwa sosai batada kowa sai shi din a yanzu sai Omar Daya zama tamkar yayanta.

Har sukai kwanakinsu suka gama suka tafi Dad din Baya wani samun Daman ganin Jamaal sbd Jamaal din dayaji Baya buqatan ganinsa sbd abinda yayiwa mum din,
Shi Dan Kai tsaye ne zai iya Jin tsanar Dad din Dan haka ya zabi nesanta kansa dashi a Dan lokacin kafin ya sauko.

Bayan rasuwar mamma kaman yanda Omar ke Kiran Mrs Jaden sosai yake kulawa da Dad dinsa shida matarsa Nur sbd tsufa da manyanci Daya rufesa sosai,
Ko shekara baa rufaba da rasuwar mamma Dad din Shima ya rasu bayan sun mallakawa Omar komai nasu ya gaji wata irin sabuwar dukiya me yawan gaske shi kadai take hankalinsu mamman yayi mummunan tashi abinda suke jima suna dannewa ya taso Dan haka gaba Daya idanuwansu da zuciyoyinsu suka koma kan OMAR JEEDEN SEELAH Wanda shi a nasa bangaren Akoda yaushe yanzu cikin baqin ciki da kuncin rashin MASOYAnsa na asalin gaske yakeyi kasim seelah da iyayen riqonsa da suka daukesa tamkar Dan cikinsu da suka Haifa.

******Bayan abubuwa sun lafa komai ya zama daidai,kowa ya fuskanci rayuwarsa ciki kuwa harda Dr Aleena wadda hasken idaniyarta,Rabin ranta datake jinsa tsakiyar zuciyarta fiyeda komai da kowa 'danta JAMAAL MAM SEELAH ya tsaya cak a kan rayuwarta Bai bari damuwa ko wani qunci ya lalata rayuwarta ba Saida ya tabbatarda da koma asalin Dr Aleena seelah dinta ta dawo rayuwarta ta da mace me qwazo da aji da wayewa tareda sanin

ya kamata da burgewa harma da kokari akan aikinta ta bangare Daya Kuma ga sauran dukiyarta datake kulawa sosai da ita tana sake fadada business dinta dukiyarta na qaruwa sbd tanada connections da dama sosai.

Jamaal shine karfin gwiwanta Kuma kuzarin datake karfafa kanta tana komawa babbar macen Daya kamata sbd Sam Bai yarda yaga rauni a tareda ita ba,
Dan shi din kwata kwata ba mutum ne Mai yadda Wani ya takaka ba Koda kuwa Yana sama dakai ne Dan Yana girmama sanin darajar Kai fiyeda komai.

Jamaal shine ya Dora mahaifiyarsa a turban hasken musiluncin da mahaifansu ya kasa dorata duk tsawon shekaru zaman auren da sukai har sai da yayanta sukai wayo Jamaal ya musuluntar da ita itada mahaifiyarta da Shikenan mahaifiyarta zata mutu ahlulkitabinta.

Tana son danta Haroon sosai kaman yanda takeson Jamaal Amma matsayin Jamaal daban yake Dana kowa aranta Kuma daga Dad din har Haroon sun San da Hakan sedai Shima Dad din yafi qawa zucin Jamaal sbd tsananin zafin kansa Dan Yana kaunarsa akan Hakan fiyeda komai,
Jamaal dinsa Baya daukan reni ko kadan sabanin Haroon da karatun sheriar da yakeyi duk ya Sanyaya zuciyarsa ya koma Yana kallan komai akan tsari na sharia Dan tsoron aikatawa Dan gudun sabawa sharia.

Duk Dad keson Jamaal kusa dashi Hakan Baya samuwa sedai ya kawo musu ziyara a ya Dan yi watanni ya koma Amma Sam Baya iya rabuwa da mahaifiyarsa Dan itace abinda yafi komai so a duniya fiyeda koma da kowa Dan haka itama mum din Bata fargaban zuwansa Dan tasan zai dawo mata.

****Dad Omar Jaden seelah ya dawo Nigeria da zama a karo na farko tin bayan barinta sedai yazo yayi ziyara yayi Hutu ko wani lalurar ya koma Amma wannan Karan ya dawo ne sbd nacin Yan uwansu su mamma da lameenu Da suka matsu su hade guri Daya da Dan uwansu Rabin jikinsu,

Dawowansa Nigeria ya Sakasu samun wata irin nutsuwa da Kwanciyar hankalin da Basu taba samuba tinda suka rabu dashi se yanzu Daya dawo gasu gashi ahali Daya zuria Daya.

Duniyar duk Wanda yasan seelahs gabaki Daya da iyalinsu Basu taba sanin su ukun ba uwa Daya Uba Daya suke ba sbd tare aka Sansu tare ake jinsu hakama suna Daya da suke amfani dashi hakama dukkaninsu Babu Wanda ya taba fadawa wani ko Yan jarida masu fira dasu abu Daya suke fada musu su din Yan uwane da jini Daya yake yawo a jikinsu.

Kaman mansions dinsu suke a jere haka securities dinsu kusan duk Daya ne Kuma dawowan Alh Omar Jaden seelah ya Saka aka sake samun securities na gidansa daban shi Amma na gidan lameenu da Mam Daya ne.

Tareda Jamaal ya dawo Nigeria Dan haka Jamaal din a gidansa yake zaune tareda shi sbd Mom Nur Bata biyaosa ba tana can itama aikinta datakeyi acan Bata saki ba shi Kuma Bai takurata ba.

Alh Mam ya sake aure tini ya auri matar wani abokin huldansu Daya rasu anan Lagos wadda suke kira da Mum Atee asalin sunanta Atika.

***Tinda Alh Omar ya dawo Nigeria kullum busy yake daga shi har su Ahmed da Aron da yanzu bawai masu aikinsa bane Suma sun zama kaman abokanan aikinsa Dan ya Basu matsayi me kyau Dan haka Sam basa zama sai sunga sun gama daidaita komai nasa anan Nigeria din yafara huldodinsa kaman kowa.

Da farko su Alh Lameenu sun masa tayin su hade dukiyarsu kaman yanda ta Mam da lameenu din take Amma sbd akwai dukiyar dayake son warewa mahaifiyar kasim da haryanxu tana Raye sai yace su datakata tukuna.

Hakan da yayi ba qaramin kular dasu yayi musamman lameenu
Dan haka ko sati biyu baa rufa ba da maganar aka bugawa Alh Omar din waya cewan innar kasimu ta rasu gidanta datake ciki Wanda Omar din ya Gina mata a kauyen na alfarma da Kwanciyar hankali kawai cikin dare akaga ya kama da wuta Dan haka gawarta ma kurmus aka samu.

Ya shiga tashin hankali da mamaki sosai da Jin wannan mummunan labarin sbd baifi sati ba da yayi magana da ita a waya duk da ta tsufa sosai.

A ranar ya shirya suka bi jirgin shi da JAMAAL da Baba Ahmed zuwa gombe.

Sai dare suka Isa
Suna sauka motocin da aka tanada suna jiransa da securities suka kama hanyar kauyen da sai sunyi kusan kwana da wuni Basu Isa ba Dan gaba Daya yayi Nisan da kaman ma baa Nigeria suke ba can asalin asalinsu Wanda ake Kiran kauyen da suna Kartako.

Tafiya sosai sukai tareda jigata Amma dai dole sai je yayi jana'izan inna Dan kuwa itace uwar Data rage masa a duniya Kuma ta tafi tabarsa kaman yanda kasim ya tafi ya barta.

Koda suka Isa Jamaal duk karfin halinda amai ya ringa yi sbd Bai taba wannan wahalan ba duk da ga AC ga komai a mota Amma dai ya gaji matiqar gaske baima taba zuwa irin wainnan gurarenba ko a waya kuwa Bai taba ganinsu ba bare Dan dayasan hakane da Bazai ce zai taho tareda Dad Omar din ba.

Isowarsa ya Saka mutane taruwa anata tururuwar gaidashi kaman zasu masa sujjada sbd girmamawa Dan kaf kauyen Babu Wanda baisan Omar seelah ba,
Seelah Daya kwalli Daya daya rage Mai tinawa da asalinsa tareda taimkawa kowa Dake kauyen,
Shi kadai seelah din Daya rage musu tin daga kan iyayensu har sauran da tini suka mance da kauyen.

A taqaice ma dai shi kadai suka sani a yanzu.

Anyi jana'izan tin kafin isowarsa Dan haka addua kawai akayi ya zauna ya tattauna da manyan kauyen sosai wainda duk suke a bushe kaman Kara,
Kowa ka kalla a kauyen kaman kazo karkarar aljanu haka suke duk sun bushe duk da Yana tallafawa sosai Dan kaman shine yake ciyar da kauyen gabaki Daya.

Inna duka rayuwarta Yaya biyu ta Haifa,
Kasim da indo wadda take aure a kauyen kusa dasu harda 'yayanta biyu Maza sai kanwar mijinta AMEENAH datake riqo Dan haka ya buqaci ganinsu.

Koda aka aika Kiranta tazo tana ganinsa ta fashe da kuka Dan shine Dan uwanta itama Daya daya rage mata.
#MAMUH#
#JAMAAL JEEY SEELAH
#DEEP
#HAROON SEELAH
#LOVE
#CRAZINESS
#ZAFIN KAI
#AMEENATOU

ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap

Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee
#ZafafaBiyar

10
ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash

Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

****
Zuciyar Omar sosai ta sosu ganin rayuwar da Ayshatu Indo take ciki Dan haka take ya Yanke shawarar mayar dasu cikin gombe sbd rayuwar 'yayanta ta inganta hakama mijinta Wanda take ya amince Dan Daman Yana fita binni yan kasuwancinsa na siyarda dabbobi.

Lamarin masu abin duniya Babu Bata lokaci a ranar suka juyo suka baro sai washe gari da asuba suka iso gombe.

Lafiyayyar tsadaddiyar hotel din Daya sauka anan aka saukar dasu Ayshatu da yayanta da mijinta Jamaal kuwa acan sama ya sauka dakinsa daban sbd rashin lfy sosai ya rufesa.

Amina ma kanwar mijin Ayshatu sosai take ta amai da zazzabi me karfi Daya Saka dole aka sanar da Omar yasa aka kaisu asibiti take aka Bata gado.

Lamarin kaman wasa saiga Jamaal ya kwanta ciwo Shima Dan haka a ranar yabi jirgi ya shida Aron suka koma Lagos.

Suma su Ayshatu jinya sosai sukai asibiti ta Amina wadda taji jiki sosai sbd Bata taba fitowa binni ba.

Koda aka sallamosu asibiti anriga an samu gidan ansiya lafiyayye daidai su an Saka musu furnitures daidai misalin masu rufin asiri sbd bayason ya sakar musu kudi sosai yanason sufara sanin rayuwar garin idan zasu iya tukuna.

Duk wannan abin da akeyi Jamaal da idonsa baiga mutanen da Dad Omar yaje Gani a kauyen ba bare wainda yazo dasu.

Abinka da mutanen kauye da karamci da son mayarda alkhairi Kai tsaye Babba yayiwa Omar kyautar Kanwarsa dayake so fiyeda komai a duniya wadda yafisonta akan 'yayansa Daya haifa da cikinsa.

Ita kanta Ayshatu Jin tayi tayi Naam da Hakan Dan haka ta roki Omar akan ya amince.

Shiru yayi tareda kallan budurwar yarinyar da akace an basa din tana zaune a tsakar gidan tana alwala cikin nutsuwa da sanyin jiki.

Fara ce sol kamanta da Yayanta Wanda yake kaman ubanta Dan ya Isa haihuwan nata kaman an tsaga Kara,
Ba qazama bace tanada tsafta sosai shiyasa haskenta yake fresh a Koda yaushe duk da tana kauye kwata kwata Bata aikin wahala sbd idan akwai abinda Babbah ya tsani Gani a rayuwarsa shine ganinta tana wahala shiyasa baiyi wata wata ba yayi kyautarta inda zataje tayi rayuwar Kwanciyar hankali.

Kawu Nuhu Wanda matarsa da yayansa harma da Amina da Yan kauyensu da yawa suke Kiransa Babbah Ya taso a baida kowa a rayuwarsa sai Kanwarsa da mahaifiyarsa ta bar masa bayan ta rasu gurin haihuwarta,
Amina sunan mahaifiyarsu ne data rasu ya mayarwa Kanwar tasa,

Masifaffe ne shi Kuma mafadacin da baida sauki hakama baisan kowa ba sai kansa,
Babu abinda yake girmamawa da ganin mutuncinsu idan ba kudi ba,
Yana girmama kudi,
Yana Basu girmansu,
Yana ganin kimarsu fiyeda kowa Dan kowa zindir yake kallansa idan har baida kudi,
Masu kudi kawai yake saukewa hula ya mutunta,
Duk duniyarsa Amina ce kadai abinda yafi so fiyeda kudi,
Itakadaice abinda take sakasu rissinawa idan ya kafe akan Abu,
Ko Mai garin kauyensu shakkar rashin arzikin babba yakeyi sbd Baya shakkar kowa hakama kauyensu da zagayen ansan Amina ce kadai abinda yake Saka zuciyar babba girgiza Amma ko Barayin dabbobi na shiga gidan kowa a kauyen Amma basa shiga gidan babba Dan Shima kiris ne ya rage masa ya zama Dan ta'addan idan har zaiyi kudin Dan haka Daman dama Kawai yake Jira ta barin kauye sai gata Allah ya kawo.

Kafin Ayshatu yayi aure so biyu suna rabuwa sbd suna kuntatawa Amina sai da ya auri Ayshatu ya Bata matsayi me girma a ransa sbd tsananin son da takewa Amina na tsakani da Allah tin daga zuciyarta Kuma ta riqeta tamkar yarta data Haifa har itama ta haifi nata yayan biyu duka Maza daga Nan haihuwar ta tsaya har suka fara girma.

Duk yanda babba ke tsananin son Amina nata son datake masa yafi Hakan Dan ita sbd shi ta zabi zama kimtsatsiya muka kamilar yarinyar datafi kowa nutsuwa a kauyen tareda mutunci Dan kuwa Bata fita ko kofar gida ko ganinta sai dace ake ganinta Dan kwata kwata Bata fita koyaushe tana cikin gida killace.

Tana tsananin son Dadah da Babba kaman sune suka haifeta Dan haka ko yanzu da suka Bada aurenta ga Wanda Bata taba ganiba bare sani Bata musu ba kaman yanda Shima Omar din kawai ya karbeta bayan ya karanceta cikin qanqanin lokaci.

Bai buqaci komai daga garesu bayan matar kaman yadda suka basa ita Dan haka Kai tsaye ba wani biki ko wata hidima auren kawai aka dauka bayan wata Daya da dawowansu gombe kenan Dan haka Kai tsaye ya tafi da ita Amma Saida babba ya rakota har gidanta yaga duniyar da suke ciki ya koma Yana hawayen rabuwa da Amina.

Ansaka yayan Ayshatu makaranta hakama babba an basa jari kasuwanci yakeyi ba laifi Kuma Yana more rayuwarsa a binni Dan idan ya fara yawo ko gajiya bayayi ita Kuma Ayshatu kasuwancin cikin gida takeyi itama na Yan kulle kulle.

Matar Omar Bata daga hankalinta akan aurensa ba sbd Jin wacece matar daga kauye ta fito,
Hakama su mamman mamakin auren kawai sukayi ta yanda mutum kamarsa da duniya ake respecting da shaawa ace ya auro yar kauye yarinya Kuma,
Shi Alh lameenu hankalinsa tashi yayi da auren sosai Wanda gaba Daya zuciyarsa yaji tana kasa samun nutsuwa ya Kalli Alh mam a lokacinda yake sake Jin damuwar auren yace,

"Mamman me kake Gani zai iya biyo bayan wannan auren na Omar?
Yaushe ne burin shekara da shekaru zai cika?
Wannan burin daf yake da zama tarihi idan har Omar zai fara aure aure."

Wayar sake hannu Alh mam ya ajiye gefen tsadaddiyar Turkish Royal sofa din Dake palon dasuke Yana dagowa ya Kalli Alh lameenun yace,

"Kana tinanin wannan burin ko shi Omar din zai iya hanasa cika?
Idan ban mallaki dukiyar Omar ba har abada bana kallona Mai arziki Duk kuwa abinda zan Tara din....

Katsesa Alh lameenu yayi da cewa

"Hankalinmu na kwance ne duk shekarun Nan sbd Omar Bai taba samun haihuwa ba,hakama acan Baya mun Jira ne mr and Mrs Jaden su mutu dukiyarsu ta taru ta zama ta Omar din kafin mu dauko mataki
Yanzu dukiyar ta zama tasa Kuma gashi a kusa damu yanda muke so Amma Kuma yanzu yaqara aure
Baka Tinanin zai iya samun haihuwa idan har yaci gaba da auren Nan??

Shiru Alh mam yayi zuciyarta na daukan nauyi ahankali Dan kuwa basajin zasu iya tsayawa jiran Omar samu haihuwa,idan ma ya fara samun haihuwar to idan yayan dari zai Haifa sai sun kawar dasu gefe sbd Babu wani Rai da bazasu iya janyewaba akan buri da kudirinsu dayafi shekara da shekaru tin suna matasansu.

Tinani suka shiga dukansu musamman lameenu da hankalinsa gaba Daya shi ya tashi akan auren shi tin kafin wani abu ya shigo gabansu yaji Yana buqatan a cire matar da Omar din ya auro daga lissafi.

Rayuwar Amina a gidan mijin data kasa sabawa da shi sbd rayuwarsu akwai banbanci tazarar sama da kasa Amma Kuma sbd masu aikin da aka zuba mata da Mai kulawa da ita da koya mata abubuwa da yawa sai tafara Dan sakewa tana koyan abubuwan da dama Wanda Bata dauki lokaci ba mijinta kuwa ya amsheta amatsayin matarsa.

Zamansu Daya ya Saka soyayyarta da tausayinta masu karfi shigar Omar
Ita kuwa Daman tini ta kamu da sonsa kawai tana kama kanta ne sbd ganin kaman yafi karfinta.

Sabuwar rayuwa sosai suka Bude ta sabbin ma'auratan da suke cikin sabuwar soyayyar juna,
Gogewa tafara yi ta zama matar gidan mijinta Dan kuwa sosai take kokarin kulawa da mijinta kaman wadda tayi boko ta waye sosai.

Shi kuwa sanyinta da nutsuwarta tareda tsananin nutsuwan dayake samu da ita ya saka zuciyarsa kamuwa da Sonta fiyeda yanda yayi tinani gashi ita din yarinya ce sosai take narke masa tana sakashi Jin kansa tamkar sabon saurayi duk ta gama kame gangar jiki da zuciyarsa.

Jamaal ma yaji dadin zama da ita sosai fiyeda yanda yayi tinani duk da batajin turanci shikuma ba sosai yakejin hausar ba Baya ma iya doguwar Hausa duk kame Kame ne,

Jamaal ya koma gidan Dad dinsa sedai Bai wani jima ba ya koma sbd hutunta Daya qare na makaranta.

*********Kaman yanda ake cewa kaddara ta rigayi fata kwatsam sai ga ciki a jikin Amina Wanda ya girgiza duniyar Alh Omar Jaden seelah,
Ya girgiza sosai sbd Bai taba Saka ran zai haihu din ba,
Yanada ciwo a zuciyarsa na shekaru akan rashin haihuwa Kuma ya Riga ya

cirewa haihuwar Rai shiyasa bayyanar cikin ya girgizasa matikar gaske.

Ita kanta Amina Bata Saka ran samun haihuwa ba sbd ta Riga ta yaddarwa kanta zata zauna dashi ahakan ba haihuwa so itama samun cikin ya Sakata mamaki me tsananin gaske da farin cikin gaske duk a lokaci Daya.

Tinda ta samu cikin ya daukesa suka bar kasar kusan watanninsu uku kafin suka dawo lokacin cikin yakai wata shida Babu Wanda yasan dashi bayan shi da ita sai masu aikinta da suka Saba da ita sosai suke mata biyayya.
#MAMUH#
#JAMAAL JEEY SEELAH
#DEEP
#HAROON SEELAH
#LOVE
#CRAZINESS
#ZAFIN KAI
#AMEENATOU

ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee
#ZafafaBiyar

7
*_ASHNA BEAUTY SKINCARE_*
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

****
Iyayen Aleena sunada wani irin qyanqyami da kabilanci ga Wanda basu sani ba Sam duk da suna kallan su mamman din a matsayin family na Mr Jaden sedai Sam Sam Basu aminta da mamman ba duk da Shima fari ne sosai kaman Omar Kuma kyakkyawa daya kusa ma yafi Omar din kyau amma dai hankalinsu yafi Kwanciya dari bisa dari akan Omar dasuke ganin kaman a taredasu ya taso duk da basusan yarinyartasa ba Amma ai a tinaninsu a hannun Mr Jaden ya taso Kuma dansa ne Daya haifa acan.

Aleena a zuciyarta mam kaman yanda yanzu ake kiransa ya kwanta mata dari bisa dari sbd yakai duk mataki da tsarin datakeson namiji yakai mata,
Yanada kyau sosai da wayewan da baya shakka ko tsoron kowa,
Hakama yanada class Wanda taku ne Daya iya abinsa tinda ya samu kansa sabuwar duniyar datafi wadda suka fito,.yanada ilimi da dukiyar kansa da bazai taba damuwa da tata dukiyar ba hakama ya Bata tabbacin shine zai tattaro ya dawo qasar da zama bazai taba daukanta zuwa koina ba Dan haka taji Hakan ya mata.

Omar Bai taba tinanin akwai Kokuma wata manufa zata shigo cikin maganar auren mamman da Aleena ba dan haka yafi kowa farin ciki
Su kansa su mum dinsa sunyi farin ciki daga baya Daya nuna musu Yanason su nuna farin cikinsu da Hakan.

Ansha fitina da damuwa sosai akan iyayen Aleena su amince Amma suka qi musamman mahaifinta Sam Sam Bai amince ba.

Har Aleena ta cire Rai sai kwatsam Dad din nata aka wayi gari ya mutu a dakinsa kwance Yana Yana bacci.

Sun shiga tashin hankali sosai sbd Aleena na tsananin son Dad dinta fiyeda mum din shiyasa ma ta hakura da maganar auren mamman bawai Dan shekarunta basu Kai tayi abinda ranta yakeso ba sai dan Dad din kawai.

Jadens family sun shiga tashin hankali da firgicin mutuwar Mr Harris sbd kusancinsu da zamtowansu family friends tin tsawon lokaci me tsayin gaske.

Omar dasu mamman sun shiga damuwa sosai sosai Dan haka Omar ma yaji Yana sake son auren Aleena da mamman Dan ta samu musulunta ita da mum dinta kafin Suma su rasa wannan damar kaman Mr Harris.

Shi kansa mamman yasan yanzu Kam Babu wata shamaki da zata shiga tsakaninsa da auren Aleena musamman yanzu da nauyin komai na kamfanin Dad dinta da uban dukiyarsa zasu dawo kanta.

Mutuwar Mr Harris ya taba Aleena da mum dinta sosai musamman mum din da Bata sake lafiya ba
Ba Bata lokaci Aleena ta sake amincewa mamman sbd tsananin kulawansa da tattalin dayake nuna musu ita da mum dinta.

Sunyi register na aurensu da komai hakama auren musilunci suka fara yi wedding dinner Daya sukai bayan daurin auren da kwana Daya anan
Duniya ta sake sheda auren nasu Wanda da yawa manyan mutane da

respected families Dake tareda su kusa da nesa duk sun samu halartowa.

Babban sa'ar da mamman yasake tsintar rayuwarsa a ciki shine gabatar dashi da Mum din Aleena tayi ga abokanan huldansu na business da sauransu,
Da yawa ta gabatar dashi take ya nutsu ya fara samarwa kansa matsayin da suna a cikin manya ta hanyar nuna nutsuwa da tinani tareda sanin ya kamata harma da bayyanarda tsananin kauna da son dayakewa Aleena da mahaifiyarta da yanzu shine zai tsaya musu.

Da yawan mutane sun yaba dashi Dan take take aka ringa recognizing nasa shida lameenu Wanda yake gabatarwa a matsayin Dan uwansa Kuma abokin tasa huldar.

Omar Baya buqatan gabatancin kowa sbd shi din sananne ne a cikinsu tini Kuma duk yanda suka yaba dasu mamman Omar ne a ransu da idanuwansu fiyedasu.

***Bayan auren mamman da Aleena ya nutsu ya duba ya karanta da kyau yaga duk inda yake tinanin dukiyar Aleena abin ya wuce Nan Dan haka ya sake iya takunsa Dan kuwa son dayake nuna mata tini ya qarasa gamawa da ita da mum dinta take suka Dorasu akan dukiyarsu sbd ita Aleena batada time sbd karatunta na likitanci da saura kadan ta kammala.

Lameenu ya koma Nigeria sbd gudanar musu da ayyukansu na can Kuma Shima Yana komawa Babu Bata lokaci yayi aure Wanda daga mamman har Omar sun halarta angama sun dawo.

Bayan dawowarsu ba jimawa Aleena ta fara aiki a Special Care hospital din data Gina me tsarin Daya dauki kudi masu yawan gaske da hankalin mutane tareda zuba qwararrin doctors da qwararrin nurses da ma'aikata.

Fara aikinta yayi daidai da bayyanar ciki a tareda ita Wanda ya Saka mahaifiyarta da ita murna sosai kamar me
Sedai duk murnarsu basukai ko Rabin ta mamman ba da Daman haihuwar yake Jira dukiya ta tabbata tasa Dan kuwa abinda zata Haifa shine zai gaje dukiyar to Kuma ai shine uban abinda zai Haifa din.

Omar yabar Poland Yana UK gurin qaro ilimi akan harkar business sosai Wanda Shima acan ya Hadu da tasa matar yar asalin kasar Jamaica tin Yana can suka Kai karshe sedai shikam a Jamaica din sukaje Akai aurensu Kuma kowa ya samu halarta hadda Aleena da mum dinta duk da auren musulmai ne sun halarta.

Bayan auren daga Omar din har Nur dinsa a UK suke sbd itama karatun takeyi Amma ita yanzu ne ma ta fara a matakin farko take.

Lameenu na Nigeria,
Mamman na Poland
Omar na UK,
Haka kowannensu yake gudanar da rayuwarsa bisa tsari da yanda yake Sonta Dan kuwa kowa takai masa iya iyakar yanda yakeson.

Haihuwar Aleena ce ta sake hadasu guri Daya sbd farin ciki Mai tsananin gasken da suka samu rayuwarsu a ciki da karuwar seelahs,

Duk wani Wanda yake Hulda ko yasan seelahs Saida ya sheda farin ciki me tsananin gaske da sukeyi da samun haihuwar farko a cikinsu Kuma Allah a Karan farko Saiya albarkace su da samun 'yan biyu duka Maza.

Mam Bai taba dauka ma zaiji irin farin ciki da tsananin kaunar yayan fiyeda komaiba Saida aka haifosu ya rungumesu jajaye dasu kaman wasu taurari.

Mum din Aleena har hawayen farin ciki ta ringa yi tsabar murna kusan tata dukiyar mallaka musu ita tayi a matsayin will dinta idan ta mutu a Basu 60% na dukiyarta sauran 30 a bawa Aleena din.

Wannan will din ba qaramin dadi yayiwa mam ba Dan haka soyayyar 'yayansa ta ninku a ransa Dan kuwa ya tabbatarda sune mukullin arzikinsa mara adadin dabai samu riqewaba sai yanzu,
Sune sa'arsa Daya Dade Yana jira ta shiga hannunsa,
A yanzu Daya samesu yasan dukiyar Aleena tasa ce itama tinda ta mahaifiyarta ta zama tasa burinsa Daya ne ya rage a rayuwarsa shine mallakar dukiyar Omar wadda duk abinda zai mallaka idan ba ita suka mallaka ba bayajin zai iya numfashi me dadi.
#MAMUH#
#AMEENATOU
#LIFE
#ROM
#JJS
#THE SEELAHS

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee
#ZafafaBiyar

12
A bangaren su Alh Lameenu abubuwan sun jagule musu gabaki Daya sbd wankin hula na Neman kaisu dare,Daren ma mara kyau sbd rayuwar Omar jeden Daya rak tana Neman gagararsu dauka bayan tsare tsaren da suka ringa yi ana kaiwa rayuwar hari,

Kan Mam ya dauki zafi matiqar gaske Dan gaba Daya kaman anyi masa asiri Jin yakeyi idan ba cike burinsu sukai ba kwata kwata bazasu taba samun Kwanciyar hankali da nutsuwa ba musamman yanzu da kullum Omar seelah ne yanzu a jaridu da labarai,

Shi Lameenu matar Omar ce ta tsaya masa a Rai da maqoshi Dan kuwa jikinsa na Basu zata iya Bata musu aiki kwata kwata daga ranar data samu

ciki ko makamancin Hakan Dan haka shi idanuwansa akanta suke tafara barin duniyar gaba Daya yakeso kafin su sake dawowa kan Omar din Dan haka Kai tsaye ya Yanke shawarar ayi me yiyuwa a huta kafin su zauce akan dukiyar da bata shigo hannunsu ba har yanzu kaman abin Baki sai wahala sukeyi shekaru da ciwon Rai da baqin cikin da kullum zuciyoyinsu ba lafiya.

Shi Mam ba iya matar Omar yakeson a gama Dan matsalarta yanzu ba harta Omar din Dan ya gaji da ganinsa a gabansa Kuma samansu,
Ya gaji da Jin sunan Omar jeden na shiga kunnuwansa,
Ya gaji da Jin sunan Omar jeden a kafofin yada labarai,
Shi kansa Omar jeden seelah din ya gaji da ganinsa Yana yawo Yana numfashi Yana samun mutuntawa da respect da cika idanuwan mutane,
Ya gaji da duk wani abu Daya shafi Omar ga uwa Uba 'dansa dayake tsananin son ya kasance a karkashinsa Yana tareda Omar din Yana sonsa kusan fiyeda yanda yake sonsa shida yake ubansa Daya haifesa Dan haka ya gaji a rufe chapter din Omar din kawai a huta.

Wani numfashin Jin nauyin zuciyarsa na rayuwa Lameenu ya sake Jin abubuwan da Mam din ya fada Dan Shima Kam yakai maqura,
Wani mugun nauyi ne danne da zuciyarsu duk tsawon shekarun Nan tin daga ranar da arzikinsu kasim ya bayyana a ashalawa.

****
Koda cikin Amina ya shiga wata Tara ya Isa haihuwa har lokacin Babu Wanda yasan dashi bayan uban cikin da Aminansa Ahmed da Aron sai su Babbah,
Duk huldarta da muamalarta dasu mum Atey Basu taba lura da ciki a jikinta ba sbd boyewa takeyi cikin hijab hakama ko gidan lameenu Basu San da cikinba sbd Aminar nada zurfin ciki sosai hakama faruwar tashi tashen hankalin Daya ringa samun mijinta ya sanar da ita kada kowa yasan da cikin shiyasa ta sake Adana kanta ma da cikin ya tsufa kwata kwata ta Dena fita koina ko gurin mum Atey din ta Dena zuwa kwata kwata sedai Haroon ne ke shigowa sosai Kuma Shima Bata taba barin yaga cikin ba.

Shirye shiryen fita da ita ta haihu a Poland Omar keyi hakama su Babbah sunacan sunata zumudi da Shirin haihuwarta Dan sunso abarta ta dawo haihuwa Amma Sam Omar yaqi yarda da Hakan dole suka hakura suka bar zancen Amma dai zasu taho idan ta haihu.

Dayake tamkar yar cikinta dadah Kejin Amina tini ta hada mata kayan fitar zaqin haihuwa da wasu maganin gargajiyar da zai Sakata samun saukin nakuda babba zai kawo mata ya dawo kafin ta haihu su taho tare.

Shi kansa babban cikin zumudin zuwan yake Dan duk yaga Omar wata

sabuwar jakar arziki yake samu daga garesa Dan haka Baya ganin wahalar Nisan tafiyar kudin yake kalla da Kuma Amina dazai Gano.

Ranar asabar da asuba Babba yabar gombe yahau motar Lagos zuciyarsa cikesa zumudin haduwa da 'yar uwarsa wadda hakanan yake Jin sabuwar soyayyarsu ta jini tana qaruwa a ransa har kirjinsa na nauyi
fatansa dai ya Isa lafiya.

Acan Lagos kuwa tin safe da Amina ta tashi takejin yanayinta Babu dadi kwata kwata,ciwon mara da nauyin marar takeji sosai gashi Omar Yana gida kwata kwata ya Dena fita a kwanakin sbd hatsarin da rayuwarsa take ciki yayi yawa Dan haka aka dakatar dashi daga fita sai an gama bincike.

Rashin fitarsa ya Saka masu jiran fitowan tasa basuda zabin Daya wuce kawo aikinsu har cikin gidansa sbd tarkonda aka hada masa a waje Yana jiransa bazai taba tsallakesaba Daya fita da tabbas sai yabar duniya a ranar Daya fitan shiyasa ma daga Aron har Ahmed sun Kai matiqar wuyan lameenu da mam sbd sun zama kamar wasu makaman kariya ga Omar din.

Batareda ta nuna halinda take ciki ba sbd kada ta damar da Omar din Amina ta ringa kulawa dashi sbd Shima Yana fama da ciwon Kai gashi masu debe masa kewa da firarrakinsu idan har suna gida to suna babban garden na Bayan gidajensu dashine ya hade gidajen nasu uku ta kofofin Baya acan suke zama suna hutawa tareda wayoyinsu hatta abincin Daren yawanci acan sukeci tare wani lokacin gaba dayansu harda iyalinsu tare suke ci cikin kulawa da shakuwa.

Mam Baya kasar Yana Poland yaje dubo Jamaal haka kawai,
Lameenu ma a ranar yayi tafiya da safe zuwa Abuja wani meeting.

A jikin mijinta ta kwanta bayan dataji karfin jikinta duk Yana Neman karewa Amma har lokacin Bata nuna masa abinda yake damunta ba.

Kwanciyarta a jikinsa ya sakashi Jin wani irin sanyi da kaunarta data cikin dayake jikinta na sake dabaibayesa musamman yanzu da kowanne lokaci zata iya haihuwa shiyasa ma ya matsu suyi tafiyar.

Qamshin jikinsa ta shaqa ahankali tana Dan rufe idanuwanta suka Danyi laushi sbd rashin kuzari.

Shi kuwa yanda take sauke numfashi ahankali cikin jikinsa tana sake narkewa ya sakashi Jin Sonta na hanasa riqe kansa Dan haka ahankali ya fara shinshinarta Yana shaqar nata qamshin Yana Jin dadin dumin jikinta a

fatarsa.

Tanajin Hakan ta lumshe idanuwanta ahankali tana lafewa Dan tasan me Hakan zai haifar.
Rungumeta yayi dakyau Yana hade fuskansu guri Daya yayi kissing hancinta ahankali kafin ya hade bakinsu Yana lumshe nasa fararen idanuwan masu kyau Yana zare doguwar rigar Dake jikinta a natse.

Cikin sanyi da nutsuwa ya tafiyar da ita har sukai wata nutsatsiyar making love daga Nan bacci ya daukesa me nauyin gaske bayan yayi wanka.

Itama lallabawa tayi mararta na sake kullewa taje bedroom dinta tayi wankan tsarki ta sake wani wankan ta fito tayi sallan laasar itama ta shige daki tanason Jin ko zata iya baccin Amma Sam baccin yaqi zuwa.

Safiyya ta kira Mai aikinta datake kulawa da kusan komai na gidan tace ta kawo mata ruwan Tasha Amma Mai zafi bamai sanyi ba.

Koda Fatima ta kawo mata ruwan Taga yanayinta cikin kulawa ta tambayeta ko a kira doctor ko Akira mum Atey.

Girgiza mata Kai tayi tana sake danne abinda takeji Amma Sam Baya dannuwa Amma dai duk da haka Bude Baki tayi cikin sanyi tace

"Karki sanar da kowa zuwa anjima idan jikin baiyi sauki ba zan sanar da Daddy"

Numfashi Mai sanyi safiyya ta sauke ahankali cikin tausayin Aminar idan nakuda ce tace

"Toh shikenan Allah ya Baki lafiya yakuma saukar Dake lafiya"

"Amin" Aminar ta amsa daqyar tana Dan daurewa bayan ta amsa ruwan a dogon glass cup Tasha kadan ta ajiye.

Bayan fitar safiyya sosai tafara Jin yanayin na karuwa har Akai magrib ta tashi daga Palo Takoma bedroom tayi alwala tayi sallah,
Tana idarwa ta fito taje bedroom din Omar bayanan ya fita sallah.

Koda ya dawo a tare suka zauna palonsa sukaci abinci Wanda kadan ya Bata a baki tace ta koshi ta tattara kayan da kanta ta fita dasu.

Daga can Bata dawowa dakinta a ta shige tayi sallar ishai tayi Shirin bacci ta kwanta a dakinta sbd batason zuwa dakinsa ya gane halinda take ciki.

Yana masallaci sallan ishai Babba ya iso ba qaramin mamakin ganinsa yayi ba sbd Babu Wanda yasan yana tafe har aminan Bata saniba.

Cikin kulawa da farin ciki sosai ya tarbesa suka shigo Kai tsaye masaukinsa suka nufa sbd Amina tariga tayi bacci dukansu sun sani Dan haka babban yace abari da safe kawai tagansa har murna saitafi ma.

Ba musu Omar yayi Naam Dan Hakan Dan haka take aka kawo masa abinci kala kala aka sake gyare masa boys quarter din aka kawo cartons na ruwa da drinks aka Saka a fridge sukai Saida safe ya fice yabarsa akan Saida safen.

Har bedroom dinta yace yaga bacci ya dauketa me sanyi da nutsuwa Dan haka Bai tayarda ita ba ya kyaleta ya wuce bedroom dinsa kawai sbd yasan tana buqatan hutawa sosai Akai Akai sbd cikin jikinta.
#MAMUH#
#MAM#LAM#OMAR#SEELAHS
#JAMAAL JEEY SEELAH
#DEEP
#HAROON SEELAH
#LOVE
#CRAZINESS
#ZAFIN KAI
#AMEENATOU SEELAH

ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee
#ZafafaBiyar

12
A bangaren su Alh Lameenu abubuwan sun jagule musu gabaki Daya sbd wankin hula na Neman kaisu dare,Daren ma mara kyau sbd rayuwar Omar jeden Daya rak tana Neman gagararsu dauka bayan tsare tsaren da suka ringa yi ana kaiwa rayuwar hari,

Kan Mam ya dauki zafi matiqar gaske Dan gaba Daya kaman anyi masa asiri Jin yakeyi idan ba cike burinsu sukai ba kwata kwata bazasu taba samun Kwanciyar hankali da nutsuwa ba musamman yanzu da kullum Omar seelah ne yanzu a jaridu da labarai,

Shi Lameenu matar Omar ce ta tsaya masa a Rai da maqoshi Dan kuwa jikinsa na Basu zata iya Bata musu aiki kwata kwata daga ranar data samu ciki ko makamancin Hakan Dan haka shi idanuwansa akanta suke tafara barin duniyar gaba Daya yakeso kafin su sake dawowa kan Omar din Dan haka Kai tsaye ya Yanke shawarar ayi me yiyuwa a huta kafin su zauce akan

dukiyar da bata shigo hannunsu ba har yanzu kaman abin Baki sai wahala sukeyi shekaru da ciwon Rai da baqin cikin da kullum zuciyoyinsu ba lafiya.

Shi Mam ba iya matar Omar yakeson a gama Dan matsalarta yanzu ba harta Omar din Dan ya gaji da ganinsa a gabansa Kuma samansu,
Ya gaji da Jin sunan Omar jeden na shiga kunnuwansa,
Ya gaji da Jin sunan Omar jeden a kafofin yada labarai,
Shi kansa Omar jeden seelah din ya gaji da ganinsa Yana yawo Yana numfashi Yana samun mutuntawa da respect da cika idanuwan mutane,
Ya gaji da duk wani abu Daya shafi Omar ga uwa Uba 'dansa dayake tsananin son ya kasance a karkashinsa Yana tareda Omar din Yana sonsa kusan fiyeda yanda yake sonsa shida yake ubansa Daya haifesa Dan haka ya gaji a rufe chapter din Omar din kawai a huta.

Wani numfashin Jin nauyin zuciyarsa na rayuwa Lameenu ya sake Jin abubuwan da Mam din ya fada Dan Shima Kam yakai maqura,
Wani mugun nauyi ne danne da zuciyarsu duk tsawon shekarun Nan tin daga ranar da arzikinsu kasim ya bayyana a ashalawa.

****
Koda cikin Amina ya shiga wata Tara ya Isa haihuwa har lokacin Babu Wanda yasan dashi bayan uban cikin da Aminansa Ahmed da Aron sai su Babbah,
Duk huldarta da muamalarta dasu mum Atey Basu taba lura da ciki a jikinta ba sbd boyewa takeyi cikin hijab hakama ko gidan lameenu Basu San da cikinba sbd Aminar nada zurfin ciki sosai hakama faruwar tashi tashen hankalin Daya ringa samun mijinta ya sanar da ita kada kowa yasan da cikin shiyasa ta sake Adana kanta ma da cikin ya tsufa kwata kwata ta Dena fita koina ko gurin mum Atey din ta Dena zuwa kwata kwata sedai Haroon ne ke shigowa sosai Kuma Shima Bata taba barin yaga cikin ba.

Shirye shiryen fita da ita ta haihu a Poland Omar keyi hakama su Babbah sunacan sunata zumudi da Shirin haihuwarta Dan sunso abarta ta dawo haihuwa Amma Sam Omar yaqi yarda da Hakan dole suka hakura suka bar zancen Amma dai zasu taho idan ta haihu.

Dayake tamkar yar cikinta dadah Kejin Amina tini ta hada mata kayan fitar zaqin haihuwa da wasu maganin gargajiyar da zai Sakata samun saukin nakuda babba zai kawo mata ya dawo kafin ta haihu su taho tare.

Shi kansa babban cikin zumudin zuwan yake Dan duk yaga Omar wata sabuwar jakar arziki yake samu daga garesa Dan haka Baya ganin wahalar Nisan tafiyar kudin yake kalla da Kuma Amina dazai Gano.

Ranar asabar da asuba Babba yabar gombe yahau motar Lagos zuciyarsa cikesa zumudin haduwa da 'yar uwarsa wadda hakanan yake Jin sabuwar soyayyarsu ta jini tana qaruwa a ransa har kirjinsa na nauyi
fatansa dai ya Isa lafiya.

Acan Lagos kuwa tin safe da Amina ta tashi takejin yanayinta Babu dadi kwata kwata,ciwon mara da nauyin marar takeji sosai gashi Omar Yana gida kwata kwata ya Dena fita a kwanakin sbd hatsarin da rayuwarsa take ciki yayi yawa Dan haka aka dakatar dashi daga fita sai an gama bincike.

Rashin fitarsa ya Saka masu jiran fitowan tasa basuda zabin Daya wuce kawo aikinsu har cikin gidansa sbd tarkonda aka hada masa a waje Yana jiransa bazai taba tsallakesaba Daya fita da tabbas sai yabar duniya a ranar Daya fitan shiyasa ma daga Aron har Ahmed sun Kai matiqar wuyan lameenu da mam sbd sun zama kamar wasu makaman kariya ga Omar din.

Batareda ta nuna halinda take ciki ba sbd kada ta damar da Omar din Amina ta ringa kulawa dashi sbd Shima Yana fama da ciwon Kai gashi masu debe masa kewa da firarrakinsu idan har suna gida to suna babban garden na Bayan gidajensu dashine ya hade gidajen nasu uku ta kofofin Baya acan suke zama suna hutawa tareda wayoyinsu hatta abincin Daren yawanci acan sukeci tare wani lokacin gaba dayansu harda iyalinsu tare suke ci cikin kulawa da shakuwa.

Mam Baya kasar Yana Poland yaje dubo Jamaal haka kawai,
Lameenu ma a ranar yayi tafiya da safe zuwa Abuja wani meeting.

A jikin mijinta ta kwanta bayan dataji karfin jikinta duk Yana Neman karewa Amma har lokacin Bata nuna masa abinda yake damunta ba.

Kwanciyarta a jikinsa ya sakashi Jin wani irin sanyi da kaunarta data cikin dayake jikinta na sake dabaibayesa musamman yanzu da kowanne lokaci zata iya haihuwa shiyasa ma ya matsu suyi tafiyar.

Qamshin jikinsa ta shaqa ahankali tana Dan rufe idanuwanta suka Danyi laushi sbd rashin kuzari.

Shi kuwa yanda take sauke numfashi ahankali cikin jikinsa tana sake narkewa ya sakashi Jin Sonta na hanasa riqe kansa Dan haka ahankali ya fara shinshinarta Yana shaqar nata qamshin Yana Jin dadin dumin jikinta a fatarsa.

Tanajin Hakan ta lumshe idanuwanta ahankali tana lafewa Dan tasan me

Hakan zai haifar.
Rungumeta yayi dakyau Yana hade fuskansu guri Daya yayi kissing hancinta ahankali kafin ya hade bakinsu Yana lumshe nasa fararen idanuwan masu kyau Yana zare doguwar rigar Dake jikinta a natse.

Cikin sanyi da nutsuwa ya tafiyar da ita har sukai wata nutsatsiyar making love daga Nan bacci ya daukesa me nauyin gaske bayan yayi wanka.

Itama lallabawa tayi mararta na sake kullewa taje bedroom dinta tayi wankan tsarki ta sake wani wankan ta fito tayi sallan laasar itama ta shige daki tanason Jin ko zata iya baccin Amma Sam baccin yaqi zuwa.

Safiyya ta kira Mai aikinta datake kulawa da kusan komai na gidan tace ta kawo mata ruwan Tasha Amma Mai zafi bamai sanyi ba.

Koda Fatima ta kawo mata ruwan Taga yanayinta cikin kulawa ta tambayeta ko a kira doctor ko Akira mum Atey.

Girgiza mata Kai tayi tana sake danne abinda takeji Amma Sam Baya dannuwa Amma dai duk da haka Bude Baki tayi cikin sanyi tace

"Karki sanar da kowa zuwa anjima idan jikin baiyi sauki ba zan sanar da Daddy"

Numfashi Mai sanyi safiyya ta sauke ahankali cikin tausayin Aminar idan nakuda ce tace

"Toh shikenan Allah ya Baki lafiya yakuma saukar Dake lafiya"

"Amin" Aminar ta amsa daqyar tana Dan daurewa bayan ta amsa ruwan a dogon glass cup Tasha kadan ta ajiye.

Bayan fitar safiyya sosai tafara Jin yanayin na karuwa har Akai magrib ta tashi daga Palo Takoma bedroom tayi alwala tayi sallah,
Tana idarwa ta fito taje bedroom din Omar bayanan ya fita sallah.

Koda ya dawo a tare suka zauna palonsa sukaci abinci Wanda kadan ya Bata a baki tace ta koshi ta tattara kayan da kanta ta fita dasu.

Daga can Bata dawowa dakinta a ta shige tayi sallar ishai tayi Shirin bacci ta kwanta a dakinta sbd batason zuwa dakinsa ya gane halinda take ciki.

Yana masallaci sallan ishai Babba ya iso ba qaramin mamakin ganinsa yayi ba sbd Babu Wanda yasan yana tafe har aminan Bata saniba.

Cikin kulawa da farin ciki sosai ya tarbesa suka shigo Kai tsaye masaukinsa suka nufa sbd Amina tariga tayi bacci dukansu sun sani Dan haka babban yace abari da safe kawai tagansa har murna saitafi ma.

Ba musu Omar yayi Naam Dan Hakan Dan haka take aka kawo masa abinci kala kala aka sake gyare masa boys quarter din aka kawo cartons na ruwa da drinks aka Saka a fridge sukai Saida safe ya fice yabarsa akan Saida safen.

Har bedroom dinta yace yaga bacci ya dauketa me sanyi da nutsuwa Dan haka Bai tayarda ita ba ya kyaleta ya wuce bedroom dinsa kawai sbd yasan tana buqatan hutawa sosai Akai Akai sbd cikin jikinta.
#MAMUH#
#MAM#LAM#OMAR#SEELAHS
#JAMAAL JEEY SEELAH
#DEEP
#HAROON SEELAH
#LOVE
#CRAZINESS
#ZAFIN KAI
#AMEENATOU SEELAH

ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee
#ZafafaBiyar

13
KISSA TRAINING CLASS

MASU SO SU KOYI KISSA
MASU SO SU IYA KISSA
MASU SO SU SAN KAN KISSA
MASU SO SU ZAMA HATSABIBAI AKAN KISSA
GANE IDAN AN SHIRYA MIKI KISSA
KISSAN IYA KWACE DANGIN MIJI
KISSAN IYA KWACE MIJI
BA BOKA BA MALAM BAKUMA MAGANI KAWAI KISSA KADAI

ZOKI SHIGA AJIN KISSA DA NAIRA DUBU KACAL!!!
5DAYS TRAINING CLASS WANDA BABU YANDA ZA’AYI KIYI TRAINING DIN NAN BAKI IYA KISSA DA KISISINA BA.
KISSA SHİNE BABBAN MAKAMIN MATAR AURE❤
ZOKI SHIGA KAFIN KISHIYARKI TARIGAKI SHIGA

KISSA CLASS PAYMENT IS 1k

GUESS WHAT 5 LUCKY ACTIVE MEMBERS ZASU CI NAIRA DUBU ASHIRIN EACH□□□ 20k EACH

ANOTHER 5 LUCKY MEMBERS ZASUCI KYAUTAN SET NA TURAREN WUTA BY RUKY□□

ANOTHER 5 LUCKY MEMBERS ZASUCI KYAUTAN KAYAN MATA FROM HONEYDROPS KAYAN MATA□□
JOIN YANZU YOU MIGHT BE THE LUCKY WINNER

CHAT ME UP DON SHIGA WANNAN KISSA TRAINING CLASS
07012181461

****
Kwantawa yayi Yana waya da Nur wadda ke sanar dashi zuwan Mam ayau din gidanta ya kawo mata ziyara tareda Jamaal harma ya Bata kyautan 5000 dollar.

Numfashi ya Dan sauke ahankali Yana Jin dadin kulawansu ga Iyalin juna shiyasa ma yake Jin damuwar tinanin Dake shigarsa na son tattarawa ya koma inda ya fito sbd tsaron lafiyarsa data iyalinsa da 'yayan da zaa fara Tara masa amma Kuma Yana cikin damuwa da baqin cikin rabuwa da 'yan uwansa da sukai alkawarin rayuwa tare su mutu tare.

Bayan gama wayarta guraren 1 na dare ya tashi yayo alwala kaman yanda ya Saba yazo ya tayarda sallah.

Ya Dade a farke Yana adduoinsa da Babu Daren da bayayinsu tinda ya samu kansa a rayuwar Kwanciyar hankali da nutsuwa Bai taba tsallake Daren da Baya sallolin dare da adduoi ga iyayensa na asali da suka haifesa Dasu kasim ba da iyayensa na riqo harma da 'yayan da baisan zai haifa ba Yana musu adduar zuwa duniya lafiya suyi rayuwarta lafiya Kuma su komawa ubangijinsu lafiya.

Karfe uku na dare ya miqe daga lafiyayyar gadonsa bayan ya kwanta sbd dubo Amina Dan Basu taba kwana na tareda ba idan har Yana gari sai yau din,
Kuma motsi yaji kaman harma da magana Dan haka fito Yana sake kallan agogo Kai tsaye ya nufi hanyar bedroom dinta.

Koda ya tura kofar bedroom din tana zaune tsakiyar gadonta ta hada zufa sosai idanuwanta sunyi jajir tana cikin azaba Mai tsananin gaske.

Cikin sauri ya qaraso gurinta Yana ambatar sunanta cikin kulawa Mai tsananin gaske da tashin hankali.

Hawa gadon yayi Yana kama hannunta datake qanqame gado dashi,
Cikin tausayinta me tsananin gaske yace

"Labor ne?,tin yaushe kika fara ciwon?
Meyasa Baki sanar saniba?

Saukowa yayi gadon ya koma bedroom dinsa ya dauko wayarsa yafara Neman wayar Ahmed yanason sanar dashi suna buqatan zuwa asibitin a tsakiyar dare Kokuma kawo likita gida Amina zata haihu.

Kasa samun wayar Ahmed din yayi yakoma Kiran ta Aron shikuma tashi Bai dauka ba.

Saukowa yayi kasa ya nufi bangaren masu aiki da kansa yayi knocking ya kirawo safiyya ta fito sbd tafara manyanta dole tasan kan haihuwa kafin ya samu Ahmed.

Komawa yayi dakinsa Yana ci gaba da Kiran wayar Ahmed Baya samu Dan haka ya yanke shawarar fitowa da kansa yaja mota yakaita asibiti sedai fitowarsa harabar gidan yafara cin karo da abinda ya girgizasa.

Jini yagani a gurare daban daban a harabar gidan Wanda yake fresh da alama yanzu yanzu jinin ya zuba duk inda ya fito.

Tashi hankalinsa yayi take ya juya da sauri zai koma cikin gidan sedai ko taku Daya beyiba wutar gidan ta dauke gaba Daya abinda Bai taba faruwa dasuba a rayuwar gidan Dan haka gabansa yayi mummunan faruwa da wani irin mugun sauri ya nufi ciki Yana jefa kafafunsu cikin duhu wayarsa tini ya saketa ya dawo ga matarsa.

Acan cikin gida kuwa tini nakuda ta tasowa Amina gadan gadan a yanda take safiyya ma Bata tinanin zaa iya daukanta zuwa asibiti Dan komai yazo gab.

Babbah da Shima haka kawai ya kasa bacci duk tsananin gajiyar Daya debo Yana Jin motsi ya leqo idanuwansa suka sauka akan Omar Daya fito harabar gidan seikuma gashi an dauke wuta.

Harya koma ya kwanta saikuma ya Tina da akwai me ciki a gidan kodai nakuda ta tasowa Amina ne?

Tashi tayi batareda tinanin komaiba ya fito daidai ganin wulgawar mutane

kusa Guda biyar zuwa cikin gidan ta kofar Baya take gabansa ya Fadi Dan yasan dai gidan baa dauke wuta hakama su waye suka shiga gidan.

Shima duhun ya ciyo yayo cikin gidan Kai tsaye kofar da mutanen suna shiga Shima ita ya shiga Dan Baya tsoron barayi Sam tinda Shima ya samu damar satar zeyi idan bazaa kamasa ba.

Shigowar babbah ta kofar Baya da shigowar Omar ta kofar gaba duk basuyi nasarar rigan mutanen Isa ga dakin Amina ba inda take kwance cikin tsananin azaba.

Da kawu da Omar tare suka Isa kofar Hawa sama sedai an datseta taqi buduwa.

Da sauri Omar ya Kalli kofar Yana jijjigawa jikinsa da zuciyarsa na daukan wani irin rawa da mugun tsoro.

Kawu da baigama fahimtar komaiba cikin rawar murya yace naga shigowar mutane na biyo duk yanda Akai Barayi sun shigo gidan.....

Katsesa Omar yayi cikin wata irin rawar murya da tashin hankali da cewa

"Amina na nakuda su kadai ne aciki,
Ba Barayi bane,Amina na cikin hadarin gaske....

Kasa qarasawa yayi sbd mummunan rawar da jikinsa keyi zuciyarsa kaman zata fito sbd tashin hankali.

Waje ya koma da sauri Baya ganin gabansa Dan lalubo wayarsa,

Babbah kuwa Jin wannan mummunan tashin hankalin zancen kofar ya ringa duka Yana ambatar sunan Amina Amma kofar kaman Bango ko motsi Batayi sbd tsadanta da yanayin ginin.

Rawa jikinsa ya dauka tareda shiga tashin hankalin da Bai taba tinanin ya shigaba a rayuwarsa.

Acan waje kuwa securities Omar ke kwalawa kira Yana karade harabar gidan kaman mahaukaci Yana ihun Kiran sunan securities Yana sake Saka Kiransu Ahmed Wanda a lokacin Kiran ya shiga take suka nufo gidan cikin gaggawa da tashin hankali
Securities din gidan kuwa tsit Babu ko motsinsu bare alaman akwaisu ga wani irin duhu Dan Babu haske kona farin wata.

Amina Dake cikin wani mummunan hali Bude kofar dakin da Akai aka shigo ya Sanya safiyya juyowa da hasken fitilar wayar aminah din tana haske kofar Dan daukan Omar ne sedai mutanen data Gani ya Sanya wayar hannunta subucewa tana kallansu zuciyarta na daukan rawa da duka.

Amina kuwa ko dagowa Bata iya yiba saima sake rintse idanuwanta datayi sbd azaba sedai kafin ta Bude idanuwan daga rintsewan datai kakkaifan makami ya ratsa gefen kirjinta ya shige.

Budewa idanuwanta sukayi ahankali cikin wani sanyin azabar Daya danne na azaban nakudar datake ciki sedai kafin ta karasa budewa ya zare ya sake kutsa mata wuqar a gefen cikinta jininta ya feso masa har a fuskarsa dake rufe da black abu.

Yana Ciro wuqar daga cikinta wuyan safiyya data mutu a tsaye kawai ya soka ya zare suka juya da sauri suka fice sedai suna Bude kofar babba Dake Bakin Kofar cikin mummunan zaucewan tashin hankali sukaiwa mummunan dukan Daya zube a gurin sedai sbd karfin hali da tsananin son ganin Amina Bai sumeba duk da hancinsa Daya bare da jini take rarrafawa yayi Yana hayewa saman su Kuma tini suka fice suna ficewa Omar na dawowa sedai yaga ficewansu da gudu yabi bayansu a zauce Yana Jin tamkar ya rasa hankalinsa da tashin hankalin da batai Bata Saka masa Rana ba.

Ahmed da Aron sun Riga jamian tsaro isowa Dan haka Babu wata wtaa suka fado gidan.

A daidai kofar Baya suna kokarin ficewa Omar ya riqe Wanda yake Baya a cikinsu sedai ga mamakinsa kamshin Daya shiga hancinsa duk da Baya hayyacinsa ya girgizasa sedai kafin yayi nasarar ganin idanuwansa dasuke kadai ne a bayyane Lameenu ya daga wuqar hannunsa ya daga setin zuciyar Omar zai daba masa Aron yayi saurin janye Omar din da mugun sauri sedai cikin tsautsayi wuqar ta sauka tsakiyar wuyansa ta Baya take jininsa ya feso fuskar Omar gaba Daya ya rufeta.

Wani irin dakatawa zuciyar Omar tayi da bugawa Yana qamar da idanuwansa akan bayan Wanda yayi kusan Yana guduwa batareda iya ko motsa idanuwansa ba Dan kuwa shock ne asalin shock ya kashesa gaba Daya ga Aron a jikinsa ya sake gaba Daya.

Ahmed da hasken wutar gidan da aka kashe yake ya kunna Koda yazo mummunan ganin dayayi ya sakashi sakin mummunan ihu yana qarasawa da gudun gaske ya dauke Aron daga jikin Omar dayayi mutuwar zaune.

Mutuwar su kasim ce tafara dawo masa daki daki da yanda ta kasance,

Shin me idanuwansa suka ganar masa kaman lameenu,
Me yake faruwa ne da rayuwarsu?
Me shedan yake nuna masa?
Meyasa lokacinda su kasim suka rasu su lameenu Basu tayasu fada da wainda suka kawo musu hari ba sai daga baya,
Da gaske bacci sukeyi Koda ake fadan?
Wane bacci ne zaisa ayi kisa gabanka kace bakaji ba??
Innalillahi wainna ilaihirrajiun
Innalillahi wainna ilaihirrajiun.

Fita hayyacinsa yayi take yana Neman samun bugawar zuciya Ahmed ya daukesa da saurin gaske yayi ciki dashi cikin tashin hankali Yana tsinewa jamian tsaron Daya kira da Basu isoba har lokacin.
#MAMUH#
#MAM#LAM#OMAR#SEELAHS
#JAMAAL JEEY SEELAH
#DEEP
#HAROON SEELAH
#LOVE
#CRAZINESS
#ZAFIN KAI
#AMEENATOU SEELAH

ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*

Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#Arewabook@Mamuhgee
#ZafafaBiyar

14
KISSA TRAINING CLASS

MASU SO SU KOYI KISSA
MASU SO SU IYA KISSA
MASU SO SU SAN KAN KISSA
MASU SO SU ZAMA HATSABIBAI AKAN KISSA
GANE IDAN AN SHIRYA MIKI KISSA
KISSAN IYA KWACE DANGIN MIJI
KISSAN IYA KWACE MIJI
BA BOKA BA MALAM BAKUMA MAGANI KAWAI KISSA KADAI

ZOKI SHIGA AJIN KISSA DA NAIRA DUBU KACAL!!!

5DAYS TRAINING CLASS WANDA BABU YANDA ZA’AYI KIYI TRAINING DIN NAN BAKI IYA KISSA DA KISISINA BA.
KISSA SHİNE BABBAN MAKAMIN MATAR AURE❤
ZOKI SHIGA KAFIN KISHIYARKI TARIGAKI SHIGA

KISSA CLASS PAYMENT IS 1k
GUESS WHAT 5 LUCKY ACTIVE MEMBERS ZASU CI NAIRA DUBU ASHIRIN EACH□□□ 20k EACH
ANOTHER 5 LUCKY MEMBERS ZASUCI KYAUTAN SET NA TURAREN WUTA BY RUKY□□
ANOTHER 5 LUCKY MEMBERS ZASUCI KYAUTAN KAYAN MATA FROM HONEYDROPS KAYAN MATA□□
JOIN YANZU YOU MIGHT BE THE LUCKY WINNER

CHAT ME UP DON SHIGA WANNAN KISSA TRAINING CLASS
07012181461

****

Acan Babbah Koda yakai kansa dakin Amina daqyar Yana ganin mummunan abinda ya faru a dakin ya ke jiki yayi ya Fadi Dan Jan jiki ya Isa gareta Babu abinda Baya rawa a jikinsa ya kamota gaba Daya Yana girgiza mata Kai cikin mummunan tashin hankalin da kuka me tsananin gaske kaman yaro Yana girgiza mata Kai Yana hanata magana sedai itama bazata iya maganar ba wani irin yunkurin gaske takeyi me karfi tanason haihuwa kota halin Yaya shikuwa kukansa karuwa yakeyi sbd duk yunqurinta jini ne ke zuba kaman famfo daga inda aka soketa da wuqa Hakan Kuma nuni ne da bazata Kai labari ba.

Kuka babba keyi sosai Yana rufe raunikan nata da duk rigar jikinsa Daya cire Yana ambatar sunanta da cewa

"Aminatou karki tafi ki barni Dan Allah,
Ameenatou ki bari ni na tafi na barki Dan Allah karki sake yunqurawa Ameenatou kece abinda kadai nake da ita Ina kalla inajin farin ciki Dan Allah Ameenatou karki sake yunqurawa"

Omar ne da Ahmed suka shigo hankali tashe.

Ahmed na ganin haka yaje da gudu yazo da dayar me aikin wadda itama ta taba aure da haihuwa har biyu
Tana zuwa abinda ta gani ya Sakata rikicewa gaba Daya sedai kafin ma tayi kokarin taimkawa Amina din tini Aminar tayi wani irin yunkuri me karfin gaske saigashi ta haife cikin dayake jikinta ko numfashin yunqurin Bata sauke ba ranta ya fita.

Tsabar tashin hankali da firgicin da Maryama ta shiga da madubun da safiyya

ta fada ya fashe na dakin ta Yanke cibiyar ta dauko babyn ta fito kawo Dake tsananin kukan tashin hankali Yana ganin haka yasan Amina ta tafi tabarsa.

Kafin su karbi yar Dake hannun Maryama wuta kawai sukaga ta kama gidan.

Daga babbah har Omar akan gawar Amina suka tsaya cikin tsananin kukan tashin hankali mara misali sbd har gwara Omar yataba sheda mutuwar Yan uwansa ta kisar gilla Amma babba Bai taba Ganin wannan mummunan masifar da balain ba ganin idonsa na kisar gilla ta danyar jini.

Wuta ce kawai take sake balbale gidan Wanda ya Saka Ahmed fara janyosu daga gawar Dan ficewa daga gidan Amma Sam sun fita hayyacinsa kamanma sun zauce.

********Wutar gobarar da baasan ta Ina ita Kuma ta faro bace ta rufe gidan gaba daya hakama duk kofofin fita an rufesu.

Sosai wuyar tafara ci a cikin gidan gashi duk hanyar fita Ahmed ya nema Babu dole Omar ya dawo hayyacinsa ya karbi yarsa yanajin tsananin baqin kasacewar ranar haihuwarta ranar mutuwarta data iyayenta.

Rungumeta yayi tareda kallan babbah da gaba Daya Baya hayyacinsa ya miqa masa ita.

Babbah na karban babyn Jin yayi bazai iya barin ya rasa yar aminatounsa ba Dan haka cikin wutar ya kusa ya fice ta glass din window da duk ta yanke bayansa muguwar yanka ma kuwa.

Inda kawu ya fice tanan Maryama ta fito a nakashe itama duk yanka har a fuska.

Duk yanda Omar yaso fiddo gawar Amina Hakan Bata samuba sbd tsananin da wutar tayi Ahmed janyesa yayi ya fito dashi ta dole.

Yana ihun Kiran Aminansa Amma ba yanda suka iya.

Tsananin wutar ya Saka Jamaa tashi da fitowa sai alokacin jamian tsaron suka iso hakama fire service sun iso sedai kwata kwata baa samu damar Ciro gawar Amina da Aron ba da safiyya harma da securities dinsa da baa ganiba ana kyautata zaton Suma gawarsu na ciki Tinda Suma ana zargin Barayin hardasu suka kashe.

Fadar Mummunan tashin hankalin da jamaar Dake anguwar suka shiga a

cikin Daren bame yiyuwa bane,
Hakama Omar tini ya Yanke jiki ya Fadi Akai asibiti dashi tareda masu basa kariya sosai.

Babba Dan Maryama Babu Wanda yagansu suna fitowa suka silale Dan tseratar da rayuwarsu musamman Maryama data haukace gaba Daya ta fice hayyacinta Dan Bata taba Ganin jini kaman yau din ba da gawa harta mutane biyu.

Duk inda babba ya Saka kafa ya dauke anan take Saka tata Dan ta Ganowa rayuwarta tsira idan ta bisa kafin safe.

Shi kuwa babba gabaki Daya ya fita hayyacinsa Babu abinda yakeji yake Gani bayan Kai kansa gida da abinda Amina ta Haifa wadda haryanxu Bai tsaya ya duba me ta Haifa din ba hakama baisan sanin a raye baby take ko mace.

Tafiya sukayi sosai a cikin duhu harsuka fice daga anguwar gaba Daya batareda angansu ba daga Nan suka samu inda suka shige suka boye.

Sai lokacin ya dago babyn daga dunqular da yayi mata yana Jin motsawarta Dan tinda tayi kukan bayan haihuwarta Bata sake kuka ba tayi shiru.

Suna cikin wani mugun tsohon shagon Akai asuba aka fito.
Ana fitowa sallah suka samu abin Hawa tin akwai duhu suka nufi Tasha.

Suna Isa toilet din tashar shine yabarwa Maryama yar yashiga bayan gidan cikin tashar ya wanke jikinsa tas hadda kayansa dasuke kaca kaca da jini ya wanke ya fito kaman zai qame sbd sanyi Amma haka ya bawa kayan mintina suka Dan sha iska ya mayar jikinsa yake ya karbi babyn itama take ta wanke nata jikin ta dawo suka fara rarraba idon yanda zasuyi.

Koda gari yayi haske sosai tini labarin gaborar gidan Alh Omar jeden tafara Dan yawo sedai baa fidda maganar kisan da akaiwa matarsa da Amintaccensa Daya Aron ba sosai.

Kawu da kansa ya ari waya a tashar ya kira numbern Dadah ya aika Hafiz shagon POS da kudi masu yawa aka Aiko masa a acct din me POS Daya samu Nan Tasha.

Har kudinsa harna Maryama ya biya suka kamo hanyar gombe da jaririyar yarinyarda Allah ya taimakesu batai musu kuka ba hakama ruwan Roba kadai suketa Bata tana jikin Maryama sbd kaucewa zargi har suka kwana suka wuni a hanya suka iso.

Suna sauka Mai tsaye gida suka nufa.

Kallo Daya dadah tayi musu hankalinta yayi mummunan tashi sbd ganinsu da jinjira.

Da farko babba kasa magana yayi sbd zuciyarsa datai wani irin bushewa da nauyin gaske hakama Bai fita daga shock ba har lokacin Amma ya hakanan ya Bude Baki daqyar ya hada kalaman cewa 'yar Amina ce ta shiryata tukuna sbd tin daga Lagos har gombe zindir babyn take dunqule a zanin gadon dakin mahaifiyarta.

Rawa jikin dadah ya dauka kanta Yana Neman juyawa ta Bude Baki zatai magana Maryama ta fashe Da wani irin kuka mai karfin gaske tana kasa magana itama sbd sai alokacin ta samu kukan yazo mata.

Ita kanta Dadah fashewa tayi da kukan batareda sunce mata komaiba jikinta ya Bata tabbas Babu Amina,
Amina ta tafi gurin haihuwa kenan.

Kukan dadah ya Saka babba Dake daki ya idar da sallah fashewa da wani irin kuka Mai qarfi da tsananin radadi me zafin gaske zuciyarsa na yanka.

Tsit gidan yayi sbd kukan da kowannensu keyi me ciwo da qunci.

Dadah na kuka tana yiwa babyn wanka da ruwan zafi masu tsafta sai alokacin babyn ke fasa kuka sosai ba kakkautawa tanayi.

Tana gama mata ta dauko zaninta sabo me tsafta ta nadeta.

Babbah sosai yayi kukan da Saida yakoma Yana bawa dadah da Maryam da yayansa tsoro sosai Dan Babu Wanda ya taba Ganin ko hawayen Babbah bare kukansa hakama kowa yasan soyayyar Amina a ransa ko yayansa bayawa wannan soyayyar.

Fitowa yayi bayan Maryama taci abinci ya Bata kudi me Dan yawa ya sallameta akan itama ta kama hanyar garinsu ta tafi Daman sbd bazai yiyu tafiyarsa da jinjira tin daga Lagos bane ya sakashi tahowa da ita.

Ita kanta Maryama din matse take da Isa garinsu jos Dan haka take ta nufi Tasha komai dare gwara ta Isa nata ahalin itama.

Bayan tafiyar Maryama cikin tsananin tashin hankali da kuka Mai radadi babbah ke sanar da mutuwar da aminatu tayi ta kisan gilla jininta na kwarara a hannuwansa da jikinsa Amma Dan karfin hali Saida ta haife cikin jikinta ta

rasa tata rayuwar.

Duk abinda yaketa dannewa tin daga lokacinda ya tsaya gaban gawar Amina Jin yayi Yana yunkuro masa take ya fara amai Yana wani irin jijjiga take ya rikicewa Dadah.

Rawa jikin dadah ya dauka itama kuka takeyi haka su hafizu da Basu wuce shekaru goma Sha biyu ba zuwa Sha hudu suka kama mata shi sukai Kai daki sedai jiki Kam ba sauki.

Mota taje ta samo cikin tashin hankali suka kwashesa zuwa asibiti take akai emergency dashi zuciyarsa ta kumbura komai zai iya faruwa.

Barinsu Hafiz asibiti dadah tayi ta nufi kasuwa ta suyiwa babyn kayan sakawa guda uku da man shafawa Se Madara ta dawo gida ta sauko da ita daga bayanta ta shiryata ta bata Madara a fida kaman yanda inda ta siyo suka nuna mata tareda koya mata.

Tana gama Bata ta sake goyata ta koma asibiti.

Isarta asibiti tararda jikinsa ya sake rikicewa Dan haka itada yaran duka kuka sukeyi sosai cikin mummunan tashin hankali.

******
Acan Lagos Koda gari ya waye Omar ya fita hayyacinsa sosai ga uwa Uba mutuwar Amina data jijjigasa sosai ta taba har cikin kansa,

Jamian tsaro sun fidda gawawwakin da tini suka soye sosai Babu dadin kalla Akai jana'izansu hadda Omar din Wanda ko tsayuwa Baya iyawa a wheelchair yake komai nasa ya tsaya.

Babban tashin hankalin Daya sake girgizasa shine Nur Dake Poland ankira itama tana asibiti tsakanin Rai da mutuwa baa San meya sameta ba Amma kaman taci ko ta shaqa abinda yakeda mummunan poison dan haka tana asibiti tsakanin Rai da mutuwa.

Wannan mummunan labarin Bai wani girgiza Omar ba saima sake Sakasa akan tinanin abinda yaketa yaqi da zuciyarsa da tinaninsa ya kasa yadda wato rayuwarsa Yan uwansa ke so kome? Shin da gaske sunada Saka hannu a lamarin dayake bibiyar rayuwarsa ruwa jallo ko tinaninsa ne ke Neman lalacewa yake zargin Yan uwansa?
Idan haka ne abinda aka haifar masa tana cikin mummunan hadarin rayuwa,
Tayaya zai Bata kariyarda Babu Wanda zai tabata sbd dukiyar duniya?
Kozai rasa komai bazai taba barin wani abu ya samu 'yarsa daya tak ba da

Aminarsa ta haifar masa.

Wasu Hawaye masu dumin gaske ne suka gangaro masa Yana Jin nauyi da radadin zuciya kansa na nauyi me karfi sbd Bai taba tinanin rayuwarsa zata mutu a dare Daya haka ba harma data 'yarsa da bataji ba Bata Gani ba itada mahaifiyarta data rasu batareda sanin me tayi aka kashetan ba.,

Bai taba kawo tinanin zai samu arzikin samun haihuwa ba Amma ya nesanta kansa da abinda ya samu dan masifar daudar duniya wato kudi ba,
Tayaya zaiyi rayuwa da 'yarsa idan har Yana riqe da wannan dukiyar yasan har abada dashi da ita bazasu taba zama cikin tsaro ba Dan haka bazai bari asan ma da ita a duniyar ba bare kaiwa rayuwarta hari.

Idan har da gaske Yan uwansa ne masu bibiyar rayuwarsa kaman ta yan

Zuciyarsa kusan kasa dauka tayi take Shima ya samu attack aka sake komawa asibiti dashi cikin gaggawa.

A Daren aka Ahmed yabi jirgi ya Isa gombe ya tararda halinda babba yake ciki ya tausaya musu sosai hakama ya tausayawa Babyn fiyeda kowa a halin yanzu sbd zata taso batareda tasan mahaifinta ba bare waye shi indai har tsawon lokacinda komai zai dawo daidai.
#MAMUH#
#MAM#LAM#OMAR#SEELAHS
#JAMAAL JEEY SEELAH
#DEEP
#HAROON SEELAH
#LOVE
#CRAZINESS
#ZAFIN KAI
#AMEENATOU SEELAH

ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#Arewabook@Mamuhgee
#ZafafaBiyar

15
KISSA TRAINING CLASS

MASU SO SU KOYI KISSA
MASU SO SU IYA KISSA
MASU SO SU SAN KAN KISSA
MASU SO SU ZAMA HATSABIBAI AKAN KISSA
GANE IDAN AN SHIRYA MIKI KISSA
KISSAN IYA KWACE DANGIN MIJI
KISSAN IYA KWACE MIJI

BA BOKA BA MALAM BAKUMA MAGANI KAWAI KISSA KADAI

ZOKI SHIGA AJIN KISSA DA NAIRA DUBU KACAL!!!

5DAYS TRAINING CLASS WANDA BABU YANDA ZA'AYI KIYI TRAINING DIN NAN BAKI IYA KISSA DA KISISINA BA.
KISSA SHİNE BABBAN MAKAMIN MATAR AURE❤
ZOKI SHIGA KAFIN KISHIYARKI TARIGAKI SHIGA

KISSA CLASS PAYMENT IS 1k
GUESS WHAT 5 LUCKY ACTIVE MEMBERS ZASU CI NAIRA DUBU ASHIRIN EACH 20k EACH
ANOTHER 5 LUCKY MEMBERS ZASUCI KYAUTAN SET NA TURAREN WUTA BY RUKY
ANOTHER 5 LUCKY MEMBERS ZASUCI KYAUTAN KAYAN MATA FROM HONEYDROPS KAYAN MATA
JOIN YANZU YOU MIGHT BE THE LUCKY WINNER

CHAT ME UP DON SHIGA WANNAN KISSA TRAINING CLASS
07012181461

****
Shi kansa Ahmed wani tsananin kaunar yarinyar yakejin Yana shigarsa har cikin Rai da jininsa,

Jinin Omar abin so da girmamawa ne garesa,
Ahalin Mr Jaden Koda Baya duniya abin kauna ne garesa,
Son duk wani ahali na Mr Jaden tamkar ya tabbata ne garesu shi da Aron Wanda ya tafi Shima yabarsa,

Kaman yanda Aron ya Bada rayuwarsa Dan Bada kariya ga Omar tabbas Shima bazai taba kasa a gwiwansa ba gurin bawa Omar da abinda ya Haifa kariya ba,

Sedai kaman yanda Omar ya yanke shine idan har sunason Bata kariyar da zatai rayuwa a sake batareda tsoro ko fuskantar hadari da barazana ga rayuwarta data Wanda take hannunsu shine barinta a hannun Babbah tareda yin nesa da ita tareda Yanke alaqa dasu gaba Daya har sai ranarda komai ya fito fili ya tabbatarda abinda yake zargi akansu tinda Babu hujjoji manya a hannunsa.,

Wannan shine babban gatan da zaiyiwa 'yarsa ya Bata kariya shine Yanke alaqa dasu batareda duniya tasan shine ya haifeta ba,

Batareda duniyama tasan yanada 'yar da zata gajesa ba.

Rungume babyn a jikinsa Ahmed yayi tareda Jin kaman ya tafi da ita ga mahaifinta da zuciyarsa ke cikin tsananin qunci me nauyin gaske akan rashin mahaifiyarta da ita,

Wayarsa ya fiddo ahankali ya Saka Kiran Amintaccen Daya baro a asibitin gurin Omar da securities masu tsananin gaske yace ya bawa Omar wayar.

Duk da Yana cikin wani irin mawuyacin hali ya amsa wayar sbd sanin me Hakan ke nufi.

Ahankali cikin sauti mara karfi da sanyi da nutsuwa yakewa yarsa huduba ta cikin wayar da Ahmed ya Kai kunnenta sautin muryar mahaifinta na shiga kunnan ahankali.

Da sunan mahaifiyarta ya kirata bayan hudubar wato AMEENATOU OMAR JEEDEN SEELAH.

Yana gamawa Hawaye masu radadin gaske suka sauko daga idanuwansa daidai Nan ya kashe wayar tareda lumshe idanuwansa yanajin bazai taba warkewa daga wannan quncin baqin cikin da aka jefa rayuwarsa ba kaman yanda bazai taba yafewa duk Wanda yakeda Saka hannu a cikin duk kowace kisar da akaiwa Yan uwa da iyayensa harma da matarsa da 'yarsa da aka tilasta masa rabuwa da ita ba Koda kuwa su Lameenun ne da gaske.

Ahmed baicewa Dadah komai ba Saida ya miqa mata AMEENATOU kafin ya sauke jakar dake rataye a jikinsa ya miqa mata ya Bude bakinsa da yayi nauyi ya sanar da ita maganar data qamar da ita daga tsayen tareda dorawa da kalmar

"Allah ya Raya AMEENATOU"

tana kallonsa kaman gunki harya bacewa ganinta ya fice daga asibitin gaba Daya.

Yana fita Kai tsaye a ranar ya juya ya koma sbd Bai yadda da kowa a tareda Omar ba yanzu idan ba kansa ba.

Ko da ya Isa cikin dare Kai tsaye asibitin ya nufa ya tadda jikin na Omar ya sake rikicewa hakama ga babban mamakinsa Alh Lameenu seelah harma da Mam seelah ya diro qasar suna asibitin harma da iyalansu cikin mummunan tashin hankalin da damuwa me tsananin gaske data Saka zuciyar Omar kasa dauka take yaji zuciyarsa na Neman fashewa da yanda suke nuna baqin

cikinsu akan abinda ya faru da damuwa shiyasa jikinsa ya rikice.

Abinda yake sake taso masa yaji kansa na Neman bugawa shine sauyin securities da ko yaushe akeyi masa Yana daukan tsananin kulawa ne Ashe na daukan ransa ne.

Kaman yanda Basu nuna komai na haka ya danne nasa baqin cikin yana fatan samun lafiyarsa data Nur tukuna yasan ta yanda zai fara bincike akansu Dan kuwa mutuwar kasim data aminatu itace mutuwa mafi zafi dasukaiwa Yan uwansa.

Ahmed ma Sam Bai nuna komai a fuska ba saima Shirin barin kasar a take Daya fara yiwa Omar Dan ko zasuyi bincike bazasuyisa Omar na kusa dasu ba Dan akwai hadari me girma tattare da Hakan,
Hakama idan a hukuma zasu miqa zancen meye hujja ko evidence nasu Kuma maganace akeyi ta cikin gida me duniya zata fada akan Omar idan Kai tsaye ya fito ya fada Yana zargin Yan uwansa na jini akan kisar matarsa da Yan uwansa a Baya batareda yanada hujja ba.

Ahmed Bai fadawa kowa kasar zasu bari ba shi kadai ya gama shirye shiryen komai hakama washe gari dukkanin abokan kasuwancin Omar take ya hada meeting na gaggawa dasu ya sanar dasu barin Omar kasar kwata kwata Dan haka dole a nada sabon president a kamfaninsa.

Ta bangaren kadarorinsa kuwa duk masu kulawa dasu ya qara musu tsaro da ma'aikata.

Su mam irin kulawan da suke bawa Dan uwansu tareda tattalawa yasa Shima duk da baida lafiya sosai yake nuna Jin dadinsa Yana jinjinawa kaunar da suke masa sukuma Hakan na sake musu dadi sosai ba qaramin tashin hankali suke ciki ba na Lameenu dayace kaman Omar yaso ganesa Dan haka suke ta bibiyar Omar din da kulawa me tsananin gaske Dan su Gano idan ya fahimci wani abin Amma basuga alamar Hakan ba dan sosai yake nuna musu Jin dadinsa akan kulawansu da kaunar junansu na asalin jinin Seelahs.

Basu San da tafiyar ba sai ranarda su Omar din zasu wuce ya sanar dasu zai koma Poland sbd jinyar kansa da Nur da har lokacin take kwance ba sauki.

Kallan juna sukai a sace zufa na Dan jiqa Alh Lameenu ta cikin tsadaddiyar shaddar Dake jikinsa kansa ya Dan Sara Dan kuwa idan har Omar ya tafi me Akai kenan?

Su da suke fatan daga asibitin Nan sai barzahu sbd sun gama kammala komai a asibitin mutuwar tsafta zeyi irin tsarin mamman seelah,

Banbanci Aikin mamman da lameenu shine shi mamman Baya aikin gilla sbd ya tsani Bata jikinsa ko hannuwansa da jinin Wanda ya kawar,
Koyaushe yafison neat aikin da bama zaa San wani ne yayisa ba,
Zai aikaka batareda ko kadan ansan wani ne yayi Hakan ba shiyasa duka ayyukansa dayayi da kansa suke neat ba zargi ba hukuma ba komai,

Ko a qasar turawa dasukeda bincike aikinsa neat ne,
Tin daga kan sirikinsa mahaifin Dr Aleena har sirikarsa da Mr Jaden babu Wanda zai taba kawo tinanin kisa ce ba mutuwar Allah ba Dan haka Babu wani bincike Daya hau kan mutuwarsu komai nasa a natse hankali kwance yake yinsa shiyasa ya masifar iya takunsa ko a gurin mutane anfi ganin girmansa da mutuncinsa ake masifar girmmamasa Dan ya iya Jan zarensa cikin aji da dubara.

Sabanin Alh Lameenu da shi Kai tsaye yakeyin Abu Babu kwana kwana Babu sauki ba sassauci idan zaiyi aiki da kansa na danyar jini yakeyi Dan kuwa shi jini ne zaa zubar ba Imani ba tausayi bare gudun abin zaije ya dawo shiyasa ma ya buqaci ko yanzu yayi aikin Omar da kansa sbd tabbatarda matsalarsu tazo karshe yasan shine ya kawar da ita matsalan da kansa abinda yake zuciyarsa na shekaru ya fada masa yaji sanyi.

Maganar tafiyar Omar ta girgizasu musamman mamman da yanzu ne yake buqatan daukaka kansa sbd yayansa dasuke gab da Isa riqon dukiyar mahaifinsu su zama matasan da Suma zaa ringa ambatar sunansu da mutuntawa a matsayin yayan Alh Mam seelah,
Hakama babban fargabar Mam itace Omar na komawa Poland 'dansa dayake jiran ya gama karatunsa ya dawo dashi hannunsa Hakan bazata yiyuba sbd matiqar Omar da Mum dinsa na guri Daya Jamaal bazai taba dawowa Nigeria gurinsa ba shikuwa yanzu Yama fi Jin tsananin so da kaunar Jamaal a tareda shi fiyeda Haroon Dake tareda shi sbd Jamaal Dake nesa yafi shiga ransa sabanin Haroon da kullum suna tare.

Lameenu kuwa shi a yanzu yafi buqatan rayuwar Omar din fiyeda dukiyar tasa,
Idan Omar yabar duniya shine zaiji ya samu nutsuwa sbd ya kasa yadda da Omar Bai ganesa ba yaqi nunawa ne kawai Dan haka shi yanzu asirinsa baa rufe yake ba matiqar Omar na duniya gashi Yanxu Yana maganar yabar inda suke ganin duk wani motsinsa zai tafi inda basa ganinsa Dan haka komai zai iya faruwa Dan haka hankalinsu su dukan baa kwance yake ba da tafiyar.

Ga babban mamakinsu da shock dinsu kafin suyi wani yunkurin rarrashinsa su hanasa tafiyar a ranar ma jirginsu zai daga Ahmed Babu Bata lokaci ya buqaci securities aka rakasu har airport suka daga.

Su Mam Basu sake shiga tashin hankali da firgici ba Saida suka samu tabbacin ba Poland Omar ya koma ba Nur ma tini aka bar Poland din da ita Ashe Kuma daga Dr Aleena har Jamaal Babu Wanda yasan kasar da suka koma Dan Ahmed baibar kowace irin clue ta inda ma suka tattara suka koma din ba sbd Yana buqatan lafiyar Omar da Nur ayanzu fiyeda komai da nutsuwa da samun Kwanciyar hankalisu su dawo daidai tukuna kafin su fuskanci komai.

Kaman bacewar hayaqin Daya tashi sama haka suka bacewa kowa bat Babu labarinsu,
Duk wainda suke communicating dasu Yan amanar asalinsu ne da ko zasu mutu bazaka ji sirrin Omar a bakinsu ba.

Shi kansa Jamaal hankalinsa tashi yayi sosai da Hakan sedai mum dinsa ta kwantar masa da hankali tareda basa tabbacin duk inda Omar yake ya kebance kansa ne Dan bawa kansa kariya da damar samun lafiya tukuna duba da abinda ya samu iyalinsa a lokaci Daya.

Wanna ya Saka hankalin Jamaal Kwanciya Badan ya Dena binciken inda Dad Omar din yake ba.

Su Mam kuwa tini hankali ya tashi musamman da suna zaune cikin damuwa da tsananta binciken akan Neman Omar da kwata kwata ya Yanke kansa daga kowa hatta su duk alaqa da kusancinsu suna matsayin Yan uwansa Bai nemesu ba ya datse hadda su kenan Hakan ya tabbatarda Kila yasan wani abun gameda su kenan ko me?
#MAMUH#
#MAM#LAM#OMAR#SEELAHS
#JAMAAL JEEY SEELAH
#DEEP
#LOVE
#ZAFIN KAI
#AMEENATOU OMAR JEEDEN SEELAH
#ROM

ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap

Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
16
*Turaren wuta da exculsive gyaran jiki course*

Assalamu alaikum yan'uwana mata, a yau na kawo muku sana'a mai matukar riba wanda kina zaune a gida zaki yi, kudade na shigo Miki

Baya ga haka akwai abubuwan gyaran jiki masu yawa da
Wannan course din zai koya Miki, anyi shine musamman saboda samarwa mata sana'ar yi suna daga gida ba tare da sunje ko ina ba.

Da labarci muce *bakhoor*
Da Turanci muce *incense*
Da Hausa muce masa *turaren wuta*

Abubuwan da zaki koya a idan kika siya course din.

Zaki koya yanda ake hada turarenwuta kamar haka:

- Turaren wuta na ko wane irin icce mai hadin sugar.
- Turaren wuta marar hadin sugar
- Turaren wuta irin na Yan Senegal
- Turaren wuta irin na Yan Yemen
- Turaren wuta na wardrobe
- Turaren wuta na gari
- Humra fara
- Humra baqa
- Room freshener
- Mopping mist

Abubuwan da zaki koya a gyaran jiki:

- Halawa
- Body cleanser
- body scrub
- hadin kurkur
- hadin dilka
- turaren jiki
- dilka body wash
- dilka body oil

Duka wannan zaki koyesu ne a farashi mai sauki kan 20k kacal.

Sannan Bayan wannan akwai bonuses kamar haka:

- Yanda zakiyi branding kasuwarki

- Yanda Zakiyi packaging

- Yanda zakiyi ma kayanki kudi

- zaki samu littafin da zai koya maki yanda zakiyi kasuwanci online (WhatsApp)

- Zaki samu number mai siyar da kayan turarenwuta na 'yan maiduguri da

kuma mai siyar da kayan turarenwuta na 'yan sudan.

Banda bonuses, duk lokacin da akayi upgrading course din, wato aka qara sababbin abubuwan qamshi zaki same su kyauta ba tare da kin qara biyan ko sisi ba. Saboda za'a qara koya wasu abubuwan nan gaba.

Idan kika siya wannan course din Zaki samu sana'a wadda zakiyi a gida, zaki koya kina daga gida, kina daga daki a kwance.

Idan kika siya wannan course din Zaki San sirrika na hada turarenwuta da kayan qamshi masu dadi. Zaki koya abubuwan da ba kowa ya sansu ba.

Idan kika siya wannan course din Zaki samu contact na masu siyar da kayan turaren masu inganci ba irin Wanda ake masu hadi da wani abun su rage qamshi ba. Zaki samu masu siyar da kayan turaren wanda ba algush sannan kuma ba tsada.

Idan kika siya wannan course Zaki samu access da support group inda a ko da yaushe kike neman wani taimako wajen hada turare, ko kina son kisan wani abun za'a fada maki.

Idan kika siya wannan course din, zan taimaka maki wajen gina kasuwancinki mai inganci ta hanyar baki shawarwari da kike buqata.

Idan kika siya wannan course din ko baki da jarin siyan kayan turare Zan nuna maki hanyar da zaki samu Jari mai tsoka wanda zai isheki kiyi kasuwarki hankali kwance.

Idan kin shirya siyan wanna course ɗin, ki min magana ta WhatsApp a 07082281566.

****
A gombe kuwa Koda Babbah ya samu kansa ya farfado cikin Dan saukin Daya samu dadah tayi kukan Daya sauya kamannin fuskarta harta gaji,

Tayi kukan rashin Amina,
Tayi kukan tausayin babyn da Amina ta bari,
Tayi kukan tausayin Babba da yanda zai rayu cikin quncin da har abada bazai bar zuciyarsa ba na rasuwar Aminansa.

Kallo Daya Babbab yayiwa Dadan cikin ciwo yaji zuciyarsa ta sake samun rauni,
Yar datake rungume a jikinta ya kalla kafin ya miqa hannuwansa Dake wani

irin rawa da rashin karfi yace ta doro masa ita.

Hadiye hawayen idanuwanta tayi kafin ta matso ta Dora masa babyn Daketa baccinta hankali kwance.

Rungumeta yayi jikinsa Yana tina ranarda mahaifiyarsa ta haifi Amina ta rasu ta bar masa ita a hannunsa a rungume,

Cikowa idanuwansa sukai da hawayen da suka kasa riquwa Saida suka gangaro kan fuskarsa data fada lokaci Daya kaman ya Dade a kwance Yana jinyar.

Gawar Aminansa ce ta dawo a idanuwannsa lokacinda take cikin jini Tako ina a jikinta.

Sake rungume babyn yayi Yana Jin duk wata so da kaunar dayake wa Aminansa ta ninkuwa so Babu adadi akan 'yar Dake hannunsa,
Idan Yana yiwa Amina kauna ninki dari to yana Jin yanawa 'yarta so dubu,
'yar hannunsa kyauta ce da Allah ya basa bayan ya amsar masa Amina,
Duk Wanda yakeda Saka hannu a kan mummunan kisan da akaiwa Aminarsa to matiqar zai sansan bazai taba barin yayi mutuwar mutunci ba Amma tinda Allah ya bar masa abinda Amina ta Haifa Yana yiwa Allah Godia hakama bazai taba barin ko wani Mai sunan Omar ya kusanci wannan yar ba bare wani abin ya sameta kaman yanda ya samu mahaifiyarta.

Sakon da Dadah ta sanar masa akan Omar ya buqaci da har abada idan bashine ya nemesu ba kada su taba fadawa duniya ko kowa cewan 'yarsa ce wannan ba,
Kada su taba barin asan waye mahaifinta koma tanada hadi da jininsa gaba Daya idan har suna son tseratar da ita su Bata kariya to su Yanke alaqa da komai Daya danganci ko sunansa ga wannan 'yar.

Wainnan kalaman sune sukai tsananin tarwatsa zuciyar Babbah fiyeda radadin dayake ji,
Shi dayake jiran bayanin dalilin mutuwar yar uwarsa a bakin Omar din shine zai Yanke alaqar komai dasu tareda Yanke alaqa hadda ta sunansa akan yarsa.

Wani nauyi kirjinsa ya dauka tareda zafi me tsananin gaske,

Dago babyn yayi daga kirjinsa ya Kai bakinsa kunnenta yayi mata hududa Shima a hankali cikin so da kulawa me tsananin gaske kafin Shima ya Bude Baki ya ambaceta da sunan AMEENATOU NUHU BABBAH batareda yasan sunan da mahaifinta Shima ya kirata dashi ba kenan na mahaifiyarta Dan

haka yarinya taci sunan mahaifiyarta AMEENATOU
Banbanci kawai shi mahaifinta ya kirata da AMEENATOU OMAR JEEDEN SEELAH shikuwa Babbah ya ambaceta da AMEENATOU NUHU BABBAH.

duk wani taurin zuciyan Babbah da rashin hakurinsa dawowa yayi sabo fil a take Dan haka da karfin hali ya kwana gari na wayewa yasa aka sallamesa batareda ya warke yanda ya kamata ba Amma yanda yakejin zuciyarsa idan ba abinda zuciyarsa keso yayiba zai iya samun bugawar zuciya Dan haka Kai tsaye gida suka nufo.

Suna dawowa wanka kawai yayi ya fice daga gidan.
Bai dawo ba sai dare.

Yana dawowa ko abinci Bai iya ci ba ya shige dakinsa haka suka kwana jigum jigum kaman gidan zaman makoki.

Da sassafe sai ga baqi sunzo gurinsa.

Dadah na daki tanaji Akai cinikin gidan aka Kai karshe batareda tsayawa lissafin komaiba Babbah ya sallama gidan take aka Saka masa kudin a banki tareda rubuce rubuce da shedu ya miqa takardun gidan.

Suna wucewa ya sanar da Dadah duk abinda sukeyi a siyar da komai yau washe gari zasu bar garin.

Da farko hankalinta ya tashi Amma duba da yanda komai yake tafiya da abinda ya faru itama taji zatafi samun nutsuwa Subar inda aka Sansu su koma inda Babu Wanda ya Sansu su Gina sabuwar rayuwa tareda Ameenatou Dan Bata cikakkiyar rayuwar yancin data cancanta.

Tin a ranar suka fara shirye shiryen barin gari sedai Basu samu wucewa washe garin ba Saida Babbah yayi tafiyar kwana shida ya dawo yaje ya Siya musu gida a inda Babu Wanda ya Sansu Kuma baa birni sosai ba a local government sbd samun nutsuwa.

Sunyi bankwana da makota da abokan arziki da kasuwanci sun bar garin gombe batareda sanarwa kowa inda zasu komaba sbd ita kanta Dadah babban Bai sanar da ita ita zasu koma dinba sbd tsaro sedai sunje ta Gani.

Tafiyar wuni guda Mai Nisan gaske sukai sai gasu a wani garin da Dadah Batama tantance sunansa ba Amma dai akwai Fulani sosai a garin dayake a gajiya sosai Bata damu da tsayawa tambayar babban ba gashi dare yayi Dan haka Kai tsaye Dan karamin gidansu Daya Siya musu suka Isa Wanda yake

sabo ne daidai misalin rufin asiri Kuma ya Siya komai ya zuba tin daga kan katifun Kwanciya da Yan abubuwan amfani.

Ruwan zafi ya fita ya siyo sukasha shayi da bread sai indomie,
Hakama ya sake fita ya samo ruwan zafi a gurin me shari Wanda bana shayin ba akaiwa Ameenatou wanka aka gasata sosai sauran su Hafiz suka sukai wankan,
Shima babban wankan yayi Dana sanyi itama dadah Dana sanyi tayi
Dayake sun Riga sunyi sallolinsu tini suka kwanta sai baccin wahala da rashin dadin Rai.

Washe gari duk wani sauran abinda basuda Saida ya fita ya siyo musu shi ya kawo,
Abinci ma haka ya Siya Wanda zai Dade musu Bai qare ba ya ajiye,

Bai taushe hannu ba ya bazama yaje ya nema makaranta ya Saka su hafiz a a biya kudin da komai daga bokon har Arabic sbd so yake Kai tsaye ya fuskanci rayuwarsa shida iyalinsa,

Kayan baby Ameenatou kuwa tin daga kayan sakawa har Madara da abubuwan buqatanta Babu abinda Bai siyo ba Dan haka dadah itama ta sake jikinta yanda ya kamata tana kulawa da ita tamkar ma itace ya haihu Dan duka makota da Wanda suka ringa shigowa suna gaisawa sun dauka itace ta haihu din itama Bata Musa din ba sai aketa mata barkan haihuwan ana tambayar sunan yar.

Dayake baai mata yankan suna ba sai da sukai kwana biyu sun gama hutawa da gyaran gidan kafin Babba ya yankawa Ameenatoun tasa rago Akaci Akai sadaka.

Tin dukkaninsu sunata fama da kadaici da bakunta har suka fara sabawa tini dadah tafara Yan sana'ointa data Saba Yara ma sun fara zuwa makaranta tini,

Babbah ma shago ya Bude a kusa ba nesa ba na siyarda hatsi Dan haka suka dauki hanyar zama Yan gari musamman Babbah Daya danne komai ya koma babbansa na Baya sbd kawai su zama cikin farin cikinda idan Ameenatou ta tashi itama zata tashi cikin farin ciki tsakanin iyayenta Dan baida niyar tasan basune asalin wainda suka haifetaba duk da sunyi mata tsufa a iyayen Amma dai sune suka haifetan kawai.

Dan haka ahankali suka nitsa rayuwa na tafiyar dasu cikin Kwanciyar hankali da amince Dan tini ya rufe Babin Omar a rayuwarsa data iyalinsa Dan kuwa bayajin har abada zai bari Omar ma yasan inda suke bare tinanin ma yanada 'ya a hannunsu.

****
Lagos

Zaune suke duk inda jini yake yawo a jikin Mam seelah tafasa yakeyi Yana Jin kaman kansa zai rabe sbd baqin ciki da damuwa.

Shikuwa lameenu tini yafara ficewa hayyacinsa sbd kansa Bai sake cikakkiyar lafiya ba tinda lamarin Nan ya faru sbd ya kasa tantance gaskiyar abinda yake gudana a Kai da zuciyar Omar Wanda har lokacin baida alaqa da kowa Babu labarinsa.

Ga dukiyar dai ya tafi yabarta kusan a hannunsu Dan duka kadarorinsa yanzu kusan a hannunsu suke amman Sam basuda nutsuwan cinsu tinda basuda tabbacin Shirun nasa na Menene,
Amma dai ko na Menene Abu Daya suka tabbatarda shi shine fitowarsa Koda zasuyi gaba da gaba ne saisun kar karshen matsalarsu Dan yanzu rayuwarsa ma itace abin buqatan tinda yasan Menene sukai masa.

Shigowar BB babban Dan hannun damarsu Mam dinne ya Saka Lameenu dagowa da idanuwansa dasukai ja ya kallesa kafin yayi magana cikin girmamawa BB ya Kalli Lameenun kafin ya Maida kallansa kan Mam Yana Dan sauke Kai cikin nasa zafin zuciyar da fargaban abinda zai fada yace

"Ranka ya Dade binciken da muketa son tabbatarwa akan gawawwakin da jamian tsaro suka fitar bayan kashe gobarar gidan gaskia ne gawa uku kadai aka samu daga cikin gida sai gawar security dinnan Daya daga waje bayan Kuma idan aka cire Sir Omar da Ahmed gawa BIYAR ya kamata a Gani a cikin gidan.....

Wani mugun zufa me zafin gaske ne ya tsinkowa lameenu kansa na sarawa
Shikuwa Mam wata mummunan sarawa kansa yayi ya dauki ruwan Dake gabansa yakai bakinsa Yana Sha sbd Jin koina jikinsa kaman Yana ci da wuta.

Dan gyara tsayuwa BB yayi Yana kallan Lameenu Daya zuba masa ido Yana jiran sauran bayanin yaji Shima wani zufa ya tsitsifo masa sbd abinda zai fada yace

"Cikin gawawwakin da aka samu an samu tantancewa da tabbacin akwai ta matar sir Omar din Amma Kuma Babu ciki a jikin gawar Wanda ni Kuma ta tabbatarda naga tsohon ciki a tareda ita a Daren.....

Ruwan da Mam ke Sha ne suka dawo ta hancinsa gaba Daya ba shiri sbd mummunan tashin hankalin da Bai taba Jin irinsa ba.

Lameenu kuwa take bugun zuciyarsa ya Nemi tsayawa cak sbd firgicin da Bai taba samun kansa ciki ba.
#MAMUH#
#AMEENATOU
#DR J SEELAH
#DESTINED
#LOVE
#ROMANCE
#LIFE
#REVENGE
#HAROON SEELAH
#IDENTICAL TWINS
#ZAFIN KAI
#THE SEELAHS

ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
17
Shi kansa BB zufan yaje hadawa zuciyarsa na tsalle Dan yasan ansamu babbar matsala data jawo musu wani Sabon aikin me girma daban.

Mam kuwa bayan ta hanci da ruwan suka biyo bar cikin kansa sukai yaji Yana Neman zaucewa da sauri ya dago idanuwansa da suka sauya take zuwa jajir ya Kalli BB dukkanin jikinsa na Neman sakewa daqyar ya hado kalmomi a bakinsa cikin sanyi da nutsuwan son fahimtar komai daki daki yace

"Wane ciki kake Bada tabbacin ka Gani a jikin matar Omar?
Na haihuwan Dan mutum kokuwa na samun qoshi datai a gidan??".

Kansa ya saukar kasa bayan ya Kalli lameenu Wanda shi kwata kwata Neman rasa gane komai yakeyi
Ya Dan sake saukar da kansa qasa yace

"Tabbas cikin haihuwa ne a jikinta,
Kuma kaman yanda Daya daga cikin securities dinmu Dake ganin gidan ya tabbatar mana tabbas tana daukeda juna biyu tsoho matar Sir Omar din..

Hakama a Daren Koda muka shiga ni naga cikin da idanuwana sedai abinda yasa ban fada ba na dauka ba amfani tinda itada cikin sun tafi kenan sai gashi ance Babu ciki a jikin gawarta hakama baa samu gawar baby Koda konanniya ce a gidan,
Gashi Babu sauran mutum biyu Daya kamata Suma ace an samu gawarsu a gidan,

Dame aikinta Daya Wanda kowa ya tabbatarda masu aikinta biyu ne hakama a Daren ranar shi Sir Omar din yayi baqo Wanda bamusan ko wayeshi din ba a gun sir Omar din
a cikin gidan ya kwana muma da idonmu mun gansa mun sumar dashi Amma baa samu gawarsu ba.....

Jinin Mam da lameenu wata irin qunar masifaffen tashin hankali sukeyi musamman Lameenu da idanuwansa suka rufe baiga cikinba da Saiya tabbatarda a tsakiyar cikinta zai kutsa azabbiyar wuqarsa me barka kayan cikin mutum ya tabbatarda mutuwar haihuwar magaji ko magajiyar Omar jeden seelah.

Mam kuwa a Karan farko da zufar tashin hankali mara misaltuwa ta rufesa sbd babbar babbar uwar matsala da budaddiyar masifa ta riga ta fadowa rayuwarsu tinda Omar ya rufesu akan samun haihuwarsa hakama idan har Babu ciki a jikin gawa Kuma Babu gawar baby a gidan to ta tabbata Omar ya boye abinda aka haifar masa hakama idan ya boye abinda ya Haifa Hakan na nufin ya San wani abu Dan bazai yiyu Babu komaiba Omar ya boye musu haihuwarsa ta farko daya kamata ace sune sukaiwa abinda aka haifar huduba Dan shine kaf yakewa nasu yayan huduba.

Wace sabuwar masifar ce wannan ta bullo musu?
Me Lameenu yayi?
Tayaya zaace yaje yayi aiki irin wannan da kansa Amma ya kasa tantance ciki a jikin Amina..

Cikin wani irin mafi girman tashin hankali da sake jiquwa a zufan gaske duk ac Daya gama cika palon Lameenu yace

"Kenan nakudar haihuwa takeyi a Daren Kokuma wani abin na damunta sbd a dakinta me aikinta Daya take tareda ita hakama Shima Omar ya fito a cikin Daren har harabar gida..... innalillahi wainna ilaihirrajiun.

Wani kallan baqin ciki da tashin hankali Mai tsananin gaske Mam yayiwa Lameenun Yana Jin inama dashi su BB suka hada suka kashe cikin duhun ya huta da baqin cikin dayake ji yanzu akan wannan shirmen da baqar ranar Daya nuna musu Dan samun haihuwan Omar itace babbar baqar kaddarar data sake Hawa kansu tinda Babu yanda zaayi ko sun kashe Omar dukiya ta zama tasu yanzu yanada me gadons gaba Daya,

Kashe Omar batareda sun tabbatarda sun gane inda abinda aka haifar masa yake ba kaman aikin banza ne Dan haka dole saisun fara kawar da magaji ko magajiyarsa sun tabbatarda babu me gadonsa bayansu kafin su kawar dashi,

Gaba Daya yanzu lameenu ya jiqa masu aiki ya dawo musu dashi Baya,
Ta Ina zasu fara da sanin inda ma zasu Gano mutanen biyu Dan idan ma akwai haihuwan ko Babu a bakinsu zasu tabbatarda komai a zahiransa.

Lameenu ma Jin yayi zuciyarsa da gangar jikinsa na rawa sosai akan ta inda zasu fara Neman wannan haihuwar da itace tayi musu shamaki yanzu da cikar buri bama Omar din ba Dan kuwa shi fitowarsa kadaice ta shiga tsakaninsa da mutuwarsa Dan kawar dashi ya zama dolen dole tinda yasan komai dabai kamata ya sani ba akansu.

BB kansa ma cikin baqin ciki da zafin zuciyar samun wannan babbar matsalar a aikinsu yakeji duk da yanzu ko zasu rayukan mutane dari saisun Nemo inda mutum biyun Nan suke Dan wannan Karan Mam seelah ne da kansa sai cike aikin batareda barin matsala ya kawar da matsalarsu.

Dayake Lameenu yasan shine ya Bude kofar wannan sabuwar masifar data samesu Kuma yasan Mam Bai taba samun matsala a abu ba idan ya tashi aiwatarwa a natse yake cikakkiyar aikinsa ba damuwa Dan haka duk yashiga damuwa kan tashin hankali Amma dai koma yayane yasan bazasu taba samun baccin nutsuwa daga Nan har shekaru masu zuwa matiqar Mam Bada hannunsa ya kawo karshen jinin Omar ya batar dashi a duniya ba.

Babban arzikin Omar yaci shine Basu taba sanin qanwar mijin Ayshatu kanwar kasim yake aure ba,
Hakama Basu taba sanin waye ma mijin Ayshatu din ba bare inda yake Dan haka suka bazama sakin mahaukaciyar dukiya Baji ba Gani Mai aikin gidan Omar jeden suke nema da baqonsa,
Amma dai me aikin sukafi Maida hankali nema itada aka sani sbd shi baqon haryanxu basuda tabbacin wayeneshi?
Daga Ina yake?
Meye alaqarsa da Omar din?
Yaya kamanninsa suke?
Dan haka Maryama suke nema ido rufe Baji ba Gani,
Ta bangare Daya kuwa su aje matsalar Omar a gefe saisun gama data abinda ya Haifa din Wanda suke da tabbacin Yana sane ya boyesa koma inane sbd kada su sani.

**********Ahankali ahankali Suma cikin tsananin rashin Kwanciyar hankalin zuciya da tsananin son cikar buri lokaci da shekaru suka ja musu batareda sun samu sanin inda Maryama take ba Amma dai Basu taba cire Rai kona daqiqa bane daga tsananta bincikensu Wanda duk tsawon shekarun da aka

dauka wannan burin koyaushe karfi da zaquwa yake qarawa ransu sbd kullum dukiyar Omar tamkar hakin da ake bawa ruwa takeyi sai yaduwa take sake yi tsananin Sonta da maitarta na karuwa ransu tana yaduwa a jini da gangar jikinsu tareda tsiruwa a zuciyarsu duk kuwa da daukaka da tarin arzikin da Suma suketa qaruwa a rayuwarsu.

****

Shekaru sun tafi a yanzu Sunan SEELAHs Babu inda Bai shiga ba Dan kuwa sunyi wata irin kafuwar da Babu Wanda zai iya girgizasu idan ba ubangijin Daya Basu ba,

Sunyi suna me karfin gaske,
Sunada power fiyeda yanda ake tinani,
Sune masu fada aji,
Masu taka Wanda suka so,
Masu yin yanda suke so,
Nera da dollar sun zaunu a SEELAHs kaman basusan meye matsala ba a rayuwarsu,

Tin shekarun da suka gabata suka tashi daga inda suke suka sauya anguwar datafi kowace anguwa tsaro da tarin asalin masu nerar data amsa sunanta nera,

Kaman yanda gidajensu suke a jere acan Baya hakama yanzu mansions dinsu a jere suke guda uku sbd duniya su uku ta sani haka zasu cigaba da zama su ukun har sai Omar yabar duniya Dan haka Koda suka tashi barar da dukiya aka Gina mansions din da Omar sukayi duk da har lokacin Bai taba dawowa Nigeria ba duk da ya bayyana Amma inda yake rayuwa yanzu komai dukiyar dasuke ji Dan ita Basu Isa su tinkaresa da matsala ba a gurin sbd shi kansa ya goge sosai yanzu baida wani sanyi ko kawaici kaman Omar din Baya sosai yake tafiyarsa business dinsa da rayuwarsa batareda ya waiwayo Nigeria hakama Yana sane yaqi waiwayo yarsa yafison yagama ganin gudun ruwan Yan uwansa Dan Yana bayyanarda ita zata zama cikin hadari duk tsaron dayakeda shi bazai iya wasa da rayuwarta ba ya daukota ba Dan yasan ko Babbah zai rasa ransa Yana can Yana kulawa da ita cikin Kwanciyar hankali da tsaro musamman dasuka samu tabbacin su kawun sun bace Babu me labarin inda suke duk bincike kuwa su kansu Basu Gano inda suke ba Dan haka ma ya kyalesu sai koma ya lafa zai nemeso duk inda suke.

****

DR JAMAAL SEELAH Wanda aka Fi sani da DR JEEY SEELAH matashin likitan daya qware sosai a aikinsa,

Likita ne da ba iyayensa kadai ba dukkanin mutane suke tsananin alfahari dashi sbd qwarewansa akan aikinsa duk da ta bangare Daya mutum ne Mai tsananin zafin Kai da Baya daukan reni barema kallan kadai idan kayi kaine kake Rena kanka sbd asalin abinda ake kira da kwarjini da Asalin class me sakaka kama kanka kawai daga ganinsa.

Duk duniyarsa mutum uku ne kadai suke ganin Asalin dariya ko kyakkyawar murmushinsa Dake kashe me kallansa,

Daga mahaifiyarsa Rabin ransa da Babu Wanda ya Kai masa ita a duniya,
Sai 'dan uwansa Rabin jikinsa Barr Haroon seelah sai patients dinsa Suma ba duka ba,

Bayan wainnan ko mahaifinsa dayake tsananin sonsa fiyeda duk abinda ya mallaka Baya ganin wainnan abubuwan daga garesa.

JEEY SEELAH shine Asalin definition na SEELAHs kaman yanda Dad dinsa me fada sbd rashin tsoronsa da zamana Dan Kai tsaye hakama reni Baya tinkarosa,
Izzarsa da nutsuwarsa tareda class me sanyi ko su iyayensa sun shafa masa lafiya kwarjininsa suke Gani suna daga masa kafa ba kamar Haroon ba duk da idan ba nutsuwa kayi ka tantance kamewan JEEY ba kwata kwata haryanxu baka taba ganesu sbd kamanninsu sosai suke sake kamewa Dana juna.

DR JEEY SEELAH shi gaba Daya kusan rayuwarsa a Poland yayita da mahaifiyarsa harya gama karatu ya fara aiki acan kafin ya tattara ya dawo Nigeria sbd takurawar Dad dinsa da Dan uwansa Amma dai Yana yawan zuwa duba mahaifiyarsa,

Akwai rayuwar turai sosai a tattareda shi musamman duba da yanda yake gudanar da rayuwarsa Dan kwata kwata baya iya rayuwa gida Daya da iyayensa Dan haka Akai masa part dinsa daban a cikin mansion din Wanda yakeda Dan nesa da bangaren su Dad da Haroon.

Bayan banbancin halayya da rayuwa tsakaninsa da haroon akwai na hasken fata Wanda shi yafi Haroon sbd banbancin tsadaddiyar rayuwar da sukeyi komai nasa na musamman ne da ko mace kafin a samu me gudanar irin wannan classy rayuwar sai an tona.
#MAMUH#
#DR JEEY SEELAH
#BARR HAROON SEELAH
#AMEENATOU BABBAH
#THE SEELAHS

#ROMANCE
#ZAFIN KAI

ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
18
Shekarun Dr Jamaal Seelah Kusan 15 zuwa 16 da dawowa hannun Dad dinsa kwata kwata,
Kuma a wainnan shekarun abubuwa da yawa sun faru wainda suke akan wani matsayi na daban.

Tinda Jamaal ya dawo gurin mahaifinsa ya zama dukkanin wani abin alfahin Dad din sbd iliminsa da zafin kansa a komai daban yake Dana kowa dayake cikin ahalin seelahs,

Likita ne shi Kuma marikin dukiyar mahaifinsa ne shi Mai kulawa da kusan duka kamfaninsu batareda Saka hannun Haroon aciki ba sbd gaba Daya Haroon ya koma tamkar wani matsoraci kaman yanda Dad din ke fada shiyasa kwata kwata Dad din Baya wani yinsa.

Haroon shine yasan ciki da wajen huldodin su Dad sosai sbd shine lawyer dinsa a yanzu Daya zama cikakken lawyer me zaman kansa Kuma kwararren Daya San aikinsa,
Yasan duka boyayyun illegal huldodinsu da Babu Wanda JEEY ya sbd tsananin taka tsantsan da boyewan da suke masa Dad Baya kaunar yasan ko aikinsa Daya mara kyau Dan kuwa JAMAAL din na sani zai iya barinsa har abada ya komawa Dr Aleena Kuma zai iya Jin haushi ko tsanarsa ko janyewa daga garesa Dan haka duk wata mummunan boyayyar harkarsu Babu wadda JAMAAL SEELAH ya sani suna tsananin kiyaye Hakan,

Haroon Daya San komai baida ikon fadawa JAMAAL din bare Bude hanya komai kankantarta da JAMAAL din ze sani hakama shi Daya sani Yana taka tsantsan sosai akan bayyanar sirrinsu sbd sanin hukunce Sharia da shariar kanta,
Sharia da aikin shariar ya ratsasa sosai da yake kiyaye kaidojin aikinsa Baya shiga shiga huldodin Amma dai shine me riqe da mukullin rufe sirrin batareda barin hanyar fitarsa ko kadan ba hakama Baya taba barin kowace matsalar da zata bayyanarda huldar iyayensa ta aikin danyar zinariyar Dake tafiya da rayukan mutanen da Basu da adadi ba hakama da drugs masu tsananin hadarin gaske wainda BB ne akan wannan bangaren duk da shine riqe da sirrinsu na boye da babu Wanda ya sani Haroon din Shima baisan iyayen nasu sun taba dauka rayukan mutane da hannuwansu ba Kuma Yan uwansu tamkar jininsu Dan haka Bai taba kallan Dad dinsa ko daddy lameenu a matsayin komai ba face jajirtaccin Dake Gina ahalin seelahs a boye batareda sanin irin gwagwarmayar dasuke fama da ita ba.

JAMAAL SEELAH a yanzu da dukiyarsu da komai yake hannunsa Yana

gudanar dasu ne akan ilimi da kwarewa sosai dukiyarsu Daketa business din gaskia da duniya ta sani take sake habbaka da samun cigaba da nasarori Dan haka Dad ke sake Jin tsananin alfahari da farin cikin kasancewar Dr Jamaal Seelah dansa ne jininsa ne.

A can Poland a asibitin mahaifiyarsa yake aiki Amma anan din duk girma da tsari tareda dukiya me yawan da Dad dinsa ya kashe aka Gina masa asibitinsa ta kansa maidata yayi asibitin marasa karfi da tallafi Dan kuwa raayinsa ne gidan asibitin duba mara lafiya cikin tsananin sauki da Bada taimako sosai.

Hakan da yayi Dad Bai hanasa ba Bai Kuma nuna komaiba duk da Hakan yayi tsananin Bata ransa Se kawai sukai Hakan batareda saninsa ba ana kawo magani mara quality a asibitin Amma cikin ikon Allah Hakan Bai taba bawa Dr JAMAAL din matsalaba saima sake daukaka da suna da mutunci harma da girma dayake samu gurin mutane sbd tausayinsa duk da kwata kwata baida sakewa ko kadan sai a gurin patients dinsa wannan zakaga ya sake musu kyakkyawar fuskarsa me daukan ido sosai Amma badai ma'aikatansa ba harna asibiti harna sauran business dinsa.

Daga Baya Suma su Dad da sukaga asibitin sake qarawa SEELAHs girma da mutunci sosai takeyi tareda mutunci sai suka koma suna Jin dadin Hakan Amma dai a fili kawai cikin ransu Dad din Babu abinda yake so da burin kaman Jamaal ya aje komai kwata kwata ya shiga cikin huldansu ya riqe komai sbd dagashi har daddy lameenu kallan Jamaal sukeyi amatsayin sa'arsu Dan duk abinda ya Saka musu hannu Akai sai yayi musu yanda sukeso harma fiye Dan haka suka rasa yanda zasuyi su sakashi cikin huldansu na boye sunada tabbacin zasu samu harma abinda basutaba tinanin samu ba karshe ma dukiyar Omar Dake kashesu da ransu a duk numfashin dasuke shaqa tasu zaso tafi tasa su Dena wahalarda kansu duk da ciwon dukiyar Omar da rayuwarsa ma gaba Daya wani mummunan kurjin ciwo ne Da Babu ranarda zai fashe yabarsu saisun rufe kasa da idanuwansa.

Dr Jamaal Bai cika zama available sosai ba a Seelahs specialist da safe sai yamma Kokuma da daddare shine Asalin lokacinda kake samunsa a asibitin Dan yafi samun nutsuwa sosai acan da dare zai zagaya patients nasu sosai ya duba su tareda Basu kulawa sosai.

Su kuwa a bangaren su Dad Hakan shine daidai yayi musu
Da safe Yana tareda su a gurin aiki da yamma zuwa dare Yana asibitinsa sukuma ana gudanar musu da tasu huldar lokutan.

********Rayuwa tayiwa kowa yanda yake so sosai harma da qari dan kuwa

lokaci yaja ayau sunkai JAMAAL SEELAH yana musu huldodinsu da duk sukeso batareda yasan da yawa ayyukan dayake musu na harkar banza bane sun taru sun rufesa duk da kulawansa sosai sun fisa kiyayewa sbd Bai taba tinanin wani abu Yana gudana a cikin familynsa ba da Bai saniba,

Sam Babu tsoro ko shakka ko rashin saa a lamarinsa saima izza da Kai tsayen da Babu acikin familyn kamansa,

Idan akwai abinda yafi farin ciki da Kwanciyar hankali tareda alfahari da Jin Babu kamansa to Dad Mam Yana ciki,ko sunan wani idan ba Jamaal ba bayason ana ambata a 'dansa,

A duniya ko asirinsa Baya tsoron ya bayyana ga duniya kaman yanda shakkarsa Daya da tsoronsa Daya JAMAAL yasan su din su waye ne,
Me sukeyi a boye,
Ina suke zuwa,
Me suke hadawa da kuncewa uwa Uba abubuwan da sukai da rayukan da suka kawar ciki hadda na Dad Omar dinsa Daya kasa cire masa shi daga zuciyarsa kwata kwata duk kwata kwata haryanxu Babu Hulda tsakaninsu da Omar din.

Wannan kadai ne yake jijjiga zuciyarsu da tsoro da fargaba Amma bayan wannan ko Hukuma da duk wata sharia da masu yinta baima daukesu abin sakawa a lissafi ba Dan ya Dade da karbe wannan power din a hannunsa dukkanin wata hukuma da sharia sune suke juyata yanda sukeso su Saka a kawar musu da Wanda duk sukeso da sunan sharia.

Yanzu cigaba da karfin da suka sake samu akan barnarsu shine da sharia suke amfani a kawar Dana kawarwa a rufe na rufewa har karshen rayuwa,
Sun Dena Bata hannuwansu da jini Amma na Abinda Omar ya Haifa da Omar din shikam halastacce ne a gurinsu.

A bangaren Daddy lameenu ma kaman yanda Mam ke bugun gaba da alfahari da Jamaal haka yake wannan alfaharin dashi Dan kuwa manyanci ya Saka da yawa fiyeda Rabin nauyin dayake kansu Jamaal din ya dauke musu hakama Bai taba banbanta matsayi ko kaunar Dad dinsa akanshi ba sbd sanin shi din qanin mahaifinsa dayake kallo uwa Daya Uba dayane Dan haryanxu kaf familyn Babu Wanda haryanxu yasan ba uwa Daya Uba Daya SEELAHs suke ba.

Allah ya hore musu Jamaal din fiyeda yanda sukai tinanin samun ya dawo gurinsu dan haka Dr JAMAAL JEEY MAM SEELAH ya zama tamkar wani kofa ko bangon kariya da dukkanin ahalin seelahs Tako ina shi zaka fara tinkara idan zaka tinkari familynsa musamman iyayensa.

Haroon seelah tini ya zama kaman wani shadow a gidan baka cika jinsa ba idan ba mugun abinsu da Jamaal Bai saniba bane zasu yi to shine zaa nemosa.

Kauna da shakuwa dayake tsakanin twins din wani irin karfi gareta da Babu ranar da Dad Baya bawa Haroon tabbacin kada Koda wasa Jamaal yasan meye sirrin dayake gudana a cikin seelahs Dan hakan daidai yake da rabasu da zaiyi har abada,
Shi kansa Haroon tsoro da shakkar bari Jamaal Koda tsautsayi yasan wani abu ko fahimtar wani abu bare sanarda shi Dan gudu da shakkar fitintinu da tashin hankalin dazai iya biyowa Baya,
Shi kansa Yana shakkar Jamaal yasan cewa shi yasan komai Amma Bai sanar masa ba Dan haka Shima a cikin shakka da taka tsantsan din Jamaal yake.

******Yau a gida ya kwana sbd tafiyan dayayi wani aiki da suke Gina sabuwar kamfanin qera karfe na Seelahs a Nasarawa ba a cikin gari ba can wajen gari sosai kusada wani kauyen da Baya nesa da cikin Nasarawa din hakama kusan filin Gina kamfanin ya shiga garin sosai Dan haka kaman a garin ma zaa ce kamfanin take dan girmansa yaci kusan garin sosai.

Baccin ragewa jikinsa gajiya yayi na kusan awa uku bayan dawowan nasa kafin ya tashi sanyeda farar doguwar wandon TT me santsi ta kayan bacci.

Jikinsa Babu Riga daga doguwar wandon data zauna a qugunsa kaman zata sauka sai farar fatar jikinsa Dake glowing tana daukan ido hutun dayake cikin Yana bayyana.

Ba slippers a fafaren qafafunsa sbd saukowansa daga gado kenan Kai tsaye toilet ya nufa Kai tsaye ya Bude ya tareda zira takarmin toilet din marasa nauyi da dadin takawa ya zare doguwar wandonsa Yana nufar shower Kai tsaye Dan wankan yake buqata kafin komai.

Ya jima a cikin toilet din ba sosai ba kafin ya fito daure da towel ash daure a qugunsa kaman towel din zata Fadi sbd lazy daurin da yayi masa
qamshin shower gel na LE LABO SANTAL ne ke tashi jikinsa ahankali me sanyin dadin shaqa.

Ficewa yayi daga bedroom din nasa a yanda yake ya nufi hanyar dining room.

Fridge ya nufa Kai tsaye ya Bude ya dauko energy drink din E-Bull ya Bude yakai bakinsa yasha Yana juyowa yaji an Bude kofar palonsa Kai tsaye an shigo batareda ya waiwayoba yasan Haroon ne sbd shi kadai ne me shigowa bangarensa Kai tsaye batareda buqatan kira a waya Dan Jin Yana Nan ko

Neman izinin shigowa.

Haroon Daya qaraso tsakiyar palon tareda nufo inda Jamaal din yake Kai tsaye
Yana kallan yanayinsa Haroon yayi ya Dan dauke Kai Yana Bude fridge din shima ya dauko drink din me sanyi kadan ya Bude yafara Sha Yana son sanar da Jamaal din son karban harkar sabuwar kamfanin nasu na Nasarawa.
#MAMUH#
#DR JEEY SEELAH
#BARR HAROON SEELAH
#AMEENATOU BABBAH
#THE SEELAHS
#ROMANCE
#ZAFIN KAI

ASHNA BEAUTY SKINCARE
Free class free class
Assalamu alaikum yar uwa kina neman inda zaki koyi sanaa wadda zaki dugara dakanki Ashna skincare and more tazu muku da garabasa ta musamman inda zata kawu muku yanda ake hada wannan abubuwan kyauta
Carwash
Airfreshner
Liquid soap
Gamasu nemana hanyar shiga zaku nemeta ta wannan number kamar haka whatsapp only 09031383058
Karku Bari wannan damar ta wuceku

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700

Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee

19
Haroon duk yanda yaso sanar da Jamaal kasawa yayi sbd shigarsa a aikin site din bazaiyiba tinda kwata kwata bayason aiki guri Daya da Jamaal inde na kulawa da harkokin Dad dinsu ne Dan tsoron bawa Jamaal daman fahimtar wani abin Koda tsautsayi ne Dan haka yauma hadiye zancensa yayi Yana dawowa Palo ya zauna a daya daga cikin lafiyayyun kujerun palon Yana cewa

"Amma yau din a gida zaka kwana tinda tafiya ka dawo ba buqatan zuwa asibitin ko?"

JEEY din baice komaiba Saida ya karasa shenye abinda yake hannunsa ya ajiye gwangwanin E-Bull din ya juyo Yana nufar hanyar bedroom dinsa Yana gyara towel dinsa kadan Daya kusa zubewa a qasa ya Bude Baki Yana cewa

"Inada patients Dake jiran dawowana na dubasu,
And inada ma da surgery da zanyi so meyasa zanyi kwanciyana a gida?
I can't even sleep or have a rest if ba hospital din naje ba you know that"

Yana kaiwa Nan ya shige bedroom dinsa Dan shiryowa.

Bai wani jima sosai ba ya fito shirye cikin farar freesize Casablanca hoodie rigar data bayyanarda freshness dinsa sosai
sai half trousers fari Shima da slippers din Bally a kafarsa da haskenta da tsaftanta kaman ba akai yake tafiya ba.

Qamshin turaren Allure ne na Chanel ya gauraye palon gabaki Daya daga fitowarsa Wanda ya tabbatarwa da Haroon ya fito ya Dan dago nasa fararen

idanuwan Shima ya kallesa Yana ajiye remote dayake hannunsa Yana sauya channel Yana duba time na agogon dayake daure a hannunsa yace

"Please kayi dinner damu mana to kafin ka tafi asibitin,Dad yayi tinanin zuwanka da Rana Kaci abinci tareda mu amma baka fito ba."

Zama yayi kusa da Haroon din Yana kunna wayarsa da tinda ya shigo gida ya kasheta Dan samun hutun dayake buqata.

Zamansu guri Daya ne kadai wasu lokutan yake taimakawa kowa ganesu da tareda banbance waye Jamaal waye Haroon sbd fatarsu Daya Dan banbanta sai Kuma halayya da yanayi Amma suna rabewa basa guri Daya shikenan gane waye wannan waye wancan zaiyi matiqar yin wuya har Dad dinsu kuwa musamman idan zaiyi maganar Sirri da Haroon ya ringa kokarin tantancewa kenan kada yaje yayi da Jamaal ya lalata aikin shekara da shekaru.

Cikin sauti me nutsuwa da Kwanciyar hankali ya Bude Baki yace

"Idan na tsaya Kaine zaka kaini asibiti bazan driving ba ka yadda da Hakan?"

Murmushi me kyau da nutsuwa Haroon ya sake Yana gyada Kai da cewa

"Har bakin office ma kuwa zan kaika DR JAMAAL SEELAH."

Murmushi Shima ya saki Yana kallan Haroon din Dake Dora masa da bayanin yanda Dad zaiji dadin Hakan Dan farin cikinsa a rayuwa ya zauna table cin abinci da gabaki Daya iyalinsa.

Kiran sallan magrib ya Saka Haroon miqewa ya nufi hanyar Daya bedroom din dayake palon na Jamaal Yana cewa

"Kayi magana da mum kuwa?takira dazu tana buqatan sanin yanda ka dawo wayanka is off."

Shigewa yayi bedroom din batareda yaji amsan JAMAAL din ba,
Toilet ya nufa Kai tsaye yayo alwala ya fito suka fito tare zuwa masallacin gidan da suke sallah a ciki tareda su Dad da masu gadinsu da securities.

Tareda iyayensu sukai sallah suna gamawa sukayo ciki gaba Daya Banda Dad Lameenu daya fita tareda drivernsa zuwa wani gurin.

Dad cikin kulawa ya Kalli Jamaal Dake cika masa ido tamkar bashine ya haifesa ba ya tambayesa yanayin aikin Nasarawan Dan kuwa ba qananun dukiya zuka zubawa wannan aikin ba Wanda idan bakiyiba zasu tafka asarar

da jijjigasu matiqa Dan haka Koda wasa bari kowa ya Saka hannu a aikinba sai Jamaal ne kadai project din da komai da komai yake hannunsa.

Cikin nutsuwa suke tattaunawa har suka Isa cikin main palon mansion din inda yake tsare da luxuries na Jin dadin rayuwa da asalin Hutu.

Hanyar dining room suka nufa dukkaninsu daidai fitowan mum Atey da itama Hutu da Jin dadin rayuwa yake bayyane a tattareda ita.

Tana ganin Jamaal ta washe Baki cikin kulawa tana cewa

"Dr jeey tin dazu nake cewa kana hutawa baka fitoba bare muyi Maka barka da dawowa"

Dan kallanta tayi a gazarce Yana Dan sake fuska kadan batareda murmushinsa ya bayyana ba ya amsa da

"Eh na gaji ne Koda na iso Ina buqatan ishashiyan Hutu,.thank you"

Fitowan Ayesha 'yarta ne ya sakashi Dan daga girarsa Daya sama Yana Dan dauke kallansa daga gefen kwata kwata suna cigaba da magana da Dad akan abinda suke tattaunawa.

Gurin Haroon ta nufa tana sake fuskanta gaba Daya da farin cikin ganin Jamaal din tace

"Dr sannu da dawowa."

Batareda ya waiwayoba yanda ya kamata ya Dan juyo kadan yace

"Yawwa thank you"

Zama tayi a kujeran kusa da Haroon tana gaida Dad Shima kafin ta dawo da kallanta kan Haroon tana magana kasa kasa kada kowa yaji me take fada masa Yana dariya fuskansa a sake sosai sbd akwai shaquwa da kulawa sosai a tsakaninsu.

Mum kuwa gefen Dad ta zauna sai ya zamana gefen Jamaal din shi kadai ne Daman Hakan shine raayinsa Dan haka take masu aiki suka qarasa kawo abubuwan da Babu a dining din su ruwa da drinks da cutlerys Dan Basu gama hada table ba masu gidan suka hau.

Mum Atee sosai takeson samun shiga kamar me gurin Jamaal sbd tini ta gama da kame Haroon ta koma itace uwarsa komai da ita yakeyi a matsayin

uwa shi kuwa Dr ko a mafarki ba'a Haifa macen da zata maye gurbi ko samun matsayin mahaifiyarsa ba bayan mum dinsa itace kadai tak dinta Dan haka duk tsananin dagiya da son nuna masa tsananin kauna da kulawa da mum Atee keyi Bata taba samun shiga yanda takeso ba Amma dayake ta iya naci da kisisina Bata Dena nuna masa kulawa da tattalin ba saima sake dagewa datakeyi Dan tagama fahimtar Dr din shine SEELAHs ma gaba dayanta yanzu da zuwa Nan gaba hakama Dr ne kadai zata kama ta kama dahir a zaman seelahs harma ta taka matsayin shugaba a cikin matan zuriar duk da akwai wainda suka rigata dadewa a family harda manyan Yaya Amma dai nata burin daban ne akan nasu Dan ita ba zaman auren kadai tazo yiba hadda nemawa Kai suka da matsayi.

Cikin nutsuwa da wayewa sukecin abincin da sakewa dukkanin kulawan mum Atee akan Jamaal take tana tura masa abubuwan datasan Yana ci tana basa tabbacin sbd shi Akai girkin.

Sun jima sosai gurin cin abincin kafin suka gama suka baro dining din Kai tsaye Palo suka dawo suka zauna harsu mum din suka zauna suna magana tsakaninsu ita Dan Haroon da Ayesha shikuma Yana magana da Dad.

Anayin ishai suka fito Sallah suna gamawa Kai tsaye bangarensa ya nufa ya sauyo kansa daga guntaye zuwa dogon Riga da wando na Dior black ya fito Yana qamshi ahankali wayarsa kawai ce a hannunsa sai laptop.

Haroon already Yana harabar gidan Yana waya Dan haka Yana ganin fitowan Jamaal din ya Bude motar ya shiga Shima Yana isowa ya Bude ya shige suka fice harabar gidan securities da suka San Dr Jamaal din ba dawowa zeyiba a Daren suna masa a dawo da safe lafiya.

A hanyar ta zuwa tinda suka fito Jamaal ya kira mum dinsa ya Saka handsfree ya ajiye a tsakiyansu suna magana da ita su duka biyun cikin tsananin kaunar datake musu da wadda sukewa junansu Suma.

Suna Isa Haroon a harabar asibitin ya ajiyesa ya juya ya fice sbd ana jiransa wani guri.

Shi Kuma Kai tsaye ya wuce office dinsa duk inda ya wuce ana masa barka da zuwa cikin girmamawa da kulawa harya Isa office ya Bude ya shige.

Laptop din ya fara ajiyewa da wayarsa kafin ya rage AC kadan sbd tin kafin ya iso ake sake tsaftace office dinsa a kunna AC dasu humidifier.

Ajiye remote din yayi bayan ya rage AC Yana nufar files din dayake kan desk dinsa Bai taba ba ya nufi toilet ya wanko hannuwansa ya fito bayan ya goge

hannun da towel fari qarami.

Sensitizers ya fara shafawa hannuwansa kafin ya nufi files din ya fara dubawa.

FADILA ALIYU MUHD shine sunan dayake kan file din.

Budewa yayi cikin nutsuwa Yana dubawa tareda karanta dukkanin bayanan dake ciki.

Dr zayyan ne ya shigo office din bayan yayi knocking Yana sanyeda kayan theatr da fitowansa kenan ganin Jamaal ya sakashi sakin ajiyan zuciya da numfashi me sanyi sbd suna tsananin buqatansa akan patient din da aka juye masa file nata.
#MAMUH#
#DR JEEY SEELAH
#BARR HAROON SEELAH
#HASSAN AND HUSSAIN
#AMEENTOU
#FADILA
#LOVE
#ROMANCE
#CRAZYINLOVE

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
20
Dagowa yayi bayan ya gama sauraron bayanan Dr zayyan akan patient din Daya gama karanta severe long term asthma take fama dashi Wanda gabaki Daya rayuwarta da oxygen take rayuwa.

Idanuwansa ya dago yakai kan inda ake rubuta shekarun patient yaga shekarunta duka duka ashirin da Daya.

Dagowa yayi ya kalle Dr zayyan kafin yace komai nurse ta kwankwasa office din cikin sauri ya shigo ta sanar dasu ana buqatansu emergency ne yanzu yanzu fadilan taqi yadda a Saka mata oxygen dinta tayi nisa komai zai iya faruwa a daidai lokacin.

Dr jamaal dinne ya wuce gaba riqesa file din suka biyo bayansa cikin sauri.

Tin kafin ya iso nurse Farry na hangosa ta dauko masa hands gloves ta tarbesa da ita ya miqa mata file din hannunsa yana sakawa Yana karo sauri Dan isowa ga patient din da kusan ranta ma zaa iya cewa ya kusa fita Dan kuwa ta fizge oxygen nata gaba Daya gashi matsalanta pneumonia ne yafara mata mummunan kamu kafin asthma ya rikido.

Yana qarasawa da sauri yakai hannuwansa duka biyu ya Dora akan nata tareda dafeta Yana cewa ayi sauri a Saka mata oxygen din da gaggawa.

Dayake tayi nisa sosai Babu Bata lokaci aka mayar mata da oxygen din har lokacin Bai saketaba sbd Nisan datai ba lallai oxygen din ta shigeta da sauri ba Dan haka ya Bada umarnin ayi gaggawan kawo alluran da zai mata.
Gaba Daya sauri sukeyi Dan cetan rayuwarta musamman iyayenta dake kofar dakin suna kuka sosai Dan tini suka cire Rai daga gareta ganin yanda rayuwarta yake sama Yana qasa numfashinta na barin jikinta.

Addua suka hau cikin tashin hankali da fatan samun sauki da lafiyan Fadilan.

Sunyi tsananin laushi da zama abin tausayi akan ciwonta da lalurarta tsawon shekaru,
Duk abinda suka mallaka ya qare tas basuda komai bayan rayuwarsu sbd ciwon fadila,
Da oxygen take rayuwa koyaushe Yana tareda ita,
Mahaifiyarta da mahaifinta ita kadai garesu hakama tayi karatu sun inganta rayuwarta sedai ciwonta a yanzu da itama take ganin ta gaji sbd ta zamarwa iyayenta lalura,
Komai dasuka mallaka tana kallo ya qare duk sbd ciwonta dayake cin kudin da yanzu sun Dade da fin karfinsu dan haka take ganin kaman idan ta mutu zasu rage Shan azabar da sukesha sbd ita,

Mahaifinta yakai a yanzu ayyukan wahala yakeyi ya samo musu abinci Dana ciko cylinder oxygen dinta,
Takai ta kawo ma yanzu ba cinsu da shansu yake nemowa ba oxygen dinta yake yiwa nema a wahala da kunci tareda tsananin rashi suke rayuwa.

Kusan lokaci me tsayi likitoci suka sauka akanta kafin suka samo numfashinta ya dawo daidai duk da ba sosai oxygen din take kawai lungs dinta ba sbd mugun Nisan datai
Allah ne kadai yayi tanada kwana a gaba ma da tini wani zancen akeyi Amma dai ta samu oxygen din Kuma Daman nata Dan kadan ne ya rage dole Dr Jamaal ya Bada umarnin aka Saka mata sabo na asibitin tasu.

Rubuce rubuce yayi sosai a file nata tareda zuba mata fararen idanuwansa masu kyau Yana kallanta kafin ya dauke idanuwan nasa ya maidasu kan rubutun dayakeyi ya gama ya miqawa nurse din Dake gefensa suka fito Yana zare gloves din hannunsa Yana tattaunawa da sauran likitocin suka nufi wata patient dinsa Dayake ji da ita dattijuwa ce sosai tana fama da diabetes duk ya rikitata kaman me matsalan kwakwalwa ga tsufa Dan haka aketa fama da ita shikuma Yana lallabata sosai shiyasa idan ba shi ya Bata magani ba Bata sha sai anyi daqyar.

Round yayi a asibitin ya duba patients sosai har kusan 11 kafin ya juyo ya dawo dakin dasu fadila suke ya sake dubata yayiwa iyayenta tambayoyi sosai akan ciwonta Yana sake rubutu acikin file din kafin ya Basu tabbacin Inshallah zata tashi Amma ba yanzu ba zata iya kawai gobe da Rana ko Yamma ba Dan haka su kwantar da hankalinsu.

Sai 12 ya koma office dinsa yana shiga Kai tsaye toilet dinsa ya wuce ya wanke hannuwansa sosai tareda fuskansa ya sake shafo sensitizers ya fito ya rage hasken office din yazauna tareda janyo laptop dinsa ya Bude bayan ya dauko ruwa me sanyi kadan daga fridge dinsa ya Bude yasha kadan ya ajiye

gefe yafara aikin dayake gabansa.

Washe gari bayan sallan asuba kaman yanda ya Saba Saida ya sake duba patients dinsa da yawa harda fadila kafin ya wuce gida.

Haroon Bai zo ba driver ne yazo ya daukesa sbd safe ne sosai.

Suna Isa gida Kai tsaye part dinsa ya nufa Yana shiga ya tube kayan jikinsa ya jefasu laundry room dinsa ya fito da underwear kawai ya jikinsa ya nufi bedroom dinsa.

Wayarsa kawai ya kashe ya jefar kan sofa ya nufi toilet ya shige
Wanke bakinsa kawai yayi da mouthwash na spray mint flavor batareda yin wani brush din ba Dan yayi a office
Yana gamawa wanka yayo ba jimawa sosai ya fito daure da towel cikin nutsuwa ya shirya a gaban mirror tsaye kafin ya saka underwears da kayan bacci marasa nauyi ko kadan ya haye gadonsa ya rufe jikinsa tareda kashe hasken dakin take bacci ya daukesa me dadi da nutsuwa.

Baccin awa biyu da rabi yayi kafin ya tashi ya sake brush ya shirya ya fito cikin ash Armani's ya nufi cikin gida Kai tsaye palon Dad dinsa ya nufa acan suka gaisa ya fito daidai fitowan Haroon suka nufi dining room tare suna magana.

Breakfast sukai suna gamawa suka fito Kai tsaye motarsa Bentley continental gt ya nufa ya Bude ya shige tareda tayarwa Kai tsaye ya nufi gate securities suka Bude masa gate ya fice
Shima Haroon ko gate din baa rufeba ya Saka kan tasa tsadaddiyar motar ya fice zuwa nasa office din.

SEELAHs ya nufa office dinsa Wanda yanada ma meeting da baqi da safen su Dad ma duk zasu halarta sbd mahimmancin Taron meeting din.

Se karfi uku da Rabi ,hudu saura mintina kadan ma ya baro office Dan haka Yana dawowa sallah ya fara yi a masallaci kafin ya shige.

A dining na palonsa ake Kai masa lunch dinsa ana jere masa Dan haka abincin ya zauna yaci Yana gamawa sake kwantawa yayi bacci sai yamma ya tashi yayi wanka ko abincin Dare baici ba ya fice sbd hankalinsa Yana asibiti.

Yana Isa acan yayi sallan magrib Yana fitowa masallaci office dinsa ya dawo dan yanada patient da zai duba.

Sai bayan ishai yasha ice tea a office dinsa da cake kafin ya fito round nasa.

Fadila ce patient ta karshe Daya duba Kuma yayi mamakin ganinta zaune Amma gaba Daya Babu farin ciki ko kadan a tattareda ita,
Mahaifiyarta tayi kuka har idanuwanta basa dubuwa ga damuwa qarara a fuskanta,

Shi kansa mahaifinta Yana cikin tashin hankalin sallaman da zaa musu basuda kudin oxygen nata
Sunsan Babu oxygen Babu rayuwar yarsu ne Dan haka suke cikin mafi girman tashin hankali.

Da farko Dr Jamaal din ya dauka damuwan tashin hankalin jiyan ne Bai sake su Dan haka ya sake Basu qwarin gwiwan ta warware Inshallah.

Godia sukai masa suna sake maimaita farin cikinsu akan taimakon gaggawan Daya bawa fadilan jiya.

Fadila Dake zaune idanuwanta a rufe da oxygen dinta a hancinta Bata iya Bude idanuwanta ta kallesa ba sai qamshinsa Mai sanyi da dadi Daya cike iskan gurin gaba Daya Yana Sakata Jin jikinta na sake mutuwa gabaki Daya.

Shima a hankali ya juya ya Dan kalleta kafin ya dauke idanuwansa akanta Yana barin gurin.

Ranar ma a asibitin ya kwana sbd sunada emergencies sosai Dan haka Koda gari ya waye sosai yake a gajiye yabar asibitin.

Kwanansu fadila biyu a asibitin aka sallamesu batareda an cajesu komaiba sbd Dr Jamaal din Daya sanar da Hakan.

Daqyar baban fadilan ya samo kudin da sukai refilling Rabin cylinder na oxygen suka tafi.

Sati biyu sukai suka dawo asibitin da ita Rai hannun Allah Kuma sukai babbar sa'ar Dr Jamaal na asibitin Dan haka Shine ma ya amshi matsalarta tareda shiga damuwa sosai sbd ganin Halinda take ciki yafi na Baya muni.

Daqyar suka samu numfashinta ya dawo bayan sunsha wuya sosai Dan haka Kai tsaye ya tattauna da iyayenta sosai ya fahimci tsananin rayiwan da suke ciki da azaban da fadilan Kesha tin tana yarinya har zuwa yanzu datake ganin kaman ta zama musiba ga iyayenta.

Da kansu iyayen suka ringa masa Hawaye suna rokonsa ya fahimtar da ita suna tsananin Sonta ahakan Basu taba gajiyawa da ita ba bare kallanta a matsayin musiba.

Lamarin fadila da iyayenta tsaya masa yayi arai Dan haka Ya karbi file dinta gaba Daya ya mayar da ita patient dinsa da shi kadai ne yake dubata hakama ya dauke musu siyan oxygen nata shine me siya.

Ta Dade sosai wannan Karan kafin aka sallamesu Kuma duk wanna taimakon da dadewan da sukai asibiti Bata taba dagowa ta kallesa ba sedai ta riqe qamshinsa da kaf asibitin Babu me irinsa bayan shi kadai,

Shi kansa Bai taba tsayawa ya kare mata kallo Dan ba dabiansa bane qarewa mace kallo dan haka tsakaninsu gaisuwa da Godia ne kadai Amma umman da baban sun Saba ahankali ahankali Dan sosai Allah ya Saka musu kaunarsa da tsananin ganin girmansa Dan tinda suke wannan dawainiyar ta 'yarsu Babu Wanda ya taba taimaka musu sai shi Dan haka suke tsananin kauna da ganin girmansa.
#MAMUH#
#DR JAMAAL
#AMEENATOU
#HAROON SEELAH
#FADILA
#JEDEENDS
#THE SEELAHS

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700

Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
21
Acikin kankanin lokacinda bamai tsayi ba iyayen fadila suka zama tamkar wasu ahalin Daya hada jini dasu Dan kuwa sosai yake taimka musu bayan matsalan ciwon Fadila wadda a yanzu tafara Dan sakewa tana amsar rayuwarta da kaddararta sbd shi din Daya bayyanar mata da wata sabuwar rayuwar hakama tana ganin iyayenta cikin walwala sbd taimako da kulawansa sai kawai ahankali take kallansa da wani irin matsayi me girma.

Shi kansa Dr Jamaal idan akwai abinda Bai taba tinanin zai samu kansa a rayuwarsa kwata kwata ba to son wata 'ya mace ne Amma Kuma ga dibbin mamakinsa sai gashi zuciyarsa Mai tsananin kamewa da kiyaye ko kallan mace ta kamu da wata tsaftatacciyar son fadila Mai tsananin gaske da Bai taba tinanin samun kansa a wannan fannin ba.

Son dayake mata ya ginu ne daga tausayi me tsanani tare Kuma da nutsuwanta da yanda ita gaba Daya Bata taba abokiya ba bare sakewa da mutane sbd tana kallan kanta a matsayin matacciyar data ke yawo da kararrin kwana,

Bata taba sakewa tayi muamala da mutane ba koyaushe a kadaice take sbd halinda rayuwarta ke ciki na koina da oxygen take yawo maqale a hancinta Babu abinda batareda shi oxygen dinnan takeyiba Dan haka rayuwarta take tsit Babu kowa a cikinta face iyayenta,

Hakan ne shikuma yayi masa sbd macen da batada hayaniya ko tashin hankali ko Daya itace macen dayakeda raayi wadda bazasu samu hayaniya ko damuwan zama ba,
fadila ta samu shiga zuciyarsa ne sbd wainnan halayen nata hakama ba qaramin so me girma da tsafta zuciyarsa ta kamu dashi Dan hka Kai tsaye ya sanar da iyayenta da sukaji kaman zasu shide Dan tsaban farin ciki da basa

fadilan da dukkanin Saka albarkansu.

Fadilan da farko duk da sanin nesa nesa sosai yayi mata zarra yafi karfin ajinta dari bisa dari Amma kasa amincewa tayi da Hakan sbd tasan tausayi ne yake mata tsagwaronsa Amma ahankali ahankali tsarinsa da kalan tasa kulawan ya Sakata mutuwa gabaki Daya akansa batareda tasan da Hakan ba sai jinta tayi cikin sonsa sosai fiyeda yanda ma shi ya samu kansa.

****
Haroon ne Kai tsaye Wanda yasan JEEY din yasamu irin macen dayake so duk da yayi tsananin mamaki me girman gaske dayaga fadilan black beauty da ita me tsari da nutsuwa Amma Kuma a yanda yasan JEEY yasan tsari da rayuwarsa ba lallai fadilan itace macen da raayi da rayuwarsa ke buqata ba sbd fadilan tayi sanyi da nutsuwa da yawa Wanda shi Kuma nasa nutsuwan da rayuwar rashin son hayaniya yafi na fadilan Dan haka rayuwarsu taruwa zatai ta mutu ba dadi ko annashuwa acikinta Dan haka yakega kaman rayuwar JEEY da mace me yar hayaniya da son Nishadi ya kamata sbd ta kawo annashuwa rayuwarsa.
Amma tinda Dr Jamaal Seelah guda ya Riga ya bawa fadila zuciyarsa babu abinda zaiyi bayan Shima ya kaunace sosai tareda girmama raayi da zabin Rabin jikinsa.

Alaqar Dr Jamaal da fadila yayi nisa sosai Wanda ahankali ahankali ya dawo da ita mace Mai farin ciki da annashuwa da walwala ba kaman yanda rayuwanta yake a Bayaba a tauye cikin qunci,
Shi kansa yana mamakin yanda yake tsananin son fadila wadda ta wani bangaren sai kawai Sonta ya fara sauyashi zuwa ga Maison qara zurfafa iliminsa na Addini Dan babanta malamin Addini ne Dan haka sai kawai ya sake zama busy Sam baida time na zaman gida ko zaman Shan iska da fita dasu Dad kaman yanda suka Saba duk weekend shi da Dad dinsa da Dad Lameenu da Haroon harma da matan family din wasu lokutan.

Idan yaje office da safe duk abinda yake gabansa ajesa yakeyi idan 2 tayi ya baro ya dawo gida ya shirya ya wuce karatun dasuke dauka shi da baban fadilan a wani course dayayi musu Register Mai tsada na karatun Addinin basa fitowa sai gap da magrib suna fitowa abinci da wanka kawai yakeyi ya wuce asibiti ya kwana acan wani lokacin Kuma ya dawo gida.

Baban fadilan ayanzu ya zama kaman mahaifinsa sosai suka samu shaquwa hakama ummanta wadda itace mace ta farko data samu matsayin uwa a gurinsa bayan Mum dinsa.

Ahankali ahankali harkokinsu Dad suka fara tabuwa da wannan sauyin da aka samu daga JAMAAL din Dan kuwa aikin site ma tini ya fara kokarin

damqawa Haroon komai sai gashi baaje koina ba suka fara samun matsaloli abubuwa na tabuwa.

Babban abinda yake Kara dagawa su Dad hankali da sauyin shine faduwan dasuka farayi hakama yanda Jamaal din ke sake zurfafa a harkar Addini sai sukejin tsoron tayaya zai fara dasu idan yaji rai ta Dan Adam su baa bakin komai take a hannunsu ba
take sukaji kwata kwata aurensa dama yarinyar da iyayenta Bai kwanta musu ba musamman Dad Jin yayi yayiwa yarinyar da mahaifinta mummunan tsana hardai yanda yake bayyane so Mai tsananin gaske yakeyiwa yarinyar.

Dad Lameenu yafi Dad daga hankalinsa Dan kuwa bincike ya tabbata musu da mahaifin yarinyar yagama mallake zuciyar JAMAAL Dan haka komai lalace musu ma zeyi Idan Jamaal ya auri yarinyar,
Gata ba lafiyayya ba.

Duk yanda suka daga hankalinsu a boye da tsanar auren dayake son aje a nema masa baisani ba Dan Basu taba nuna masa shiyasa haka yakejin ma auren yake buqatan ayi kawai dan fadila ta dawo cikakkiya a rayuwarsa da kulawansa Dan ganin yakeyi koyaushe zaa iya samun matsalan oxygen nata wani abu ya sameta idan Bata tareda dashi.

Sosai yake sake samun sabbin akidu da ilimin Addini sosai Dan haka duk da Baya samun time na aikin dukiyarsu sosai Amma dai yanzu Yana tsananta taka tsantsan da bincike Dan Hana Haram shigowa cikin tsaftacciyar dukiyarsu.

Baban fadilan da kansa yake Kara masa karfin gwiwan tsananta bincike Dan kaucewa Haram.

Wannan shine babban kuskuren dayayi batareda yasaniba shi baban fadilan Dan kuwa shigar da zargi da tsananta binciken dayake Saka Jamaal yi tsakaninsa da iyayensa Dan dukiyarsu tini yakai maqura gurin tsananta batawa su Dad Rai.

Dan haka Kai tsaye Dad yace Jamaal bazai auri fadila ba Bai amince ba kwata kwata.

Mamaki ne ya kama Jamaal sbd baiga illan fadila Dan haka Shima yace baiga matan da a duniyar Nan zai iya nawa matsayin matarsa ba idan fadila.

Kafewa Dad yayi Shima akan wallahi tallahi Jamaal bazai auri fadilan ba.

Tin lamarin na kaman wasa sai gashi ya zama babba Dan kuwa maganar

fasuwan auren Neman tabbata yakeyi Dan Mam Kai tsaye ya kira Dr Aleena Dan yasan ita kadaice duniya zata iya Hana Jamaal auren yarinyar ya hanu.

Dr Aleena kwata kwata batason Jamaal din Yana samun yawan sabani da Dad dinsa kaman Baya shiyasa ma Daya matsa ita ta hakura tabar Jamaal din ya dawo gurinsa Dan gudun abinda zaije ya dawo Dan idan Mam ya rasa abu yafison kowa ya rasa Dan haka ita tsananin son datake wa danta ta hakura ta gansa daga nesa yafi mata ace Baya duniyar gabaki Daya.

Maganar aurenma Yana gama magana da ita ta kira Jamaal din ta rarrashesa akan ya janye daga maganar fadilan ya sauya wata idan tausayinta yakeyi kobai aureba zai taimakawa rayuwarta.

Shiru yayi Bayan ya gama sauraron bayanan Mum din ya sauke numfashi mata sauti Dan yanajin fadan ya rabu da fadila wani abu ne har abada bazai iya ba,
Su tinaninsu tausayinta kadai yakeyi?
Basusan wane irin karfin son dayake mata da zai iya rabuwa da Dad ya aure su koma gurin mum dinsa suyi rayuwa acan.

Maganarta ta Saka hankalin mum din tashi Dan kuwa tasan fitina ce kwance zaiyi da Dad dinsa akan auren Duk da tana son fadilan itama sosai da 'dan nata sbd ganin irin zurfi da kakkaifan son dayake mata da batama dauka Jamaal Seelah zai taba son mace a kusa ba harma Mai karfi irin Hakan.

Koda ta sanar da Dad din Jamaal ya dage kan yanason yarinyar ransa mummunan sake Baci yayi Dan haka ya fuskacesa da kansa yayi masa fada sosai
Shi kansa Dad Lameenu Kai tsaye yace Bai aminta da aurenba.

Haroon da mum Atee ne suka ringa son lallabata Jamaal su fahimtar dashi ya hakura tinda mahaifinsa Baya son yarinyar
ga tarin mamakinsu daga karshe Jamaal zabar komawa yayi gurin mum dinsa.

Haroon rintse idanuwansa yayi cikin sabuwar damuwa Dan daman abinda yasan zai iya faruwa ne Kuma yaketa gudun ya faru din.

Mum Atee kanta sosai ta shiga fargaba ta ringa binsa da lallashi da son fahimtar dashi rashin kamatan Hakan Amma gaba Daya yaji zai iya aje komai na Seelahs ya koma Dr Jamaal din mahaifiyarsa ita data amshi fadilansa hannu bibbiyu.

Wannan shine mafi bacin Rai da tashin hankalin da Dad dinsa ya shiga ganin kawai Rana tsaka Jamaal ya zabi mace fiyeda su,
Kuma macen ma nakasashiya da zata Bata musu aiki da yawa tareda sauya musu Jamaal din gaba Daya Dan kuwa tin yanzu ya sauya fiyeda kashi 70 akanta ana auren Jamaal zai janye daga tarin companies dinsu da nauyin seelahs gaba Daya dayake kansa ya koma likita kawai Kuma me tattalinta shikenan su komai nasu ya rushe a banza bayan tin kafin ayi auren uwarta ma suka hada jini da majina da gumi suka hada dukiyar.

Dad Lameenu Daya tsani tsayawa lamari na basa ciwon Kai batareda ankai karshen matsalar ba ayita ta wuce Jin yayi zai iya komai akan Hana Jamaal tafiya yabarsu hakama bazai iya barin ayi auren ba tinda auren Jamaal din kaman downfall dinsu ne abubuwa da yawa zasu biyo Baya,
Na farko saisun wayi gari Jamaal ya tattara komai ya ajiye ya koma asalin Dr dinsa kawai,
Na biyu mahaifin yarinyar Daketa son dorasa akan wata turban dazai haddasa babbar fitina a tsakaninsu da babu Wanda yasan ma Ina zata tsaya,
Na uku auren Nan rabasu da Jamaal zaiyi kwata kwata zai koma kaman mahaifinsa fadilan shine mahaifinsa hakama yanda yakeson yarinyar Babu abinda zai hanasa tattara kulawansa akanta.

To duka idan Hakan ta faru su meye matsayi Dan makomarsu?.
#MAMUH#
#DR JEEY
#AMEENATOU BABBAH
#HAROON SEELAH
#THE SEELAHS
#LIFE
#HOTLOVE
#TOOHOT
#ROMANCE

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
22
Fadila da tinda aka fara wannan tashin hankalin ta shiga nata tashin hankalin Mai tsananin gaske da damuwa tareda janyewa daga kowa Dan kuwa tasan bama zata taba samun Jamaal ba yaudaran kanta takeyi data bari ta jefa kanta a duniyar da Bai kamata ace ta jefa kanta ba.

Ummanta da baban damuwa suka shiga Suma gashi damuwan yafara tabata yau lafiya gobe ciwo harta Kai oxygen ma wasu lokutan da dama tana zarewa kanta batareda saninsu ba saidai su sameta tana kokarin rasa rayuwarta suyi gaggawan Kiran Dr Jamaal din Wanda Shima tini kansa ya fara daukan caji Dan kuwa sosai take kokarin rasa rayuwanta a lokuta da dama idan Hakan ta faru.

Zafi sosai kansa ya dauka kaman yanda iyayenta Suma kansu ya dauki zafi daga karshe batareda sanin Jamaal din ba baba yaje har office din Alh Lameenu seelah yayi magana dashi bayan dogon jiran Daya Sha da bin dokoki sbd baida appointment dashi.

Bayani da nasihu yayi masa akan su hakura subar yaran suyi aure tinda suna son juna Kuma ya sake Basu tabbacin yarsa batada wata tarbiya mata kyau ko halayen da zasu sakasu Jin Dana sanin barin dansu ya aureta ciwonta Kuma kaddara ce da Allah yafi kowa sanin dalilinsa na yinta a Hakan.

Harya gama bayaninsa da nasihunsa Harma da waazinsa Dad Lameenu baice komaiba sai daga karshe yayi masa Godia fuska a sake Yana nuna ya gamsu

da bayaninsa Kuma insha zasu tattauna da Dan uwansa zasu taho da jamaarsu maganar neman auren.

Bayan tafiyar baban numfashi Dad Lameenun ya sauke Yana Jin gwara su bari ayi auren idan har sunason riqe Jamaal a hannunsu batareda ya barsu ba.

Da daddare suna tareda Mam a office dinsu na gida yayi masa bayanin komai Wanda kusan Shima Mam din shawarar Daya Yanke kenan ganin Jamaal din yafara Shirin barin kasar da gaske barinsu zeyi Wanda yafison ya rasa wani bangare na dukiyarsa me yawa Daya rasa Jamaal a bangarensa.

Ranarda Jamaal yagama samarwa fadila Visa auren kawai za'a daura musu ya tafi da ita Dad dinsa akan dining gurin cin abinci ya sanar dashi ya amince da auren idan har zai zauna dashi bazai barsa ba har abada sedai mutuwa.

Wani sanyi ne ya fara cike zuciyar Haroon kafin mum Atee data sakin hamdalan farin ciki hakama Ayesha data shiga damuwan tafiyarsa.

Shikuwa dagowa yayi ya zubawa Dad din fararen idanuwansa batareda yayi masa alkawarin dayace yayi masa dinba Dan kuwa baiyi alkawarin barin mahaifiyarsa har abada ba haka Kuma idan ya daukota daga qasarta ya dawo da ita kusa dashi baiyi mata adalciba shiyasa Bai taba gwada cewa zai dawo da ita kusa dashi ba kwata kwata duk yasan idan yace ta dawo kusa dashi din zata dawo Amma dai bayason yi mata Hakan Dan qasarta itace Kwanciyar hankalinta da nutsuwanta.

Murmushin yaqe Dad din ke sakewa na yake Yana nunawa Jamaal din ya amsa fadilan dari bisa dari.

Numfashi Jamaal din ya sauke Yana Dan lumshe idanuwansa tareda Jin wani nauyi dayake kirjinsa ya sauka Dan kuwa Koda ya tafin zuciyarsa bazata taba samun wannan nauyin ya sauka ba tinda bawai baya kaunar mahaifinsa bane Yana tsananin kaunarsa fiyeda tinani kawai dai shi ya iya boye Abu ne dakuma yawan samun sabanin raayin dayake samu da Dad din ba kaman Haroon ba da duk abinda Dad yafada masa yayi me kyau da mara kyau to ya zauna.

Cikin farin ciki me tsanani da Jin dadi Haroon yayiwa Dad din Godia Yana bayyanarda Jin dadinsa ga sulhun da aka samu tsakanin Dad da Jamaal din Dan idan Jamaal ya tafi ya barsa baisan wace rayuwar zai fuskantaba a gurin Dad din idan Jamaal Baya nan hakama yasan bazai taba iya musu ayyukan nasarorin da Jamaal yake musu ba musamman bangaren manyan harkoki da baida sani ko kadan akansu.

Jamaal ma Jin yayi tausayin Dad din nasa ya shigesa sbd ya amince ne da auren yasani Badan har dari bisa dari din Daya fada ba Yanason auren sedan Yana tsananin sonsa fiyeda nasa farin cikin bayason rabuwa dashi.

Godia yayiwa Dad din cikin nutsuwa da kulawa tareda bayyanar masa da kaunar da Dad din ke tsananin son Gani daga garesa.

Hakan da yayi ba qaramin Saka Dad din farin ciki me girma yayi ba Wanda harya bawa Haroon tausayi sbd idan akwai abinda Allah ya jarabta Dad din dashi shine Jamaal da kaunarsa.
Ko Alh Lameenu lokuta da yawa shi kansa Yana tsoro da shakkar yanda Mam ke tsananin son Jamaal Dan haka yake gudun kada Hakan ya zama raunin Mam su samu matsala sosai me girma tinda Jamaal din kwata kwata ba page Daya suke dashi ba akan abinda suke aikatawa Dan ma Allah ya rufa musu asiri ba shine lawyer ba Haroon ne da kashinsu ya Dade da bushewa duk power dasuke riqe da ita suna juya sharia yanda suke so da sai Jamaal ya tabbatarda sun rasa komai.

A Daren ranar firan da suka jima a tsakaninsu basuyiba Saida sukai shida Dad ciki kulawa da kauna har tsawon dare kafin ya fito ya wuce part dinsa tareda Haroon da Shima ranar kaunar Yan biyunsa ta motsa a part din zai kwana.

Bedroom dinsa ya wuce Kai tsaye ya fada wanka zuciyarsa na samun nutsuwan dayake buqata wadda ya rasa a kwanakin sbd rigimansa da Dad.

Haroon ma Dayan dakin ya nufa wankan yayi ya fito Kai tsaye ya nufi bedroom din Jamaal ya Bude closet dinsa ya dauko kayan bacci black ya Saka ya fito yaje kwanta,sai a lokacin Jamaal din ya fito ya shirya cikin fararen kayan bacci ya kwanta tareda dauko wayarsa Yana Kiran fadila a natse.

*******Amincewan Dad shine babban abinda yayiwa kowa dadi da farin ciki har bangaren su fadilan wadda batada wani qwari ko kuzari Amma tayi murna sosai.

Babu Bata lokaci Jamaal ya buqaci ayi auren Dan kuwa a yanda yake sane da ciwonta yayi tsanani sosai Dan kuwa yanzu lungs dinta sunyi Nisa sosai oxygen ma Neman gagara riqesu yakeyi Dan haka yake buqatan auren zai fita da ita yaga wasu likitocin da zasu duba case dinta sosai tareda shi.

Bai sanarwa kowa ba har iyayenta matsalanta yayi muni sedai daga su har fadilan jikinsu yayi sanyi sosai Dan sosai kullum take sake zama weak

numfashin ma ahankali ahankali take iya shaqarsa.

Hakanan suke lallabawa Dan asamu ayi bikin,

Fadila da kanta ta cire Rai daga rayuwa a yanzu Amma dai babban fata da burinta shine ta samu zama matar Jamaal kafin Allah ya dauki ranta,
Tanason cika masa burinsa na son ganinta a matsayin matarsa mallakinta kafin ta koma ga Allah Dan haka take fata Dan rokon Allah ya Bata qwari da qarin kwanakin da zata cika masa wannan burin.

Su kansu iyayenta duk yanda jikinsu yayi sanyi ga yanayinta a yanzu ta Basu qwarin gwiwan karban kaddararsu,
Suma a yanzu fatansu ta zama matar Jamaal kafin Allah ya dauki ranta
Idan hakan ta faru zasuyi farin ciki ko bayan ranta sbd burinta ya cika Kuma Jamaal ya zama sirikinsu baiyi musu wahalar banza a banza ba.

Jamaal kwanakin auren na sake kusantowa Amma kwata kwata kansa ya dauki zafi baida lokacin komai bayan tattaunawa da Neman yanda zaiyi ya kawowa fadilan sauki ta samu shakar numfashi me dadi da nutsuwa Dan lamarin yafara karya masa zuciya Amma Koda zaiyi yawon duniya da kasashe ne zai Nemo mata lafiya idan har Allah yayi zata warke din.

Kwanaki na sake kusantowa na auren fadila na sake zama weak sosai Dan yanzu gaba Daya tayi fayau kaman Babu jini a jikinta hakama sai qanqancewa takeyi tana rama da komawa karama.

A daidai wannan Gabar iyayenta sunyi kuka harsun godewa Allah sbd tinda take fama da ciwon tsawon shekaru Bata taba komawa Hakan ba sai yanzu gashi ita kanta wannan Karan ta fidda Rai daga rayuwa adaidai lokacinda taso ace ta rayu Dan bawa Jamaal farin ciki.

A rayuwar seelahs Babu Wanda ya taba tinanin zaa samu Jamaal a hali na fita hayyaci sbd kwallafa Rai a Abu sai yanzu.

Duk yanda su Dad suka dauki matsayi da girman yarinyar a zuciyarsa abin ya wuce Nan Dan haka hankalinsu yasake mummunan tashi akan lamarin auren.

Gaba Daya Jamaal ya aje komai ya tattara hankalinsa gaba Daya akan Neman mafitan ciwon fadila,
Kai tsaye ya ajiye komai har aikin asibiti sbd gaba Daya ta koma a kwance take rayuwa a kwanakin ga oxygen din kwata kwata kaman ya Dena mata aiko Dan haka take ya fasa jiran sauran kwanakin auren yace a daura kawai zai fita da ita waje mum dinsa ma tana Jira zasu taru da wasu likitocin su duba matsalanta Daya kasa Ganowa.

Babu Wanda yayi musu da maganar auren nasa dayace a matso dashi Dan Babu wani biki ko hidiman ma da zaayi tinda amaryan a kwance take tana Neman numfashinda zata shaqa ma ta rayu.

Haroon baitaba sani ko ganin haka asalin so yake ba sai akan Dan uwansa Wanda Bai taba Ganin abinda Jamaal yaso fiyeda komai ba bayan iyayensa dashi sai Fadila,

So ne me tsafta da karfin gaske da Allah ya jarabcesa dashi na yarinyarda ba lallai ta rayu ba Dan koshi da ba likita ba baiga alaman tashi ga fadila ba sedai kwata kwata Jamaal ya kasa yarda da fadilan bazata warke ba ta tashi ta basa 'yan biyun datai alkawarin basa Shima yayi alkawarin ita kadai ce zata zama uwar yayansa,
Ita kadai ce macen dayake son ta Haifa masa wasu Jamaal and Haroon Kokuma Mamman da Omar.

Tausayinsa sosai Haroon yakeyi tin yanzu Daya kasa gane komai ya jinginar da rayuwansa kwata kwata akan fadila da iyayenta da suka koma sune masu basa hakuri da qwarin gwiwa.
#MAMUH
#SEELAHS
#AMEENATOU BABBAH
#LOVE
#HOTLOVE

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k

Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
23
Mum dinsa ya buqaci zuwanta a kasar sbd ta tayasa duba yanayin na fadila dayake tsananin basa faduwan gaban da Bai taba samun kansa da tsoron wani abu ba sai yanzu Dan kuwa ko chances na surviving nata yaqi yadda ya duba sbd Bayason Jin ko kalaman rasawa.

Duk wani ayyuka Dake gaban Dr Aleena ajiyesu tayi tayi shirin zuwa Nigeria cikin damuwa sbd Jamaal da gaske ya Saka damuwan da tsoron matsalan fadila sosai.

A daidai gaban dayake yanzu shine ko dubata Baya iya yi da kansa saidai sauran likitoci su dubata.
Da kanta take kokarin bawa kanta kuzari da karfin hali Dan basa nutsuwan cewa tana samu sauki duk da Babu saukin datake samun saima tsananta da abin yakeyi.

Ranar da mum dinsa ta sauka Nigeria
Tareda Haroon sukaje daukota airport.

Kyakkyawar baturiyar da bazaka taba cewan itace ta haifi manyan zaratan matasan Dake tsaye suna jifanta da kallan tsananin kauna da kewa musamman jamaal da ganinta gabansa ya Saka dukkanin rauninsa Daya kasa bayyana gaban kowa bayyana a gaban mahaifiyarsa.

Itama kallansa tayi tareda zuba masa idanuwanta masu haske irin nasu tana kallansa zuciyarta na karyewa da tausayin abinda take hangowa acikin idanuwansa.

Hannuwanta ta ware daidai lokacinda ya ranqwafo yayi mata kyakkyawar runguma Yana lumshe fararen idanuwansa dasuka Dan sauya Yana Jin nauyin Dake zuciyarsa Yana rabuwa sbd ganinta

itama rungumarsa tayi dakyau tana Jin inama zata iya cire ciwon fadilan ta dawo dashi kanta Dan kawai bawa Jamaal din farin cikinsa.

Sun jima ahakan tana fada masa magana me sanyi cikin kunnuwansa tana shafa bayan kansa kafin suka saki juna ya riqe hannunta Daya Yana Jin nutsuwan Daya rasa tsawon lokaci na shigarsa kadan kadan.

Rungume Haroon tayi tana Jin kaman zata hadiyesa Shima kafin suka juya zuwa mota hannunta na cikin na Jamaal Wanda ke sanye da guntun wandon Dior da rigarsa ash sai fcap da sunglasses fuskansa Babu wani walwala sosai sai daukan ido yakeyi acikin Rana shida mum dinsa harma da Haroon da baiyi haskensu ba.

Mota suka shiga Kai tsaye Haroon ne me tuqin mum na Baya sai Jamaal din a gaba.

Kai tsaye gidansu fadila mum ya buqaci a fara zuwa tafara dubata tinda shine abinda ya kawota kasar.

Suna Isa kofar gidan babanta na waje tareda siddeeq 'dan kanwarsa data jima da rasuwa itama Yana karatu a Lagos din a hostel yake zama Amma tinda ciwon fadila yayi tsanani ya dawo gidan dole sbd baban yakai baida cikakkiyar lafiya Shima sbd zuciyarsa Dake kasa daukan rashin yarsa duk ya Tina da Hakan.

Suna ganin motar Seelahs suka San Jamaal ne.

Haroon ne yafara fitowa Dan haka suka tinkarosa siddeeq na masa barka da zuwa Saida Jamaal din ya Bude dayar kofar ya fito suka gane ba shine suka tinkara ba Haroon ne Dan haka suka juyo suka dawo bangarensa suna masa barka da zuwa.

Cikin girmamawa ya gaida baba Yana tambayar siddeeq exams dinsa Daya gama a jiya.

Fitowan Dr Aleena ne ya Saka baba da siddeeq kallanta suna tabbatarda itace mahaifiyar su Jamaal din sbd kamannin da suka hada Dan haka cikin mutuntawa da girmamawa sosai suka gaidata suna mata sannu da zuwa cikin turanci.

Amsawa tayi itama a mutunce kafin sukai cikin gida gabaki dayansu.

Umma ma tarban mutunci da girmamawa taiwa mum din da Haroon duk da Shima ya zama kaman na gida yanda Jamaal yakoma Kai tsaye Dan gidan

baida shamaki da koina da komai.

Dakin fadila suka nufa tana zaune a jingine da gado an mata kariya da pillows masu taushi idanuwanta a rufe tana Jan wani kasalallen wahalallen numfashin dayake shiga lungs dinta daqyar.

Kallo Daya mum tayi mata ta juyo cikin sanyin jiki ta Kalli Jamaal Wanda yanayinta yake karanta Dan ko a Poland tana cikin manyan likitocin da ake alfahari dasu manya.

Qarasawa tayi har inda fadilan ke zaune ta Bude idanuwanta ahankali da Jin qamshinsa da shi kadai ne yake Ankarar da ita da zuwansa.

Akan mum ta sauke idanuwanta dasukai ciki sosai Bata iya budesu duka sosai sbd rashin karfi sosai.

Durqusawa mum tayi gabanta tana mata sannu cikin tsananin kulawa da nutsuwa kafin ta Kai hannuwanta biyu ta kamo hannun fadilan Daya tana gyara zamanta gefenta cikin sanyi ta tambayeta Yaya jikin.

Cikin nutsuwa da sanyin murya me tsananin taushi ta amsa tareda yi mata sannu da zuwa sbd karfin hali.

Tsit dakin yayi kowannensu na tsaye daga waje daga Jamaal din Se mum ne kadai a dakin tafara dubata tana Jin shakkar abinda tafara tinanin matsalan take.

Kallansa tayi lokacinda ta zare oxygen din hancin fadilan takai hancinta tana shaqa kadan tana Dan rufe idanuwanta Dan shaqarsa cikin relaxing komai nata.

Numfashin fadilan ne yafara sama sama Dan haka ta mayar mata dashi ahankali tareda sake kamo hannunta tana Jin pulse nata.

Cikin abinda Bai gaza mintina arbain na zuwa hamshin ta kusan gama karance matsalan fadilan ta gangan jikinta.

Kallan Jamaal tayi Wanda gaba Daya ya tashi daga likita a lokacin ya koma kaman me jiran sakamako.

Numfashi ta sauke tareda miqewa tsaye ta dawo gefensa ta tsaya a natse tace

"Ina buqatan ganin file nata yanzu a fito dashi daga asibiti a kawomin"

Kallan fadilan yayi tareda kamo hannunta Daya acikin nasa yayi mata sannu kafin ya Kalli mum cikin Dan sassauta murya Yana baro gurin fadilan yace

"Mum asibitin zaa tafi da ita yanzu ai sbd acan ne zatafi samun cikakkiyar time da kulawa da duk abinda ma zamuyi..."

Kallan fadilan itama mum tayi cikin sanyi da tausayi kafin ta dawo da kallanta kansa tace

"Abarta a gida zan dubata anan tareda duk abinda nakeson tantancewa sbd Ina tinanin koma Menene matsalan daga oxygen data shaqa ne yayiwa lungs nata mummunan illa a yanda na karanci numfashinta da kyau da yanda kirjinta yake amsa zuwa lungs din but Ina buqatan sabon oxygen akawo daga wani gurin daban bana asibitinku ba."

Manyan idanuwansa da suka mum din kallansa tana Jin sanyin jiki ya zuba mata Yana Jin gefen kansa na sarawa sbd tinanin oxygen nata nada matsala shine abinda Bai taba shigowa kansa da bincikensu ba sbd daga asibitinsu ake Bata shi Dan haka ma ne Bai taba tinanin Koda bugun iska wai zaa samu matsala a oxygen din datake shaqa ba,.

Hakan ne ya hanasa Gano asalin matsalan Dena shigarda da numfashi keyi dakyau kenan duk qwarewansa a aikinsa ko me??

Jin yayi kansa na Neman daukan zafi Dan haka mum tayi saurin fahimtar dashi tana tinani ne kawai Amma suna buqatan wani oxygen din kafin su tabbatarda Hakan ne.

Fitowa dukai dukkaninsu shine a gaba mum din na Baya Basu sanar da kowa komai ba Sukai musu sallaman zasu dawo anjima suka fito.

A mota shiru yayi yaja sauraron bayanan Mum datake qara Bude masa komai sbd itace take gabansa sosai a kwarewa da sanin aikinta.

Haroon ma kasa yadda yayi da zaa iya samun matsala a cikin oxygen din Daya fito daga asibitinsu sbd wannan babban laifi ne ake magana Wanda zai Saka a dole license na asibitin gaba Daya a rufeta Kuma hakanma zai iya taba aikin likitocinsu da yawa harma dashi Jamaal din.

Shiru Jamaal yayi Bai iya cewa komai sbd Jin zuciyarsa na tarwatsewa idan har ya tabbata akwai abinda yake cikin oxygen din fadila yayiwa lungs nata mummunan illar da Babu gyara bazai taba yafewa kansa ba akan sakacinsa.

Suna Isa gida Kai tsaye hanyar bangarensa sukai parking ya fito da kansa ya budewa mum din mota ya kama hannunta ta fito
Haroon kuwa kayanta ta fiddo dasu daga bayan motar suka nufi kofar palonsa.

Kai tsaye har bedroom din dayake part dinsa Daya yakaita Haroon ma ya shigo da kayanta yana sake juyawa zancen fadila a ransa tareda tsoron halinda Jamaal zai shiga idan Hakan ta tabbata,
Yana tsananin son Dan uwansa fiyeda komai da kowa a duniyarsa Dan haka bayason damuwa ko bacin Rai Bare tashin hankalinsa Dan haka duk ya rasa sukuni.

Key din motarsa ya dauka ya fice Kai tsaye asibitinsu ya nufa ya buqaci oxygen daban da sunan wani patient din zaa sakawa hakama ya buqaci wani daban da sunan fadilansa kafin ya dauko file nata ya fito asibitin.

Wani asibitin abokinsa ya buqaci wani oxygen din take ya biya ya karba ya dawo gida.

Koda ya dawo mum tayi sallah taci abinci ta huta ba laifi Dan haka ta sake wanka suka fitowa zuwa gurin fadila batareda Haroon ba sbd shine yayita kulawa da mum din tareda Mum Atee da Bata nunawa Dr Aleena din komai na hakama mummy Sarat matar Dad Lameenu ta shigo sbd Dr Aleena mutuniyata ce sosai
Tarba me kyau tayi mata tareda asmy da hawwah yayanta.

Kai tsaye daga gida office dinsa suka koma asibiti acan suka hau tsananin bincike da tantancewa tareda aune aune.

Kansa ba qaramin zafi ya dauka ba
Ita kanta mum din tana cikin fargaba da tashin hankalin abinda zasu iya tabbatarwa.

Haroon ya kira yaje ya taho dasu umma da fadila wadda kwata kwata bayason ana damar da ita da yawo.

A cikin Daren kwana sukai shi da mum dinsa da wasu amintattun likitocinsa suna bincike da aune aune harma da hotunan Daya kamata suyi mata duk sunyi.

Sai asuba suka samu kansu tareda tabbatarwa da Jamaal chances na surviving dinta Bai wuce 2% ba sbd koma Menene aka rikida oxygen din data Dade tana shaqa yayiwa lungs nata da cikin mummunan illanda sai addua kawai Amma dai idan har ta take lokacin aurensu zasu tafi da ita waje su

miqawa wasu manyan likitocin su Gani ko zaa samu 2% din tayi Aiki.

Sakamakon Bai gama kammaluwa duka ba Dan haka mum ta Hana a sanar da Jamaal din abinda suka fara Gani Dan bandashi Akai sauran aikinba ta sallamesa ne.

Da kansa ya mayar dasu umman gida Haroon Kuma ya tafi da mum gida.
#MAMUH#
#DR JAMAAL JEEY SEELAH
#AMEENATOU SEELAH
#DR ALEENA SEELAH
#MAM SEELAH
#LAMEENU SEELAH
#OMAR SEELAH

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
24
Koda suka Isa gida mum tayi magana sosai da Haroon ta sanar dashi matsalan datake shakkan sanar da Jamaal Dan batasan tayaya zai fara ba Kokuma ta Ina zai fara binciken Wanda yayi wannan mummunan aikin na rashin Imani da tsoro tareda rashin tausayin daukan ran Wadda take fama da rayuwarta tin haihuwa.

Shiru Haroon yayi sbd Shima hankalinsa ya tashi da wannan zancen Dan kuwa yafara Jin tsoro da wani irin tashin hankalin na sake shigarsa idan har Jamaal ya tsananta bincike duk da baisan waye yayi wannan aikinba Amma dai Yana shakkar binciken Hakan ya binciko masa abinda zai karasa dagula Rai da kansa bayan yanzu lafiyan fadilan suke tsananin fata Dan itace farin ciki da abinda Jamaal dinsu ke buqata.

Koda Jamaal ya dawo gidan cikin Bai Nemo kowa ba Kai tsaye bangarensa ya nufa ya shige bedroom dinsa ya rufe kansa aciki.

Wanka yayi Yana fitowa sallahn azahar kawai yayi ya kwanta sbd kansa Dake Neman tsagewa da ciwo.

Bacci sosai yayi Wanda yake cikeda mafarkai masu nauyi Dan haka Yana tashi da laasar wani wankan ya sake jikinsa ya sake daga nauyi ya shirya ya fito cikin doguwar jallabiya fara qal Data kwanta jikinsa tayi masa wani irin kyau na nutsuwa.

Masallaci ya fita acan yayi sallah tareda Dad dinsa Wanda yayita Kiran wayarsa Baya samu.

Zuba masa idanuwa Dad din yayi bayan sun gama gaisawa ya tambayesa jikin fadila sbd gobe ne daurin auren nasu Wanda zaayi sa kaman na Wainda suka samu cikin shege sbd kawai yanayin amaryan.

A daidai wannan lokacin da gabar Jamaal din kansa yayi sanyi matiqa tareda shiga wani irin fargaba da tsoro me tsananin gaske.

Kai tsaye bangaren Jamaal din suka nufa hadda Dad din Wanda zaiyi magana da Dr Aleena Dan Basu zauna suka tattauna ba tinda tazo.

Suna shigowa tana zaune Palo tana karanta wasu bayanai ta email dinta da Dr Martinez ya dawo mata dashi Akan matsalan fadilan Data tura masa bayanan da komai nata tin jiyan.

Akan Jamaal idanuwanta suka fara sauka ta rufe iPad din hannunta tareda kifeta gefenta tana mayar da kallanta kan Mam da Shima ita yake kalla cikeda kulawa Dan har cikin ranta Yana Sonta Amma yasan bama zai fara maganar mayar da aurensa da ita ba sbd Jamaal dayaji zafin rabuwarsu fiyeda komai hakama dawo da aurensu Jin yakeyi kaman zata iya sanarda Jamaal wani abin game dashi ne shiyasa bayason zaman Jamaal a hannunta ya dawo dashi hannunsa tintini.

Sannu da zuwa tayi masa cikin sakewa da kulawa tana sake murmushinta me kyau da tsari.

Shima cikin farin cikin ganinta da kulawa yake amsawa yana qarasawa ya zaune kujeran gefenta Jamaal kuwa gefenta ya zauna Yana Saka hannunsa cikin nata sbd samun sassaucin abinda yakeji zuciyarsa na ciki ayau din.

Fira sukeyi sosai tsakanin mum din da Dad da Haroon Wanda ya raba hankalinsa kan firar da Kuma Jamaal Wanda Bai iya furta ko kalma Daya ba Dan Yana cikin nasa tinanin daban.

Abinci mum Atee ta Aiko anan bangaren aka jere musu a dining din Jamaal ta Basu Daman cin abinci a tsakaninsu da 'yayansu.

Mum da kanta ta takurawa Jamaal cikin kulawa Mai tsananin gaske yasamu yaci abincin yasha ruwa yabar dining din and magrib datai.

Yana barin gurin mum ta bisa da kallo kafin ta dawo da kallanta kan Mam Dan karantar yanayinsa sbd ko kadan batason yasan me suka gano batareda sun fitar da fadilan waje ba.

Sallan magrib sukai suna gamawa Jamaal yabar gidan da motarsa.

Dad da Haroon ne tareda Dad Lameenu suka dawo ciki.
Kai tsaye office dinsu na gida suka nufa harda Haroon suna tattauna maganar wani aikin dayake hannunsa na fito da yaran BB da tsautsayi yasaka aka kama dayansu sbd wani aikin boyen da yayi musu.

Suna gama maganar dagowa Dad yayi ya Kalli Haroon Yana karantar yanayinsa tsawon mintina kafin yace

"Meyake faruwa ne da Jamaal Bayan gobe ne daurin aurensa??
Akwai wani matsalan ne Daya kamata na sani?
Menene yake faruwa?

Dad Lameenu ma zubawa Haroon idanuwansa yayi Yana kallansa Dan Jin

Abinda yake faruwa da Basu saniba.

Dagowa Haroon yayi ya Kalli dad din Yana Jin jikinsa na sanyi,
Numfashi ya sauke ahankali kafin ya sake dagowa cikin sanyin murya yace

"Jikin fadila ne yayi tsanani sosai,
Mum ma ko bayan isowanta jiyan Saida ta dubata sosai karshe ma a asibiti suka kwana akanta Amma dai angano matsalar daga oxygen data amfani dashi yayi mata mummunan illa Kuma abin tashin hankalin shine oxygen da ita kadai take amfani dashi ne aka gurbata da wani abin Amma dai mum tana kan binciken zasu gane Menene"

Dad Lameenu wani numfashi ya hadiye ya koma masa ciki kafin ya Dan juya ya Kalli Mam Wanda Babu abinda yayi
kafin yayi wata magana Mam din ya rigasa da Bude Baki a natse yace

"To shi Jamaal din yasan da Hakan?
Yasan me sakamakon ya bayar?

"No sai sauran results din sun Hadu zuwa gobe mum zata sanar masa"

Wani sanyayyar numfashi Mai hade da bayyanarda alhini da tausayi Dad Lameenu ya sake
Shikuwa Mam har lokacin Bai nuna kowanne irin yanayi ba sai shiru da yayi kafin ya sauke karamin numfashi Yana Mata fatan samun lafiya ya sallami Haroon din ya fice yabarsu.

Tinda ya fita babu Wanda yayi magana a cikinsu sbd zuwa yanzu da suka manyanta kowa yagama sanin tinanin da kowa keyi a kowanne lokaci wani abin ya taso.

Jamaal Bai dawo gida ba sai dare sosai bayan ya baro gidansu fadila jikinsa a matiqar mace Dan yau fadilan da kanta take kuka tana rokon ya mata alluran da zata rasa hankalinta Dan ta Dena Jin Abinda takeji zuwa safe.

Iyayenta kuka sukeyi da Hawaye a gabansa na tausayinta
Duk wata karfin zuciyarsa Saida kukan fadilan ya karya masa shi.

A goben da zaa daura masa aure da ita a goben Inshallah zasu bar kasar sbd komai na tafiyan ya kammala goben ne ranar tafiya.

Mum dinsa ma jikinta mutuwa tayi da yanayinsa Dan haka Bata takurasa sosai ba akan abinci,ice tea ta hada masa kadai ya Sha ya shige bedroom

dinsa.

Wanka yayi ya kwanta Kai tsaye Yana rufe idanuwansa wani nauyi na karuwa a zuciyarsa.

Karfe uku na tsakar dare Haroon ya fito daga bangarensa cikin tashin hankali da damuwa me tsananin gaske ya nufo part din Jamaal da wayarsa a hannu yayi knocking.

Knocking yakeyi sosai Amma Sam Babu alaman ma suna jinsa Dan haka ya cikin tashin hankalinsa Dake karuwa ya Kalli wayarsa Dake sake ringing Kiran siddeeq Yana shigowa..

Juyawa yayi kawai da sauri ya koma dakinsa cikin gaggawa da rawar jiki ya Dora jacket babba akan sweatset din Dake jikinsa ya zari keys din motarsa ya fito.

Baiyi wata wata ba ya fada motan ya tayar cikin zafi yayi wani mugun horn dashine ya tayar da Dad dinsu da shi kansa Jamaal din harma da mum dukkaninsu a tare suka tashi zaune suna sake Jin horn din a kunnensu sosai.

Time kowannensu ya kalla cikin mamaki Mai girman gaske.

Ziro kafafunsa daga gadon Jamaal yayi tareda saukowa Yana nufar window na dakinsa ya ware curtain Yana kallan harabar gidan daidai motar Haroon din na ficewa daga gidan cikin wani irin gudu me zafin gaske.

Sakin curtain din yayi cikin tsananin mamaki tareda juyowa Yana ziro slippers a kafafunsa Shima jacket din ya Sako kan kayan baccin jikinsa ya fito Palo Kai tsaye Yana nufar kofar ficewa daidai Nan mum itama ta fito tana cewa

"Lafiya kuwa?
Meyake faruwa?

Batareda ya juyowa ba yace ta koma daki zai dubo meyake faruwa.

Yana fitowa harabar gidan Dad ma Yana fitowa cikin mamaki da shakkar abinda ya fidda Haroon a lokacin.

Securities din gidan ma duka suna tsaye a harabar gidan

Dad da mamaki yace

"Meyake faruwa?
Waye ya fita da motan Haroon din?

Jamaal kuwa Yana isowa Kai tsaye yace

"Wats going on here?"
Waye ya fita?
Ina Haroon?

Daya daga cikin securities dinne ya Kalli Dad yace

"Sir,sir Haroon ne ya fita Amma security Daya yabisa sbd dare ne sosai Kuma baima tsaya mukasan meye matsalan ba ya....

Jamaal da kallo Daya yayiwa gate din da Haroon ya fice Bai tsaya Jin sauran zancen ba ya juya ya koma Kai tsaye key ya dauko da wayarsa Daya kunna Yana kokarin Kiran numbern Haroon.

Dad na ganin fitowansa da key cikin mamaki da tashin hankali yace Maza securities su janyo mota su bisa Dan bazai bari yayansa duka biyu su fice a Daren ba batareda yasan meyake faruwa ba da rashin tsaro.

Mum ma hankalinta tashi yayi mummunan yi da sauri ta dauro jallabiya me girma akan kayanta ta fito Amma Jamaal yace kada Dad yabari ta biyosa.

Daukan wayar Haroon yayi daidai da isar Jamaal motarsa cikin murya Mai sautin Kai tsaye yace

"Meyake faruwa?
Meyasa zaka fita a wannan time din?
Bazaka iya sanar da kowaba kafin ka fita?
Ganinan fadamun inda kake kawai...

Shiru yayi tareda dakatawa daga Bude motan dayake kokarin yi maganar da Haroon din ke fada cewan gobara ne sosai ya kama gidansu fadila.

Wani mummunan jiri ne Mai qarfi sosai ya debesa yayi saurin daga motar
Mum ma da saurin gaske ta qaraso gurinsa itada dad tana tambayarsa Menene Amma Sam Bai ya cewa komaiba sai idanuwansa da suka sauya take ya dago ya zuba mata Saida gabanta yayi mummunan faduwa.
#MAMUH#
AMEENATOU
#ZAFIN KAI

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
25
Dad na ganin Hakan yayi saurin kallan Abdul Yana cewa Maza a fiddo mota a biyo bayansu da ita sbd yasan koma ya cewa Jamaal yayi zamansa ba zaman zeyiba Dan haka ya koma ciki Ya Sako jallabiya doguwa fara kal ya fito.

Koda ya fito tini Jamaal yabar gidan Dan haka Kai tsaye shi da mum da securities suka mara masa Baya zuciyarsa na nauyi da fatan kada komai ya samu 'yayansa a cikin wannan sililin Daren ace sun fita Babu Wanda yake tareda jamian tsaron lafiyarsa a cikinsu har gwara Haroon ance security Daya ya bisa
To Jamaal fa¿.

Mum kuwa duk a tsorace take ma kwata kwata sbd tsoron idan ba wani abin ne ya faru ba me girma ko zai faru,

Koma dai Menene itadai fatanta Allah ya tsare mata 'yayanta ya Basu kariya da kaucewa musiba da masifa kowace iri.

Dad daya kasa tantancewa ko canko Menene yake faruwa shiru yayi Yana fatan Isa ga yayansa cikin gaggawa kafin kome zai farun ya faru tukuna...

Bayan motar Jamaal suke hangowa Yana gudu sosai Wanda ya Saka jinin Dad fara Hawa Yana Jin zuciyarsa na wani irin tsalle da rawar tashin hankali Dan kuwa Jin yayi kaman zuciyarsa ne a cikin motar Jamaal din ana wannan gudun da ita.

Mum kuwa idanuwanta a rufe ma suke tana Jin alamun itama BP dinta ya haye sama a take.

Hanyar gidansu fadila da suka nufa ya Saka Dad Jin wani irin Abu me nauyi Yana saukowa daga maqoshinsa zuwa kirjinsa sbd ya tabbatarda idan ba ciwonta yayi ajalinta ba to tabbas lameenu ya aika su BB rufe aikin kwata kwata kafin asanar da Jamaal sakamakon Wanda Shima akwai tanadin da yayiwa Hakan Amma a cikin sanyi da cike aiki take batareda barin kowace alama ba.

Tin daga nesa wutar Dake cin gidan sosai suke ganinta
Take jikin mum ya dauki rawa hawayen tashin hankali na ciko idanuwanta sbd Jamaal kada yace zai shiga gidan.

Dad da Shima dukkanin jikinsa ke cirewa sbd wannan tsoron tini yace ayi parking cikin daga murya.

Ko gama parking baayiba Dad ya Bude motan ya fito yayi gurin Jamaal da sauri Yana Kiran sunansa hankalinsa tashe sedai Jamaal din Baya jin komai fadila kawai dayake buqatan Gani a hannuwansa.

Haroon da siddeeq ne suka hango zuwansa da gudu Haroon yayo gurinsa ya tareda tareda rungumesa sosai daidai isowan Dad idanuwansa kaman zasu fado sbd tashin hankali da sauri ya rungume Jamaal din ta Baya Shima Yana Jin zufa na tsinko masa.

Jamaal zare jikinsa yakeson yi Amma sun masa wata irin kyakkyawar runguma Haroon na cewa

"Fadila is safe siddeeq ya fito da ita"

Wannan kalaman ne suka Saka Jamaal din jikinsa ya saki tsawon minti Daya kafin ya dago idanuwansa jajir Yana buqatan ganin fadilan.

Ambulance ta asibitinsu ce ta iso cikin gaggawa aka dauki Fadila wadda batasan Ina kanta yake ba tareda umma wadda itama take a sume sbd hayaqin Daya bugeta.

Motan kashe gobara ce itama ta iso daidai lokacin sukuma suka bar gurin zuwa asibiti cikin gaggawa.

Siddeeq barinsa Akai tareda mutane da masu kashe gobara harma da Police da suka iso gurin cikin tashin hankali sbd baba Dake cikin gidan baa fiddosa ba,

Mum asibiti suka marawa su Jamaal Baya itada da Dad Wanda yakejin Yana dawowa hayyacinsa daidai sbd barin yayansa gurin Dan motan Haroon ne bayan ambulance din sukuma suna bin tasa motar.

Ana Isa asibiti cikin gaggawa likitoci suka amshi fadila da umma aka shige emergency dasu
Haroon kuwa da Dad Jamaal din suka zauna tareda dashi Dan basa karfin gwiwa.

Mum da ita aka shiga emergency din Dan taimakon gaggawa fadilan take buqata sbd Bata tareda oxygen nata tini ya fizge yana can.

Zaman jiran tsammani me azabar gaske sukeyi dukkaninsu tin daga Jamaal din har Dad da Haroon,

Haroon sai Kai da kawo yakeyi Yana Jin kaman ya yayewa Dan uwansa abinda yake ji.

Sai asuba likitocin suka samu shawo kan fizgo numfashin fadila aka Saka mata wani oxygen din bayan mum ta tantancesa.

Umma kuwa Daman tini ta farfado Dan Daman hayaqi ne ya sumar da ita Amma dayake mijinta da yarta ne a ranta tini ta farko cikin sanyin jiki da fargaban baba da akace Yana can tareda siddeeq ita Kuma fadila tana asibitin tareda ita.

Dad da mum ne suka koma gida bayan sallan asuba suka bar Haroon tareda Dan uwansa.

Suma bayan sallan asuba dubo fadilan yai suka dawo office dinsa anan yayi shiru Yana tinanin yanda zasuyi su sanar da umma gawar baba na asibitin.

Siddeeq ya kalla cikeda kulawa da tausayawa Dan Shima maraya ne gaba da Baya su baba dinne gatansa danginsa yanzu baba ya rasu.

Har karfe tara na safe suna asibitin Kuma Basu sanar da umma komai ba sai guraren goma suka taho dakin datake Jamaal ne Kai tsaye ya sanar da ita rasuwan baban cikin dacin zuciya da tausayi me tsanani.

Numfashi ta sauke ahankali me zafin gaske batareda ta motsa ba sbd jikinta ya Bata Hakan Kuma zuciyarta tini ta amsa Hakan ta karbi jarumta.

Dago jajayen idanuwanta dasukai jajir tayi ta Kalli siddeeq Dake Hawaye sosai zuciyarsa na tarwatsewa.

Cikin karfin hali ta Bude Baki ahankali tace

"Haka Allah ya kaddaro Kuma na amsa wannan hukuncin na ubangiji,Allah yaji qansa yayi masa Rahama ya bamu danganar rashinsa."

"Amin" dukkaninsu suka furta cikin damuwa da sanyin jiki.

Karfe goma da Rabi Akai janazah dinsa aka rufesa suka dawo.

Kaman yanda yake ayau din zaa daura aurensa da fadila baa daga ba Dan haka bayan karfe biyu na Rana aka halarci masallacin da zaa daura musu aure.

Cikin fararen kayanda suka bayyanarda kamanninsu sosai shida Haroon suka fito tareda mahaifinsu Wanda Shima fararen kayan ne a jikinsa irin na 'yayansa Wanda aka zuba kudi kaman baa San darajansu ba aka Siya kayan aka Dinka.

Qamshinsa daban yake Dana kowa Dan haka take qamshinsa ya doke nasu nasa kadai ake ji Kuma a Hakan cikin Baya tattareda walwala ko Daya sbd halinda matarsa take ciki duk da haka kawai saukin da Basu tsammata ba yazo mata da safen duk da batada karfi ko kadan har lokacin Amma ta Bude idanuwanta sosai tayi magana dashi tareda nuna masa ta samu karfinda inshallah zata iya adon aurensu da zaayi a yau din.

Karfe biyu daidai Aka daura masa aure da Fadila kaman yanda yake buri da fata ta tabbata cikakkiyar hankalinsa,matar Dr Jamaal Mamman seelah.

Bayan daurin auren Yan jarida da media da ba'ama San ya Akai suka sani ba suka karaso gurin sedai kafin su samu Daman daukan hotinansa yabar gurin batareda ya tsaya komaiba sedai Haroon ne ya tsaya a amatsayin Jamaal din

yana miqa godiyarsa ga wainda suka halarta Yana amsa adduoinsu batareda ansan bashi a gurin ba Dan hatta su Dad din Basu dauka Haroon bane Jamaal ya tafi.

Siddeeq ne yake Jan motar Jamaal din har suka Isa asibiti zuciyarsa wani fayau yake jinta jikinsa na sanyi kalau batareda yasan wane irin yanayi ne yakeji a jikinsa ba.

Suna Isa asibitin kusan dukkanin wani likitan Dake asibitin Yana dakin fadila cikin tashin hankali da gaggawan cetan ranta kowa na nuna kwarewansa Dan sanin mahimmancinta Mai tsananin girma ga Dr Jamaal din.

Hatta mum dinsa tana dakin cikin nuna kwarewanta da son cetan ran sirikitarta wadda rashinta zai taba rayuwar danta fiyeda yanda suke tinani.

Ganin umma zaune bakin dakin idanuwanta jajir dukkanin jikinta a Sanyaye zuciyarta tayi wani irin nauyi da kirjinta ke Neman kasa dauka.

Dakatawa yayi cak bakin Kofar dakin ganin yanda nurses ke fitowa da gudu suna komawa cikin bawa abinda sukeyi mahimmanci me girma.

Siddeeq ma kasa motsawa yayi daga inda yake tsaye zuciyarsa na bugawa da karfi ya juya Ina Dr Jamaal din yake ya kallesa da jajayen idanuwansa Dake sauyawa da fargaban abinda suka tarar.

Kasa motsawa Dr Jamaal din yayi tsawon mintina biyu Yana Jin dukkanin wani sanyi na gauraye gangar jikinsa kafin ya daga kafafunsa ahankali ya Isa kofar dakin ya Bude ya shiga daidai kunnuwansa na dauko sautin maganar Dr zayyan.

"Time of Dead 3:06"

Innalillahi wainna ilaihirrajiun" shine abinda mum ta fada jikinta a matiqar Sanyaye zuciyarta na shiga wani irin sanyi da mutuwar jiki me tsananin gaske.

Sauran likitocin ma gaba Daya jikinsu sanyi yayi musulman ciki suna ambatar

"innalillahi wainna ilaihirrajiun da allahu Akbar"

Kafiran ciki kuwa tausayinta Dana Dr Jamaal ne yake rufesu sbd tasha wuya sosai itama a iyama lokacinda ta fara zuwa asibitin kadai bare rayuwarta ta

Baya.

Ficewa likitocin suka fara ganin Dr Jamaal din a tsaye bayan sun rufeta har fuska sun gama rubuta komai a file dinta anyi signing anrufe an ajiye a gefe shikenan ita ta huta da gwagwarmayar duniya.

Mum dinsa ce kadai ta rage ta tako ahankali batareda ta iya cewa komaiba sai hawayen Daya ciko idanuwanta Yana gangarowa ta rungumesa ahankali cikin mutuwar jiki tana basa hakuri hawayenta na Kara gudu.

Fashewan kukan umma me sautin daya sake karya zuciyar kowa ne ya sauka cikin kunnuwansa take ya rintse idanuwansa dasukai wani mummunan ja yanajin dukkanin zuciyarsa na kakkaryewa tana watsewa.

Siddeeq ne ya rungume umma Yana tarota jikinsa sbd kukan datakeyi hadda na mijinta data rasa a ranar kukan Bai fitoba sai yanzu data rasa yarta taji abinda ya dunkule a zuciyarta ya fashe mata.

Wani irin kuka me cin Rai da qunci me tsanani takeyi sautinsa na karya dukkanin zuciyoyin sauran likitoci da Jamaar Dake gurin Amma Babu me iya cewa komai sbd tana buqatan yin kukan.

A ciki ma mum ce keyiwa Jamaal din kukan dashi zuciyarsa Bazata iyaba sbd Jin ma yakeyi baida sauran emotions kwata kwata bayajin komai face dutse a zuciyarsa.

Labarin na Isa gurinsu Dad da Haroon gabaki dayansu asibitin suka dungumo cikin tashin hankali musamman Haroon Dan kuwa JAMAAL ne a ransa,
Jin yakeyi rasuwar fadilan Shima tana gigita kansa da nutsuwansa dan haka a rikice ko Gani sosai bayayi suka iso asibitin.
##MAMUH

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
26
Shi kansa Dad da Dad Lameenu cikin damuwan halinda Jamaal yake ciki suke,
Mum Atee da Ayesha ma tini suka iso motansu mummy Sarat na bayan tasu Dan haka take asibitin ya cika da familyn seelahs cikin damuwa da tashin hankalin yau wace irin Rana ce?
Mahaifinta ya rasu yau,
An daura mata aure yau itama ta rasu a yau din.

Haroon na isowa kallo Daya yayiwa Dan uwansa yaji idanuwansa sun ciko da Hawaye masu tsananin zafin gaske suna gangarowa ya rungume Jamaal din.

Dad ma na isowa rungumesa yayi Yana kallan mum Dake hawaye sosai sbd tausayin fadilan da wuyar datasha tareda tausayin danta Dan shine yake cikin azabar zuciya yanzu me tsanani ta sani.

Dakin gawar suka bari suka koma office dinsa gaba dayansu familyn kowa fuskansa Babu dadi Dan tausaya masa bisa ba rashin dayayi Dan kuwa Babu Wanda Bai tabbatarda irin so da matsayin da fadila take dashi a rayuwarsaba.

Umma siddeeq ne kadai a tareda ita sai mum data koma gurinsu daga baya Dan ummanma itace abar tausayi fiyeda kowa Dan itace tayi rashinda sai me karfin Imani ne zaiyisa Rana Daya Bai zauce ba.

Ganin Halinda umman ke kokarin shiga ya Saka mum Bada umarnin a kwantar da ita cikin gaggawa Dan taimaka mata.
Bayan an kwantar da umman harma anyi mata allurai da wasu abubuwan an samu tayi bacci ta baro gurinta ta dawo gurin Jamaal Daya kebe kansa a dakin dayake cikin lafiyayyar office dinsa ta fara kokarin yi masa nasiha da basa karfin gwiwan bawa zuciyarsa hakuri.

Gida kowa ya koma sbd Shirin janazah dinta wadda zaayi a Seelahs din bisa ga umarnin Dad tinda ta riga ta zama matar dansa.

Kafin lokacin yayi Yan uwan umman su uku tini suka iso daga garinsu mata biyu namiji Daya.

Su kansu sun tausayawa Jamaal sosai bayan yar uwarsu dasuke cikin tsananin tausawa rashin datai.

Fadan halinda Jamaal ya shiga Baya misaltuwa Dan kuwa ya kebe kansa daga kowa baya buqatan kowa Baya son kusanci da kowa ko kadan.

Abu Daya da suka sani shine Babu Wanda yaga hawayensa bayan Dan uwansa idanma yayi sbd ya nesanta kansa da kowa bayan Haroon Babu Wanda yasake ganin ko fuskansa.

Yanayin jikin umma Daya rikice da Kuma shi kansa Jamaal din Daya rufe kansa ya Saka dole aka daga jana'iza din har zuwa da safe dakuma yayan baban fadilan Dayake hanyar isowa Shima.

Sai dare sosai Jamaal ya baro asibiti tareda Haroon suka iso gida bayan Haroon yaje ya kamawa Yan umman din masauki hakama Dan baba ma Daya iso duka guri Daya aka saukesu tinda gidan ya kone Babu yanda zaa iya kwana cikinsa.

Koda suka iso gida karfe kusan Sha biyu na dare Dan haka Kai tsaye part din Jamaal din suka nufa.

Mum da Dad ne a palon suna magana cikin Dan daga murya sbd bacin ran da mum ke ciki me tsananin gaske tace

"Kasan Hakan shine yayi sanadin rasa ran yarinyar Nan bawai gobaran da aketa yadawa ya kasheta ita da mahaifinta ba?

Tayaya zaace acikin asibitin iya oxygen dinta ne datake amfani dashi ake gurbatawa da Poison,

Shin bakai tinanin halinda 'danka zai shiga ba idan ya rasa macen dayake so fiyeda komaiba?
Tayaya kake tinanin zaka fuskancesa idan yasan sakamakon Poison datake shaqa a oxygen ne ta rasu,
Tayaya kake tinanin zai amsa zancen kaman kasheta ne Akai Kai tsaye Babu kwana kwana?
Bakaji tausayin yarinyar Nan ba tsawon rayuwarta rayuwa takeyi cikin wahalar rashin numfashi sai an Siya mata??

Cikin nutsuwa batareda daga hankali ba Dad din ya kalleta da idanuwansa yace

"Ko zan me kike nufi da wainnan kalaman naki?
Me kike nufi da oxygen nata?
Ke da kike likita kikasan aikinki har kikasan akwai poison a iskan datake shaqa meyasa Baki sanar masa shi 'dan naki ba kika bari har ta rasa ranta....

Katsesa mum tayi hawayen idanuwanta suna qara gudu tace

"Ban taba son sanin 'yayana Susan waye Asalin mahaifinsu ba sbd Hakan zai tarwatsa zuciyansu,Amma wlh tallahi Babu ranar da bana danasanin Kaine uban yayana masu tsafta,
Me kake tinani?
Na fito na fadawa JAMAAL Ina tinanin mahaifinsa yasan Menene yake damun matar da zai aura sbd shine yasan meye ne yake damun oxygen datake shaqa??
Bazan fada masa ba Amma koman Daren dadewa yayanka zasusan waye Asalin mahaifinsu Wanda Baya barin komai ba dalili,
Yanzu data bar duniyar saika ringa kwana da Shirin koyaushe danka zai iya sanin waye ya kashe masa matarsa data mutu a ranar da aka daura masa aure da ita...

Wani numfashin me sanyi da nutsuwa Dad din ya sauke zaiyi magana Haroon dayake gaba ya shigo Yana kallan mum dinsu da kalaman dayake ji abakinta Dan kuwa bazai taba yadda da Dad dinsa zai iya kisa ba duk da Barnar dasuke aikatawa bayan fage Amma mahaifinsa bazai iya kashe Rai ba bare macen da already tana fama a tsakanin Rai da mutuwa.

Jamaal kuwa idanuwansa dasuka qarasa rinewa gabaki Daya ya dago ya zubawa Dad din Wanda ya miqe tsaye Yana kallan jamaal din zufa na joqosa daga kuryan jikinsa.

Mum ma mummunan faduwa gabanta yayi zufa na tsitsifo mata Dan kuwa Bata fatan Jamaal yaji abinda suke fada.

Dad Jamaal din yake kallan Yana kokarin danne abinda yake ransa Yana ambatar sunansa cikin kulawa zeyi magana Jamaal din ya juya ya kallo Mum ya Bude bakinsa da yayi masa wani irin mummunan nauyi Kai tsaye yace

"Results din fadila duka sun tabbatarda oxygen nata ne yayi sanadin komai har rasuwanta right??

Wani mugun zufa da faduwan gaba ne ya Saka mum juyawa ta Kalli Dad Wanda Shima ita yake kalla kafin ya matso zaiyiwa Jamaal din magana Jamaal ya katsesa da sake jefawa mum tambayarsa.

Numfashi ta sauke zuciyarta na nauyi ta matso tareda kamo hannunsa Daya cikin tsananin sanyi da baqin ciki tace

"Eh, oxygen nata shine yaringa poisoning nata ahankali harta rasu Amma muna Saka ran daga karfin da yayi mata ne da oxygen din shiyasa ya zama kaman poison ya mata illa..

Baice komaiba zame hannunsa yayi daga cikin nata ya zari keys din hannun Haroon ya juya ya fice.

Duk yanda Haroon yaso binsa kasawa yayi sbd mamaki da shock din dayake ciki Shima duk da Babu tabbacin Dad dinne itama mum kawai zargi ne sbd Dad baiso aurenba da farko.

Koda ya Isa asibiti Kai tsaye file din fadila ya dauko yafara dubawa ko Gani sosai bayayi kafin ya fito ya nufi lab dinsu a cikin Daren ya buqataci sabon awo tsakanin oxygens din sabo da tsoho Dana fadila.

Haroon baro gida yayi ya biyosa asibiti Amma Sam kwata kwata ya kasa samun ganinsa Dan kuwa a cikin Daren gaba Daya ya daga hankalin asibitin akan sabon awo da komai Wanda ya bawa likitoci da ma'aikatan lab dinsu tsoro da shiga tashin hankali Dan kuwa da farko binciken boye Akai baa son daga zancen.

Koda asuba tayi tsaban tashin hankali har an hada results din Wanda ya tabbatarda mutuwar fadila due to gurbatan oxygen nata ne.
##MAMUH

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
27
Wani mummunan jiri ne ya dibi Jamaal din Wanda sai alokacin ya fashe Da kukan Daya girgiza Haroon da mum dinsa da isowanta kenan asibitin cikin tashin hankali da tsananin tsoro sbd Kwana sukai itama da Dad din cikin tashin hankalin fitina da maganganun da suka Sakata Jin son barin qasar a ranar.

Duk wani sheda ko alaman inda poison din ya samu shiga oxygen dinta Jamaal yayi daga daren zuwa safe Bai gane ba sai Abu Daya wato yawan zuwan BB asibitin Wanda ya samu tabbacin duk karshen wata yake zuwa so Daya dubiyan kaninsa yaronsa da suka karya da gangan suka ajiyesa asibitin yaqi warkewa sbd Daya kusa warkewa saisu sake lalata gyaran.

Hakama mum dinsa ta kasa fada masa komai taqi sake maimaita masa tabbas mahaifinsa ne yayi Hakan,

Wane asalin rashin Imani ne zai Saka a taba fadila macen da numfashin duniya Bata iya shaqa saina Siya,

Gida suka dawo Kai tsaye palon Dad dinsa ya nufa zuciyarsa na qunan dayake Jin har wata wuta ce take cin kansa.

Babban abinda fara bawa su Dad din mamaki da shakka shine Kai tsaye kafin goman safe tini akaiwa su BB da yaransa kaf mugun Kamun Daya fara yaduwa a labari tareda tabbaci akan zargin kamasu da sirka poison acikin oxygen na asibitin SEELAHs Wanda yayi sanadin rayuwar matar Dr Jamaal Seelah din,
Hakan ya qarawa labarin saurin yaduwa sosai da gudu kaman wutar daji take Yan jarida sukaiwa asibitin da gidan kawanya.

A yanda Jamaal ya nufo su Dad din mum dinsa ce tayi saurin Shan gabansa tareda riqe hannunsa Dan duk mugun halin Dad bazata so yayanta suyi sa'insa da mahaifinsu ba bare maganar datai da Dad a ajiyan ta tabbatar mata da Dad Babu abinda bazai iyaba Dan haka ta riqo hannun jamaal ta girgiza masa Kai cikin qaramin sauti ta Bude Baki tace Karkayi komai karkace komai wannan umarni nane,
Haqqin dayake hanunusu bazai taba taba yayana ba kaman yanda bakuda sani bakuda haqqi bazanso ka taba gurbata kanka aikinsu ba.

Cikin Bacin Rai me tsananin gaske Dad da Alh Lameenu suke kallanta zaiyi magana cikin hada zufan tashin hankali mum Atee ta shigo cikin tashin hankali tana sanar musu ga asibitin SEELAHs can ana kokarin Banka mata wuta.

Dayake tini Jamaal ya Saka Aka sallami kowa tareda dauke gawar fadila tana can anai mata sutura baice komaiba Se hannun mum din Daya kama ya juya suka bar palon sbd ta dauresa da maganarta da alkawarinta bazaicewa su Dad komai ba Amma yayi alkawarin sai ya tabbatarda basuda komai,
Ahankali zai tabbatarda yasan komai da mum taqi fada masa da abinda su Dad din ke boyewa,
Bai damu da dukiyar seelahs ba Saiya tabbatarda Babu komai Daya rage acikinta sbd da ita akai kisan fadila.

Karfe goma da Rabi Akai janazan fadila aka rufeta,
Ana dawowa ya sallami su umman da kudi me yawa da zaa kula da umman kafin ya waiwayosu.

Siddeeq kuwa anan Lagos din ya samar masa gurin zama kafin daga baya zai bisa idan anmasa komai.

A wannan mummunan ranar baa kwana ba SEELAHs suka rasa asibitinsu tareda shiga shakku a zuciyoyin mutane da take abin yafara kokarin tabasu duk da su Dad din sun tashi tsaye kada Hakan ya tabasu Dan kuwa sunfara ganin matsala babba na Neman tinkaro su.

A wanna mummunan ranar Dr Jamaal Mamman seelah ya Yanke duk wata alaqarsa da ahalin seelahs ya goge sunansa daga kudin tarihin gidan Dan har abada bazai taba sake hada alaqa dasu ba kowace iri ce ya yanketa Baya buqatanta.

Haroon ya shiga Mummunan tashin hankalin wannan masifar data fadowa familynsu a Rana Daya lokaci daya,
Tayaya zai iya rayuwa a tsakanin mutum biyu dayafi so a rayuwarsa sun rabu sun yanke alaqa a tsakaninsu,
Kaman yanda Jamaal din ya Yanke alaqansa da Dad Kai tsaye Dad din cikin fushi da bacin Rai ya yanke Shima alaqansa dashi sbd Hakan ne kadai zai rufa asirinsu su tsira a yanzu sbd a wuni Daya yayi qasa da asibitinsu ga faduwansu na Neman tasowa a qanqanin lokaci Dan haka nesantar su da Jamaal din kadai zai sakasu samun tattara mutuncinsu su dawo dashi a idon mutane da abokan kasuwancinsu kafin manyan sirrikansu su bullo komai ya lalace batareda sun shirya ba Dan Basu hango wanna masifarba su kansu a yau din.

Dr Aleena kanta Hakan shine nutsuwa da Kwanciyar hankalin datai shekaru Bata samu ba yanzu da alaqa ta Yanke kwata kwata tsakanin Jamaal dinta dasu Mam din Dan haka ta tattara itada Jamaal a ranar suka bar qasar a cewansu har abada bashi ba dawowa bare alaqa tsakaninsa dasu,
Haroon na ran Mum Amma Kuma koyaushe Haroon din zabar mahaifinsa yakeyi akan mahaifiyarsa Amma Kuma kaunar Dan uwansa ta take ta kowa da komai Dan haka tafiyar Jamaal ta jijjiga duniyarsa Dan baisan ya zaiyi rayuwa babu Dan uwansa dayake kalla kaman Yana kallan mahaifiyarsa da Bata taredashi.

Jamaal Koda yabar qasar Nigeria yabarta cikin tsananin ciwo da quncin zuciya da tarwatsewanta,
Abinda yakeji a zuciyarsa wani dutse ne da bazai taba sauka da zuciyansa ba,
Son fadila yayiwa zuciyarsa mummunan illan busar masa da ita da bazai taba hucewaba bare son wani abin ba daban bama mace ba wadda wannan Kuma wani Babi ne Daya rufe ya kona bare ma ace akwai ranar budewansa.

Ita kanta mum tabaro kasar cikin tsananin damuwa da ciwon Rai sbd sun ringa sun sauya mata 'da da dawowansa daidai Kila har abada Se Kuma wani

ikon Allah datake fatan yazo,amma Jamaal Kam ya koma Asalin Dr jeey dinsa babu wata sakewa ko walwala Se kamewa.

Suna Isa Poland ko wata Bai rufa ba ya tafi Umrah daga can ya wuce Hutunda Bai dawo ba sai bayan watannin dasuka sauyasa ya koma wani lafiyayyan balareban bature ya sake budewa sosai sbd geamin da sauya rayuwarsa da yayi gaba Daya.

Ita kanta mum din ganinsa Saida ya Sakata Tara hawayen farin ciki a cikin idanuwanta na ganin wata irin kyau da tsantsan hutun Daya bayyana a tareda shi da wata lafiyayyar qasumbar data kwanta a fuskansa farinsa yayi mugun bayyana.

Sabuwar asibitinsa akai bikin budewa take yafara aikinsa tareda Bude Babin sabuwar rayuwa.

****
Ameenatou,Ameenatou wlh idan na kamaki a hannuna saina balla hannunki"

Hafiz ne ya fada Hakan Yana daga takarmansa Da baa Saka musu ruwa a jiqe suna tsiyayar ruwan wankan datai masa dasu zuciyarsa kaman zatai bindiga ta fashe sbd takaici.

Dadah Dake tayata Saka zip din doguwar rigar atampar data Saka sbd duk girmanta da zamanta budewar komai yi mata akeyi sbd tsaban gata da sangarta hatta ruwan wanka wani lokacin se an Saka yananta sun Kai mata tace

"Meenon Dadah wanka kikai masa da takarma ko sbd Neman magana?.

Dariyar data lotsa dimple dinta sosai tayi tana yin Dan qasa da murya sbd kada Yaya Hafiz din ya juyota tace

"Dadah bansan takarman basason ruwa bafa Kuma tin safe yau fada kawai yaketa yi dukana yakeson yi kawai"

"Duka dai? Kaman wata babyn roba Saiya dakeki Ina kallo.

"Eh Dadah nidai wlh karki bari ya dakeni tinda dai na zama budurwa kaman yanda Babbah ya fada."

Kaman Yaya Hafiz din yaji abinda ta fada ya shigo dakin da takarmin Yana

cewa

"Wlh bazan yadda ba tinda aka hanani dukanki se anbiyani takarman Nan,
Kunsan nawa na siyesu kuwa?
Idan ban ballaki ba zuciyata bazaitai sanyi ba"

Kanta yayo tayi saurin yin bayan dadah tana cewa

"Wlh bansan sabo bane bafa"

Wani sabon takaici ne ya ciyosa yace

"To dole Se kinmin wanka da takarma tsaban reni"

Kallansa dadah tayi zatai magana yace

"Allah dadah Kun gama Saka yarinyar Nan ta Rena ni,
Kwata kwata Kun sangartata Bata ganin girmana,
Yanzu fa wannan takarman bayan daurin auren da zani sbd zuwan Asalin me gidanmu na aikin site da zaiyi a kwanakin Nan ya sakanu siyansu sbd zaa dibi ma'aikatan da zaa tafi dasu can kamfaninsu na Lagos aiki ni inason zuwa shiyasa nakeson fitowa fes Amma tsaban mugunta yarinyar Nan ta jiqamun su"

Daga bayan dadah so takeyi tayi magana tana gudun ya jefota da takarman Dan haka Saida ta sake shigewa sosai tace

"Wannan baturen Dana taba Gani a site din da dadewa danaje karban kudin tafiya makaranta gurinka shine ze sake zuwa?
Dan Allah zanje kaje Dani Yaya Hafiz zan shanya Maka takarmin.....

Cikinta yayo cikin takaici kafin ya kamota Babbah ya shigo gidan take ta Bude Baki daga bayan dadah tace

"Babbah gashinan Yaya Hafiz ze taba baka yar budurwa"
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*

Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
28
Babbah na Jin Hakan yasan itace batada gaskia Dan bakinta Sam Baya bari tayi banna ko Neman magana ta cut dan haka ya nufo dakin Yana cewa

"Kai Hafiz banason zafin Rai fa,
Me tayi?
Yafe mata idan ta sake na bari ka Dan kadan dauki matakin Amma dai yanzu yafe mata kaga tayi wanka Karka Sakata gumi."

Wani sabon takaici ne ya siqe Hafiz yace

"Hakafa da ake mun ya Saka yarinyar Nan ta Rena ni gaba Daya bata ganin girma na,
Allah duk ranar data shiga hannunsa saina balla siraran kafafun Nan nata"

Fitowa tayi daga bayan dadah tana marairaice fuska hadda ciko idanuwanta da Hawaye tana matsowa gabansa ganin Babbah na Nan tasan bazai taba barin a Daketa ba a gabansa shiyasa ta fito din ta Kalli Hafiz Dake juyawa zebar dakin tayi saurin riqo hannunsa tana sake narkar da fuska tace

"Yaya Hafiz dina Dan Allah kayi hakuri wlh tallahi inshallah bazan sake jiqa Maka takarminba bama zan sake sakawa ba nayima Maka alkawari na shiryu"

Dago idanuwansa da sauran fushi ke cikinsu yayi ya kalleta Yana Hana kansa hakura Dan yasan fada tayi indai itace ko fita bazaiyiba saita sake Bata masa Rai sunyi fada.

Hawayen idanuwanta take kokarin saukarwa tana sake basa hakuri take yaji zuciyarsa ta fara saukowa daga fushin sbd duk masifan rashin jinta Neman maganarta basa iya fushi da ita Dan kaman yanda su dadah suka gama sangarta haka Suma Yannan nata sun gama sangartata da kauna me tsananin gaske da dukkanin gidan ake mata Sam Babu me qaunar ganin hawayenta shiyasa idan taso Abu Hawaye take musu saisu kasa riqe fushinsu su watsar.

Hararta yayi Yana daga takarman Dake hannun nasa ya kalla kafin ya dawo da kallansa kanta Yana daidaita murya daga fushin da yayi yace

"Shikenan na hakura Amma kika sake tabamun kaya saina fasa Miki Baki kinsanni sarai."

Gyada Kai tayi da sauri tana cewa

"Eh bazan sake ba,komai bazan Saka tabawa naka ba saina tambayeka,Amma Dan Allah Yaya Hafiz da gaske baturen Nan zai sake zuwa site din aikinku?

Tsoki Hafiz din yayi Yana fincike hannunsa daga nata Yana wucewa cikin haushin ma Bata lokacinda da yayi Dan ya dauka tuban gaske tayi Ashe sbd me gidansu da shi Yama kasa iya riqe sunansa take magana Wanda Rabon da su gansa anjima sosai Dan tini aikin site din ya tsaya cak Anma Dena project din kwata kwata dukansu an sallamesu Se yanzu ne zaa sake tayarda aikin an mayar dasu aikin masu rabo kuwa har Lagos zaa tafi dasu.

Gefen dakinsu ya nufa ya shanya takarmansa kafin ya shige dakinsu Yana kokarin qarasa shirinsa ya fita abinda yake gabansa.

Ita kuwa juyar da idanuwanta tayi tana juyawa ta koma dakin dadah tana cewa

"Babbah nidai kace Yaya Hafiz koba yau ba idan baka Nan karya Dakar Maka ni,
Nida nakeson auren bature tayaya zai aureni idan akaimun Tambo."

Batareda babban ya kalletaba Yana fitowa daga dakin yace

"Bama ze fara dukanki ba bare tambon ai yasani sarai,
Yadai samu sa'ar dokarmun ke a Baya yanzu kuwa Babu yanda zaayi Ina kallan tsaleliyar budurwa a gabana Ina jiran ganin aurenta ya dakarmun ita, ko kudi aka basa bazai dakeki ba indai Ina Nan."

Dadi zancen yayi mata ta juyo tana kallan Dadah data karasa Saka mata zip tana cewa

"Dadah ko Babbah Baya Nan Dan Allah ki ringa tinawa Yaya Hafiz zancen Nan Koda nayi masa lefi"

Miqewa dadah tayi tana nufar gaban tsohuwar madubinta ta dauko turaren Ameenatun dasu Hafiz ke Siya mata Baya taba yankewa tareda duk wani abu da sabuwar budurwa ke buqata kwata kwata basa wasa da lalurarta ko buqatunta sbd tini suka manta da ba uwarsu Daya ubansu Daya da itaba Dan kaunar da suke mata kusan duk Neman da sukeyi Dan inganta rayuwarta ne duk da ta renasu sosai har gwara Yaya Abdul tana girmamasa sosai akan Hafiz data Rena sbd biye mata dayake yi kusan Babu ranar da basa fada tin kafin suyi wanna girman,
Da suka girma kuwa tini suka koma yanzu shiri anjima fada yace Saiya karyata ko balla mata kafafu.

Fesa mata turaren me sanyin kamshi daidai dadah tayi tana dauko mata hijab gogagge kalan kayanta ta miqa mata tana cewa

"Ki Dena shiga sabgarsa tinda Kinga dai bakyason tabo ko Daya a jikinki,
Idan Baki Dena ba ko a hanyar rakaki makaranta Saiya miki dukan ba sanin kowa bare me cetan ki."

Bata fuska tayi tana qarasa Saka hijabin tace

"Ai Babbah yace ko a waje karya taba masa ni"

Takarmanta dadah ta fitar mata kofar daki tana cewa

"Zo ki tafi kinyi latti sosai"

Jin haka ya Sakata fasa Saka takarman tana dawowa Baya ta dauko wayar Dadah din ta danna Taga karfe Hudu saura mintina kadan ita da ake fara tarewan latti karfe biyu da rabi.

Dadah na ganin ta ajiye wayar tana narke fuska tafara daga murya tana

Kiran Hafiz.

"Hafiz fito ka Kaita makarantar ka roqi malam Dan Allah ayi mata hakuri bazata sake latti ba uzuri ne yasakata lattin."

Hafiz Dake daki Yana Saka kayansa Yana jinsu yayi musu shiru Dan babu hakurin da zaije bawa malam Dan kullum haka takeyi duk ya lalace ya qare a hanyar makarantarta bawa malamai hakuri da uzurin karya Baya hanyar bokonta Baya hanyar islamiya kaman mara aikin yi.

Sake qwala kiransa Dadah tayi yanaji yayi kaman Baya gidan Dan yakai malaman suna ganinsa suke sauya fuska.

Babbah Daya fito bandaki sarai ya hango Hafiz din a daki yace

"Yana jinki Kaita ne bazaiyiba idanma kin takurasa haka zaibi hanya Yana mangaremun yar budurwa Dan haka muje na Kaita da kaina ai mun Saba ba akanta farau latti ba hakama ai uzuri ne,wuce maza muje.

Saka takarmanta tayi ta fito dadah na miqo mata jakarta tana cewa "A dawo lafiya yar budurwan Babbah"

Hafiz Dake kallansu ta window da harara yabi Bayan Ameenatoun Yana cewa

"Duk anbi an sangarta yarinya Bata ganin girman mutane Dan an renasa ace kullum Saiya Rakata makaranta saikace qaramar yarinya,
Duk an ishemu da wata yar budurwan Babbah da Dadah mtseww"

Dadah Dake jinsa cewa tayi

"Idan ka gama yi mana fada ubanmu saika fito ka wuce inda zaka tafi ka dawo da wuri ka biya mata ku dawo tare."

Yana Jin Hakan ya fito baice komaiba ya fice Yana gyara zaman rigar shaddarsa a jikinsa dan qamshin turarensa me arha na tashi Dan gurin fira zasu gurin budurwansa.

Yana fita Dadah ta bisa da kallan mamaki tana girgiza Kai Dan tasa wannan Doron dayake dagawa Yana qamewa fira zasu.

Yana fita Abdul ya shigo gidan sanye da kayansa na aikin securityn Bankin first bank kadai dayake ta gurarensu.

Gaida Dadah yayi Yana cewa

"Budurwan gidan ta fita ne naji gidan tsit."

"Taje makaranta Babbah ya tafi Rakata jiya da shekaran jiya bataje ba tana fama da yatsarta datai tintibe Se yau ya Sena mata ciwo ta shirya ta tafi"

Yana Jin Hakan yashigewansa Yana cewa

"Wannan budurwan daya bita da Kun cire mata shi Dan Babu Wanda zaiso ta ahaka Kun gama lalata kayarku"

Banza tayi masa ya shige ya tube ya fito sanyeda da wando dogo ba Riga da kwandon kayan wankansa ya wuce Bandaki bayan ya debi ruwa a bokita Dan Shima wankan zeyi ya fice fira zashi Shima yau din Dan ya kwana biyu Bai ziyarci budurwansa ba.

A hanyar makaranta Saida Babbah ya Siya mata agwaluma cikin bakar leda ta Karba ta Saka jaka suka Isa tana Dan narkewa babban shikuma Yana ganin Hakan ya Bada himmar yiwa malam bayanin rauni taji jinya sukai sosai.

Malam iliya ya Saba da wannan karfin halin na Babbah Dan haka baiyi musu ba yace Allah ya tsare gaba ta wuce aji kawai.

Wucewa tayi Babbah na mata adduar adawo lfy da adduar Allah ya Bata ilimi fiyeda kowa makarantar.

"Amin" tace masa tana wucewa gaba kadan kadan tasake cewa

"Babbah kasa Yaya Hafiz yazo daukan fa"

"Tin kafin a tashi zan korosa"

Dariyar mugunta tayi tana wucewa aji da sauri.

Tana shigowa ajin kawarta ta musamman ta tarbota cikin murna daga Nan sukai gurin zamansu.

Dayake sune manyan makarantar da zasuyi sauka a kwanakin kusa a tacesu shiyasa su kadai ne ajinsu daban Amma sauran makarantar kusan aji Daya suke sedai kowa da karatunsa da ake masa Yana bayarwa ranakun laraba da litinin.

Tin kafin lokacin tashi ya qarasa yi Babbah ya ringa Kiran Hafiz a wayarsa

me malatsai Yana cewa yaje ya taho da Ameenatou din.

Hafiz idan akwai abinda yafi zafi da takaici Yana cikinsa Dan kuwa a gaban budurwansa yake babbah keta masa wannan Kiran Dan haka dole yayi sallama da ita ya nufi hanyar makarantar Yana tafe Yana masifa da bacin Rai.

Yana Isa ana tashinsu suka kamo hanyar gida Yana Jin kaman ya mata shegen duka a hanya Amma Yana Hana kansa sbd balain Babbah dazai tarar a gida.

Ita kanta dayake tasan a siqe yake da ita Dan haka ta matso kusa dashi tana fada masa Dan Allah idan zaije fira gobe suje tare Taga matarsa su Saba mana.

Duk yanda zata Saka fushinsa sauka ta sani Dan itace ke kunnasa Kuma ta saukesa Dan haka kafin su Isa gida tini suka shirya fira sukeyi sosai hadda dariya.

Dayake magrib ta matso sosai suna Isa gida Baima shiga ba ya juya ya masallaci dagacan Kuma akwai inda zashi.
FOR MORE PAGES FOLLOW ME AT MAMUHGEE @AREWABOOKS
#MAMUH#
#AMEENATOU
#HOTLOVESTORY
#HOTROMANCE
#ZAFIN KAI
#TWINS

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700

Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
29
Da daddare Bata wani ci abinci ba furan babbah kadai tasha kadan tace batacin abinci ta koshi,

Rakata wanka dadah tayi sbd Bata iya zuwa bandaki ita kadai da daddare sai anrakata Dan haka tana Gamo wanka doguwar Riga kadai ta Saka ta Kwanta bacci Dan Allah yayi mata baccin wuri Dan haka yawanci Se dare Hafiz ke samun cikakkiyar yanci a cikim gidan daga wahalan Ameenatou da takaicinta.

Dakinta shine a tsakiyar nasu Babbah Dana su Yaya Hafiz din sbd duka duka gidan dakuna uku rak sai bandaki da tsakar gida da kitchen dinsu karami.

AMEENATOU BABBAH wadda kusan kowa ya sani da budurwan Babbah kaf wainda ke garin shedu ne Kuma zasu Bada sheda a koina cewan Babu yar gata Kuma sangartacciyar da gata yayi mata yawa a garin kamarta,

Babbah fadan tsananin son dayakewa yar budurwan tasa bama Mai yiyuwa bane,hakama dadah akanta kowa ya sheda yakuma tabbatarda son da ake cewa ana yiwa auta na musamman ne Dan kuwa kauna da banbancin datake nunawa akan Ameenatou daban yake a ranta akan sauran yayan nata.

Su Hafiz kuwa dasuke yannanta sunfi kowa Bata kariya da tattalin tarbiyanta da kiyaye huldodinta da kowa,
Bata zuwa gidan kowa,Bata yawo baa aikenta komai yimata sukeyi,
Tin tana yarinya sune suke Rakata makaranta su daukota haryanxu data zama budurwan datake nanatawa Rakata akeyi makaranta kuma a koma a rakota gida ko Daya daga cikinsu Kokuma Babbah da kansa Wanda duk manyancinsa babu ruwansa zuwa yakeyi takakka idan aka Daketa a makaranta shiyasa kowama ya gaji ya shafa mata lafiya basa dukanta sbd

sharia ce da zance Baya karewa har gaban manyan gari Kona makaranta
Babbah Sam Sam Baya yadda da laifin Ameenatou Koda sama da kasa zata hade kuwa Baya yadda da tayi lefi Kuma wani lokacin Yana sane da batada gaskiyar Amma Baya yadda sedai idan sun dawo gida yayi mata fadan kafin ya lallasheta daga baya.

Duk da su bamasu hali bane Suna rufin asiri sbd su Hafiz na aikin karfi hakama babban duk da manyanci sosai Yana Dan babbuga sanaar dabbobin Daya Saba Babu wani samu sosai Amma sbd inganta rayuwan Ameenatou Babu Wanda yayi qasa a gwiwan Nema.

Ameenatou Bata rasa komai ba sbd Tako ina Babu abinda take nema ta rasa,
Tana cikin gata gaba da bayanta hakama har yanzu datake budurwanta batasan basu babbanta ne suka haifeta ba kaman yanda a garin kaf Babu Wanda yasan da Hakan,
Har mamakin akeyi yanda sukeda manyanci sosai Amma sunada qaramar 'ya sedai Babu Wanda ya taba kawo tinanin basune asalin iyayen nataba duba ma da yanda suke tsananin jinta fiyeda komai.

Ameenatou duk gatanta da sangartan da Akai mata tanada tarbiya sosai Dan kuwa sun Bata kyakkyawar rayuwa su Hafiz musamman Yaya Abdul Basu bari gatan ya lalatata gaba Daya.

Bangaren Bata ilimi kuwa sai inda karfinsu ya kare Dan kuwa makarantar primary ma ta kudi tayi Bata gwamnati ba duk da bawai kudi Basu yawa sosai ba Amma dai private school ce.

Secondary ma Bata gwamnatin takeyiba yanzu tana shekarar gamawa Dan haka daidai gwargwado tanada iliminta kaman su Hafiz din da Suma sunyi karatun bokon Dana Addini kowannensu nada diploma Amma dai Babu wani aikin bare Dora karatu me kyau da amfani sai suke Yan buge bugensu.

A cikin gidan kauna da shaquwa ce sosai a tsakaninsu da barkwanci tin daga kan babban har Dadah dasu Hafiz,
Sosai suke cikin Kwanciyar hankali da farin ciki,
Hafiz da Ameenatou akwai shakuwa da rigima sosai fiyeda Yaya Abdul duk da Shima akwai shaquwan da kauna sosai Amma shi Bata renasa ba kaman yanda ta Rena Hafiz.

Duk inda zata makarantar boko ko islamiya ko wani abin daban basa barinta fita ita kadai shiyasama duk irin shirmen soyayyar da kawayenta keyi ita Bata yi hakama Allah Bai Saka mata shaawan soyayyar da sukeyiba kwata kwata batama ganin kanta a wadda ta Isa fara soyayya.

Akwai masu Sonta da yawa sbd kyau da haskenta tareda gatanta da kyan jikinta Amma suna shakkar tinkararta da maganar soyayya sbd kullum tana tafe da babanta ko yannanta hakama gata kaman Me rariya a Baki koka zagaya kaje makaranta kace kana Sonta tana Isa gida take fadawa yayunta ko Babbah azo ana rantse rantse a gaban me gari ace kana bibiyanta shiyasa kowa ya kama kansa da ita duk da akwai Yan nacin da duk masifar Babbah suna Nan kan bakansu.

Tinda dadewa Yaya Hafiz ya daukota daga makarantar boko ya biya da ita site gurin Hafiz yace tinda lokacin tashinsu yayi ya wuce da ita gida shi gurin aikinsa ana nemansa.

A ranar idanuwanta suka ganar mata kyakkyawar halittar da Bata taba ganin me kyansaba tinda take.

Da farko kasa yadda tayi da mutum ne seda ya tinkaro inda suke sanye da baqaqen kayan dasuka fidda farinsa sosai ga Rana tana haskasa sai wani daukan ido yakeyi duk sai Taga su Yaya Hafiz da sauran ma'aikatan gurin sun koma mata kaman wasu halittun daban ba mutane ba.

Bakinta ta sake tana kallan fuskarsa dake sanye da black sunglasses me shegiyar kyau da fcap akansa Yana magana kaman ranar zata kashesa Dan kuwa alamunsa sun nuna Hakan.

Fitowa tayi daga inda take ta nufi inda yake Kai tsaye Dan kuwa idan ba gabansa ta tsaya tayi masa kallan kurulla ba bazata tantance abinda idanuwanta suka ganiba.

Hafiz ne yayi saurin riqeta daidai tana gap da Isa gabansa Yana cewa

"Ke Ina zakije?

Kwacewa tayi tana cewa

"Yaya Hafiz wannan baturen shine oganku?
Kullum ze Riqa zuwa ne??

Tunkuda keyarta yayi ya maidata inda yace ta jirasa tayi wani Dan qaramin ihun Jin zafi tana cewa

"Tambaya fa nayi Kuma baka ban amsaba ai"

Jin maganar mace a gurin ya Sanya JAMAAL juyowa ya Kalli gurin daidai Hafiz na rufeta da bayansa Yana fuskewa.

Ganin Babu kowa yasashi juyawa Yana ci gaba da sauransu bayanin da ake masa ita kuma ta fito tana cewa

"Bazanyi magana ba kallansa kawai zan riqa yi" ta Dora hannunta Daya a bakinta tana zubawa Jamaal din idanuwanta masu haske da kyau tareda yin shiru.

Sautin muryansa me tsananin nutsuwa da kamewa acikine Taji Yana magana Rabi duk turanci Wanda ita bama irinsa malamansu keyiba dasu kansu Dan Wanda suka iya.

Tinda tafara kallansa tana Jin muryansa Yana magana Bata qara motsi ba har Saida ya gama ya juya yabar gurin Bata motsaba sai murmushi takeyi.

Hafiz Daya gama aka sallamesu sbd maigidan nasu Daya wuce kama hannunta yayi yaja suka bar gurin Saida sukai Nisa ta kwace hannunta tana matsowa kusa dashi sosai tace

"Yaya Hafiz Yaya sunansa?
Bature ne ko balarabe?

Suna Isa gida ta bawa babba da dadah labarin Taga irin Wanda zasu Nemo mata a matsayin miji idan zasu mata aure.

Tin daga wannan ranar Ameenatou Babu ranar da Bata maganar baturen ogansu Yaya Hafiz,
Kaf gidan saida suka gaji da Jin kalan kyansa datake fadan kaman Rana zata konasa yanata kyalli.

Haka zalika tin daga lokacin Yaya Abdul ko Babbah suna daukota daga makaranta gurin Hafiz suke ajiyeta shikuma daga Nan yaje da ita gida duk Dan sbd tagansa Amma kuma abin mamaki tin daga ranar Bai sake zuwa ba bare ma ta gansa daga qarshema sai gashi anrufe site din gaba Daya tareda aikin dole suka koma Neman wasu ayyukan kafin idan Allah yasa zaa dawo da aikin sai gashi kuwa kwatsam ance su shirya su koma bakin aikinsu Kuma me gidanma yananan tafe da kansa.
#MAMUH#
#AMEENATOU
#THE SEELAHS

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
30
Washe gari Tin 7 na safe Yaya Abdul ya shirya fita aiki ya tsaya jiran Budurwar babban Amma dai lokacin ma dadah ke tadata bacci cikin lallabawa da tausayinta akan tashin safen Wanda yake kular da Hafiz Dake tsakar gidan Yana wankin kayansa Dana Ameenatou din.

Brush tafara kafin Tayo wanka ta fito ta nufi daki Dadah haryanxu data girma tayata shiri takeyi.

Sai kusan takwas saura ta gama shiryawa ta fito tsakar gidan ta zauna gefen Babbah dake zaune kan tabarma.

Farin Koko me kyau da aka zuba mata zuma aciki ta dauka a cup da fanke manya manya da zafinsu sun soyu tafara Sha tana fadawa Babbah gobe bazata je makaranta ba duk idanuwanta rage girma sukeyi Bata samun bacci

gashi da Rana ma Bata samu.

Cikin kulawa da yadda da abinda ta fada din Babbah ya gyada Kai Yana cewa

"Na lura da Hakan sarai 'yar budurwata magana ce kawai banba sbd Yan Saka idon gidan Nan Amma gobe Babu inda Zaki ai ana son Rai da hutawa"

Juyowa Hafiz yayi sbd ya Dena mamakin lamarin babbah da budurwan tasa Amma takaici Baya barinsa yin shiru Dan haka Baki sake yace

"Wlh duk ranar da kika sake tsallaken zuwa makaranta bazaki sake zuwa site ba ko oga yafara zuwa aiki kuwa,
Sai naga karshen rashin bacci."

Kallan babbah ta dago tayi da idanuwanta da suka narke tana masa alaman yayi magana.

Inda yake babbah ya juya ya kalla Yana jifansa da wani mugun kallo yace

"Nine nace bazata goben ba sai naga abinda zakayi"

Yaya Abdul da hakurinsa ya fara karewa sbd yayi masifan lattin Danma Babu ranar da Baya latti sbd ita cikin kulewa yace

"Zan tafiyata idan Baki nutsu kin gama abinda yake gabanki ba Kokuma ki tashi mu tafi hakanan Baki gama cin abincin ba."

Dadah Daketa Kaida kawon hada mata jakarta da ruwanta a sabuwar roban ruwa me tsafta sosai da Yaya Abdul ya sake siyo mata miqawa Abdul din dayake tsaye Yana harare harare tayi tana cewa

"Dan taimaka riqe mata kafin ku Isa"

Baida lokacin batawa na musu Dan haka ya karba kawai zai sake magana Dadah ta rigasa da cewa

"Yi hkr saura kadan fa ta gama karta qware duk Kuna Neman rikitata"

Hafiz ajiye wankinsa yayi Yana nufota Babbah ya jefesa da wani kallan daya sakashi tsayawa Yana cewa

"Babbah wai meyasa kakemun hakane duk lokacinda naso gyarawa wannan yarinyar zama duk ta renani ko abokaina fa sunsan ta renani a gabansu Babu

kalan sakarcin da batamin gudun nakeyi wataran na harzika na babbalata jinin mutane yayita Hawa"

"Karka wani Sakaya fito fili kace jinina Dana uwarku ya hau,
Zaka koma aikin gabanka kokuwa saina ce Abdul din ya tafiyarsa ka aje wankin ka Kaita"

Ball yayi da takarmanta Dake gabansa Yana juyawa ya koma aikinsa Dan ba qaramin aikinsu Babbah dinne ba ace ya aje wankinsa ko wanka beyiba ya Rakata makarantar.

Miqewa tsaye tayi bayan ta gama tana goge bakinta da tsaftacciyar kyallen sabuwar atampa da Dadah ta miqo mata ta Saka takarmanta masu kyau Wanda suka Hafiz dinne ya siyo mata Dan komai nata Hafiz da Yaya Abdul ne ke Siya
Babba kuwa a siya mata kayan ciye ciye da kwalama Yan canjinsa suke karewa sai fura da asalin Madaran fulani me kyau dayake siyo mata duk dare Wanda yawanci ita take Sha Bata cika cin abinci ba sai idan Yaya Abdul ya siyo mata kwai zuwa makaranta take ci da dare.

Suna fita tana gefensa tana masa surutu suka kama hanyar makarantar Yana amsata sama sama sbd hankalinsa na kan gurin aikinsa dayayi latti gashi Basu yadda da kowaba akanta da tini mashin zai ringa Bata kudi tana Hawa Amma kwata kwata Basu yadda da kowaba akanta shiyasa duk tsananin latti da rashin jinta basa iya barinta taje ita kadai makaranta kuma itama kanta sbd sabo da Hakan Bata iya tafiya koina batareda dayansu ya Kaita ba tsoro ma takeji na bin hanya ita kadai.

Suna Isa gate din makarantar ya miqa mata kayan ciye ciyen Daya Siya mata na break Dan basa Bata kudi kwata kwata.

Karba tayi tana masa Godia da fuska a cakude sbd lattin datai tasan Kuma Yaya Abdul din Babu rokon dazaije yayi mata Dan haka ta juya ta shige tana ciko idanuwa da hawaye Dan a tausaya mata.

Cikin babbar sa'arta malamin data tarar Yana Taron lattin Baya ko kallan inda take kwata kwata sbd tashin hankalin Daya taba Sha shida Babbah da Hafiz akan dukanta Daya taba yi
Babbah yazo makarantar ya rufe ido ya zuba musu tsiya rigima har gaban shugaban makarantar kawu yayi mirsisi ya nuna Yar budewarsa Bata da laifi shine Babu lafiya shiyasa batazo da wuri ba.

Dayake sunsan ba yadda zeyiba daga Nan har hukuma Dan haka suka basa hakuri aka rufe maganar,

Tin daga lokacin da yawa malamai basa taba Ameenatoun sbd Babu me buqatan rigima kowa na fama da kansa.

Simi Simi kaman munafuka ta wuce ciki tana Jin dadi a zuciyarta Dan idan akwai abinda ta tsana a duniya shine a taba lafiyar jikinta,
Bata kaunar abinda ya taba jikinta shiyasa Sam batason duka ko faduwa bare Jin ciwo.

Idan kuwa taji ciwo a gidan jinya zata kwanta a ringa fama,kafin ta warke zuciyar Hafiz saita kumbura ta huce yafi so a kirga sbd yanafin kowa Shan wuya da takaici Dan a kansa sakarcin yake karewa.

Farin jini datake dashine ya Saka yakeda kawaye masu tsananin son binta koina Amma da Aminiyarta Daya Khadija.

Karfe biyu saura Yaya Abdul yazo ya dauketa Kai tsaye gida suka nufa ko shiga beyiba ya juya ya koma gurin aikinsa ita Kuma ta shige a gajiye duk da Yaya Abdul din ya Siya mata yoghurt me sanyi sosai yazo mata dashi Amma dai batasha ba tana shigowa ta miqawa Dadah hadda Jakarta da komai ta tube a tsakar gidan ta daura zani ta nufi bandaki Tayo wanka tana fitowa abinci kawai taci Tayi sallah ta share dakinta dana Dadah duk da fes suke Dan Dadah akwai tsafta.

Tana gamawa bacci kawai ta kwanta abinta.
Sai kusan hudu ta tashi tayi Shirin makaranta dayake Hafiz yasan lokacin gama shirinta tana gamawa Yana dawowa yace ta fito su tafi yakaita sauri yakeyi akwai inda zashi.

Tin a cikin gidan suka fara rigima har suka Isa ta shige ya juya ya wuce inda zashi.

Da yamma kuwa babbah ne ya biya mata suka dawo gida tare Yana Bata labarin inda yaje da abinda ya Gani tanata Jin dadi.

Da daddare yau kusan kowa Yana gida lokaci Daya sukaci abinci su a tsakar gidan tanata zuba shagwabarta yanda takeso a cikin iyayenta da yannanta.

*****
Zaune yake a gaban Dad dinsa jikinsa gabaki Daya a mace,
Daga shi har Dad da Dad Lameenu dasuke palon su a zaune Babu me walwala ko farin ciki ko kadan a zuciya da fuskokinsu,

Tarin bacin Rai da baqin ciki ne yake sake tirnike zuciyar kowannensu Yana Kona jininsu.

Dad Lameenu dayake Jin kwata kwata baiga amfanin Haroon a rayuwarsu ba sbd Babu inda suka Kara gaba kullum sai Baya sukeyi suna Neman durkushewa ba shiri,

Rashin JAMAAL a rayuwarsu wani babbar balai da masifa ne Dan kuwa sun sheda Hakan Kuma suna kan shedawa tin daga ranar Daya barsu komai sai rushe musu yakeyi,

Shi baimaga dalilin wani Yanke yanken alaqa ba da Mam yayi da Jamaal din dan kuwa da Haroon din ya miqawa Dr Aleena can taje dashi tayita kayan rashin amfanin dashi.

Mam kasa cewa komai yayi sbd yanason ya kasawa ransa iya danne tsananin rashin 'dansa JAMAAL a taredashi,
Yanason ya Hana abinda yake cin zuciyarsa gameda rashin Dansa,

A tsawon shekarun Nan da suka diba basa tare Babu ranar da Baya kwana ya tashi da tsananin son kasancewa da JAMAAL,
Babu ranar da Baya kewansa,
Babu ranar da Baya baqin cikin faduwa da rushewan da sukeyi sbd rashinsa.

Kallan Haroon ya sake yi Yana ajiye takardun hannunsa Daya gama karantawa y
Zuciyarsa na quna yace

"Se yaushe ne zaka zama me amfanin dazanyi alfahari dakai amatsayin Dana?
Kasan irin millions din da muke rasawa akowace safiya tindaga ranar da Jamaal ya tafi kuwa??

Zaka iya lissafa asara da faduwan da muketa yi kullum?

Menene yake faruwa acikin kanka ne da kwata kwata Babu Abu Daya a cikin lamuranmu dayake tafiya daidai?

Aikin site dincan a yanzu shi kadai ne abinda ya rage a tayar shine abinda zai hanamu karasa rugujewa sbd ka lalata komai,
Ka rusa abinda mukai aiki tukuru da jini da majina muka hada,
Ka rusa abinda Dan uwanka yayi aiki dare da Rana ya hada duk kana Neman lalata komai a cikin shekaru kalilan."

Dad Lameenu kuwa kasa magana yayi sbd Jan da idanuwansa sukai zuciyarsa na quna cikin baqin ciki da tashin hankali.

Har abada bazasu hada Haroon da Jamaal ba sbd Jamaal zakin namiji ne da kosu suke shakkarsa,

Ga Haroon yau ya Sakasu a tsaka me wuya sbd Bai iya komaiba sai rusasu yakeyi da rashin amfaninsa.

Cikin zafin zuciyar Dad yace

"Ka tafi ka fara Shirin tafiya wancan babban project din,
Abu Daya nakeso ka sani,
Wannan aikin shine aikin dana Saka dukkanin burina akansa yanzu
Samun matsala akan wannan aikin shine rugujewanmu gaba Daya Dan haka ko rayuwa nawa zaa ci a aikin Nan banason ka tinkaroni da matsala duk tsanani duk rintsi,

Ka nutsu dakyau ka fahimci mahimmanci wannan aikin a gurinmu,
Ka tafi kasan abinda kakeyi idanma haryanxu rabuwarka da Dan uwankane ta kasa sakinka to ka sani wannan Karan a shirye nake da kawar da matsalata kowace iri ce."

Wani abu me dacin gaske Haroon ya hadiye kansa da kirjinsa na wani irin nauyi da radadin dayake cikinsa na tsawon shekarun Nan,

Tinda Jamaal ya rabu da Dad Bai sake sanin farin ciki ko samun kauna daga mahaifinsa ba Kona Rana Daya ne,

Shi kansa ya sani baida jarumta ko ilimin aiki irin wanna da Kuma izzar gudanar da manyan huldodin kasuwanciba irin Jamaal,

Baida sa'a kaman Jamaal,
Baida cika ido da kwarjinin kasuwanci acikin manyan mutane na gida Dana waje kamar Jamaal

Rayuwarsa gaba dayanta akan abinda ya karanta ya kwallafa ta sedai Kuma babbar jarabansa itace kauna da son kyautatawa mahaifinsa Daya rufe masa zuciya da ido Amma duk yanda yake kokari Dan zama hasken idaniyar Dad din Hakan Bai taba samuwa ba saima lalacewa da komai yakeyi.
Baya tareda mahaifiyarsa,Baya tareda Dan uwansa Baya da kowa sai mahaifinsa da sauran dangin seelahs da duk Babu Wanda yake appreciating nasa ta koina da komai sai Hakan yafara tabasa ahankali ahankali har

depression na shigarsa batareda kowa ya sani ba bare fahimta.

A yanzu da shine komai na Seelahs yadawo hannunsa shine yake juyata Babu abinda Bai saniba na sirrinsu Dad sedai bazai taba iya fadawa Dan uwansa Hakan ba,

Bai iya illegal huldodinsu ba,
Bai iya juya business na Seelahs ba na bayyane Dan haka gaba Daya rayuwarsa ta tashi daga Haroon seelahs Takoma wani mutumin daban dabai San kowanne farin ciki ba bare walwala sbd haryanxu Babu abinda yakeso kaman burge mahaifinsa ya samu yabo da alfahari daga garesa.

Wannan aikin na site a yanzu shine abinda zai basa Daman samun yabo da kauna daga Dad dinsa yanda yake buri Dan haka yayi alkawari tareda sakawa ransa zaiyi aiki tuquri akan wannan project din.
Shiri ya fara na tafiya Nasarawa tareda sakawa Akai masa booking na hotel da komai.
##MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
31
Bayan ficewan Haroon daga palon kallan Mam Dad Lameenu yayi cikin nauyin zuciya da rashin Jin dadin komai na duniya yace

"Dole muna buqatan tsananta binciken abinda àka haifawa Omar duk inda yake sbd sanin inda suke zai Saka Omar din dawowa daga inda yake ya dawo cikinmu sbd sanin munsan yanada 'da a duniya,

Idan ba Hakan mukaiba cikin gaggawa wlh muna gap da rasa komai munaji muna Gani Dan haka yanzu Kam dole mu tashi tsaye dakyau mu samo 'dan Omar"

Mam da zuciyarsa tafi ta lameenu tsananta a cikin baqin ciki da tafasa tareda bacin Rai baice komaiba sbd Daman ya hangowa kansu Hakan daga ranar da suka Dora Haroon akan komai nasu,
Sam baida jarumta ko amfanin da zai musu yanda ya kamata.

Ta bangare Daya yasan duk Wanda zasu Saka a magajin nasu me gudanar da komai bazasu taba samun Jamaal ba Dan kuwa shi din zakinsu ne.

Numfashi ya sauke ahankali Yana kallan takardun gabansa da idanuwansa da sukai jajir Yana kokarin daidaita tafasar da zuciyarsa keyi,
A yanzu shima Babu abinda ruhi da zuciyarsa suke tsananin buqata kaman dukiyar Omar Dan ita kadaice zasu mallaka suyi tsayuwarda Babu ranar rushewansu a kusa sbd koba komai a tsaftace take Babu jinin kowa aciki Dan haka zeyi wuya ta shiga hannunsu ta lalace kaman yanda tasu ta dauko hanyar lalacewa duk Dan sbd Allah ya basa sakaran 'da mara amfani sosai duk da Yana son dansa sosai Amma Sam Baya kaunar rashin amfaninsa har ransa yake Jin baqin ciki da tsanar Hakan.

Wayarsa ya miqa hannunsa Daya ya dauka cikin nutsuwa ya Nemo numbern BB ya Saka kira Yana dauka yace

"Ina buqatan ganinka yanzu"

"Yes Sir" ya fada Yana zare sigarin Dake bakinsa Yana zuqa cikin palon gidansa.

Cikin mintinan da Basu wuce hamsin da Yan Kai ba saigashi ya iso gidan Kai tsaye motarsa yayi parking ya nufi hanyar office dinsu Yana zare baqin glass dinsa Dake rufawa jajayen idanuwansa masu Bada tsoro asiri.

Yana shigowa ya rufe kofar tareda qarasawa ya tsaya gabansu cikin girmamawa da kulawa ya gaidasu Yana kallan fuskokinsu ya sheda akwai sabon bacin Rai da sabuwar matsala wadda kwanan wani zai qare Kila a kwanakin Dan kuwa Kai tsaye yake gane girman bacin ran uwayen gidan nasa.

Kallansa lameenu yayi cikin tashin hankali da son danne tafasar zuciyarsa yace

"Yaya ake ciki a bincikenmu??

Gyara tsayuwa yayi Yana dagowa yace

"Ranka ya Dade tsawon shekarun Nan wlh bamu taba dakatawa daga binciken inda suke ba,
Babu kalar yawon da bamuyiba state state da kauyuka gurin nemansu,
Acan Asalin kauyen na iyayen matar sir Omar din muntashi kauyen gaba Daya Dan kunasa mukayi da gidajen Dake cikinsa dayawansu ma Babu sun mutu,
Hakama itama me aikin munyi nasarar sanin inda aka daukota aiki daga Jos Amma bamu gama sanin a inane take a jos din.....

Cikin daga murya da bacin ran da suke jimawa Basu ganiba a gun Mam ya katsesa idanuwansa na qara yin jajir yace

"Ko nawa zaa kashe a kashe a Nemo mana matarnan Ina buqatan Jin komai daga bakinta zuwa kunnuwana,
A yanzu wannan aikin shine tabbatuwar arzikinmu da tsayuwarmu,
Samun wannan matar shine duk wani abu damuke buqata da ranmu da zuciyarmu,
Omar jeden Yana kallanmu daga nesa amatsayin matsiyata wainda ya take ya wuce nesa ba kusa Dan haka nakeson nuna masa Munfi karfinsa da gaske shi din a tafin hannunmu yake Dan kuwa idan ban zubar da jinin 'dansa ba bazan taba Ji ko samun nutsuwan zuciya ba.."

Lameenu dakejin zuciyarsa har wani rawa da tsallen tashin hankali takeyi sbd Jin inama zasu samu ganin matar da Gano komai a ranar da hannunsa zai cike aikinsa dabai qarasa ba Dan kuwa barin 'dan Omar a duniya kaman aikine da Basu samu cikawaba Wanda bazai taba samun nutsuwa ba idan ba

cike aikin yayi ba daidai.

Cikin sauti me tattareda radadi da son samun abinda zuciya keso Dad Lameenu yace

"Ko nawa zaa kashe a kashe acika wannan aikin Daya gagara cikuwa shekara da shekaru,
Duk Wanda yasan wani abu gameda me aikin gidan Omar a nemesa aji nasa bayanin a Kuma kawar dashi bayan karban bayanan Dan basason barin sheda ko Daya datasan meyake faruwa Da abinda ma zai farun.

BB da Shima daya kawar da rayuka sunkai nawa akan wannan binciken Jin yayi zuciyarsa ta sake daukan zafi Dan rashin sauki ko kadan Dan haka Koda zasu tada kauyuka da rayuka nawa wannan Karan Se sun Nemo inda matar Nan take sunji me aka haifawa Omar din da inda abinda aka haifa din yake.

Kudi masu yawan gaske Dad Lameenu ya kira Haroon ya bawa BB da yaransa akan aikin Nemo matar wadda Shima Haroon yake tsananin so da buqatan a Gani din duk da Yana Jin shakkar abinda zai iya biyowa bayan samun me aikin da Kuma samun Abinda Dad Omar ya Haifa, duk da haka Shima Yana Nan Yana bincikensa sosai a boye sbd zaiso yasamo information da zai taimaki Dad dinsa Dan ya yaba masa Koda so Daya ne Kuma yayi alkawarin Yana samun Information koman kankantarsa zai sanarwa Dad din.

Bayan bawa lameenu kudin sanar dashi yayi duk information da zaa samu Shima ya sanar dashi ko yayane.

"Angama Barrister" BB ya fada Yana ficewa daga palon Haroon din zuciyarsa cikeda rashin Imani da Jin ya dauki sabon caji Baji ba Gani yayiwa kansa alkawarin Nemo matar Nan duk inda take a cikin Jos da zagayenta.

*****Anyi Hakan da kwana biyu Haroon ya tattara ya tafi Nasarawa sbd gaba Daya Dad ko kallan daraja Baya masa sbd tsananin bacin Ran dasuke ciki akansa Dan haka ya sake shiga damuwa sosai da rashin walwala duk da Bai bari Mum dinsa da Dan uwansa dashi kadai suke communicating a Nigeria sai siddeeq da duk motsin Haroon Yana sane dashi Yana sanarwa Jamaal Dan kuwa kwata kwata Jamaal Bai yadda dasu Dad din akan Dan uwansa ba.

Duk tsananin damuwa da kadaici da rashin mutuntawa ko daraja da Haroon din yake cikinsu Jamaal Yana sane da komai sbd Yana sane ya saka Haroon daukan siddeeq Aiki ya zama Dan hannun damarsa batareda su Dad sunsan asalin waye Siddeeq dinba hakama Haroon kansa baisan ma siddeeq din yanada alaqa haryanxu da Jamaal ba sbd kwata kwata abinda ya sani dashi

kadai Jamaal ke magana a Nigeria Dan ko mum Atee duk nacinta ta gaji ta barsa Dan ko kwana zatayi tana kiransa Bata samunsa.

Koda ya karbi aikin project dinnan zuciyarsa cikin shakku da fargaba take sosai tareda tsananin tsoro Dan baisanma ta inda zai fara gudanar da wannan aikin da Dad ya basa damar karshe akansa ba,
Baisan Yaya zai fara ba gashi baisan ta Ina zai fara rokon taimakawan Jamaal ba Dan yasan Jamaal din bazai taba Saka hannu a aikinsu Dad ba Dan haka yake cikin damuwanda tini tafara taba ayyukansa da rayuwarsa Dan kuwa komaima kaman ya Dena ganewa daidai.

Tareda siddeeq suka sauka Nasarawa har babban hotel din da Aka kama masa motar data daukesa ta Kaisa.

Siddeeq ne yakai masa kayansa har dakinsa ya jere masa kafin ya fito ya nufi nasa dakin dayake kusa da nasa Shima ya jere kayansa ya fada toilet sbd zasuyi kwanakin da basusan yaushe ne ranar tafiyansu ba tukuna.

Shi kansa Haroon wankan yayi Yana fitowa ya shirya cikin kaya marasa nauyi yayi Sallah kafin ya kunna wayarsa sai alokacin ya kira Dad ya sanar masa sun iso.

Babu wani yabawa Dad din ya sake maimaita masa mahimmanci da tsananin buri dasuke dashi Akan aikin Nan tareda tabbatar masa da idan aka samu matsala to babusa Babu shi.

Wannan kalman itace kalma mafi Munin data girgiza zuciyarsa ta qarasa tarwatsa duk wani Dan sauran dubaru Dan kokarin Daya rage masa Dan haka ya sake shiga damuwa da tashin hankali me tsananin gaske gashi bayajin zai iya ajiye aikin Dan kaman nauyi ne Daya rataya akansa hakama bayajin Dad din ze barsa ya ajiye din Dan.

Jin yayi ciwonsa na tsananin ciwon Kai da depression na dawo masa sosai Dan kuwa take yafara Jin kaman kansa ze juye Baya gane komai,

Wayarsa ya kashe tareda wurgi da ita Yana silalewa qasa hannuwansa riqe da kansa Dake Neman bugawa tareda bugun zuciyarsa.

Maganinsa yafara rarrafawa Dan nemowa yasha amma kwata kwata Baya Gani daidai saima juyawa dayaji kaman anayi dashi,
Hannuwansa Dake wani Irin rawa sosai suna kakkarwa ya dago Yana kalla sunai masa bibbiyu.

Sake rarrafawa yakeyi Yana faduwa Yana tashi harya Isa gaban mirror inda

siddeeq ya ajiye masa maganinsa kafin yakai hannunsa ya dauka ya Fadi akan mirror din kayan Dake Kai suka zube qasa Wanda sautin ya Isa har dakin siddeeq Dake maqale da nasa da sauri ya fito ya shigo dakin Yana ganin Halinda yake ciki da sauri ya qaraso Yana daukan maganin ya Bude roban ya Ciro Daya ya Saka masa a Baki tareda dauko ruwan Roba a fridge ya basa.

Yana shanye magana ko mintina uku beyiba sai gashi ya fara dawowa daidai Yana hada zufa idanuwansa nayin jajir.

Boyayyar ajiyan zuciya me zafi siddeeq ya sauke Yana kallan Haroon dan kuwa da Baya kusa wani abin ya samesa baisan me zaicewa JEEY ba.

Miqewa Haroon din yayi da kansa Yana kasa kallan siddeeq ya Bude Baki ahankali ya furta

"Thank you"

Kujera ya nufa ya zauna ahankali har lokacin zufa yake tsiyayowa ya dauki tissue Dake gabansa aje Yana Dan gogewa kadan.
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
32
Abinci siddeeq yayi order tareda abubuwan dayasan Haroon zai buqata kafin ya fice ya koma dakinsa Dan sanarda JEEY ciwon Haroon gaba yakeyi sosai.

Bai samu wayar JEEY a lokacin ba Dan haka Shima abincin yaci kafin ya kira manyan ma'aikatansu da zasuyi Aiki dasu Dan Yana buqatan fara zuwa site din yaga komai ya gana da tarin ma'aikatansu masu yawan gaske kusan shine zai karbi Ragamar Aikin sbd Haroon Babu abinda zai iya.

Su Hafiz da suka shirya tsaf washe gari tinda safe suka halarci site cikin farin cikin dawowansu bakin aikinsu Dan suna samu sosai a aikin.

Kusan ma'aikata sama da hamsin Dana garin da wainda da yawansu daga wasu garin suke zuwa, manyan kuwa daga Lagos wasu suka taho wasu Kuma daga Abuja Dan haka tini site ya rayu ya cika da leburorinsu da masu kulawa dasu da masu tsari da Zanen.

Lafiyayyar tanti aka kafawa oga kwata kwata Haroon seelah da kujeran zamansa da table da duk abubuwan da zai Dan buqata a zaman da zai ringa yi idan yazo site din.

Siddeeq dayake sosai yakeda nasa ilimin da qwazon aiki tareda dubaru irin wainda duk ya koya a karkashin maigidansa na Amana JEEY Dan haka tinda suka taho shine yake fitowa site din ya gana da ma'aikata da abokan aikinsu na project din suka sake Bude sabon bayani tareda gabatar da kansu da ayyukansu tini aka fara aiki Babu wasa sbd kowa da gaskensa yake.

Saida aka kwana biyu Haroon ya koma daidai kafin ya fara fitowa site aiki zuciyarsa cikeda fatan samun nasarar abinda sukeso
Ta bangare Daya Kuma ya tsananta bincikensa akan Abinda su Dad suka Hana kansu zama da tsayi gurin nema sbd ya samo information me amfani dazai Hana Dad yafesa idan aka samu matsala a wannan aikin.

***Yar Budurwan Babbah kuwa kusan tafi su Hafiz shiga farin cikin komawansu aiki Dan kuwa tasan baturenta zata sake Gani Wanda kamanninsa suke Zane daram a idanuwa da zuciyarta Dan haka ta daga hankalin babbah da Dadah Saida suka Saka Abdul ya Dinka mata sabon uniform duk da a shekarar zata kammala Amma sbd rigima Saida aka Dinka mata sabbin uniform din.

Shi kansa Babbah da Dadah akan dole suka ringa farin cikin komawansu Hafiz aikin site sbd Ameenatoun data sakasu nuna murnan dolen.

Da daddare bayan Yaya Abdul ya shigo mata da sabbin uniform din a leda me kyau ya miqa mata Yana cewa

"Wlh safar banza ma bazan Kara Siya Miki ba sbd bansan uban me zakiyi dasu ba keda duka duka baifi wata uku ba zuwa hudu ki kammala karatun Amma shine tsaban an renamun da wayo zaa sakani dinko sabon uniform."

Hafiz Daya fito wanka Ya gama shafa Mai Yana gyara kansa da brush na brushing Kai yace

"Kafin ma aje can ka fada mata yanda ka dinko sabon uniform dinnan tana faduwa jarabawa da su zataci bikin sallah Dan Babu uban dazai mata Dinkin sallah da f9 duk cikeda takarda...."

Babbah Dake shigowa ne ya katsesa da cewa

"Ubanta ne zai Dinka mata basai kaja da Nisa ba,
Kuma faduwa jarabawan ma ai rabo ne tinda yafi Babu...

Cikin narke fuska tana kokarin ciko idanuwanta da Hawaye tace

"Babbah to ai na Maka alkawarin bazan Fadi bafa ka gaya masa,
Kuma ni Allah wanna sallan shi kadai ma nakeso yamun komai tinda ya koma aikin site...

Wurgi yayi da Brush din hannunsa Yana yowa kanta yace

"Bazaki Dena renani ba ko?
Na rantse a gidan Nan kika kawo faduwan jarabawa silipas bazan Siyaba na sallanki sedai duk me Shure.....

Katsesa dadah tayi da cewa

"Babu me shurewa Dan bakayiba."

"Ai da kin bari ya qarasa da bakinsa Muji waye ze Shure din" inji Babbah Yana karban ledan hannun Ameenatou datake nuna masa kayan babu guga.

Miqawa Hafiz kayan yayi Yana cewa Maza gama shiryawa ka goge mata ko a shagon abokincan naka me dinki ne.

Kallan ledan kayan yayi Yana sake Jin takaici na siqesa ya juya ya kalli inda Yaya Abdul yake zaune Yafara cin abincinsa hankali kwance yace

"Dena kallona Dan kasan Babu inda zani guga yanzu Kaine me abokai masu shagunan dinki"

Kanta ya dawo da kallansa zeyi magana Dadah ta bisa da rarrashinda yasan anriga an cucesa ne ake toshe masa Baki.

Jinjina Kai yayi Dan zata shiga hannunsa ne gobe tinda shine zai daukota makaranta.

Wucewa yayi daki ya qarasa shiryawa ya fito baicewa kowa komaiba ya fice Yana jinta tana masa a dawo lafiya itada Dadah yayi musu shiru ya fice Dan wankan dayayi fita zashi aka sakashi zuwa guga duk yaje ya sake hado gumi duk da Daman shine mai yi mata guga Amma dai yau din ba lokacin yinsa bane.

Bayan fitarsa Abdul ne ya fara yiwa Ameenatou din fada Babbah ya dakatar dashi da cewa yabar zancen Nan tinda dai ba fandarewa yarinyar Nan tayi na.

Da daddaren kafin ta kwanta Saida ta Jira Hafiz din ya dawo sukai karatu dayake sake nuna mata abubuwan da Bata ganeba
Anan dai ya shiririce firar da Bai tafi ba kenan.

Washe gari Abdul ne yakaita makaranta ya wuce aikinsa daga can.

Karfe biyu saura Hafiz ya iso makarantar cikin sauri sbd aikinsa Daya baro ya taho yakaita gida ya koma.

Tana ganin sun kama hanyar gida ta riqe hannunsa tana narkewa tana rokonsa suje site tinda zeyi latti kafin ya dawo kuma ai uku suke tashi Dan haka bama wani Jira zataiba zai gama su wuce gida.

Yana Jin Hakan yasan wa takeson Gani Kuma cikin sa'arta maigidan nasu

Yana Nan kaman yanda ta Saka masa suna bature Suma gurin tinda dadewa suka Saka masa suna baturen.

Kaman bazaije da itaba sbd ba gurin zuwan mata bane idan ba irin masu tallan nan ba duk da an dauki nauyin abincinsu acan ake basu abinci tin farkon aikinsu Amma dai yanzu tinda aka dawo dinnan baa fara Basu ba hakanan suke siyan na masu Siya shi Kam dai iyakacinsa ruwa Basa cin abincin siyarwa waje.

Kallanta Yayi Yanajin kaman bazai tafi da ita ba Amma mum matsalarsu shine Bata iya rokon Abu su kasa Bata shi Dan haka yace

"Muje Amma tattara aikina zanyi na ajiye mu dawo gida sai gobe na Dora."

Wani kyakkyawar murmushin daya lotsa simple dinta sosai ta sake tana Jin dadi tace "Eh na yadda Yaya Hafiz dina Rabin Raina"

Harararta yayi Yana yin gaba tana biyosa tareda miqa masa Jakarta ya karba Yana kallan fuskanta kafin ya kalli ranar da ake qwalawa yasan zeyi wuya batai zazzabi ba idan ta Dade a cikin Rana Dan haka kudin aljihunsa ya taba ya ciro yaga nawa ne.
Wani shago ya tsaya ya shirya umbrella ya Bude mata yana miqa mata.

Karba tayi murmushin tsananin kaunar yayan nata datakejin sonsu fiyeda yanda suke jinta kawai dai Bata iya zama basuyi rigima ne ba Amma tasan kaunarta a zuciyoyin iyayenta da yannanta bame misaltuwa bace.

Bata tafiyan sauri Dan haka a natse suka iso site din ya Kaita inda ya Saba cewa ta zauna ta jirasa yace ta zauna ta jirasa din.

Tinda suka iso gurin taji zuciyarta tayi wani irin sanyi da farin ciki Mai nutsuwa lokaci Daya ta rasa wane irin yanayi ne ma takeji akan wannan kyakkyawan baturen Daya fita idanuwa da zuciyarta.

Zaunawa take kokarin yi a inda Hafiz ya goge mata ya wuce idanuwanta sukai kyakkyawar sauka akan Haroon Daya tinkaro inda take Kai tsaye siddeeq na gefensa Yana duba wasu takardu hakama wasu ma'aikatan na biye dashi.

Sanye yake Dan kananun kaya Ash Shima da fcap a kansa sedai Babu sunglasses a fuskansa.

Kasa zama tayi ta tsaya cak tareda zuba masa fararen idanuwansa tana Jin

farin ciki na dabaibaiyeta sedai Kuma idanuwanta sai suke ganin sauye sauye a tattareda shi duk da ta Dade sosai Bata gansaba.

Kyakkyawar fuskarsa da batai hasken ta Jamaal ba ta zubawa dukkanin fararen idanuwanta tana kallan mamakinta na qaruwa zuciyarta na sake hasko kamanninsa na Baya da suka tsaya tsaf a cikin idanuwanta.

Wayar dake hannunsa ce tayi ringing Yana gap da isowa inda take ya dakata tareda dago wayar Yana ganin sunan Wanda yake Kai ya daga Kai tsaye Yana ambatar sunansa cikin sautin nutsuwa da turancinsa me dadi Shima.

Lumshe fararen idanuwanta tayi ahankali lokacinda take Jin sauyin a sautin muryansa ma,

Bude idanuwanta tayi tana sake Dorasu akansa muryansa na sake ratsa jinta,

Idanuwanta da kunnuwanta sun tabbatar mata da sauyin abubuwa akansa sedai a zuciyarta shi din daine takeson Gani da Kuma ji Dan haka sai alokacin ta saki wani kyakkyawar murmushin daya sakata Jin kunyar kanta tana rufe fuskanta da tafukan hannuwanta tana Jin tin ganin datai masa farko shine Gani mafi farin ciki dataiwa Abu.

Haroon Daya gama wayarsa ya qaraso Yana kallan abinda sukazo dubawa gurin baima lura da mutum ba saida ya qaraso daf da ita yaganta ciki mamaki ya tsaya zai kalleta daidai Nan ta janye hannuwanta daga fuskanta kyakkyawar fuskanta daukeda murmushi sedai batasan da isowansa a gurin ba Dan haka ganinsa ya Sakata yin Baya da sauri sbd firgita da mamakin data shiga me qarfin gaske.

Shi kansa bayan yayi ahankali sbd kusancin da suka samu gashi murmushin dayake fuskanta wani faduwan gaba ya sakar masa Dan baitaba samun kusanci da mace ba haka a rayuwarsaba bayan Ayesha da yayan Dad Lameenu wainda su kannensa ne ba maganar Jin komai akansu.
##MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
33
Hafiz dayake nesa dasu da sauri ya qaraso gurin Yana bawa Sir Haroon din hakuri tareda sanar dashi Kanwarsace ya dauko makaranta yanzu wucewa zasuyi gida tabar gurin.

Ahankali Haroon ya mayar da Idanuwansa akan Ameenatou din ya kalleta Yana mamakin kalman daukota makarantar da Hafiz din ya ambata.

Ita kuwa bayan Hafiz din ya matsa ta batareda ta iya furta kalma ko Daya ba Dan samun bakinta datai da mutuwa 'dokin zuciyarta na ragewa batareda tasan dalili ba Kila Kuma zuciyarta tafi sonsa idan Yana daga nesa da ita ne.

Magana Jafar yayi mata a hankali wadda ta Sakata Dan fitowa kadan batareda ta kallesaba ta gaidasa cikin nutsuwa batareda tayi tinanin Yana Jin hausar ba.

Shi dariya ma ta basa Dan haka Saida ya saki Dan murmushi kadan kafin ya amsa Yana kallan Hafiz yace ya tafi da ita gida kawai yabar aikinsa zuwa gobe.

Ita kanta kaman tana jiran ya fada Hakan Dan haka ta wuce gaba batareda ta

waiwayoba Hafiz kuwa wanke hannuwansa yayi tareda daukan Jakarta data barmasa yayiwa Haroon din godiya yabi bayanta Yana Bude mata umbrella data manta Yana cewa

"Salon ta ishesu da kukan zazzabi zai kashewa Babbah yar budewa ne yasakata biyosa cikin wanna uwar ranar gashi duk ta ruda masa aiki"

Shiru tayi masa Saida sukai Nisa ta waiwayo tana sake kallan Haroon Dake tsaye har lokacin Yana magana akan abinda sukazo dubawa.

Tin a hanya bakinta ya mutu har suka Isa gida Bata wani ishesa da magana ba Dan haka suna shiga gidan wanka kawai tayi taci abinci tafara kokarin kwantawa yasata gaba suka wuce islamiya Badan tayi niyar zuwa lolacinba Amma sbd tanason ringa biyawa ta gurinsa site hakanan ta shirya suke tafi.
Su kansu malaman sunyi mamakin zuwanta batareda latti ba yau din Amma dai dayake batajin hayaniyar Babu Wanda ya takurata da tambaya haka ta wuni makarantar ba hayaniya har suka tashi ta dawo gida tareda Yaya Abdul.

Washe gari ma haka suka biya site ya qarasa aikinsa ta zauna tana bin duk inda Haroon yayi da idanuwanta masu haske da kyau tana Jin kaman tace ya zauna ya Dena shiga rana duk da duk motsinsa biye ake dashi da umbrella sbd Rana karta tabasa.

Tinda take zuwa Bata sake bari ya ganta ba harta gama binsa da kallo tana murmushin su koma gida.

Abinda Bata saniba tinda kwanakin suka fara ja Yana sane da duk zuwanta da tafiyarta kuma ahankali ahankali ya fahimci sbd shine yake zuwan ta dauka bature ne shi da gasken.

Da farko lamarin mamaki da dariya yake basa sbd Bai taba Ganin inda asalin gata da tattalin 'yaya yake ba sai akanta hakama baitaba ganin kauna da kulawa me tsananin gaske ba da yanne kewa kanwa irin Wanda ahankali yaga anaiwa yarinyar.

Tinda tafara zuwa Bata taba tsallaken zuwa ba Saida exams dinsu ta karato sosai suna farawa shikenan ta Dena zuwa kwata kwata sbd karatu sosai da Yaya Abdul ya sakota gaba dashi
Shi kansa Hafiz sosai yake Bata lokacinsa suyi karatun exams din tare.

Barin zuwanta ya Saka Haroon tambayar Hafiz ko lafiyanta kalau ya sanar masa axams takeyi Kuma dai Bata jin dadi sosai sbd wahalan karatun.

A nata bangaren ahankali ta dawo hayyacinta akan zuwa ganinsa Dan haka

Koda suka gama exam kwata kwata Dena zuwa tayi ga rashin lafiya sosai Daya kwantar da ita na kusan kwanaki Dan haka suketa fama da ita anata lallabawa da ita kaman kwai.

Shi kansa Haroon duk tsananin damuwa da quncin zuciyar dayake ciki Saida yazo har gida ya dubata Wanda Hakan ya Sakata Jin dadi sosai Suma su Babbah haka suka nuna masa Jin dadinsa sosai sbd Ameenatoun.

A nasa bangaren yanda ya samu iyayenta da karamci dakuma sake ganin irin so da tsananin gatan da ake nuna mata ya sakashi fara jinta a zuciyarsa sbd kallan datake masa lokuta da dama idan ta zuba masa kyawawan idanuwanta sai yakejin damuwar datake lullube da rayuwarsa kaman tana ragewa Dan haka ya Dan saki jiki da gidansu Ameenatou din musamman Hafiz dayake qarqashinsa.

A bangaren siddeeq kuwa komai na Haroon shine yake basa kulawa da tsaro yanda ya kamata Dan haka Koda yaga Haroon din yafara samun walwala da yar sakewa a cikin Iyalin Babbah sai Shima yaji ya samu nutsuwa da Hakan take Shima ya sake suka fara samun sabo da mutunci dasu din.

A bangare Daya rayuwar Haroon din na cikin matsanancin daci da damuwa tareda rashin farin ciki ko Daya sbd Dad dinsa da suka Saka ido sosai a lamarinsa hakama Babu alaman aikin Nan nasu zai samu karbuwa a inda zasu gabatar dashi Dan haka kowace dakika ta rayuwarsa cikin damuwa da 'daci me tsanani take Dan haka ciwonsa ma keyin gaba gaba koyaushe batareda sanin kowaba sai siddeeq Wanda ko numfashinsa Baya boyewa JEEY.

Shigarsa cikin Iyalin Babbah ya Saka Dan haske da farin ciki shigowa rayuwarsa a duk lokacinda yake cikinsu Dan takai kusan abinci ma wasu lokutan a gidan yake ci na dadah.

Ameenatou Kam zuwa yanzu tagama shiga zuciyarsa fiyeda yanda yake tinani duk da shagwabarta yayi yawa Amma shi Hakan ne ya kashe zuciyarsa ta mutu gabaki Daya akanta ita Kuma a nata bangaren a yanzu dayake tareda su sai ta aje maganan son datake masa ta jefasu a layinsu Hafiz duk da haryanxu kallansa takeyi a Wanda yafi kowa kyau da tsari Bata taba Ganin kamansa ba.

******Su Dad sun dukafa ba ji ba Gani sai barin kudi sukeyi hankali tashe gurin Neman Maryama Dan kuwa suna gap da zubewa gaba Daya Dan haka suka fice hayyacinsu.

BB ma sun haukace Baki ba ganin sunata tsananta bincike da zufafasa akan Maryama wadda daga karshe suka gano kauyensu.

Bayan barin dukiya me yawan gaske su BB Saida suka gano Maryama saigasu da ita har cikin Lagos sedai ko kwana batai a lagos ba Su Mam suka taho har inda su BB suka boyeta da daddare.

Mam ne ya fara tsayuwa akanta kafin Lameenu ya shigo bayan ya kashe wayarsa gabaki Daya daga wayar dayayi ya tsaya Shima yayi mata kallo Daya Yana komawa ya zauna kujeran alfarma dasu BB suka kawo musu na zama.

Shima Mam zama yayi Yana kallan BB batareda Bata lokaci ba Dan baida time na batawan yace

"Tatso mana bayanin komai daga bakinta banason rasa kalma ko Daya komai nakeson Jin a yanda yake dinsa."

Qwayar datake bakin BB ya qarasa hadiyewa idanuwansa na sake rinewa jajir ya miqawa yaronsa Daya hannu ya Saka masa wata mahaukaciyar wuqa da shape dinta kadai abin tsoro ne.
Nufar Maryama din da idanuwanta suke a daure yayi tareda tsayuwa a kanta ya kamo kanta ya Bude idanuwanta ya Saka mata wuqar gaban idanuwanta da sukasha mugun dauri cikin muryansa me kauri da karajin rashin Imani yace

"Ki kalla Menene a gaban idanunki"

Kafin ma taja numfashin tsoro da tashin hankali bare taga wainda ke zaune a gurin ya mayar mata da daurin idanuwan ya rufe.

Mayar da kaifin wuqar yayi akan jijiyan maqoshin wuyanya Kai tsaye yace

"Meya faru a Daren ranar da matar sir Omar ya ta rasu?
Akwai ciki a jikinta koda ranar tazo?
Wata nawa?
Ta haihu?
Me ya Haifa?
Ina abinda ta Haifa yake?
Waye taredaku a Daren ranar?
Ya Akai kika tsira a Daren????

Cikakken bayani zakiyi sbd rashin kalma Daya daidai take da ficewan ruhinki daga gangar jikinki."

Wasu Hawaye masu tsananin zafi ne suka gangaro daga idanuwanta dasuke a rufe zuciyarta na wani irin rawar tashin hankali da tsoro Dan kuwa tasan shikenan nata karshen yazo abinda taketa yiwa gudu sbd tasan Hakan zai iya faruwa wata ran sbd akwai tabbacin asan data tsira.

Sake daga wuyanta BB yayi Yana qarawa wuqar seti har seda ta Dan fasa wuyan jini ya Dan fito.

Zufa take fitarwa sosai kirjinta na wani irin mugun bugawar da kusan Suma su mam din kirjin nasu harbawa yakeyi sosai Dan kuwa a Baya duk zance ne sukeyi Basu tabbatarba sai yau din zasu tabbatarda masifar Dake gabansu tana can tana yawo a duniya batareda sunsan a Ina ba.

Lameenu kuwa har wani zufa yake tsiyayowa hannuwansa na rawa Da matsuwan Jin Abinda zata fadan,

Allah yasa Omar din Bai haihuba zance ne kawai,
Allah yasa suji abinda zai kawo karshen matsalar tasu idan ba Hakan ba akwai babbar matsala da kura a gaba.
##MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
34
Maryama gaba Daya ta cire tsammani daga rayuwa Dan haka cikin rawar murya da tashin hankalin da Bata taba Shiga ba ta fashe Da kuka zata fara rokonsu karsu kasheta BB ya sakar mata wani mugun marin bayan hannu Saida bakinta ya fashe Da jini sosai ya sake cakumo wuyanta Yana Dora wuqar kafin yace komai Baki na jini tace

"Koda ranar tazo tana daukeda tsohon ciki wata Tara.....

Wani mummunan zufa da sarawan Kai tareda bugawan zuciya ne ya saukarwa Lameenu da Mam lokaci Daya,
Lameenu yayi saurin kallan Mam zuciyarsa na wani irin bugawa da karfi da tsalle sbd baitaba tinanin Jin Hakan ba,
Da gasken kenan dai Omar nada magajinsa,
Magajin dukiyar da baimasan Yaya zeyi da ita ba,
Gadon dukiyar tin suna samari suke dakonta cikin ransu,
Dukiyar da suka zama abinda su kansu basuyi tinanin zama ba ko a mafarki Amma daga karshe ace share fage ne kawai sukaiwa abinda Omar ze Haifa.

Mam kasa motsawa yayi bare juyawa ya kalla Lameenu sedai zuciyarsa kusan tafi ta Lameenun shiga mafi girman tashin hankali da firgici.

Shi kansa BB wani irin zufan tashin hankalin ne ya jiqasa Dan haka ya sake danna wuyanta Yana jiran sauran bayanan
Cikin rawar murya da ficewa hayyaci taci gaba da cewa

"Bata rasu ba a Daren sai bayan data haife cikin dayake jikinta,
Sir Omar yasan ta haihu sbd da kansa ma ya karbi abinda ta Haifa,
Oga Ahmed ma yasan ta haihu a daren...."

Kukanta karuwa yayi muryanta ya tsinkewa sbd tsoro numfashinta na Neman daukewa tsaban tashin hankali da tsoron wuqar Dake wuyanta tanajin kaifinta.

Lam da duka jikinsa ke rawa da zufa kasa hakuri yayi cikin zafi da matsuwa yace

"Me ta Haifa a Daren?
Waye Wanda kuke tareda shi a gidan wannan Daren?
Ina abinda aka haifa din yake?
Waye ya tafi dashi?

Wani sabon mari BB ya falla mata cikin rashin tausayi bare Imani Yana cewa

"Koro bayanin amsosin abinda aka tambayeki kafin na ratsa wuqar Nan cikin makoshinki"

Bakinta da duka jikinta na rikicewa da jijjiga Hawaye da majina duk sun cakude a fuskanta cikin matsanancin tsoron rayuwarta tace,

"Banda tabbacin abinda ta Haifa sbd a dare duka muna cikin tsoro da tashin hankali daga sir Omar Se oga Ahmed da 'yayan Hajiya Ameenatu din ne kadai suka San Menene aka Haifa tsakanin mace ko namiji...
A Daren yayanta yazo daga gombe gurinta Kuma shine ya tafi da babyn"

Wata sabuwar zufa ce ta tsiyayowa kowannensu Dan kuwa abin yazo a yanda basuyi tsammaninsa ba.

Sake danne wuyanta BB yayi tafara jero musu bayanin komai Daya bayan Daya har address din gidan Babbah dake gombe da yanda suka tsare da Kuma yanda Taga girman son dayake wa yar uwarsa da abinda ta Haifa din tabar masa.

Abu dayane ta boye shine cewan tasan mace ce aka Haifa sbd tsaban rufewa da shiga tashin hankali kwata kwata ta manta mema aka Haifa din.

Tana gama fadan kalamanta na karshe Mam ya miqe tsaye Yana ficewa daga dakin zuciyarsa Babu inda Bata tafasa da daukan nauyi.

Lameenu kuwa bayan ya miqe BB ya kalla da idanuwansa tareda yi masa kallan dayasan me yake nufi kafin Shima ya fice Yana Jin ihun Maryama din datai so Daya Bata Kara ba aka rufe bakinta.

Mota suka suka nufa da sauri BB ya qaraso ya budewa Mam driver Kuma ya budewa lameenu suka shiga Kai tsaye aka rufe driver ya shiga da sauri ya tayar da motar BB na musu a sauka lafiya suka bar gurin.

Tinda suka kama hanya Babu me cewa komai sbd kowa da Saka da warwaran da yakeyi a zuciyarsa cikin tinanin Neman mafita data inda zasu fara Neman

Dan uwan matar Omar Wanda a yanzu sukeda cikakkiyar tabbacin 'dan Omar Yana hannunsa.

Lameenu da hankalinsa yafi na Mam tashi sbd yanada labarin project dinsu ba lallai yakai labari ba Dan kuwa komai Baya tafiya yanda akeso,
Idan Mam yaji Hakan abun sake lalacewa zeyi Dan shi Kam ya gaji da Mam Yana sake bawa Haroon Daman shikuma Yana sake rusa su sbd bazai taba zaba me amfanin da sukeso ba Babu amfanin basa damammakin da ake basa,

Shi a nasa son su cire Haroon daga komai nasu Dan baida amfani kawai su bazama Neman magajin Omar Dan kuwa Babu abinda zasuyi yanzu dukiyar ta dawo yanda take koma fiye da yanda suke tsammani bayan su mallaki dukiyarsu ta Omar Dake ransu tin shekara da shekaru.

Mam ma a cikin ransa kusan tinanin ne a ransa Dan kuwa idan ba bazama sukai suka haukace gurin Neman magajin Omar ba faduwansu zai Sakasa yiwa dansa abinda baitaba tsammata yi din ba Dan kuwa ya tabbatarda Haroon yafi kowanne 'da rashin amfani,
Ya rasa wane irin Kai ne dashi gashi tsaban rashin basira ya kasa roko ko rarrashin Jamaal ya dawo musu,

Ba komai ya sakashi sakar masa pressure da nuna masa hantara da rashin kauna ba sai Dan ya rufe ido ya dage ya Saka Jamaal dawowa garesu ba Dan yasan duk duniya Haroon ne kadai zai iya Saka Haroon dawo musu Dan kuwa duk Wanda yasansa yasan Haroon ne abinda yafi komai so da kauna fiyeda komai bayan mahaifiyarsa Dan haka suke zafafawa Haroon komai Dan Jamaal ya dawo musu Amma Haroon din kaman kansa Babu komai a ciki Se iska,

Duk maganin da suka Saka masa a drink suna susuta kwakwalwansa Dan ya zama abin tausayin da zai Saka Jamaal ya dawo garesa abin ya gagara sbd yasan duk abinda Haroon zai koma bazai taba zabar barinsaba Koda Jamaal da mum dinsa sunso daukesa bazai taba binsu ba Dan haka yakeda tabbacin Jamaal zai dawo sbd Dan uwansa.

Suna Isa gida kowa mansion dinsa ya shige batareda tsayawa office nasu Dan tattaunawa ba Dan kowannensu Yana buqatan kadaicewa Dan dawowa daidai.

Mum Atee na ganinsa da yanayinsa bayan shigowansa tasan akwai damuwa me girma Dan haka tabarwa Ayesha zaban kayan datakeyi a waya ta bisa zuwa sama tana fatan ba matsalar Haroon bane da itama zuwa yanzu lamarinsa yafara isarta Dan itace kullum me zuba maganin da suke basa a drink dinsa na cin abinci sai kuma ta tabbatarda yasha cikin kulawa da dadin Baki Wanda ahankali ahankali yake yiwa kwakwalwansa illa harma da

kuzarinsa batareda sanin Dad dinba Dan abinda yasaka ta ringa basa daban da abinda take basa din.

******Barr Haroon seelah a yanzu ba zaman Nasarawa ne ke basa nutsuwa da farin ciki ba ganin Ameenatou ne da rayuwar ahalinta da yanzu ya zamar musu tamkar Dan uwa,

Ayanzu Daya sabu da zamanta a cikin zuciyarsa Babu ranar da Baya zuwa gidan duk yanda zai gaji da ayyuka kuwa saiyaje gidan da daddare acan yake fira cikinsu sai dare sosai yake komawa masauki.

Babbah da dukkaninsu har zuciyarsu sun basa matsayi me kyau da kauna me sanyi kallansa sukeyi a Dan uwa duk da tsananin tazarar datake tsakaninsu Dan kuwa idan ya zauna cikinsu kaman saika wanke hannu zaka tabasa Dan yanda yake fita daban kaman wata acikin taurari.

Ameenatou sosai suka shaku cikin qanqanin lokaci Kuma a bayyane yake yanzu tsananin son dayake mata duk da itama tana sonsa sosai sedai hakanan wasu lokutan sai takejin kaman irin son datakewa su Yaya Hafiz take masa Amma Kuma tace bazata auri kowa ba sai shi Dan Hakan ne ma yakejin samunta a rayuwarsa zai samu nutsuwa da Kwanciyar hankalin Daya rasa tareda kadaicin rayuwar dayake ciki.

Bai taba sanin wannan son dayake a cikin kirjinsa yanzu ba shine abinda Dan uwansa Jamaal yake ji a lokacinda fadilansa tana raye ba,
Baitaba dauka zaiso mace irin son da Jamaal yayiwa fadila ba sai yanzu dayake Jin Ameenatou har cikin jininsa da ruhinsa Dan kuwa akanta ne yafara Jin Koda Dad dinsa zai yafesa idan har zata zama cikin rayuwarsa zai iya fuskantar Hakan.

Dukkaninsu Babbah sun San so me tsanani yakewa Ameenatoun Dan haka yake sake matsayi sosai a zuciyoyinsu musamman Hafiz dayake Jin farin cikin Ameenatoun zata samu rayuwar da zata zufafa iliminta Dan sunada burin tayi karatu me zurfin da zata dogara da kanta tinda bazata zauna karkashinsuba har abada.

Aikin Daya kawosa fara lalacewa yayi matsaloli suka fara bayyana sbd gabaki Daya hankalinsa da nutsuwan dayake samu a gurin Ameenatou suna can,
Idan ciwonsa yafara tasowa na damuwa Baya gane komai Baya ganin komai idan ba gidansu Ameenatou ya taho ba ya zauna ya zuba mata idanuwansa tana magana yana sauraronta Kokuma Idan tana tareda su Babbah tana zuba sangartanta son ranta batareda damuwa da Yana gurinba Dan matiqar tana taredasu Bata duba kowa duk abinda takeso zatayi Abinta shi Kuma Hakan

yake sake kashesa akanta musamman idan tana fadan shi kadai ne zai zama mijinta Babbah zai aura masa ita.

Wannan kalman itace kalman da ayanzu take fin komai Sakasa farin cikin Da bayada shi kwata kwata a rayuwarsa.

Siddeeq hankalinsa yafara tashi sosai da irin son da Haroon yakewa Ameenatou Dan karfinsa yafara Sakasa shakkar lafiyansa ga Kuma bangare Daya aikin dayake gabansu fa Babu haske ko kadan kullum sabuwar matsala ake samu Dan haka yake cikin tashin hankalin.

Ranar dasu Dad suka zauna da turawan da suke cikin aikin suka fara samun barazanar janyewa daga hadin gwiwan kwata kwata jinin Mam Hawa yayi sosai Saida aka kira likitoci gida suka dubasa aka basa magani hadda su ruwa.

Mum Atee hankalinta tashi yayi Dan haka ta dagawa Haroon hankali da kuka Saida ya dawo Lagos a ranar cikin mummunan tashin hankalin abinda ya samu Dad dinsa.

Dad Lameenu kuwa kusan zaucewa yafara kokarin yi Dan ganin Mam a halinda yake ciki yasan balain Da yakai Mam kwance ba qaramin balain da zai kawo karshensu ba kwata kwata ne ba Dan haka ya kira BB ya Bude musu wuta akan tsananta bincikensu ko Wanda ya taba sanin dangin Aminatu ne aka samu a kamosa a kawosa.
#MAMUH

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700

Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
35
Tinda Haroon ya dawo Dad dinsa ya Hanasa ganinsa Dan Baya buqatan ganin ko fuskan Haroon din.

Mum Atee ce ta ringa lallaba Haroon din da duk inda hankalinsa yake ya tashi da wannan hukuncin na Dad dinsa.

Kusan Shima kwantawa yayi ciwon sbd hukuncin Dad dinsa na qin barin ya gansa.

Da wannan damar mum Atee tayi amfani ta ringa shayar dashi kwayar da suke Banka masa Dan haka sai yafara rikicewa ahankali ahankali sbd fushin Dad din da Kuma kansa da suke Neman juyar masa.

Siddeeq Daya fahimci yanayin Haroon din ya sauya sosai ya fara tsananta sosai daukesa yayi suka koma Nasarawa Koda lamarin zaiyi sauki idan Yana ganin Ameenatou wadda itama kullum take cikeda kewansa da damun su Babbah akan kada fa yaje ya auri wata acan Lagos yabarta anan ita tana jiransa.

Dawowansu Nasarawa ciwonsa tsananta yayi gashi basa ganin likita a bayyane a boye suke Gani sbd kada Yan jarida su ji Barr Haroon seelah magajin SEELAHs yana fama da matsalar data shafi damuwa da kwakwalwa.

Su Babbah Jin baida lafiya sosai suka shiga damuwa da tausaya masa sbd kaunar da suke masa ta wuce ta ogan Hafiz da Kuma Mai son Ameenatou.

Babbah da Yaya Abdul da kansu suka takurawa Haroon din da siddeeq suka Kaisa asibiti da kansu suna zuwa aka basa gado a dakin da Babu Wanda

zaisan waye a asibitin.

Kwanciyarsa asibiti ya Sakasa sake tabbatarda bazai iya rayuwa Babu Ameenatou ba Dan kuwa kauna da kulawan da Bai taba tinanin ana samu daga ahali ba sune ya samu Dan kuwa Hafiz ne ma kusan yake kwana ya tashi dashi a asibitin babbah da Abdul ma kullum anan suke kusan wuni dadah da Heartbeat dinsa kuwa kullum sai sunzo da daddare su koma tareda su Babbah gaba dayansu.

Ameenatou duk narkewa tayi ganin yanda ciwon kwana biyu ya mayar dashi Dan haka tausayinsa ya Saka sonsa Data kasa ganewa da tantancewa cike dukkanin zuciyarta.

Kwanansa biyu aka sallamesa batareda ance musu komaiba kawai dai wai ciwon Kai da bp dinsa ne ya hau sbd damuwa da stress na aiki.

Bayan an sallamosa da kwana Daya Lagos ya tafi Dan sake dubo Dad dinsa Wanda har lokacin ko wayarsa Baya dauka.

Bayan isarsa Lagos Shima siddeeq gida ya koma Dan dubo umman fadila da yanzu Alhmdlh ta rungume kaddara tana rayuwarta cikin Kwanciyar hankali da Kuma kulawa me tsananin datake samu da kauna sosai daga siddeeq din Daya inganta rayuwarta sosai Babu abinda ta rasa saima Jin dadinta datakeyi.

******Tsayuwa Haroon yayi jikinsa na sanyi ganin Dad dinsa zaune a kan dining din cin abincinsu na dare bayan baiyi tsammanin ganinsa ba a gurin Dan kwata kwata ya Dena barin Yana ganinsa.

Mum Atee ce tayi saurin tasowa daga inda take zaune kusa da Dad din Yana washe Baki cikin kulawa da kauna sosai ta nufosa tana cewa

"Zo ka zauna yau tareda Dad Dinka zakaci abinci Inshallah duk komai ya wuce"

Kallan Dad din yayi Yana qarasowa jiki a Sanyaye zuciyarsa na sanyi hakama jikinsa na sake mutuwa sosai.

Mum Atee ce tayi saurin ja masa kujeran kusa da Dad tana cewa ya zauna ai Dad dinma yayi kewansa.

Zama yayi batareda ya dago ya Kalli Dad dinba Shima Dad din Bai kallesaba ba Saida gurin ya dauki shiru tsawon mintina kafin Haroon din ya dago ya

Kalli Dad dinsa da idanuwansa dasukai wani irin ja da sanyi cikin sanyi da nutsuwa yace

"Dad barka da fitowa,
Yaya jikin?
Allah ya karo Maka afuwa da sauki."

Numfashi mata sauti Dan dumi Dad din ya sauke kafin ya amsa Kai tsaye Babu Jin dadi ko kadan a muryansa Dan kuwa ganin Haroon din kadai tafasa zuciyarsa yakeyi Dan gap yake da yafesa gwara yasan baida 'da ko Daya a gabansa Saiya fanjama mummunan aikinsa dakyau kawai ayi me yiyuwa.

Ayeesha Dake table din itama cikin kulawa ta gaida Dad din tana masa ya jiki ya amsa Yana gyada mata Kai kafin Suka fara cin abinci Babu me cewa komai.

Suna gama cin abincin mum Atee sai sake zuba masa juice din data hada masa da kanta takeyi cikin kulawa da tattalinsa kaman Dan data haifa.

Suna gama cin abincin kafin kowa ya tashi Dad sai lokacin ya dago ya Kalli Haroon cikin kamewa Babu sakewa ko kadan yace

"Ka hada komai na SSl project ka ajiye za'a rufesa gaba Daya Wanda kasan me Hakan ke nufi ai ko?"

Wani mugun zufa ne ya fara tsiyayowa daga cikin rigar Haroon ya dago idanuwansa ya Kalli Dad din cikin tsananin kwantar da Kai yace

"Dad Ina rokon ka karamin time na cike time din da aka dibarmin tin farko akan aikin nayi alkawarin zan cika Maka alkawarin dana dauka akan aikin,
Dad please Karkayi saurin rufe komai wlh Ina iya kokarina fiyeda yanda kake tsammani,
Ko yanzu rashin lfy nayi kwana biyun shiyasa aka fara samun durkushewa Amma wlh Dad nayi Maka alkawarin komai zaizo gabanka yanda kakeso....

Daga masa hannu Dad din yayi zuciyarsa na wani irin ciwo da radadi Dan har lokacin Jin yakeyi zuciyarsa Bata warkeba.

Jajir idanuwan Haroon din sukai kaman yanda na Dad din sukai jajir yanajin baisan me zai kama ba yabar Daya tsakanin 'dansa da dukiyarsu dasuke Neman rasawa.

Mum Atee datai shiru Dan muskutawa tayi tana rokon Dad din akan ya sake bawa Haroon din dama.

Ayeesha kuwa shiru tayi dukkanin jikinta yayi sanyi da tausayin Haroon Daya rasa komai akan Dad dinsa Amma Babu Wanda ya taba appreciating nasa ko kadan.

Shiru Haroon yayi zuciyarsa na nauyi me tsanani tareda nauyin Kai shima me tsananin Yana sauraran yanda mum Atee ke rokon Dad din kafin ya amince masa da sharadin ana samun matsala zai tattara ya koma Poland Shima gurin mahaifiyarsa.

Dagowa yayi da jajayen idanuwansa ya kalli Dad din tareda masa godiya kafin ya miqe jiki a mace yabar dining din Shima Dad miqewa yayi yabar dining din.

Koda ya koma dakinsa juyawa kansa yafara yi masa tin a palonsa ya zube Yana dafa Bango kaman ganinsa zai dauke Yana Jin kansa kaman zai tarwatse.

Daqyar yakai kansa dakinsa ya Isa gaban mirror Yana Neman maganinsa Amma Bai gansa ba.

Raffowa yayi Yana barin duk abinda ya fadawa harya Isa gefen gadonsa yafara janyo drawers hannuwansa na wata irin rawa Yana yamutsa kayan ciki gurin Neman maganinsa Amma kwata kwata ya kasa ganinsa.

Buga kansa yafara yi a jikin gadonsa Yana wata irin rawar jiki.

Wayarsa Dake gefen gadon ajiye ce tafara ringing Amma Sam baima San meyake ji ba bare yaji Kiran.

Ameenatou Dake kiransa Dan Jin muryansa sake Saka Kiran Tayi tana matsuwa Daya dauka Dan haka kawai zuciyarta keson jinsa Dan yanzu zuciyarta ta gama yin naam da karban sonsa fiyeda yanda tayi tinanin tana son nasa.

Cigaba da Kiran datake masa ya Sakasa dago idanuwansa da sukai wani irin mugun jajir ya Kalli wayar.

HB ya Gani rubuce kan wayar yaga itace.

Hannuwansa Dake wata irin rawa ya dago suna jijjiga ya Dora akan wayar ya dauko tareda daga wayar ya Saka handsfree ya ajiye Yana Jinta acikin dadaddiyar muryanta me sanyi da nutsuwa tana magana.

Yana jinta Amma kwata kwata Baya iya magana saima Juyewan dayake Jin kaman kansa zeyi da azabbiyar ciwo da nauyi hakama jikinsa rawa yake qarawa sosai Yana hada zufan dayake sake tsatsafo masa Tako ina har cikin tafin hannuwansa da kansa.

Sunansa ta sake kira cikin damuwan jinsa shiru tana narke masa a wayan.

Wasu hawayen azabbiyar Sonta da tausayin kansa masu tsananin zafin gaske suka gangaro masa ya rufe idanuwansa harta gama magana yanaji ta kashe wayar batareda ta sake Kiran ba.

Kuka me zafi ne ya kufce masa Yana buga kansa a jikin gadonsa da karfi har lokacin jikinsa rawa yakeyi sosai musamman hannayensa.

Ya Dade acikin wannan azabar tsawon lokaci kafin ya Dan samu sassauci ya rarrafawa ya sake dudduba maganinsa ya gansa a Palo ya dauka da sauri hannuwansa na kakkarwa ya Bude roban ya zubo guda biyu ya jefa bakinsa tareda Isa inda ruwa suke da sauri ya dauka ya shanye maganin yana sake hada zufa me yawa kafin ya silale a palon ya zauna Yana rintse idanuwansa Yana jingina bayansa jikin bayan Daya daga cikin tsadaddun kujerun palon.

Yayi mintina sosai ahakan kafin ya dawo daidai ya sauke numfashi da ajiyan zuciya tareda miqewa tsaye ya nufi bedroom dinsa gurin wayarsa Kai tsaye ya nufa ya dauka Yana kallan time yasan zuwa lokacin Ameenatou tayi bacci Dan haka Hafiz ya kira ya tambayesa ya sanar mace tayi bacci.

Sallama sukai batareda ya kirata ba Dan kaman yanda su Babbah ke lallabata haka Shima yake lallabata kaman zuciyarsa Dan haka bazai iya tadata bacci da wayarsa ba.

Ajiye wayar yayi ya miqe ya nufi bathroom ya sakarwa kansa ruwa yayo wanka ya fito daure da towel ya shirya cikin kayan bacci marasa nauyi ya kwanta Yana rufe idanuwansa jikinsa har lokacin a Sanyaye.

Washe gari tinda safe breakfast kawai yayi dasu Dad yayi musu sallama suka nufi airport suka bar Lagos din shida siddeeq.

Bayan tafiyarsa Dad Lameenu ya Saka aka bisa Dan Saka masa ido sosai akan lamarinsa kowanne irin motsinsa da komai Dan shi Kam bazai yadda suna kallo su wayi gari basuda komaiba.
#MAMUH#
#JAMAAL JEEY
#HAROON SEELAH

#AMEENATOU
#IDENTICAL TWINS

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
36
Ameenatou na islamiya ya dawo Dan haka bayan yayi Sallah abinci yaci ya kwanta Dan samun baccin da tinda yake Lagos harya baro Bai wani samuba. Shima siddeeq hutun ya kwanta ya samu kafin yamma.

Karfe Biyar da mintina ya tashi daga babbacin na awa Daya da Yan mintina San Saida yayi laasar ya kwanta.

Wanka kawai yayi ya shirya ya karbi ke din mota daga hannun siddeeq da kansa yaja ya nufi makarantarsu Ameenatou Kai tsaye.

Yana Isa ana tayar dasu Kuma Hafiz ma Yana Isa daukota Dan haka Koda ta fito cikin doguwar hijabinta akansa idanuwanta suka fara sauka Yana tsaye jikin motarsa Yana waya ahankali kaman mara lafiya kyakkyawar fuskansa ta fada kadan gaba Daya ya juyo hankali da idanuwan duk Wanda ya fito makarantar dama masu wucewa akansa sbd ganin bature tsaye bakin makarantar tasu.

Waya yakeyi Amma Shima tinda ta fito idanuwansa na kanta yanajin jikinsa na mutuwa zuciyarsama sanyi tayi Dan baisan wane irin so ne yakewa Ameenatun ba.

Ganinsa itama ya Sakata sakin kyakkyawar murmushi tana Dan dauke idanuwanta daga kansa Dan kuwa Jin tayi ganinsa ma gaba Daya ya Sakata Jin wani farin ciki me yawa gashi tana son tayi murna sosai a fili Amma batason Yan makarantar Susan shi zata aura su fara kalle mata shi Dan gulmansu.

Nufosu tayi zata Bude Baki tayi magana Hafiz ya jefa mata wani kallan Daya sakata nutsuwa tana hadiye zancen Daya fadawa Haroon na kewan datai masa me tsanani.

Kashe wayarsa yayi Yana kallanta fuskansa daukeda murmushi Mai bayyanarda farin ciki yace

"Barka da fitowa Budurwan Babbah"

Wani sabon farin ciki taji ya rufeta sedai narke fuska tayi tana qasa qasa da murya kada Hafiz yaji tace masa

"Yanzu ba budurwan Babbah bace ai na sauya suna"

Mota ya Bude mata ya shiga ya rufe mata Saida ya zagaya ya shiga ya zauna Hafiz ma ya shigo kafin ya kalleta Yana tayar da motan yace

"Yanzu yar budurwan Barrister ce ko??

Wani sabon dadin taji Yana hararan Hafiz da Shima ita yaketa harara kaman idanuwansa zasu fado Amma taqi kallansa bare taga kwabar dayake mata ya ido sbd sakarcin Data Saba yi musu hadda Haroon din kada tayi a gaban makarantar cikin bainar jamaa.

A hanya kafin su Isa gida guri uku tana sakawa ana biyawa sbd siyan wani littafinta na islamiya da zata dashi gobe kafin suka Isa gida anata kokarin

shiga sallan magrib Dan haka Haroon din Bai shiga ba alwala kawai sukai a waje suka wuce masallaci ita Kuma ta shige gida.

Saida sukai ishai suka shigo gidan anan Haroon yaci abincin Dare tareda su Babbah na tambayar yanda ya baro mutanen gida.

Irin son dayake mata itama take masa basa buqatan ma wai saisun kebe sbd a jininsu suke jinsa shiyasa duk firar da sukeyi anan dai tareda kowa tsakar gida ake yinta Kuma ahakan suke soyewansu a gaban su Babbah Dan shi Kam idanuwansa ne basa iya kaucewa daga kallanta matiqar tana gurinda yake ita kanta kallansa shine ke sake sakawa duk tana sake shagwabe masa ko agaban su Babbah ne kuwa sai idan Hafiz ya gaji da sakarcin ya dinga fada kenan Yana hararta idan Haroon din ya tafi.

Washe gari ne zaa tafi da Ameenatou Abuja gurin rubuta jamb nata Daman hadda shi ne ya Saka Haroon din dawowa da wuri Kuma kaman yanda yaso university na Lagos aka cika Mata Dan haka tin 6 da mintina ya iso gidan da motarsa Daman Abdul tini ya shirya itama duk rigimarta Saida aka lallabata tayi wanka tin asuba ta shirya dadah ta shirya mata abincin karyawa da wuri Babbah ma sai addua yake binta da ita Yana cewa saita cinye har marking din Daya wuce Wanda akeso.

Abuja zatai jamb din Dan haka Babu Bata time suka fito itada Yaya Abdul da Haroon din suka kama hanyar Abuja idanuwan Haroon na cikin mirror Yana kallanta itama shi take kalla suna jifan juna da murmushi tana masa magana kadan kadan kaja Yaya Abdul din yaji Mai take fada masa batasan Yana ganinta ba yayi mata banza sbd yasan ma maganar idan yayi Bata bakinsa zaiyi Dan haka yayi kaman ma baisan me sukeyi ba fatansu dai kar Haroon din ya jefar dasu gurin wannan mayen kallan nasa da kullum sai Babbah yace tsoron yakeyi Haroon din ya cinye masa ita da ido ta rame kafin a tashi auren.

Sai 3 suka dawo gida a gajiye budurwan gidan ta dawo harma da zazzabi sbd kaf rayuwarta Bata taba Shan wahalan tafiya ko wata yar gwagwarmayar ba sai yau duk da komai na gata Akai mata Dan kuwa ko Rana Haroon dinta Bai bari ta shiga ba Saida zata shiga exams din ta fito mota hakama bayan fitowanta lafiyayyar tsadaddiyar restaurant yakaisu sukaci abinci Amma Sam Bata iya cin wani abincin ba sbd gajiya gida kawai takeso karshe ma haka suka koma daga shi har Abdul din suna lallabata har aka iso gidan.

Haroon ajiyesu kawai yayi ya wuce Shima Dan haka wanka dadah ta taimaka mata Tayo ta zo ta kwanta take bacci ya dauketa sedai Koda yamma tayi zazzabi sosaine ya rufeta Dan haka hankalin dadah ya Dan tashi zuwa dare Saida aka Kaita chemist kafin su dawo zazzabin ya Dan saketa Se zuwa dare

ya sake dawowa.

Koda gari ya waye Haroon Bai Isa gurin aikinsa ba Jin rashin lafiyanta Kai tsaye gidan ya taho karshe dai asibiti aka kwasa aka Kaita duk da narkewanta ne yake Saka ciwon zama wani babba.

Suna zuwa haka aka kwantar da ita sbd ganin yanda hankalin duka ahalin ya tashi hakama Haroon seelah din.

Kwananta Daya a asibitin aka sallameta bayan Haroon yagama lalacewa akanta tareda mantawa da aikin dayake gabansa Wanda duk iya kokari da sadaukarwan siddeeq gurin ganin project din ya tafi daidai ko kadan ne Hakan Bai faru ba Dan haka yake cikin tashin hankali da rashin nutsuwa.

Aikuwa Haroon na dawowa hayyacinsa ya nutsu ya fahimci gagarumar tashin hankalin Dake gabansa take ya shiga firgici Shima Dan tini ma sbd sakacinsu aka sace plans da komai da komai na project din.

Wannan mummunan tashin hankalin ya kusan Sakasa zaucewa Dan kuwa Yanke jiki yayi ya Fadi Saida siddeeq da sauran ma'aikatan suka taresa sedai gaba Daya Jin yayi Yana fita hayyacinsa kansa na Neman Juyewa hannuwansa na rawa.

Gaggawan mayar dashi hotel siddeeq yayi Shima nasa hankalin baa kwance ba Dan kuwa yasan ko Dad yaji wannan zancen sake samun hawan jini zeyi gashi Babu ya yanda zata yiyu cikin qanqanin lokaci su hada sabuwar plan din dazata sakasu Kai labarin wannan project da aka fara.

Haroon Neman zaucewa yafara yi zuciyarta na tsananta bugun Daya wuce misali hakama baisan ta inda zai fara ba.

******Dad Lameenu Dake zaune tareda Mam a palonsu na office suna magana wayarsa ce tayi ringing Ya juya ahankali ya Kalli sunan me Kiran yaga BB ne Dan haka Kai tsaye ya dauka tareda Kai wayar kunnensa Yana cewa

"Yes BB"

Bayanin komai daki daki BB ya fara korowa tin daga kan sunayen ahalin gidan Babbah da Kuma yanda Haroon gaba Daya rayuwarsa ta mace akan yarinyar gidan da Baya gane komai ba a yanzu idan ba abinda ya shafeta ba harma da bautawan dayake musu da gagarumar tsautsayi da aka samu akan project din....

Dad Lameenu Bai gama Jin karshen zancen ba wata mummunan zufa ta tsinke masa Yana cewa

"What???
Yaushe wannan babban balain ya samu??
Ina Haroon din yake yanzu??

Mam na Jin Hakan ya ajiye wayar hannunsa Daya karanta wani article da aka rubuta gameda rushewan da SEELAHs keyi a boye batareda sun bari duniya ta saniba.

Ajiye wayar yayi Yana Dan rintse idanuwansa da suka fara sauyawa Dan kuwa Yana fatan ba abinda zuciyarsa ke Saka masa bane zaiji daga Lameenun.

Cikin tashin hankali lameenu ya buqaci ganin BB yanzu yanzu Dan zuciyarsa bugawa zatai idan Yana sauraron wannan mummunan tashin hankalin ta waya.

Kashe wayar yayi Yana kasa kallan Mam da shima ya kasa tambayar Lameenun komai BB din yake Jira yaji komai Dalla dalla daga bakinsa.

Kafin BB ya iso daga Mam har lameenu da jininsa ya Dade da Hawa Dan tini aka kirawo likita Yana cikin auna BP dinsa BB ya iso take ya sallami likitan akan saisun gama magana.

iPad din hannun BB ya fara kamo hotunansu Hafiz da Yan gidan kaf ya ajiye ipad din gabansu bayan ya kamo hoton Ameenatou datake sanye cikin hijab dinta na islamiya tana murmushi asalin kyanta da kuruciyarta a bayyane tana kallan gefe Dan kuwa batasan ana daukanta hoton bama.

Bayani Daya bayan Daya a tsanake BB yafara jerowa Wanda yayi mugun girgiza su musamman Mam Dan kuwa Bai taba tinanin Shima Haroon zai fada irin kaddarar Dan uwansa ba ta yiwa mace son da Bai kamata ba adaidai lokacinda suke buqatan nutsuwansa da hankalinsa tareda sadaukarwansa fiyeda komai a duniya yanzu.

Ameenatou dukkaninsu suka zubawa idanuwansu da sukai jajir,

Tayaya Haroon zai bari zuciyarsa ta mutu akan mace bayan yasan Menene a gabansu,
Tayaya Haroon zai bari mace ta shiga zuciyarsa,
Tayaya zasu iya samun yanda suke so daga zuciyar Daya mutu akan mace.

Kenan shi tasa mummunan kaddarar akan matan da yayansa suke so ne ko me?
Shima Haroon macen ce zata shiga tsakaninsa da ita?
Ta Ina zai fara karban wannan kaddarar ta Haroon bayan haryanxu Bai fito daga baqin ciki da radadin ta Jamaal ba.

Wani nauyi kirjinsa yayi Yana tafasa da wani irin zafi da radadin da baisan mezaiyiba akan Haroon din Daya kashesu da ransu a Rana tsaka.

Lameenu da tini jininsa ya sake hayewa akan babban tashin hankalin da Basu Saka masa Rana ba da sauri aka sake dawo da likita.

Da sauri likita ya dawo Yana cewa a kwantar masa dashi flat.

Mam tsaban tafasa da qunan da zuciyarsa keyi Jin yayi Haroon baida sauran amfani a garesa ko kadan Dan haka take ya Bada umarnin a Siya masa ticket a ranar zashi Nasarawan.

Lameenu na Jin Hakan yaso wartsakewa su tafi Amma Ina hawan jinin ya sharbesa da kyau Dan haka Yana ji Yana Gani Mam din ya tafi.
##MAMUH#
#DR JEEY
#AMEENATOU
#MAM SEELAH
#BABBAH

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k

Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
37
Motoci ne na alfamar guda biyu harda securities suka dauko Alh Mam seelah daga airport.

Wayarsa Dake gefensa ya dauka tareda kasheta gabaki dayanta Dan kuwa Baya buqatan Kiran kowa sbd har lokacin zuciyarsa a cikin wani matsanancin zafi da radadin take Mai tsanani.

Daga Haroon har sauran ma'aikatansu manya da abokan huldan Babu Wanda yasan da zuwansa a ranar Kuma aaukan dare sukai Dan haka Kai tsaye masaukinsa Dake cikin Abuja aka nufa dashi Saida safe zai fuskanci Haroon, Haroon dinma ya fuskacesa.

Bayan samun nutsuwa da komai cikin Daren kasa tintsawa yayi ya shiga tinani masu zurfi da sakawa da warwaran ta Ina zai bullowa wannan masifu haka wani bayan wani,

Idan har Haroon na son wannan yarinyar sosai Yana buqatan sauya ha yar handling na abubuwan ta wata hanyar ba irin hanyar dayayi ta farko ba ta rabasa da Jamaal a daidai lokacin dayafi buqatansa da sonsa a kusa fiyeda komai dayake buqata a duniya Dan ko dukiyar Omar da sukeso idan basuda tasu dukiyar tayaya zasu karbeta?

Dole Yana buqatan sauya takun kammala komai cikin hanya mafi sanyi da karfin gaske Amma kwata kwata Babu maganar yabar Haroon yin auren wannan auren a yanzu Dan baima gama zama me amfanin dasuke buqatan ya zama ba ya moru bare idan yayi auren gaba Daya qarasa zama mara amfanin zeyi Kuma sai yanda mace tayi dashi Wanda baqin cikin haka zai iya sakashi yafesa ko illatasa Dan haka bazai taba barin ayi Hakan ba a yanzu saiyaga sauyin Haroon din.

****Har washe gari Haroon Baya cikin cikakkiyar lafiyan hankalinsa Dan shock da tsoron da zuciyarsa take ciki tareda mummunan firgici da tashin hankali ya Hanasa dawowa daidai duk da maganin Daya kwana Yana Sha a cikinsa Wanda harya wuce kaidarsa.

Ya boye kansa bayan siddeeq Babu Wanda yake iya ganinsa duk da ma'aikatansu da yawa dakeson ganinsa da masu zuwa da masu bugo waya duk ya kasa ganin kowa sbd state din dayake ciki bamai dubuwa bane hakama siddeeq din kansa duk ya dage sosai da kokarin hada mafitar gagurumar matsalar shiyasa Shima kansa Baya guri Daya.

Duk daqiqa Daya Dake wucewa sai Haroon ya Tina mahaifinsa da abinda zai iya biyo bayan wannan mummunan aikin kaddarar Daya samesa Dan haka hankalinsa ke sake tashi.

Tinda safe ya samu labarin Dad dinsa na Abuja daga bakin siddeeq Dan haka cikin sabon rikicewa duk da halin dayake ciki ya shirya ya fita aiki Dan Neman mafita koman kankantarta akan aikin kafin Dad ya iso Nasarawan.

Hafiz da siddeeq ganin Halinda yake ciki yana aiki gaba Daya cikin ficewa hayyacinsa riqesa sukai tareda zaunar dashi sai a lokacin idanuwansa suka ciko da wasu irin hawaye masu radadin gaske.

Kallan Hafiz siddeeq yayi tareda cewa ya tafi aikinsa kawai inshallah zaa samu mafita.

Dayake duk ma'aikatansu manya da wainda sukeda kusanci sosai irin Hafiz sunsan ansamu gagarumar matsala Amma bayansu Babu Wanda ya sani shiyasa Hafiz yake cikin damuwa sosai na ganin Halinda Haroon ya shiga akan Hakan.

Kasa aikin yayi ya taho gida Shima bayan siddeeq ya sauke Haroon din sunbar site gaba Daya Dan ciwonsa Daya tashi gadan gadan a gurin tin kafin kowa ya fahimci wani abu ko a gane musamman Hafiz da bazasu so yagani ko ya san ciwon Haroon din ba.

Yana Isa gida jikinsa duk a mace zuciyarsa ba dadi,
Bai boyewa su Babbah ba ya sanar dashi damuwa me tsananin da Haroon yake ciki take Babbah ya daga wayarsa ya Saka Kiran Haroon din Dan basa kwarin gwiwa da adduar samun mafita da nasara a duk inda take Amma wayar Haroon din a kashe Bata shiga kwata kwata.

Ameenatou ma Kiran nasa ta Saka kaman zatai kuka Jin halinda yake ciki

Amma kayinsa Baya shiga kwata kwata.
Yaya Abdul ma ya gwada Kiran da tasa wayar duk dai Bata shiga.

Dadah da tashiga damuwar itama kallan Abdul tayi bayan sunkai har kusan rana Ana kiransa baa samu tace

"Bara na sauke abinci saina hada masa nasa kwando ka Kai masa saika dubo mana lafiyar tasa tinda Kiran ya kasa samuwa"

Ameenatou na Jin Hakan ta marairaice fuska akan zata bisa
Dadah ta girgiza mata Kai tana cewa

"Kul na haneki da wanna tinanin Dan Babu inda Zaki....

Karbe zancen Abdul yayi da cewa

"Har sai kin fada? Ni hauka nakeyi zanje da ita gurinsa"

Tana Jin Hakan ta Bata fuska tana komawa jikin dadah din ta kwanta tana kokarin fara Hawaye Hafiz Dake gefen Babbah Yana rubuta text yace

"Kina tsiyayo Hawaye a gurin Nan saina fasa ruwan idonki Daya muga karshen hawayen rainin wayo."

Katsesa babba yayi da cewa

"Ba zataiba ta fasa"
Maida kallansa yayi kan Ameenatoun Yana cewa

"Mayar da abinki yar budurwan gidan Babbah tare zamu dubosa idan naje ai kaman kinje ne ko??"

Gyada Kai tayi tana mayar da hawayenta tana hararan inda Hafiz yake zaune Yana jifanta da tasa hararar me zafi Shima.

Saida sukai sallah sukaci abinci dayake Babbah baida gurin zuwa ranar sai suka fita tareda Abdul din Dan dubo Haroon din.

******Isarsu yayi daidai da isowan Alh Mam seelah Wanda tin a masaukin Haroon din ya tabbatarda Haroon Baya cikin cikakkiyar hankalinsa me amfani Dan kuwa duk kyau da tsananin tsadan hotel din ganin yayi 'dan cikinsa jinin Seelahs yafi karfin zama yayi rayuwa a gurin Amma sbd ba shine ya kawosa ba abinda ya kawosa yafi wannan mahimmanci a yanzu.

Babban abinda yasa yake fatan ganawar gaske suyi budaddiyar wasika da Haroon din shine yasan Lameenu akan lamari na faduwa bayada hakuri,
Bayason abinda zai Saka Lameenu ya kasa hakurin dazai iya aikata wani abin batareda saninsu ba Dan idan har zaisa abibiya lamuran Haroon din batareda saninsa ba zai iya rashin hakurin yin wani abun batareda saninsa ba haka zalika alkawarinsu ne dayake yawo a jininsu Dan zuciyarsu kowa ya shiga hanyar shiga tsakaninsu da arzikinsu ciresa sukeyi daga hanyar kwata kwata Dan haka yake buqatan Saka hankali acikin tosashiyar kwakwalwan Haroon din idan ba Hakan ba zai barwa lameenu kulawa da komai Wanda yasan me Hakan ke nufi.

Su babbah ne suka Riga Mam din isowa Dan haka ko ganinsa Basu samu yi ba Yana bedroom dinsa Dayake suite ne yake rayuwa a ciki saiga shigowan siddeeq a gaba Alh Mam seelah din da securities dinsa duk a tsaye bakin Kofar dakin ya shigo siddeeq ya rufe kofar Yana biyo bayansa cikin tsananin girmamawa.

Yaya Abdul na ganin Hakan ya miqe a natse daga inda yake zaune Shima cikin nuna girmamawa Yana masa barka da zuwa cikeda nutsuwa.

Babbah ma miqewan yayi Yanawa mahaifin Haroon din barka da zuwa a mutunce suna kallan juna sbd kowannensu sai fuskan tayi masa kama da Wanda ya sani Amma sbd kada su kure juna da kallo sai kowannensu ya Dan dauke kallansa Dad din Yana amsa gaisuwan a mutunce Shima Dan Daman shi mutum ne Daya iya taku da mu'amalantar mutane shiyasa SEELAHs sukeda mutunci sosai a idanuwan mutane sbd iya tafiyan da lamuransa.

Yanda suka gaisa a mutunce Babu girman Kai ko nuna musu banbanci ya Saka su Babbah din sukai masa sallama suka tafiyarsu Dan Basu guri da 'dansa batareda Haroon din ya fito ba Dan abinda Basu saniba Haroon din Yana jinsu Amma bazai iya fitowa a halinda yake ciki ba su gansa.

Saida suka fice siddeeq yaje rakasu kafin Haroon din ya fito hannuwansa na tsananin rawa kansa a qasa idanuwansa jajir Babu kyan Gani hakama a jiqe yake da zufa Mai tsananin gaske,

Babu inda yakejin azaba me tsananin gaske kaman a tsakiyar kansa da kirjinsa,

Jin muryan Dad dinsa a dakin ya karasa karya dukkanin Wani karfin halinsa shiyasa ya kasa fitowa Saida su Babbah suka fice Dan ganinsa a wannan halin na mafi Munin rauni zai karya zuciyoyinsu akansa gameda Basu auren macen da bayajin zai iya rayuwar Nan Babu ita su kuwa Ayanda suke

tsananin kaunar Ameenatunsu bayajin zasu taba bawa Wanda bazai iya tsayuwa a gaban mahaifinsa bama ya dago kansa aurenta sbd tinanin bazai iya Bata kariya ba ko kare martabarta.

Hannuwansa Dake rawa sosai kaman zasu qanqame yayi Baya dasu Yana kasa dagowa har lokacin kansa Juyewa yake Neman yi.

Zuba masa nasa jajayen idanuwan Mam yaji Yana kallansa sbd baisan ma me zai fara dashi ba sbd baqin ciki da damuwa me tsananin gaske Dan Shima Yana tsaka me wuyar da baisan ta inda zai fara bullowa zancen ba.

Tsadaddiyar wayarsa Daya ajiye gefensa bayan ya zauna ya miqa hannu ya dauka tareda kunnawa ya Nemo hoton Ameenatou ya ajiyewa Haroon din kan centr table Dake gabansa batareda yace komai ba tukuna.

Haroon Daya kasa motsawa bare magana dago jajayen idanuwansa yayi ya Kalli wayar da Dad din ya ajiye masa idanuwan suka sauka akan hoton Ameenatou Dake bayyane a ciki tana murmushi sanye da hijab din islamiya.

Mummunan bugawa kirjinsa yayi ya dago idanuwan da sauri sai alokacin ya Kalli Dad din da Shima shi yake kalla Yana kokarin karantar yanayinsa.

Hannuwansa Dake tsananin rawa ya sake kankamewa Yana sake kallan Dad din da kyau kafin ya Bude bakinsa Dake rawa da muryan Dake bayyanarda tashin hankalin dayafi wanda yake ciki yace

"Dad Kayi hakuri na.....

Katsesa Dad din yayi da cewa

"Ka manta mace ce ta Raba Dan uwanka da mahaifinsa rabuwa ta har abada? Ka manta matsalolin rayuwar da muke cikinsu duka ayanzu duk sbd macen da Dan uwanka ya so ne fiyeda kansa da ni mahaifinsa?

Wasu Hawaye ne masu tsananin zafi da radadi suka gangarowa Haroon Dan Bai taba tinanin samun kansa a cikin irin yanayin da Jamaal ya samu kansa ba,
Gwara kaddarar Jamaal sbd shi yanada jarumta da karfin zuciyarsa fuskantar duk Wanda zai shiga tsakaninsa da farin cikinsa matars wadda ya tsayawa har ranar karshenta harma a bayan ranta ya tsayawa macen dayake so da dukkanin zuciyarsa.

Wasu zafafan hawayen ne suka sake gangaro masa Yana rintse idanuwansa

sbd Yana fatan inama wannan jarumtar zata shigesa ya tsaya akan macen dayakewa mugun son dayakejin yafi Wanda Dan uwansa yayiwa tasa macen.

Hawayen Dake zubawa daga idanuwan Haroon dinne masu bayyanarda tsananin radadin da zuciyarsa take ciki ya Saka Dad zubawa masa idanuwansa hankalinsa na Neman tashi Dan kuwa duk tsananin quncin da rayuwar Haroon din take ciki Bai taba zubar da Hawaye ba sai yanxu.
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*

Ahankali Haroon din yayi qasa sbd kasa riqe jikinsa Dake kakkarwa sosai da yayi har lokacin idanuwansa na kan hoton Ameenatou Dake kan wayar Dad din Yana tsoron me Dad zeyi da hoton nata.

Zuciyar Dad Dake tsallen tafasa tana quna sosai akan abinda idanuwansa ke gane masa na azabbiyar Son yarinyar dayake hangowa a idanuwa da hawayen 'dansa kwalli Daya daya rage a hannunsa.

Cikin sanyi da tattara nutsuwansa dan fahimtar komai yanda zai fishesa ya Kalli wayarsa shima tareda zubawa hoton Ameenatou idanuwansa zuciyarsa na shiga shakka da rarrabar tinani akan Aminta da ita ko sabanin Hakan sbd bazaiso tarihi ya Kuma maimaita kansa ba.

Dawo da kallansa yayi akan Haroon Yana dauke wayarsa daga kan table din yace

"Sbd itane ka tattarawa dukkanin nutsuwansa kayi Watsi da ita daga aikin dayake gabanka na cika mun alkawarin dakai na sakani alfahari dakai??
Kasan wane yaqin ne a gabanmu akan wannan masifar daka jefamu akan mace?

Muryansa na kasa fitowa sosai yafara kokarin magana Amma zuwa lokacin ran Dad din ya gama tafasa Dan haka ko sauraronsa beyiba ya miqe tsaye Yana cewa

"Ka shirya a yau din zaka bar Nasarawa ban aminta da zamanka ananba bare sake ziyartar Nan din,

Kasan me zai faru daga lokacin da na sake samun labarin ko 'dan uwan yarinyar Nan Daya ka sake muamala dashi???

Zasu bata ne gabaki dayansu danginta bazaka sake samun ko labarin Wanda ya taba saninsu ba bare sanin duniyar da suka tafi...

Qarasa zubewa yayi gaban Dad din Yana fashewa da wani irin kuka Mai tsananin tausayi da tashin hankali tareda Neman ficewa hayyaci Yana bawa Dad din hakuri jikinsa da hannuwansa na tsananta rawar Daya fara bawa Dad din mamaki da tsoro ya janye kafafunsa da karfi cikin zafi zaiyi magana Haroon din ya sake rarrafowa wannan Karan Yana rokonsa da cewa

"Dad Dan Allah kayi hakuri kada ka hanani Ameenatou,
Itace ke bawa zuciyata karfin hali da zuciyan da Banda shi,
Dad nayi Maka alkawarin wanna Karan wlh zan cika dukkanin buri da abinda kakeso idan ka barni da ita,
Dan Allah Dad ban taba tambayarka komai ba sai ayau din Ina rokon ka barni na aureta nikuma nayi Maka alkawarin zama duka abinda kakeso na zama,
Ka bani Daman karshe Dad zan gyara dukkanin matsalan da aka samu a

wannan aikin nayi alkawarin Hakan please Dad.

Tafasa zuciyar Dad din ke karawa yanajin kaman ya shaqe Haroon din da kansa ya qarasashi Amma Kuma zuciyarsa na yaqi da Hakan Dan bayason rasa Dan Daya rage masa.

Rikicewa Haroon yayi ganin Dad din baida niyar sauraronsa hakama yasan kaman yanda Dad din ya fada batar dasu Ameenatou Abu ne me saukin gaske duk da Baya tinanin kashesu zaai ko makamancin hakan Amma dai koma Menene rabasa da Ameenatou kaman rabasa da dukkanin sauran Dan hankalin Daya rage masa ne Dan haka yaji Yana Neman zaucewa gaba Daya Yana tino yanda Jamaal ya rasa fadila har abada sai kawai yaji kansa ya kasa dauka ya sake rarrafowa Yana biyo Dad din cikin matsanancin fita hayyaci daidai Nan siddeeq ya shigo sedai kafin ya karasa gurin Haroon din tini yafara wani irin jijjiga Yana buga kansa da kasa Yana ambatar sunan Dad din Dana Ameenatou batareda ma yasan meyakeyiba.

Jini hancinsa da goshinsa suka fara fitarwa harma da bakinsa Yana wani irin fizga take hankalin Dad din yayi mummunan tashin da baitaba tinanin zaishiga ba ya dawo da sauri Yana Kiran sunan Haroon din da sauri sedai tini ya fice hayyacinsa dukkanin jikinsa na qara jijjiga sosai.

Siddeeq ma cikin matsanancin tashin hankali ya kamo Haroon din Yana janyo pillow na kujera ya Saka masa Akai tareda birkitasa Yana hanasa bubbuga kansa a tiles da jininsa ke fita sosai.

Rasa abinyi Dad yai Yana shiga sabon tashin hankali da mamakin Menene yake faruwa da rayuwar Haroon din,

Badai shi Kuma haukacewa zaiyiba akan mace ba,
Innalillahi wainna ilaihirrajiun"

Meke faruwa da yayansa?
Innalillahi wainna ilaihirrajiun.

Duk yanda Dad yake tsammanin lamarin ya wuce Nan sbd Haroon take ya koma tamkar me cikakkiyar tabin kwakwalwa duk tsananin zafi da bacin ran dayazo dashi jin yayi kansa Shima Yana daukan matsanancin zafi.

Siddeeq drawers ya nufa na gado da gaban mirror Yana yamutsa hankali tashe Yana Neman maganinsa Amma kwata kwata ya kasa Gani.

Cikin daga sauti da kidima Dad yake cewa

"Meyake faruwa dashi ne?
Menene Hakan nake Gani?
Ciwon hauka ya kamasa ne kokuwa?
Menene wannan din???

Duk a jere ciki daga murya da tashin hankali yake jero tambayoyi Yana kamo Haroon din Wanda yake jijjiga har lokacin.

A karkarshi pillow siddeeq ya sami maganin bayan ya haukata dakin cikin tashin hankali da mintinan da Basu Fi biyu ba ya iso da sauri yana Bude maganin ya kamo kan Haroon ya Saka masa
Tsaban rudewa Dad dinne da kansa ya dauko ruwa ya miqawa siddeeq ya basa rabi na shiga bakinsa Rabi na zubewa harya hadiye maganin.

Sakewa jikinsa yayi Dad yayi gaggawan Bada umarnin a fito dashi zuwa asibiti shi kansa siddeeq a daidai wannan lokacin yasan likitocin gaske Haroon yake buqata Dan haka ba Bata lokaci aka kwashi Haroon din sai asibiti.

Suna zuwa aka karbesa sbd duka jikinsa ya Dena rawa ko wani abin sai kawai aka miqasa da cewan faduwa yayi.

Dayake Mam yasan abinda zai iya faruwa na zuwan Yan jarida take ya Bada izinin securities kada su bar yan jarida zuwa ko sanin komai.

Har yamma sosai suna asibitin Haroon Bai farfado ba,
Dad magana yayi da siddeeq sosai yaji komai gameda ciwon Haroon da lokacinda ya fara take ya fahimci ba karamar illa maganinsu keyi masa ba Ashe Dan haka take ya sake shiga tashin hankali da damuwan kada Yan jarida ko kadan Susan dansa Barr Haroon seelah na fama da tabin kwakwalwa.

A Daren suka koma Abuja dashi sbd hankalin Dad Bai kwanta ba anan din.

Su Babbah da suka samu labarin anbar Nasarawan da Haroon hankalinsu tashi yayi Dan kuwa ciwonsa kenan yayi tsananin gaske haka suka ringa Kila mintina bayan mintina Dan Jin lafiyansa.

A cikin kwana da wunin Dad yayi sakawa da warwaran datafi dari da hamshin hakama Dad Lameenu ma hakanan ya lallabo ya taho sbd yasan Mam din na cikin damuwa da matsanancin hali Dan haka ya taho su fuskanci lamarin tare duk da Shima ya kasa warware sbd Bai dawo daidaiba idan ba Jin yayi sun samu mafitan warwara ba.

A cikin kwana da wuni Dad ya tabbatarda irin tsananin so da kwallafa Rai da Haroon yayi akan AMEENATOU sunan Daya riqe Kai tsaye sbd Tinanin dasuketa yawo akansa.

A karon farko da zai sauya raayinsa zuwa wani raayin Dan cimma burinsa cikin sauri da samun mafita biyu,tasa data rasa 'dansa.

Shi kansa Dad Lameenu yashiga firgicin tarihin dayake Neman maimaita kansa,
Idan sun rasa Jamaal sun tabarbare haka to Haroon dinma dasuke ganin baida amfani suna rasasa karasa tabarbarewa zasuyi komai yazo karshe shikenan.

Farfadowan Haroon Saida ya bawa dukkaninsu tausayi sbd yanajin jikin sosai Dan wanna Karan maganin ya Riga yayi masa illa sosai da Babu wani abinda zaa iya yi sai ikon Allah.

Su Dad kasa barin kowa yaji zancen sukai sbd a nasu tinanin maganinsu ne yayi masa wannan mummunan illar.

Duk tsananin halin dayake ciki kallan Dad dinsa yayi har lokacin yanajin raunin batawa su Dad din Rai dayayi da asarar da shi kansa baisan ta inda zai fara gyara ba.

Rokonsa gafara da sake basa Dama shine abi farko Daya furta Yana rintse idanuwansa.

numfashi Dad din ya sauke tareda Gyara zamansa Yana kallansa cikin nutsuwa yace

"Zan sake baka Daman karshen Amma ba iya akan aikin kadai ba,
Zan nema Maka auren Ameenatou Amma sai idan ka cika alkawarinka ka gyara mummunan Barna da Tsaka me wuyan daka Saka SEELAHs gaba Dayanta aciki idan ba Hakan ba ka manta da maganar aurenta Dan kuwa har abada bazaka auretaba idan ba Hakan ne ya faru ba"

Rintse idanuwansa yayi hawayen ciki masu dumi suna gangarowa ya gyada kansa cikin wani irin sanyin jikin da mutuwar jikin batareda ya iya cewa komaiba sai tsananin tsoro da shakkan Dayake mamayesa.

Dad Lameenu da Baice komaiba gyara zama yayi Yana kallan Haroon din cikin nutsuwa Shima ya Bude Baki yace

"Haroon nayi Maka alkawarin bazamu bar garin Nan ba ayau sai munje munyi gaisuwar iyaye da iyayenta sbd Neman Maka aurenta idan har zaka nutsuwa ka fuskanci nauyin dayake kanka sbd Kaine kaidai zaka iya gyara wannan Barnar data riskemu sbd kafi kowa sanin halinda muke Neman fadawa idan bamu farfado ba.

Tinda suke magana idanuwansa a rufe suka Hawaye masu zafi na gangarowa a acikinsu Saida Dad Lameenu yayi masa alkawarin nema masa auren ya Bude idanuwan ahankali ya kallesa Yana sauke Kai kasa.

Dad dinsa ma Jin yayi yayi Naam da Hakan Dan shine maslaharsu ayanzu kada su maimaita kuskuren Baya gwara su nema masa auren su juyasa akan abinda sukeso tinda zai iya komai akanta din.

Duk yanda wani zai samu Daman sanin matsalar ciwon Haroon Saida Dad ya tabbatarda Bata fita ba hatta siddeeq Bai bari likitocin sun bari yasan duk wani abinda aka bincika aka Gano ba har suka sake kwana biyu a garin Akai sallamarsa a ranar suka kwasa zuwa Nasarawa Dan Kai gaisuwan Neman auren.
#MAMUH#*_Arewabooks@Mamuhgee_*
39
****Su babbah da suka samu labarin zuwan da Dad din zasuyi gaisuwa tini aka gyara koina hatta kofar gidansa Saida aka share har kofar gidan makota aka shirya tsaf Dan tarbonsu da Aminansa guda biyu da zasu tayasa karban gaisuwan.

Dayake ranar su Dad din zasu koma da wuri suka iso guraren karfe daya na Rana Dan haka su Babbah suka tarbesu da girmamawa da mutuntawa sosai har cikin fara isowan gidan babban suka zauna a babbar dadduman da aka shimfida musu me kyau.

Dad Lameenu Dayake amsa gaisuwansu cikin girmamawa da kulawa sosai Shima tareda farin ciki me tsananin da tin anan aka fara farin cikin Samun Sirikai irinsu da duk kudi da matsayinsu sunsan mutuncin mutane da iya mu'amalantarsu.

Babbah Dad Lameenu yayi kallan tsaf Mintina Yana tantance kamannin nasa da son tabbatarda idan shine Wanda yake tinanin shi dinne.

Ganin irin kallan da Alh Lameenu kewa Babbah ya sakashi sai farin ciki yake sake shiga Yana sake musu barka da zuwa kafin ya tambaya jikin Haroon cikin kulawa sosai Yana dorawa da cewa sai anjima su Abdul su shiga dubasa Inshallah.

Abinda ya tarasu suka shiga gabatarwa Babu wani Bata lokaci suka gabatar da kansu da Neman auren Ameenatou da suka zo nemawa dansu Haroon Wanda su Babbah sun sanshi kuma sunsan aikinsa da halayensa daidai gwargwado.

Naam su Babbah sukai kafin suka suka sake gabatar da kansu da shi babban amatsayin mahaifin Ameenatou wadda shine ya haifa abarsa da cikinsa Kuma yayi na'am da Hakan ya Kuma bawa Haroon aurenta.

Farin ciki da hamdala suka ringa miqawa ana sake taya juna murna Dad Lameenu ya cire kudin Neman auren Naira dubu dari biyar ya bayar kafin suka sake miqa godiyarsu har lokacin zuciyar lameenu wani tsalle takeyi cikin rudewa da rikicewa Dan kuwa ya sake tabbatarda Babbah ne suka tana Gani asibiti gurin Omar a lokacinda aka taba Kai masa attack idan Bai mantaba Kuma ya sake dubawa ya tabbata Babbah ne ya Gani Wlh.

Abdul da shine babban yayan Ameenatou Kuma dashi Akai zaman Neman auren Alh Lameenu ya kalla cikin kulawa Yana tambayarsa Aikinsa da karatunsa.

Cikin nutsuwa da ladabi Abdul din ya amsa masa matsayin karatunsa da aikin dayake yi.

Take Alh Lameenun ya nuna raayinsa na Taimkawa yace Abdul din ya hada takardunsa zai Aiko a karba a aika masa Lagos.

Godiya Abdul din yayi su Babbah dasu Alh sabi'u makocin Babbah godiya sukai suna sake nuna Jin dadinsu kafin su Dad suka saki jiki sosai sukai fira da maganganu dasu babban anan ma sukai sallah azahar kafin suka Shirin tafiya su Babbah suka rakosu har waje inda motocinsu da securities dinsu suke suka shiga take aka bar gurin dasu.

Suna barin gurin Dad Lameenu zufan dayake hadawa tin acan yana shanye abinsa a jikinsa ya zari tissue ya goge kafin ya Ciro wayarsa.

Hotunan da BB ya turo musu nasu babban ya Nemo hannuwansa na Dan rawa ya Nemo na Babbah ya zuba masa idanuwansa.

Mam da zuciyarsa kwata kwata Bata cikin dadi Baida energy din tambayar abinda yake faruwa sbd bayajin zai taba barin ya hada zuria dasu Babbah
Ya nema auren ne sbd yana buqatan Haroon din sbd ya Jamaal ya dawo garesa Amma Badan Hakan ba bayajin zai tana yadda ya Kai kansa Neman auren.

Lameenu Daya sake goge zufansa miqewa Mam wayar yayi Yana cewa

"Wannan shine fitilar da zata kaimu ga sanin duk inda dangin matar Omar suke sbd samun Magajinsa"

Kallan wayar Mam yayi kansa na tsananin sarawa da nauyi Amma Jin Abinda Lameenu ya fada ya sakashi cire hannunsa daga goshinsa Daya dafe idanuwansa a lumshe.

Kallan Lameenu din yayi bayan ya Kalli Babbah a wayar Yana jiran bayaninsa.

Cikin nutsuwa lameenu ya tinatar dashi ganin da sukaiwa Babbah a asibiti tareda Omar shekarun Baya.

A saninsu wancan lokacin daga kauyensu Omar yace musu babban yake Amma basusan Menene alaqarsa dashi ba Dan haka dole babba yasan waye yayan matar Omar Kuma bazasu rasa sanin komai ta hanyar Saba Daman a bagiren Neman ko mutum Daya daga kauyen suke amma tsawon shekaru ankasa samu.

Wani sanyayyan sanyi ne ya ciked zuciyar Mam take yaji nauyin zuciyarsa na rayuwa sedai bayajin zasu samu yanda suke so idan suna nesa dasu Babbah din.

Lameenu Dayasan dalilinsa Daman kenan na buqatan daukan Abdul aiki take ya Saka kira yace a tanadarwa Abdul din aiki me kyau da gidan zama a Lagos inda zai dauko iyayensa ya dawo dasu.

*********Su Babbah kuwa A nasa bangaren sunan jeden da Omar yake amfani dashi shine ya hanasa sanin shima Omar din seelahs ne Dan haka farin cikinsu kawai sukeyi.

Da daddare da kansa shi da su Abdul sukaje suka dubo Haroon din Wanda ya danne ya nuna musu karfin hali duk da Yana cikin tsananin tashin hankali da Tsaka me wuya sbd sanin Neman auren bashine aurenba indai Bai cika alkawarin Daya daukanwa Dad dinsaba,

Bayan tafiyarsu da daddare tsananta damuwansa tayi sbd gwara ace baa nema aure ba zai iya runawa ya hakura da Ameenatou Koda zai rasa ransa Dan kawai yabarsu su ta tsira Amma a yanzu da aka nema masa aurenta yasan ba janyewa sedai Kuma irin kaddarar fadila da Dan uwansa yake guje musu.

A cikin Daren siddeeq ya koma Abuja Bai kwana ba Saida ya samu report na komai da akaiwa Haroon ya turawa JEEY Wanda sakonsu ya isar masa a daren daidai lokacinda ya fito wanka daure da towel dinsa gabaki Daya jikinsa wata irin sheqi takeyi kaman Bai taba Shiga rana ba.

Hannunsa yakai ahankali ya dauki wayar Yana ganin report din ya Bude sakon Kai tsaye Yana karantawa.

Tsayar da fararen idanuwansa masu gigita Wanda suka kalla yayi akan report din idanuwan na sauya ahankali zuwa ja zuciyarsa na daukan wani nauyi take.

Shigowan kira ne ya sakashi rintse idanuwan ya budesu ahankali akan sunan Haroon daya bayyana kan screen din wayar.

Iska me dumi ya sake fitarwa daga bakinsa kafin ya daga Kiran batareda yace komaiba ya Dora wayar a kunnensa Wanda yayi daidai da Haroon din na kasa riqe kansa daga zubar da hawayen radadi da kuncin dayake cin zuciyarsa da rubabbiyar rayuwarsa gaba Daya.

Shiru Jamaal din yayi har lokacin Bai furta komaiba sbd wannan shine Karan farko da Dan uwansa ya bayyanar da tsananin kunci da baqin cikin rayuwar dayake ciki garesa,

Bai taba fada musu rayuwar wulaqanta da qasqantar dayakeyi a hannun su Dad ba,
Bai taba barin sun sani ba,
Bai taba nuna musu ba
Ya shanye komai ya hadiyewa kansa baqin ciki da radadin shi kadai Amma ayau dayake cikin tsananin hali ya kasa danne zuciyarsa daga Neman taimakon Dan uwansa Dan idan ya rasa Ameenatou zai iya rasa rayuwarsa gaba Daya batareda yasan rayuwar tasa tana cikin mummunan hadarin tsaka me wuyar da kowane lokaci komai zai iya faruwa ba.

Kasa magana JEEY yayi sbd sautin fitar kukan Dan uwansa dayake tarwatsa zuciyarsa Yana Kona jinin dayake yawo a jikinsa kawai kashe wayar yayi tareda Saka Kiran Siddeeq wadda Kiran na shiga ya daga cikeda girmamawa.

Magana yayi da siddeeq Yana gamawa ya kashe wayar gabaki dayanta tareda jefar da ita.

********Ameenatou gabaki Daya ta daga hankalin mutanen gidan sbd

kwanakin Haroon kusan shida bata samun wayarsa Kuma ya Dena fita koina ko Hafiz yace kwata kwata ya dena fitowa aiki,
Yaya Abdul yaje dubosa harso biyu Amma Sam Baya samunsa hakama siddeeq Sam baa samunsa.

Daga hankalinsu Babbah tayi dadah batada aiki saina rarrashinta Hafiz ma kusan sosai suka damu gurin aiki Amma dai Sir siddeeq yace musu Yana hutawa ne sbd rashin lfy da yayi.

Babbah da kansa yaje dubo Haroon din Amma dai kaman duka kwanakin Bai samu ganinsa ba hotel din sunce Yana Abuja.

Ranarda ya cika sati Hafiz na Isa gurin aiki da safe sunfara aiki kenan lafiyayyar sabuwar motar Haroon Daya sauya batareda sun saniba tayi parking bakin site din.

Siddeeq ne ya tuqo motar Dan haka shine ya fara fitowa kafin aka Bude Dayan bangaren Haroon ya fito sanye cikin black Armani's da sunglasses Daya masifar fitarda hasken fatarsa dayake wani irin kyallin Daya Saka dukkanin ma'aikatan gurin ajiye aikinsu suna kallansa sbd kwarjininsa na yau din daban yake Dan duk Wanda yake gurin saida kwarjininsa ya cika idanuwansa hakama hasken Daya Kara a kwanakin Dan hutun Daya samu ya bayyana fiyeda mamaki.

Manyan ma'aikatansu da sauran manyan Dake cikin project din tasowa sukai dukkaninsu suna tahowa gurinsa Dan ganin sauyi sosai a fuskansa na Babu sakewa ko kadan Dan Kuma kamewa.
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
40
Takowa yayi ahankali Yana nufar cikin site din Kai tsaye dukkanin sauran abokan aikin na biyo bayansa.

Siddeeq Dake gefensa umbrella yafara kokarin Bude masa Amma ya girgiza Kai ahankali batareda ya juyoba yana kallan site din da gaba Daya ma kusan aikin Daya bari bama ko kusa dashi ne ake kan yiba.

Hafiz Daya aje aikinsa Yana goge hannuwansa ya nufi ruwa ya wanke hannun zai nufi inda su Haroon din suke saiyaga sunzo sun wuce ya inda yake tsaye Yana murmushin Jin dadin ganin Haroon din da lafiyar Daya samu wadda ta sauya musu shi gabaki Daya Dan shi kansa Jin yayi gabansa Yana faduwa da ganinsa tsaban cika ido da wani irin sauyawan da yayi Dan har gashin kansa dayake kwance kaman na mace tsaban gyara ya sake sauya musu shi,

Wucesa sukai batareda Haroon ya Kalli inda yake ba sedai Dan gyada Kai da yakeyi a natse cikin wata irin class da kamewa idan sun gaidasa tareda masa barka da dawowa.

Dukkanin Wanda yake gurin kusan mamakinsu a bayyane yake Dan ganinsa sedai Kuma ganin hadda sauyin rashin sakewa a halayyan nasa ya Sakasu shiga taitayinsu harya shige tent din da Akai masa a site sbd aiki da meeting da sauran manyan Dake cikin project din.

Suna shiga sauran ma'aikatan suka tsaya waje shi Kuma da sauran suka shiga Kai tsaye kujeran zama siddeeq ya gyara masa Yana Bude takardun Dake zube a table din Yana dauko wasu Dake gefe Yana Bude masa Suma Yana fara yimasa bayani shi Kuma Yana bin takardun da idanuwansa dasuke

farare tas.

Dukkanin sauran Manyan Dake sauraron bayanin siddeeq dayake karantowa shiru sukai suna sauraron bayanin hakama hancinsu na shaqar iskan gurin Daya sauya gaba Daya da qamshin da suka tabbatarda daga jikin Haroon din yake fitowa Dan haka saiyi sukeyi suna kallansa gashi baice komaiba har lokacin sauraron bayaninsu yakeyi Daya bayan Daya kowa na gabatar da nasa bayanin Wanda yake tabbatarda Taron marasa amfanin da aka Tara ne ya Saka aikin duka ya lalace yaqi zuwa koina.

Sun dauki mintina masu yawa anata gabatar da sabbin bayanan Yana sauraronsu kafin suka gama yayi shiru tsawon lokaci kafin ya karbi takardun hannun siddeeq din Kai tsaye ya zuba su cikin takardun da basuda amfani kwata kwata kafin ya dago idanuwansa ya kallesu yace ya bawa kowa hutun kwana uku suje kawai Nan da 3 days za'a gabatar da sabon tsarin project din.

Shiru sukai tareda dagowa suka kallesa sedai Sabon Haroon seelah suke Gani a gabansu ba Wanda suka sani a Baya ba Dan haka cikin girmamawa suka amsa umarninsa suka fito Daya bayan Daya suna son juyawa su saci kallansa Amma ba dama sbd ba fuska hakama kwata kwata ba alaman wasa yakeyi a zancen.

Suna fita rufe idanuwansa yayi ahankali tareda budesu Yana Dan duba time din Tsadaddiyar Rolex din hannunsa kafin ya kalli siddeeq a taqaice yace

"A sanar da dukkanin sauran ma'aikatan da leburas 3days hutun da zaayi Ina buqatan kwanakin"

Cikin girmamawa da yar sakewa siddeeq yace

"Anan ma kana buqatan a tanadi sabon masaukin ne??

Girgiza Kai yayi sbd kwata kwata bazai iya zama anan din na Abuja zai koma daga can zai ringa zuwa.

Fitowa siddeeq yayi ya Tara duka ma'aikatan ya sanar musu hutun da aka samu na kwana uku take suka fara murna da farin ciki Dan haka suka fara hada ayyukansu Dan kammalawa su tafi gida.

Dawowa ciki siddeeq yake kokarin yi Hafiz ya karaso Yana murmushi da sakewa yace

"Oga siddeeq barka da Rana,

Kasan ko yau da safe Saida nayi Kiran wayar Barr Bata shiga Kuma kaima na kira taka itama Bata shiga ba"

Murmushi siddeeq ya sake Yana kallan Hafiz din yace

"Network ne da Kuma Kila sbd inda kan hanya,
Yasu Babbah da Dadah??

"Duk suna lafiya,mutuniyar dai ce Kam ta Hana tsoffin gidan zaman lafiya akan rashin Jin Barr"

Wani murmushin siddeeq ya sake Yana cewa

"Ai yanayin jikin nasa ne Amma inshallah ai yanzu yaji sauki ayyuka dai ne Kam gasunan sun tarar masa Amma dai nasan zai samu time din zuwa"

Suna cikin maganar ya fito daga ciki Yana Amsa waya a kunnensa cikin nutsuwa har lokacin sunglasses dinsa suna fuskansa.

Qamshinsa ne ya fara sauya iskan gurin Hafiz ya zubawa hannuwansa Dake riqe da wayar dayake amsawa cikin wani turancin da kwata kwata Baya gane kalma ko Daya Daya fada duk da Yana Jin turancin daidai gwargwado,
Yatsun hannuwansa da kaman Basu taba shiga Rana ko taba komai ba yake kalla cikin mamakin tayaya mutum zai sauya acikin kwanaki kalilan haka.

Akan fuskarsa dake wani irin kwarjini me kyau da Asalin kyau da Hutu ya zubawa idanuwansa hakama kunnuwansa na sauraron sautin muryansa Dake magana kamanma wani yaren daban yakejin turancin Dan haka Saiya samu kansa da kasa karasawa gurin Haroon din ya tsaya gurin siddeeq Dayake jansa da zancen harya jasa suka bar gurin Yana cewa su barsa yagama waya tukuna.

Waiwayowa kadan yayi ya sake Satan kallan Haroon din Yana tafiya zuciyarsa na shiga shakkar Anya basuyi gaggawan karban maganar auren Haroon akan Ameenatou ba sbd yafi karfinsu sosai da sosai duk Bai lura da Hakan ba sai yanzu dayake Jin Yama kasa kallan cikin idanuwansa tsabar cika masa nasa dayakeyi.

Fira siddeeq yajasa sosai suna tafiya har suka fice gaba Daya daga site din ya fada masa sunanan tafe daga Nan zasu taho gida.

Sallama sukai Hafiz ya wuce gida Kai tsaye Jin suna Nan tafe Dan yasan yau budurwan gidan zata barsu su huta da rigimar rashinsa ba kunya ba tsoron

Allah.

Yana wucewa siddeeq ya dawo har lokacin waya yakeyi sedai baima gama ba ya wuce ya nufi mota ya shige siddeeq ya shiga yaja suka bar gurin.

Budurwan Babbah Jin Haroon ya dawo farin cikine ya cike ranta Dan haka ranar ko islamiya qin zuwa tayi tai wanka ta shirya jiransa gashi har lokacin wayarsa Bata shiga Dan haka ta San bazai kwana ba Saiya taho ya ganta.

Su dadah ma Kwanciya hankalinsu yayi musamman Babbah da farko harya shiga damuwa Dan ya dauka rawa maganar auren take kokarin farawa shiyasa ma da Abdul aka kirasa Lagos maganar aikinsa dayaje Babbah ya Sakasa yayi masa bincike sosai akan Seelahs din Kuma suka samu yabo a gurin mutane da Dan abinda aka sani akansu Dan haka yaji ya sake samun nutsuwa da auren kodan yanda Ameenatou ya kwallafa son Haroon din a ranta.

A ranar Dasu Dad suka koma a washe gari aka buqaci zuwan Abdul Wanda hatta ticket din jirgi Siya masa Akai daga Abuja yabi jirgi zuwa Lagos acan ma cikin mutuntawa da girmamawa aka aika mota ta daukosa daga airport bar masaukinsa saida ya kwana ya wuni ya huta da kyau aka Kaisa SEELAHs CPN acan dinma Koda ya Isa anriga an samar da aikinsa Wanda zai fara a matsayin sabon secretary din Alh Lameenu na musamman.

Yayi godiya yayi farin ciki sosai hakama ya yaba Dan kuwa table dinsa ko a bankin da yayi aikin security sai manager ne yakeda irinsa.

Bai gama shiga shock da sabon farin ciki ba Saida aka basa gurin zaman da zai tattaro iyayensa ya dawo dasu sbd karatun Ameenatou da zata fara a Lagos din da Kuma saukin sha'anin aurenta.

Sosai ya Nuna farin cikinsa da yabawa tareda alkawarin yin duk iya kokarinsa da ladabinsa akan aikin harma da girmamawan gaske.

Saida ya Kara kwana biyu a Lagos din kafin ya dawo tukuna daga baya yayi Shirin komawa su Babbah sai daga baya zasu bisa.

Duk tsananin qiyayyar da sunan Lagos da Babbah Baya ko kaunar a fada hakanan ya danne a cikin ransa ya boye sbd farin cikin Ameenatoun Dake murna sosai akan karatunta da Kuma zama da zatai kusa da Haroon Koda yabar Nasarawan.

Ita kanta Dadah dayake sun Dade da dannewa da rufe Babin Omar gaba Daya kwata kwata rayuwarsu Bata nuna komaiba Dan 'yarsu dai tayi girman da zasu iya Bata kariya daga kowa barshi uban nata da basusan ma Yana raye ko mace ba.

**Har yamma Haroon din Baizoba Dan haka Ameenatou tafara Bata fuska tana shiga fushi musamman da yaqi kiranta bayan Hafiz ya tabbatar mata Daya dawo.

Shigewanta tayi daki taqi fitowa kwata kwata a dakin take komai har dare tana fushi Babbah nata aikin rarrashi da Dadah.

Hafiz dai baima da lokacinda harkokin gabansa yakeyi sbd alamu sun nuna Haroon din ya sauya Kila sbd ciwon da yayi da Kuma Maida hankalinsa dayakeson yayi akan gaggawan kawo sauyi da mafita akan illar data rusa aikinsu gaba Daya.

Washe gari da safe tana tashi kashe wayarta tayi gaba Daya sbd ko Haroon din ya kira karya samu

Fitowa tayi sanye da doguwar rigar atampar A shape data zauna daidai jikinta hula data kasa rufe cikakkiyar gashinta me tsayi ce akanta tana son kunna wayar Amma tana Hana kanta.

Gurin Dadah ta nufa tace

"Dadah kisa Yaya Hafiz ya kaini gurin wanke kan fa ni kitso nakeso zafin kaina nakeji sosa"

Dadah datasan a fushi Ameenatoun take cikin kulawa da lallabawa ta kalleta tana gyara mata zaman hular kanta yanda ta sake mata kyau duk da gashin Bai rufe duka ba Yana daure a cikin hulan tace

"Dauko wayata na kirasa yazo yakaiki yanzun Nan"

Juyawa tayi ta nufi dakin dadahn ta dauko wayar ta fito ta Bata tana sake narke fuska kadan take Jira ta fara Hawaye.
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*

Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
41
Numbern Hafiz dadah ta Nemo a cikin wayarta ta Saka Kiransa
Ringing biyu ya daga waya Kai tsaye ta sanar masa yazo yakai Ameenatou gurin wankin kai.

Bata fuska yayi zai fara fada ta katse wayar bayan tace masa Maza kazo Ina jiranka kar yamma tayi.

Jin alamun Hafiz ya shaqa ya Saka Ameenatou dariyar da tin jiya taqi yi musu a gidan duk sbd fushin rashin zuwan Haroon din.

Ganin dariyarya ya Saka dadah farin cikin ta saki murmushi tana girgiza kan yanda fadansu da shiryawansu a a tare yake tafiya basa iya zama basuyi fada ba hakama basa iya zama a fadan Basu shiryaba.

Qin dawowa a lokacin Hafiz din yayi Saida ya gama abinda yakeyi ya dawo gidan Kai tsaye wanka yayi Yana fitowa Saida yayi sallan laasar kafin yace ya

fito su tafi.

Yaya Abdul ne ya bawa Hafiz din kudin suka fice tana kokarin kunnasa da cewa turarensa qamshin rub yakeyi ba kamshi ba.

Dakatawa yaso yayi yace yafasa Kaita Ashe Yaya Abdul na bayansu zai fita yace

"Yi hakuri kyaleta idan kun dawo ka fasa bakin rashin kunyar kafin Babbah ya dawo"

Cikin Naam da Hakan ya wuce gaba Yana cewa

"Tarata nakeyi duk ranarda nayi cikakkiyar lokacinki zan nuna Miki ni ba abokin reninki bane."

Yaya Abdul da yayi magana tana narke fuska zatai magana yace

"wuce ki bisa Dan idan ya tafi wlh Babu inda zan kaiki inda gurin zuwa"

Bayan Hafiz din tabi ta cimmasa suka fito gidan Yana cewa karta kuskura ta nuna masa reni a waje.

Cewa tayi ta yadda sbd itama tana tsoron yakaita gurin gyaran kan ya tafiyarsa yabarta.

Take suka kama wata firar suna mantawa da fada suka fito gida sunayi Yana Bata labarin sauyawan da Haroon yai ita Kuma tace ya Dena mata maganarsa fushi takeyi dashi Kuma duk ya sake kwana Baizo ya ganta ba ko ya kirata cewa zatayi ta fasa auren karatu zatayi.

Murmushin takaici ya sake Yana harararta sbd yasan yanda take son Haroon din fada kawai tayi bazata iya dinba duk da Shima Haroon din son dayake mata yafi Wanda take masa shiyasa yake mamakin abinda yasaka Yaki kiranta tinda ya fara rashin lafiyan Kuma yaqi zuwa gidan duk da ya dawo din Amma shi Yana masa uzurin tarin aikin dayake gabansa Mai tsananin mahimmanci ne kawai ya Saka Hakan.

Suna Isa gurin wankin kan ta shiga shikuma yace zaije ya dawo abinda bataso kenan Amma haka ya tafiyarsa yabarta Amma Saida ya Bada kudin ruwa da wani abin ci ko Sha idan ta buqata kafin a gama tukuna ya wuce din.

Dayake sun Saba da me saloon din ana kawo Ameenatou din tin tana yar budurwan yarinyarta harta kawo yanzu Dan haka tafara kokarin tambayarta

Ina su dadah da Babbah harma da yayanta Abdul me kame fuska ba sakewa.

Murmushinta me kyau kawai tayi sbd da yawan lokuta batada sakewa da mutane sbd tsananin taka tsantsan da ake Bata da kulawa Bata wani yadda da mutane sosai.

Fira take mata tana mata wankin kan Wanda duk taji surutun ya isheta suna gamawa wankin kan kafin ayi drying kan ta kira Hafiz tace ya dawo ankusa gamawa.

Har aka gama aka daure kan tsakiyar kanta tareda goge fuskanta ta gyara ta fito fes kyakkyawar budurwanta me daukan ido da hankali ta zauna jiran Hafiz din Wanda sai kusan 6 ya iso ya biya ta fito suka wuce tana narke masa fuskan Baizo da wuri ba saita fadawa Babbah baida aiki sai yawon fira gurin Yan matan da babu me kyau bare maana.

So yayi ya buge bakinta Amma sbd suna hanya ya danne zuciyarsa Yana harararta ta saki dariya me sanyi tana cewa

"Akwai wadda takeda kyau ne? bare kace karya nayi Maka ko sharri nai musu"

Shiru yayi mata yana jiran su Isa gida yaga ubanda zai hanasa yimata duka ayau dinnan.

Dariya taci gaba dayi masa kasa kasa tana jiran su Isa gida ta shige da gudu Dan tasan a cike yake suna Isa Saiya daki bakinta idan ba Babbah ko dadah suka ceceta ba.

Gap da magrib suka iso gidan tana Ganin sun kusa Isa kofar gidan tace

"Yaya Hafiz naga Kanata kumbura nidai kayi hakuri to Karka tabani tinda kaga oganka fa yake sona Kuma kana tabani zai iya baka aikin wahala a gurin aiki ka.....

Kafin ya qarasa ya daga hannu zai buge bakinta sbd sun kawo gap da kofar gidan Dan haka tayi gaba da gudu ya shige gidan daidai fitowansa daga cikin gidan Da gaba Daya ya sauya iskan gidan da qamshinsa Daya sakata saurin dakatawa sbd kirjinsu Daya Hadu sbd baisan da shigowan kowaba kaman yanda itama data zo da gudun batasan da tahowansaba.

Cak ta tsaya gabansa tareda dago fararen idanuwanta ta zuba masa sauran murmushin dayake kan fuskanta data shigo dashi Bai qarasa bacewaba ta tsayar da idanuwanta akan fuskar Data Saka kirjinta mummunan bugawa

hakama bugun zuciyarta qaruwa yayi tana kasa motsawa hakama tinaninta tsayawa yayi cak.

Kafin tayi Baya shine yafara Baya alokacinda kirjinsu ya Hadu batareda ya dago ya Kalli fuskartaba a cikin wani fitinanniyar nutsatsiyar murya me sanyi da kamalan Dake hade da kamewa yace

"Sorry" Yana rabata ya wuce batareda yako kalletaba bare sanin itace Ameenatou din.

Kasa motsawa tayi daga inda take tsaye harya fice daga cikin gidan yabarta da qamshin turarensa Daya cika hancinta Yana toshe kanta daga tinanin komai bayan na mamaki.

Hafiz ma dayayi kusan mutuwar tsaye daga abinda ya Gani din ya faru kasa motsawa yayi Saida siddeeq ya fito daga cikin gida Yana yiwa dadah saida safe daukeda basket din abincin da aka Saba kaiwa Haroon yagansu tsaye baisan meya faru ba Dan Bai dauka sun Hadu ba sbd saurin dayake son suyi Subar gidan kenan kada Ameenatou ta dawo su hade sbd Yasan waye JEEY idan zai iya komai har abada bazai iya kallan wata macenba Koda ba Sonta yakeyiba da sunan sake mata.

Ganin Ameenatou da Hafiz Basu ce komaiba ya Sakasa silalewa ya fice.

Ameenatou kasa motsawa tayi sbd duk da Babu haske sosai magrib tayi tana ita tantance sauyin Haroon dinta Koda ta iskan Daya bar mata tana shaqa ne da qamshinsa yake daban da dukkanin abinda hancinta ya taba shakar mata.

Hafiz dayaji ana kokarin tada sallah wucewa yayi ciki Yana cewa

"Ki wuce ciki naje nayi sallah na dawo mu Dora inda muka tsaya"

Daga kafarta Daya tayi datai mata sanyi tayi tana wucewa ciki bugun zuciyarta har lokacin Bai dawo daidaiba,batama tantance Menene ya faru ba mintinan da suka wuce,
Haroon dinta ne a gabanta ko kuwa sabon Haroon aka sauya mata a duniyarsa Babu abinda yake masa kyau da kasa Dena kalla idan ba itaba.

Tana shigowa cikin walwala dadah ta kalleta tana cewa

"Yanzu Haroon ya fita sedai baima zaunaba gaisawa kawai mukai siddeeq yace Abuja zasu koma da Daren Nan acan ya zasu kwana"

Hafiz Dake alwala Bai juyoba yace

"Mun Hadu zai fita Amma dai inaga kaman Bai gama warwarewaba Dan baima ganemu ba a duhun duk da Babu wani duhun"

Ameenatou data kasa magana har lokacin sai Daya gama maganarsa ta Bude Baki tana kallan Dadah da idanuwanta da suka sauya tace

"Kaina ciwo yakeyi Dadah aban magani"

Kallanta Hafiz yayi Yana ficewa tafiya sallah,
Dadah kuwa wayar hannunta ta karban mata tana cewa

"Kiyi alwala tukuna idan kin Sallah kunci abinci be Dena ba sai asha maganin"

Gyada Kai kawai tayi ta wuce tana Dora tana kirjinta dayake buga mata ba daidaiba Bata taba Jin Hakan ba sai tsoro ma yake Neman kamata inde na zuciyarta ta samu matsala bane aikuwa bara Babbah ya dawo.

*******Daga kofar gidan Kai tsaye Abuja suka nufa siddeeq ne Mai tuka motar shikuma Yana waya da mum dinsa wadda yake magana da ita a natse cikin Kwanciyar hankali Babu hayaniya bare daga murya ko sauri,

Kaman yanda yake komai a natse haka yake wayoyinsa a tsanake da aji.

Suna Isa Kai tsaye lafiyayyar gidan da aka kama masa aka sauya mata komai zuwa yanda zai iya rayuwa a cikinta kaman Yana Poland haka Akai mata siddeeq ya nufa dashi ga securities sosai a anguwan Amma dai shi Babu Wanda ya dauka Dan qasar ne sbd yanayinsa Dan kamanninsa tareda irin tsarin rayuwar dayake gudanarwa.

Sama da qasa ne Dan haka Kai tsaye sama ya wuce siddeeq Kuma bedroom dinsa aqasa yake.

Yana shiga bedroom dinsa wayarsa ya ajiye tareda id card na Haroon dayake jikinsa ya kwabe kayan jikinsa dagashi sai wani tsadaddiyar underwear Dake jikinsa ya nufi toilet Yana shafa gashin kansa me tsayin gaske Daya Yanke sbd Haroon.

Wanka yayo kusan mintina masu Dan tsayi kafin ya fito dauresa towel dinsa datake Neman zamewa ta Fadi fatan jikinsa fresh sai kyalli takeyi ya nufi mirror Yana kokarin miqa hannunsa kan body oil dinsa wayar Haroon Dake kunne gefen tasa kira ya shigo cikinta Wanda ya sakashi dakatawa daga

abinda zai dauka Yana kallan sunan sake rubuce kan screen din da manyan letters 'DAD'

idanuwansa ya dauke daga sunan Yana qin daga Kiran Kai tsaye har Saida ta tsinke Kiran ya sake shigowa daidai lokacinda ya ajiye towel Dake hannunsa qarami yayi receiving call din Wanda Dad Bai tsaya komaiba yace

"Haroon Ina buqatan ganinka a Lagos gobe kome kakeyi ka ajesa ka biyo flight"

Bai tsaya Jin amsar Haroon din ba bare tambayar jikinsa ya kashe wayarsa.

Wayar JAMAAL ya zubawa idanuwansa da suka sauya take kafin ya saki wani mayen numfashi a natse.
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
42
Kayan baccin Avves masu santsi da tsadan gaske ya Saka sedai baima rufe gaban riganba ya fito lafaffiyar cikinsa dake fidda murdewan jikinsa sbd motsa jiki ya sauko kasa sbd Yana buqatan ruwa da drinks sbd aikin da zai kwana yanayi sallah Kuma Daman kafin su baro Nasarawa sunyi ishai ma kafin su shigo gidan sunyi.

Siddeeq ma tini yayi wanka ya shirya cikin gajerun kayan baccin da sukaiwa jikinsa kyau Shima Dan Shima Yana motsa jikinsa sosai Dan hakane ma yafi Haroon budaddiyar jiki kaman ubangidansa.

Shima fitowansa kenan yaji saukowan JEEY da kamshinsa Dan haka ya dakata harsaida ya sauko kallo Daya yayi masa ya dauke idanuwansa sbd JEEY SEELAH ko namiji Dan uwansa yake kallansa zai iya kamuwa da sonsa bare mata Danma Baya mu'amalantar inda mata suka yawaita da baasan irin matan dazai samu masu jiransa ba, har mamakin yanda JEEY din ya kamu da son fadila yakeyi da yanda zuciyarsa take riqe da iya ita kadai yakeyi.

Ruwa Jamaal din ya buqata da E-Bull energy drink dinsa.

Daukowa siddeeq yayi ya kawo masa ya ajiye a gefe hakama already tarin manyan takardun abinda zasuyi suna gurin zube.

Kafin ya fara aikin bayan ya zauna dago fararen idanuwansa yayi ya Kalli siddeeq ya Bude Baki a natse yace

"Zamu bi morning flight zuwa Lagos ka duba mana idan akwai"

Dagowa siddeeq yayi ya Kalli JAMAAL din cikin mamakin ta yanda zasu fuskanci juna da Dad dinsa batareda ya gane shi bane,
Hakama shi kansa Jamaal bazai iya kwantar musu da Kai ba komai tsanani kaman yanda Haroon kansa bayama dagowa a gabansu saita Baci.

Cikin nutsuwa da tinani siddeeq ya sake kallansa Yana cewa

"Dr ko zan kira Dad din na sanar masa wani uzurin dazai daga tafiyar gobe zuwa jibi idan Barr da Mum din sun iso"

Girgiza Kai yayi a natse Yana cewa

"Ba buqatan Hakan,zangansa da kaina"

Sake shiga fargaba Siddeeq yayi duk da yasan idan Jamaal din ya fada ta zauna Amma a gaban Dad Kam Abu ne me wuyan gaske idan baa take zai sheda Jamaal ne gabansa ba ba Haroon dinba ko daga kamshinsa da Baya boyewa kowa da Kuma fatansa data banbanta data Haroon duk da idan suna rarrabe baka ganesu Se Wanda yayi da gaske gaske idanma kayi musu farin sani kenan hakama izzar Jamaal har abada ba Daya take data Haroon dinba.,
Tayaya Jamaal zai iya tsayuwa a gaban Dad dinsa batareda yayi masa kallan dazai Saka Dad din take Ji ajikinsa Jamaal ne.

Jamaal Daya miqa hannunsa a natse ya dauki drink din gefensa ya Bude yakai bakinsa yasha kusan Rabi ajiyewa yayi Yana Bude laptop din Dake gabansa ya kunna kafin ya fara janyo takardun Yana budewa tareda jerawa a gabansa sbd acikin kankanin lokacinda bazai ci masa time din komawa rayuwarsa ba yakeson kammala dukkanin aikin project din sabo da zaiwa Dan uwansa ya tattara ya koma bama tareda wani yasan ya shigo qasar ya fice ba.

Shima siddeeq tattara hankalinsa yayi sbd nutsuwa ga aikin da Jamaal zasuyi.

Nutsuwa yayi sosai Yana aikin cikin kwarewa da tabbatarda komai ya tafi daidai,Shima siddeeq mayarda hankali yana Wanda zaiyi a cikin aikin.

Har kusan hudu saura na guraren asuba suna aikin kafin suka ajiye suka nufi dakunansu.

Jamaal na shiga bedroom dinsa Kai tsaye toilet ya nufa yayo alwala ya fito ya Dora gatuwar jacket akan kayan jikinsa na bacci ya rufe batiran rigarsa Dake Bude ya Saka qaramar hulan sallah fara akansa ya tayarda sallan nafila.

Yana gama sallolin nafilansa ya miqe Dan sallahn asuba da Akai kira har ana kokarin tayarwa daga masallatan nesa Dayake jiyowa.

Bayan gama adhkar da adduoinsa miqewa yayi ya cire hulan da jacket din ya nufi gadonsa ya haye tareda kashe komai tin daga kan wayoyinsu da wutan dakin ya shige bargo a nitse Yana lumshe idanuwansa.

Bacci sosai yayi ya samu hutun jikinsa Dana kansa harma Dana zuciya kafin ya tashi guraren 10 da wani abu.

Toilet ya nufa Kai tsaye yayi brush da sauransu tukuna yayo wanka ya fito daure da towel ya nufi inda wayoyinsa suke ya miqa hannu ya kunnasu kafin

ya wuce gaban mirror Dan shiryawa.

Bai wani dauki time ba ya shirya ya fito cikin Ash kaftan din Tsadaddiyar yadin cashmere data tsananin sake sauya kamanninsa zuwa wani bakon baturen bahaushe hakama hulan Daya Saka ya rufe gashinsa Daya sake banbantasa Dana Haroon ta qara masa kyau sosai.

A Karan farko rayuwarsa dayayi amfani da wani turaren daba nasa ba Dan haka yakejin Baya wani Jin dadin iskan Daya bayarwa a jikinsa duk da Wanda yayi amfanin dashi Shima mugun designer ne sedai qamshinsa Daya Saba dashi daban yake a gurinsa.

Siddeeq da tini yayi musu booking tickets din 12 Dan haka Shima ya shirya tsaf cikin kaftans din Shima sai Jakar takardun aikinsu Dan laptop din dasuke hannunsa.

Jamaal na saukowa cikin girmamawa ya masa barka da saukowa kafin ya biyosa suka fito tare Jamaal din suna magana.

Siddeeq ne me tuqin Dan Jamaal Kam bayajin zaiyi tuqi harya gama ya tafiyarsa inda ya fito.

Kai tsaye office din dazai fara gabatar da aikin anan Abuja ya nufa ya zauna dasu ya gabatar musu da sauyin aikin dayayi tareda sababbin plans din dasuka matiqar Basu mamaki da sakasu farin ciki me tsananin gaske Dan kuwa tini suka fara Shirin gabatar da takardun soke aikin kwata kwata tareda raba hannunsu Dana Seelahs,

Hannu suka miqa masa cikin Jin dadi tareda taya junansu murnan sake samun damar aiki a tare Shima hannun ya miqa musu Yana sake gabatar da kansa BARR HAROON SEELAH.

Cikin farin ciki suka sake amsar tayin aiki da juna take akai hotuna da sabon Saka hannu akan new project din dazai maye wancan.

Sai guraren 11:20 suka baro Kai tsaye daga Nan office din airport suka nufa suna Isa suka ajiye motar anan airport suka shige jirgi sbd sunma iso kusan late.

A cikin jirgin yayi breakfast dinsa hankinsa kwance da nutsuwa sabanin siddeeq Daya kasa samun nutsuwa ko Kwanciyar hankalin sbd abinda zai iya faruwa idan aka samu matsalan Dad suka gane.

Suna sauka Lagos drivern Dad dinne yazo airport daukansu sbd shi Jamaal

din da kansa Daya turawa Dad text din azo a daukesa daga airport Nan da awanni.

Da farko kaman Bai gane ba Saida ya sake karantawa ya tabbatarda Haroon dinne yayi masa sakon A tura driver ya daukosa daga airport.

Numfashi ya sauke ahankali Yana jinjina lallai Haroon din yafara samun karfin zuciya tinda ya iya masa sakon Kai tsayen Nan Mai kama Dana Bada order.

Driver na Isa airport Kai tsaye siddeeq ne ya budewa Jamaal kofa ya shige bayan kafin Shima ya zagayo ya shiga gaban motar driver Dake Satan kallan Jamaal din ta mirror cikin girmamawa yace

"Barka da dawowa Sir Haroon"

Gyada masa Kai kawai Jamaal yayi sbd hankalinsa na kan sakwannin asibitin Haroon da aka turo na can Poland Yana karantawa.

Suna isowa mansion din Jamaal ya hadiye wani abu Daya danne maqoshinsa Yana kashe wayarsa gaba idanuwansa na Neman sauyawa Amma ya Hana hakan sbd dawowa ko shigowa mansion din seelahs wani abune dabai taba tinanin zai sake ba har abada idan ba yanzu da Dan uwansa Dake tsananin buqatansa ba.

Sedai abinda Basu saniba shine kaman yanda yayi alkawarin duk ranar Daya Sako kafarsa ya dawo musu Saiya tabbatarda sun rasa komai to tabbas tinda ya Sako kafarsa ayau din ya dawo Saiya gyara musu komai sbd Haroon kafin suna kallo ya rabasu da komai daga ranar Daya tabbatarda Haroon ya mallaki macen dayake so fiyeda komai ayanzu.

Kai tsaye bangaren Haroon ya nufa Yana amsa sannu da zuwan da securities din gidan ke masa cikin tsananin girmamawa da mamaki me girma na sauyin Haroon din.

Yana shiga palon Haroon Kai tsaye bedroom dinsa ya wuce ya shige toilet alwala yayi ya fito yayi Sallah Yana idarwa wayar Dad na shigowa wayar Dake gefensa.

Kallan wayar yayi tareda dagawa cikin nutsuwa yayiwa Dad din gaisuwan Data Saka kirjinsa mummunan bugawa Saida yayi shiru ya sake sauraron muryan da kyau yaji sai yaji Yana Neman rudewa sai kawai yayi Watsi da abinda yaji Kai tsaye ya Bude Baki yace

"Ka sameni yanzu a office din cikin mansion din."

"Ok" kadai Jamaal yace tareda rigan Dad kashe wayan Wanda ya sake Saka Dad din mamakin halayen da Haroon ya fara sauyawa.

Saida yaci abincin da siddeeq yayi masa ordernsa daga tsadaddiyar restaurant ya koshi kafin ya shirya ya fito tareda siddeeq Wanda shine yake nuna masa hanyar da office din yake tinda Bai saniba.

Suna kaiwa kofar office din siddeeq ya tsaya daga waje Jamaal Kuma Kai tsaye ya Bude kofar a natse zai shiga sako ya shigo wayar Haroon Dake hannunsa Kuma Kai tsaye yasan Haroon dinne Dan haka ya dakata tareda duba sakon Daya bayyana akan screen din wayar inda ya rubutu masa tini tareda rokonsa akan yayi masa alkawarin ganin aurensa da Ameenatou ya tabbata kaman yanda tin farko yayi masa wannan alkawarin zai tabbatarda shi din Bai rasa macen da itace farin cikinsa ba kaman yanda shi Bai samu tasa farin cikin ba.
Lumshe fararen idanuwansa yayi da suka fara sauyawa Yana sake Tina alkawarin da yayiwa Haroon din zai tabbatarda su Dad da hannunsu sun aura masa Ameenatou kafin yabar kasar idan har auren Bai tabbataba to Allah ne yayi su din ba ma'auratan bane Kokuma Idan dayansu Baya raye wannan shine abinda mum dinsu ta roka daga Jamaal din sbd bazata so Shima Haroon dinta ya dandani irin radadin da Jamaal ke cikinsa haryanxu ba na Rasa Macen da ita kadai ya bawa zuciyarsa.

Numfashi me sanyi ya sauke ahankali mara sauti kafin Kai tsaye ya shiga batareda knocking ba kaman yanda Haroon yakeyi kafin shigan.

Yana shigowa Dad Lameenu dayake facing kofar ne ya zuba masa idanuwansa Yana kallo cikin Dan mamaki kafin Shima Dad din ya dago Yana kallansa Dan dukkanin idanuwansa mamakinsa a bayyane,

Dad Lameenu Daya rasa abin fada cikin yar rikicewa yace

"Da Jamaal Yana kasar Nan da babu abinda zai hanani tinanin shine a gabanmu,
Haroon hankalinka kuwa kake mayarwa akan aikin gabanka kokuwa gyaran fata ka mayarda hankali Akai sbd mace??

Dad da har lokacin idanuwansa na kan Jamaal din Yana Jin zuciyarsa na kokarin dawo masa da kewan Jamaal da tsananin buqatansa dayakeyi Kuma sai zuciyar ke Jin kaman ta samu Jamaal a gabansa Amma Kuma yasan abune da bazai taba yiyuwaba Dan Koda Jamaal Yana Nigeria ya shigo bazai taba Sako kafarsa SEELAHs ba Dan haka duk yanda idanuwansa ke nuna masa

kaman Jamaal ne gabansa bazai yiyuba Dan haka ya dauke idanuwansa daga Jamaal din Yana sauke numfashi ahankali Shima Jamaal din sai alokacin ya ya dago ya zuba musu idanuwansa da suka sauya sosai sedai Bai furta komai ba Dan maganarsa a lokacin zata bayyanarda radadin ganinsu kawai Dake cin zuciyarsa Dan haka ya zabi yin shiru kaman yanda Haroon keyi a gabansu.
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*

A cikin murya me nutsuwa Kai tsaye ya gaidasu Dad din acikin jam'i batareda ya Bada amsar maganarda Dad Lameenu ya jefesa da ita ba ta farko.

Dayake dukkaninsu kowa da abinda yake bakinsa na maganar Dake cinsu Basu tantance sauyin muryanba Wanda Daman Shima Haroon idan jikinsa na

Sanyaye muryansa a natse da sanyi take fita Dan haka Babu Wanda ya tsaya amsa gaisuwan bare tambayar ya jikinsa Kai tsaye Dad dayaji Baya iya kallansa Dan yau din cika masa ido Haroon keyi sbd kamanninsa da Jamaal sun tsananta ayau dayake ganinsa kaman Jamaal Dan haka batareda y kallesa ba murya a daure da bacin ran abinda yayi yace

"Ko zaka bani dalilanka Daya Saka bawa project dinmu da ma'aikatan aikinsa Hutu harna kwana uku batareda sanar damu meyake faruwa ba??

Numfashi me sanyi ya sauke Yana dauke idanuwansa daga kallansu kafin ya Tako ahankali dukkaninsu sukai saurin kallansa ganin ya tinkarosu Yana kallansu Dad Lameenu ne yayi saurin cewa

"Amsar abinda yake faruwa muke buqatan Dani sbd Haroon Banga alamar zaka cika alkawarin daka dauka ba na sakamu alfahari dakai,
Aikin Nan fa duka duka sauran sati uku ne a time dinsa ya cika,.

Dad kallansa ya sake yi Yana Jin zuciyarsa na son shiga tinani daban daban Amma ya watsar Yana cewa

"Karka manta nutsuwanka akan aikin Nan shine tabbatan aurenka Dan Neman aure ba shine aurenba Karka manta da Hakan Dan nakai maquran rashin nutsuwan Nan taka,

A Hakan kake Neman mutuwa sbd mace kanason kayi aure batareda kasan ciwon kanka ba bare tinanin tsayuwa ka zama abin alfahari ga iyayenka ba tayaya zaka tsayu ka zama abinda matarka ko yayanka zasuyi alfahi dashi....

Dakatawa Jamaal yayi daga inda yake tsaye tareda dago idanuwansa da sukai ja ya Kalli Dad din dashi ma shi ya Dan kalla Yana cewa

"Yes, Haroon haryanxu ka kasa sakani farin cikin Da kowannen Uba yake shiga akan yayansa da alfahari dasu,
Alkawari nayi Maka akan idan kasakani farin ciki akan wannan aikin zan nema Maka auren da kakeso Amma.....

Katsesa Jamaal yayi Dan bazai iya tsayawa sauraron wainnan maganganun akan Dan uwansa ba komai zai iya faruwa Dan zai iya bayyanarda kansa Dan haka wayarsa ya daga ya kira siddeeq take siddeeq ya shigo da takardun komai dasuka gama a yau din ya karba daga hannun siddeeq ya ajiye gaban Dad din Yana kallansa yace

"Gashinan Alkawarin zan cika Maka acikin kwanakin da bazasu kai na cikan kwanakin ba Amma Kuma a ranar da komai ya tabbata a yanda kakesonsa a

ranar nakeson a daura mun auren da yarinyar....."

Daga dad har Dad Lameenu sakin Baki suke kokarin yi gurin kallansa da mamaki hankalinsu na rabuwa biyu daga abinda ya fada da Kuma karanta takardun Daya zuba a gabansu suna karantawa cikin tsananin mamakin sabuwar project din data dawo musu Da cikakkiyar damansu a hannunsu.

Dad Lameenu Daya kasa Kai karshen takardan cikin farin cikinsa Daya mantar dashi mamakin dasuka shiga yace

"Nayi Maka alkawarin daura Maka auren Ameenatou a washe garin ranar da Akai bikin Budewa duniya wannan aikin project dinnan Haroon idan abinda nake Gani da suna SEELAHs a jikin takardan Nan ya bayyana.

Dad ma mamakin ne yayi mugun kashesa kafin idanuwansa su sauka kan signature din jamaal Dake karshe wayarsa tayi ringing daga turawansu na Abujan ne Yana dauke idonsa Akai siddeeq ya matso Yana rufe file din tareda amsar masa cikin girmamawa Dan basa Daman amsa wayan wadda ta Saka Dad Lameenu washe dukkanin bakinsa cikin tsananin farin ciki Yana sake tabbatarwa da Haroon zuwa wani sati zai tabbatarda Abdul yayo parking da familynsa sun iso Lagos din gaba Daya.

Wayar da Dad keyi ta sakashi Shima dukkanin farin cikinsa bayyana Yana washe Baki Yana wayar cikin turanci Dan nutsuwa Yana Kuma Basu tabbacin wannan Karan Inshallah komai zai tafi daidai Nan da 3 zuwa 4 weeks komai ya zama cikin Shirin bikin qaddamarwa.

Dad na gama wayar Haroon din ya kalla cikeda farin ciki yace

"For the first time da yau nake alfahari dakai Son"

Kalman zafafa zuciyar JAMAAL tayi Dan haka baice komaiba sai sake fuska da yayi ya amshi zancen Dan kawai da zargi.

Buga kofar Akai kafin aka Bude tareda shigowa
 BB ne Wanda duk kwakwalwansa take Neman Juyewa sbd ba dare ba Rana a bincike da yawon garuruwa suke da kauyuka gurin Neman da haryanxu Babu me baccin arziki akansa tsakanin shi dasu Mam din.

Tinda yake a rayuwansa wannan shine aiki mafi wahalan dayakesha mara sauko ko kadan a duk shekarun Nan,
Shi kansa sbd baqar wahalan dasuke Sha a wannan aikin yakejin bazai taba samun nutsuwa ko Kwanciyar hankali ba matiqar ba Gano abinda suke Neman sukaiba kaman yanda yasan har abada uwayen gidan nasa bazasu

taba samun baccin nutsuwa da Kwanciyar hankali ba idan ba burinsu na shekarun cika yayi ba.

Cikin girmamawa yace

"Sir Haroon barka da dawowa"

Batareda Jamaal ya amsa ba Dad Lameenu ya Kalli siddeeq Wanda Shima Kai tsaye ya juya daga office din ya fice tareda Turo musu kofar.

iPad din hannunsa ya ajiye gabansu tareda bayanan daya samo akan bincikensu ya fara da cewa

"Ranka ya Dade na samu tabbacin 'yayan matar sir Omar Daya gudu da abinda ta haifa a daren yanada nasa 'yayan guda biyu Kuma dukkaninsu Maza ne sedai Kuma matarsa an bani tabbacin kafin barinsu gombe a wancan lokacin ta haihu Wanda nakeda tabbacin ba haihuwa tayi ba babyn sir Omar dinne"

Cikin zaquwa Dad Lameenu yace

"Bayanin inda suke shine babban abinda muke buqatan Jin idan an samo"

Hakama Menene asalin abinda aka haifa din?
Mace ne ko namiji??
Hakurina da bugawan zuciya akan wannan lamarin ya kusa kamani BB a gaggauta samo mana inda suke sbd tashin aikinmu yau da aka samu shi kadai bazai riqe mana matsayinmu da tsagwaran dukiyar da muka rasa ba muna tsananin buqatan dukiyarmu Dake hannun Omar.

Dad da Shima abinda yake ransa kenan ya Kalli Haroon dayake tsaye har lokacin gabansu Yana kallan fuskokinsu da bakinsu yace

"Haroon ya qara muku kudin Daya kamata banason aurensa yazo duk tsanani duk wuya batareda an samo mana inda suke ba,
Idan Kuma bamu samo Hakan ba to tabbas lokacin zuwansa garemu yayi Dan bazai taba yiyuwaba ayi auren 'dana dayake matsayin dansa batareda yazo ba,

Zuwansa Nigeria kuwa ba abune da zai taba yiyuwaba yazo ya tafi batareda ya kaiwa abinda ya Haifa da cikinsa ziyara ba Wanda shi da kansa zai kaimu ga Magajinsa batareda ya saniba.

Kallan Haroon ya sake yi Yana sake cewa

"Ka Basu duk adadin kudaden da suke buqata kaje ka fara Shirin aurenka Dan daga lokacinda Omar ya sauka a Nigeria dukkanin motsinsa a tafin hannunmu zai zama."

Gyara Kai Jamaal yayi Yana kallan BB dayakejin bazai iya barinsa ya sake ahakan iskan yanci ko Daya ba Amma Kuma Yana buqatan sanin abinda yake faruwa kafin komai Dan kuwa zantukansu sun Saka kansa daukan zafi.

Gyada Kai BB yayi Yana Jin nutsuwa da farin cikin Suma wahalallen burinsu ze Kai karshe sbd a saukake ma auren Haroon din zai kawo Omar har gida Kuma zuwansa kaman bayyanar abinda yake boye ne.

Maganganun sauran ayyukansu dasu BB din keyi ne suka fara Kai tsaye tareda tambayan huldan datake hannun BB din da yaransa ya tabbatar musu da komai Yana tafiya lafiya kalau duk da an kama wasu yaransa Amma ya tura yaronsa Daya Daya bari aka kamasa aka Saka cikinsu Sbd ya hanasu fadan komai sedai aka wayi gari sun rasu dukansu su biyu sai shi Dayan yaron nasa sun fito dashi Dan haka Babu matsala Tako ina.

Juyawa Jamaal yayi ya fito idanuwansa basa ganin gabansa sosai sbd Ja da tashin hankalin Daya tsinci kunnuwansa daji batareda ya tsaya jin sauran abubuwan da hankalinsa yake Neman kasa dauka duk da ya Dade da sanin ba imani a lamarinsu Dad bare tausayi sbd abinda sukaiwa fadila da har yanzu baida sheda ko tabbacin sune sukai Amma ayau da kunnuwansa Yana Jin abubuwan da baisan tayaya ma zaace sune suke aikatawanba,

Haroon ya San dukkanin wannan abin dayake faruwa kenan ya boye masa tinda gashi suna maganar a gabansa batareda sanin ba Haroon dinne ba.

Yana fitowa Kai tsaye mota ya nufa Yana miqawa siddeeq hannu ya basa key batareda ya Juyaba,
Kirjinsa yake Jin ya toshe masa Babu iska ko kadan Babu abinda yake buqatan so kaman ya fita daga Mansion din.

Siddeeq na ganin Hakan ya miqa masa key din motar Haroon Daya fito dashi Dan fitarsu idan sun gama.

Saida siddeeq ya nuna masa motar ya nufi inda take tin kafin ya Isa ya Budeta Yana Isa shiga kawai yayi ya tayar da reverse ya fice daga Mansion din Yana saukar da duka glasses din motar sbd iska ta shigesa.

Yana ficewa siddeeq ya Ciro wayarsa Yana shakkar abinda ya faru daga cikin office din Amma dai koma Menene Haroon Yana buqatan sani Dan dawowa

sbd ansamu matsala ga dukkanin alama.

Su Dad kuwa farin ciki da zaquwan auren ne gaban Daya ya mamayesu sbd ga dukkanin alama sanadiyar auren zasu samu abubuwa da dama dasuke so suke fata,
Haroon ya fara zama abin Alfaharin da zai sake fitar da sunan seelahs da tsayuwarsu hakama dawowan Omar dasuke fata ta sanadin auren da dole zaizo ko Dan Yan jarida dazasu yada maganar auren koina da rashin zuwansa auren 'dan farko da zaayi a Seelahs din tinda na Jamaal kaman auren boye ne da ba kowa ya saniba Amma wannan da kansu zasu Kai masa gayyata ta musamman da matsayin zamansa wakilin ango da zai karba auren da hannunsa.

******Haroon dayake tareda mahaifiyarsa tana jinyarsa cikin tsananin so da kauna da kulawa tareda tattali Jin yayi zuciyarsa ta karaya Da yanda tin farko ya zabi mahaifinsa akan mahaifiyarsa,

Bata taba nuna masa banbanci tsakaninsa da Jamaal ba sedai shine Karan kansa ya zabi mahaifinsa akanta sbd sonsa dayakeji cikin ransa fiyeda komai.
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
44
Mum Aleena datake Jin batason sake rabuwa da 'danta sbd halinda yake ciki na tsananin buqatan kulawansu dan sai sunyi da gaske zasu iya rabasa da depression din Daya kamasa,

Drug kuwa da suka samu a jininsa Basu sanar masa ba itada Jamaal sbd sunason tantance shine yake Sha da kansa kokuwa sbd sun kasa yadda ko sanin tayaya zai zama Yana Shan kwayoyi irin wainnan.

Siddeeq Kuma ya tabbatar musu da Babu kwayoyi mayen ko makamancin Hakan da Haroon yake Sha Amma Kuma duba da depression dayake ciki da tsananin matsi a Hannunsu Dad zai iya samun kansa da Shan kwayoyin Dan samun fita hayyaci ya Dena Jin komai.

Tin daga ranar da Haroon din ya taho aranar ya ringa yiwa mum din kuka kaman karamin yaro cikin ciwo da tsananin buqatan again Dan uwansa akan bayason rasa Ameenatou kaman yanda ya rasa fadila,
Shi a yanzu ba yabon mahaifinsa yake nema ba Ameenatou kawai yakeso a rayuwarsa.

A gaban Mahaifiyarsu Jamaal ya Sakasa sukaiwa juna alkawari.

Idan Haroon yayi masa alkawarin dawowa ga mahaifiyarsa Dan samun lafiyansa da rayuwar nutsuwa da Kwanciyar tare Kuma da cika burin Mum dinsu na ganin yayanta duka biyu a tareda ita to shi Kuma yayi alkawarin zuwa ya gyaro dukkanin abinda Haroon yakeso Dan samun yabo daga Dad dinsa da Kuma zama abin alfaharinsa tareda tabbatar da aurensa da yarinyar Amma ana daura auren zasu taho tare.

A daidai wanna gaban Babu abinda Haroon bazai iya yiba akan samun Ameenatou da samun nutsuwan zuciyansa data Dan uwansa da mum Dan haka ya amince da dawowa cikinsu gaba Daya bayan auren take mum ta rungumesa cikin farin ciki da Jin dadi sosai tana Jin kaman tinda ta haifesa sai yanzu ne zata samu zaman datakeson yi da 'danta hakama zata kaman yanda ta kaunaci fadila take taji tana kaunan Ameenatou har cikin ranta duk da Bata taba ganinta ba Amma tayi masa alkawarin inshallah da ita zaayi

aurensa.

Daman ba wani zama zasuyi a Poland dinba Nigeria zasu taho sbd bikin auren Da Haroon din kwata kwata yaji Baya son a dauko lokaci ayi kawai ya tahowansa kusada mahaifiyansa Dan haka sauki kawai sukeson ya Dan samu su taho saiga Kiran siddeeq Wanda ya sakashi shiga fargaba da tsoron abinda Jamaal yaji Dan haka shine ya dagawa mum hankalin komawansa baima jirata ba washe garin ranar ya Siya ticket dinsa ya tahowansa Dan bayason abinda zai janyo fushin Jamaal ya lalata masa komai adaidai lokacinda ake gap da samun abinda yakeso.

Jamaal kuwa a ranar Bai kwana a Lagos ba ya wuce Abuja tareda siddeeq ko su Dad din Basu saniba Dan idan Yana ganinsu zuciyarsa kasa riqe koshi waye din takeyi gwara ya tafi ya Jira zuwan Haroon Daya San duk inda yake idan har baida gaskia Yana hanyar dawowa.

Kwana Daya saiga Haroon din ya diro Amma Bai yadda ya Hadu da Jamaal din ba Kai tsaye Nasarawa ya wuce sbd bayason suyi hayaniya Kuma baisan Menene yaji bama tukuna bare yasan ta inda zai fara.

Da yamma sosai ya iso Dan haka wanka da sallah kawai yayi Bai tsaye komaiba ya wuce gidan Babbah.

Zaune suke a tsakar gidan sai lallabata dadah keyi sbd taqi Shan magani daga ciwon Kai zazzabi ya maqale kwana biyu anata fama da ita.

Zuwansa ya Saka Abdul sakin ajiyan zuciya hakama Hafiz Babbah Baya Nan cikin sakewan fuska da nutsuwa ya qaraso Hafiz na janyo masa kujeran zama Yana masa barka da zuwa.

Yaya Abdul ya fara bawa hannu suka gaisa cikin tsananin kulawa Yana tambayarsa kwana biyu ko numbernta Baya shiga.

Murmushi ya sake Yana cewa aikin dayake gabansa ne ya sakashi kashe dukkanin wayoyinsa sbd aikin ya koma babba fiyeda yanda suke tsammani.

Gurin dadah ya Maida kallansa Yana gaidata cikeda girmamawa da kulawa kafin idanuwansa suka koma kan Ameenatoun Dake zaune sanye da Riga da wando na bacci ko hula Babu a kanta ko inda yake Bata juyo ta kalla ba maganinta take kokarin Sha tana kasawa sbd batason magani ko kadan.

Hafiz Dayafi kowa shiga damuwan bayan Ameenatou tambayarsa siddeeq yayi suna sake shiga wata firar Amma gaba Daya hankalinsa na kan Ameenatou da yayi magana tayi masa shiru kaman Bata ji ba Kuma kowa

yasan ta jisa Daman sun San sai anyi Hakan.

Dadah ce ta Dan rarrasheta tana cewa

"Budurwa bakiji ana Miki ya jiki bane?
Duka fushin bana rashin kiransa da zuwan bane gashinan ai ya taho saiki sauko,
Yi masa hakuri kinji¿

Maganin ta daga duka ta Saka a bakinta tareda binsa da ruwa ta shanye batareda ma tasan tayi Hakan ba sbd fushin Daya taso mata.

Tinda ta fara zazzabin ko ruwa Se ta Saka anbata ko hulan kanta Bata iya sakawa sai an Saka mata sai gashi ta miqe tsaye da kanta ta wuce dakinta tana cewa bacci zatayi.

Hafiz ne ya Bude Baki yace

"Ke meye haka wai?
Inace Wanda ake fushi da ciwon akansa gashinan yazo,Kuma Ashe Zaki iya tashi da kanki kika ringa wahalar Dani da Dadah tin jiya ko bacci na fara saita kirani na kawo mata ruwa Ashe tsaban rashin tausayi ne to Zaki San dawa kikai."

Tana jinsa Bata ce komaiba saima hararan kofar datai tana Jin zafin abinda yayi mata ranar Yana dawo mata.

Dadah murmushi ta sake tana sake tambayarsa nasa jikin ya amsa mata sbd yasan halin mutuniyar sarai basai an tsaya basa hakurin abinda tayin ba,
Abdul ma sake tambayar jikin da aikinsa yayi kafin suka fada firar tafiyansa Lagos gobe zuwa nxt week Kuma su dadah ma zasu taho duk da ba zuwan kenan ba zadai suje suga inda Allah ya Kaisa dasu.

Duk firar dayaketa yi hankalinsa na kan kofan dakinta Amma Sam taqi yadda ko motsi tayi yaji dadi Bare fitowa.

Sallan magrib suka fita sukayo suka dawo gidan tareda Babbah daya masa ya jikin da fadan rashin Kiran tinda koyayane Daya samu ko mintina bibbiyu a wuni ya ware ya kira din zasuji dadi itama me fushin da bataiba.
Gashi tanata fushi da maimaita shariyan dayayi mata.

Hakuri ya bawa Babbah har suka shiga wata firar inda Babbah din ya sanar masa su Alh Lameenu sun kira akan maganar auren sukeson ta taso ayita kusa tinda dai ba amfanin jiran ko tsaiko.

Har cikin ransa yaji farin ciki Yana mamayesa sedai Kuma fushin da Ameenatou keyi me zafi akansa Yana cin zuciyarsa sbd yasan Jamaal ne yayi mata koma Menene Dan haka Shima take yaji Yana buqatan ganinsa Dan haka anan yayi sallar ishai yaci abinci suna gamawa harya fito Bata fito a dakinba Kuma babbah ya Hana kowa takurata fitowa saita huce da kanta taji ta hakura tukuna.

Yana fitowa da wayar hannunsa ya kira layinsa dayake hannun jamaal Amma Jamaal din yaqi dauka sbd Shima Yana sane da Haroon din ya dawo guje masa yayi.

Kiran dayake yi Jamaal yaqi dagawa ya Sakasa dawowa hayyacinsa akan abinda yake jiransa Dan haka dole ya shirya tinda safe ya nufi Abuja.

Koda ya Isa Jamaal din Yana bacci Dan haka siddeeq na ganinsa ya saki murmushi Mai hade da sakewa Yana masa barka da dawowa.

Kallan hanyar stairs na Hawa sama yayi kafin ya dawo da kallansa kan siddeeq din fuskansa a sake Shima Yana amsawa ya ajiye keys din hannunsa da wayarsa Daya ya nufi dining da aka cikesa tsaf da breakfast din Jamaal din ko zama baiyiba Yana Isa dining din Jamaal ya sauko daga saman sanyeda silk pyjamas farare Kal sai slippers dinsa masu shegen tsada da taushi a qafa kallo Daya yayiwa Haroon ya matse fuskansa datake sheqi kaman ba bacci ya taso ba Yana qarasowa ko zama beyiba Haroon ma ya Dan matse tasa sbd kada Jamaal din yayi masa fada a gaban siddeeq yace

"Meyasa nake Kiran wayanka baka dagawa tin jiya fa da daddare bayan isowana?"

Sai alokacin Jamaal ya juyo ya kallesa da idanuwansa da suka Sakasa Jin kunyar Dan uwan nasa na Abinda ya boye masa duk da haryanxu Yana shakkar idan gaskiyar abinda su Dad keyi ne yaji sbd da bazai zauna haka calm ba.

Ciki muryan dayake kokarin danne bacin ransa yace

"Ka taho ne sbd ban dauka Kiran ba kokuwa sbd kana son sanin abinda na sani gameda ainihin abinda kuke aikatawa a boye?"

Maganar tasa ta Saka Haroon kallansa Yana cewa

"A boye Kuma?
Me kenan??

Me kaji?
Kuma daga bakin wa?

"Daga bakin manyanka,Amma koma Menene baka buqatan sani
kaman yanda ka iya boye sirrinsu bana son sanin komai daga bakinka Amma dai ka fada musu taba Dad jeden shine babban Barna da kuskuren da zasu tafka sbd jinin wani karfi ne dashi baa zubar dashi a sake zama lafiya,
Wannan shawara ce da zaka sanar da daddies Dinka."

Yana fadar Hakan ya taba sa ya wuce zuwa dining din sbd yin breakfast.

Kasa motsawa Haroon yayi sbd Baisan me zai fada ba.

Yana gurin tsaye Jamaal ya gama breakfast dinsa ya koma sama yayi wanka ya shirya ya fito a shirye qamshinsa na cika iskar gidan ya fice shida siddeeq sbd sosai yake aikin dayake gabansa Dan kasar gaba Daya Jin yayi fita ransa tafiyansa yakeson yi batareda yabar Haroon din ba Koda me zaayi kuwa,
Aikin kawai yake son gamawa ayi auren su tafi Babu ranar dawowa.

A gidan suka bar Haroon yanata sakawa da kuncewa har sai dare suka shigowa gidan ya fice Dan a matse yake dayake ya duba Ameenatou tinda yanzu Kam baida aikin yi bayan zama guri Daya harsai jamaal ya dawo.

Yauma kwata kwata Bata saukoba duk rarrashinta da duka gidan suka taru sunai mata haka ya gama ya koma Amma dai gwara yau din ta zauna Bata shige dakinta ba.

********Jamaal gaba Daya Jin yakeyi kaman ana konasa aqasar Dan haka ya toshe dukkanin hanyar da zata Bata lokacinsa akan abinda ya kawosa ya dukufa sosai akan aikin Wanda tini ya dauki hanyar kammaluwa sbd sosai ake Aiko na masu zallan ilimi gadan gadan ba wasa ba shirme.

Hafiz dayake ganin sauyi sosai a Haroon din dayake Gani Gurin Aiki da safe da Kuma Wanda yake Gani gidansu da daddare sai ya Saka Hakan akan gurin aiki daban da gida Shima Saiya janye daga nuna kusancinsu da Haroon din gurin aiki saisun hade gida suke fira da gaisawa yanda ya kamata.

Jamaal kansa mamakin Haroon din yakeyi sbd yanda zuciyansa ta gama mutuwa akan yarinyar bayaji Baya Gani Baya gane komai idan bana Yarinyar ba da har lokacin shi Yama kasa tsayawa ya riqe sunan.

Fahimtar irin son dayakewa yarinyar ya Saka Jamaal din Jin bazai iya barin

Haroon ya rasata ba.

Ta bangaren su Dad kuwa duk lokacinda ya buqaci ganin Haroon Jamaal ne yake zuwa sbd bayason Haroon ya sake tsayuwa a gabansu Dan kada su lalata masa aikin treatment Daya basa shida mum akan lafiyansa da suketa kokarin ganin samunta Dan kuwa shiyasa suka buqaci komawansa tareda sakashi alkawarin komawan acan Dan kuwa abinda yake Sha Wanda Basu gane Menene ba yayi masa Mummunan illan da basason ma ya sani kwata kwata.
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
45
Ranar da Abdul ya cike kwana hudu a Lagos Dan fara aiki a ranar su Dad

Lameenu suka sake dawowa nasarawa maganar tsayar da aure hadda Abdul din aka taho Wanda Dad Lameenu ya jasa a jikinsa sosai yana masa kallan kaman 'dansu duk Dan sbd ya sake dasu sosai ya samu aminta dasu har zuci ya yanda komai zai taho a sauki.

Sun sake zama anyi magana an tsayar da ranar auren sati uku hudu masu Wanda daqyar dai su Babbah suka aminta da Hakan sbd kwanakin sun musu kadan duk da ba wani biki sosai akace zaayiba Tinda a Lagos zaayi komai Amma hakama sun buqaci yafiyan duk wani abu da amarya zata buqata Amma Babbah ya nuna amincewa da Hakan gaskia sbd duk fafutikan rayuwar dasukeyi shi da su Abdul na inganta rayuwarta ne su Bata gata Dan haka dole zasu wadata ta da dukiyan aure kaman kowace 'ya yar asali yar gata daidai karfinsu.

Su Dad din Basu wani ja da Hakan ba Daya dage Dan haka take suka gabatar da komai aka Yanke sukai Godia Suma su Babbah sukai godiya.

Wannan Karan harda dadah aka kirawo musu suka gaisa da ita da Ameenatou din wadda take sanye cikin doguwar Riga maroon sai veil data doro Akai.

Sun nuna yabawansu da nutsuwanta a fili sosai suka ringa sake yiwa Babbah godiya Wanda tini ya sake Jin hankalinsa ya kwanta dasu da mutuncin da suke dashi hakama Abdul ya sake tabbatar masa da mutuncin dasuke dashi harma agurin mutane Dan haka yake sake godewa Allah akan zabin da yayiwa Ameenatou dinsa Dayake ta addua da fata.

Da farko babbah baida niyar zaman Lagos din Amma a yanzu da Aure yakai 'yar budurwansa yaji bazai iya zama a nesa da inda take ba tinda harsuna da inda zasu zauna din agidan Abdul Dan haka ya aminta da komawa Lagos din gashi Daman Hafiz ma Lagos din zaibi Haroon kaman yanda yayi masa alkawarin dashi zai koma Koda aikin site ya kammalu acan zai basa aiki a kamfaninsu.

Tsayar da ranar auren ya Saka Haroon shiga lokutan farin cikin rayuwarsa Dan haka ya sake nutsuwa sosai Yana mayarda hankali cikin aikin project din da Jamaal ya tsayu akansa Dan kammalawa ya tafiyansa Dan kullum Jin yake Yana sake matsuwa da barin kasar.

Haroon ganin irin kulawa da kaunan da mahaifinsa yake nuna masa ayanzu Dayake alfahari dashi dakuma ganin abubuwa nata dawowa kan hanya sai yaji soyayyar Dad dinsa na kashe masa jiki kaman bazai iya tafiya ya barsa ba Amma Bai bar Jamaal ya fahimci Hakan ba Dan Jamaal kwata kwata ya Dena

bayyana a gaban su dad din sbd yanzu kauna zalla sosai Dad yake nunawa Haroon Dan haka yabarsa ya samu kaunar dabai samu daga Dad dinba Wadda yake tsananin so da burin samu.

*****Su Babbah kuwa A nasu bangaren sosai hidiman tayi musu yawa sbd ga hidiman Shirin biki gata tashinsu duk da ba siyar da gidansa zaiyiba Yan haya aka Nemo zaa Saka Dan haka suketa shirye shiryen tafiya da siyarda abinda ba dashi zaa tafin ba.
Su mum Atee ma da zasu taho kawo kayan aure su lefe da masu gyaran amarya Babbah cewa Yayi su barshi acan tinda suma a satin zasu iso Daman sun zabi yin auren acan ne sbd kawowa kowa sauki dangin angon masu zuwa da Jamaar seelahs din da duka manyan mutane ne da manyan qasa hakama da Yan kasashen qetare sbd sosai Mam ya fito ya nunawa duniya auren dansa zaayi Kuma aure na alfarma na Manyan masu abin duniya Dan haka aketa shiri da Kuma miqa gayyatansa ga abokanan huldansu da manyan masu kudin da suke tare harma da gwamnoni.

Ita kanta amaryan Haroon Kuma budurwan Babbah farin cikinta kusan kullum Baya boyuwa sbd a kwanakin Dan kullum auren yake matsowa cikin tsakiyar ranta take sake Jin tsananin kauna da son Haroon Wanda ya tsayu tsayin daka ya tabbatarda ya dawo da sonsa sabo fil cikin ranta.

Daga shi har ita Hafiz yace ya rasa wanne yafi rawan kafar aurenba ita dai bata tanka Hafiz din sbd ta shirya masa duk abinda Bai zata ba bayan auren tinda a karkashin mijinta zaiyi aiki.

Duk hidiman auren da akeyi Jamaal Bai shiga ko dayaba sbd baida time ko kadan na batawa aiki yakeyi gadan gadan ba dare ba Rana Kuma Hakan saka su dad farin ciki yakeyi.

Ranar dasu Babbah suka gama parking zasu wuce Lagos Kuma jirgi zasubi dukkaninsu sbd murna Ameenatou har fita tayi yau ita kadai a Karan farko rayuwanta taje gidan kawarta Aminiyarta Khadija Tayo mata bankwana itama Khadijan satin zaa fara bikinta shiyasa bazata samu binsu ba ayi bikin da ita Dan haka suka hakura dole da samun bikin juna.

Fitowa sukai tareda Khadija din ta rakota har kusan Rabi kafin ta koma ita Kuma ta wuce.

Dayake hanyar site ne gidansu Khadijan tana kawowa gurin hanyar site din ya hango motar Haroon ta tsaya a bakin hanyar da zatabi ta wuce bakin shago batareda an Budeba.

Glass ya saukan aka miqo masa Abu daga shagon Wanda take kyautata zaton ruwa ne sbd bayan motarsa aka Saka masa.

Wani kyakkyawar murmushi me sanyi ya sauke daga fuskanta tana kallan motar ta tabbatarda shine a ciki bayan yanzu da sukai magana cemata yayi Yana Abuja.

Motan ta nufo tana daga wayarta Dan Saka Kiransa taji me zai fada mata yanzu Kuma.

Tana isowa motar ta miqa hannunta Daya akan mabudin kofan Baya Dan tasan anan yake zama siddeeq ne me jan motar
Tana budewa daidai Yana dagowa daga abinda yake Karantawa daga iPad din hannunsa ya kalli kofan motar da aka Bude Idanuwansu suka shiga cikin na juna
Shikuma a Karan farko Daya Kalli idon wata 'ya mace rayuwansa bayan rasuwan matarsa.

Itama nata idanuwan kusan shine karanta na farko kallan cikim idan mutum Dan haka ta dauke fararen idanuwan nata tana sake wata fitinanniyar murmushi tareda shiga ta zauna Kai tsaye tana juyowa suka fuskanci juna qamshinsa na shigan hancinta Kai tsaye zuwa zuciyanta murmushinta Bai daukeba sedai yau din ta kasa kallansa sbd kunyar takusa zama matansa Kila yau takeji da wani shagwabbiyan murya ta dago ta zuba masa idanuwanta tace

"Shine kacemun kana Abuja sbd kada muyi bankwana kafin na wuce ko??"

Siddeeq Daya rasa ta inda zai fara gyaran matsalan Dake kokarin faruwa fitowa yayi da sauri daga motan ya zagayo ya rufe mata kofar Data shigo ya sake dawowa mazaunin driver da sauri ya zauna sai alokacin ya juyo ahankali ya saci kallan JEEY Daya zuba mata fararen idanuwansa Yana kallanta cikeda mamaki da shakkar ko tanada matsala ne Dan baisanta ba baima taba ganinta ba yake ganin.

Hadiye numfashi siddeeq yayi cikin Dan daidaita murya ya riqa JEEY din magana Yana washe Baki da nuna kulawa yace

"AMEENATOU,
barka da fitowa,yau ke kadai kika fita ne??

Hakan daya fada ya fada ne Dan JEEY yasan wacece din shiyasa ya ambaci sunan nata Kai tsaye Yana tada motar yaja ahankali suka bar gurin Yana

juyawa Dan maidata gida.

Dauke idanuwansa JEEY yayi akanta tareda rufe iPad dinsa daidai lokacin ta sake motsowa kusa dashi tanason fada masa maganar da batason siddeeq yaji sedai tana motsowa da fuskanta Dan fada mata din Yana juyowa da tasa fuskan kadan ya rage fuskokinsu ya Hadu tayi saurin yin bayan kirjinta na bugawa ta dago ido ta kallesa Shi kuwa Kai tsaye ya Bude Baki yace siddeeq ya ajiyesa site.

Kasa magana tayi sbd kirjinta Dake bugawa har lokacin shiyasa har motan ta tsaya Bata iya cewa komaiba harya Bude motan ya fice yabarta zaune tana kallan inda ya tashi da ido fuskansa da numfashinsa Daya bugu fuskanta na dawo mata.

Gida siddeeq ya wuce ya ajiyeta Yana mata zancen aikin Dake gabansa ne duk suka Saka kansa daukan zafi shiyasa Baya cikin mood kwata kwata yau din.

Bata iya cewa komaiba ta Bude motan ta ficewanta tareda shigewa gida.

Mota ta musamman ce tazo ta daukesu guraren 2 na Rana tayi Abuja dasu daga can suna Isa airport ba Bata lokaci jirginsu ya daga zuwa Lagos.

Suna sauka Lagos Abdul ne da kansa yaje da motan Aliyah 'yar Alh Lameenu wadda tinda Taga Abdul din taji yayi mata sbd batason namiji me kudin da shine zai juyata tafison Wanda itace me kudin Kuma yar me kudin dazata ringa yanda takeso baya hanata bare ma Saka ido Dan Bata wani zama kasar itama kullum tana yawo karatun ma duk ta kasa tsayawa tayi sai yawon kasashe.

Dayake Dad ne yace yaje da motan ya daukosu shiyasa ya taho da motan ya daukosu.

Gidan Abdul din a kusa da tsadaddiyar anguwan masu shi da mansions din seelah din suke yake Dan haka daga gurin mum Atey driver ya kawo musu abinci bayan isowan nasu.

Gida ne me maana Wanda ya bawa Babbah da Hafiz mamaki sosai sbd ace anbawa sabon ma'aikaci gida irin wannan me Dan yalwa da kyau da tsari Kuma komai akwai a aciki gaskia sedai Dan zasu hada zuria ne Amma tinda a cikin kudin aikin Abdul din akace kamfani zai ringa cire kudin haya sai sukafi Jin nutsuwa da Kwanciyar hankalin sakewa da Hakan.

Daki uku ne a gidan sai Palo biyu da kitchen sai back door da store sai kowanne daki da toilet dinsa.

Kowa daki Daya ya dauka Abdul Daya,Hafiz Daya sai su Babbah Daya sbd Ameenatou tafiyanta zatai gidanta Nan da kwanaki Dan haka baa Raba dakin da ita ba Amma dai na Hafiz itace a ciki da komai nata shikuma yana kwana Palo kafin ayi bikin Amma kayansa suna dakin Yaya Abdul Wanda nasa dakin na daga gefensa daban nasu Babbah ma Yana daga gefe daban na Ameenatou dinne a tsakiya.
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*

Haroon yanason dawowa Lagos Amma sbd kada ya zama ana ganinsa a

Lagos Kuma ana ganin Jamaal a site yasakashi hakura ya zauna tareda Jamaal din Wanda Shima yafara kokarin Maida hankali ya gyara career dinsa data watse ta matsayinsa na lawyer.

A bangaren su Dad kuwa tsarin katin gayyatar Omar na musamman ne,

Duk tsawon shekarun Nan da basa tare bawai sun yanke muamala ne kwata kwata ba aa Suna waya da sauran gaisuwa a waya batareda kowannensu ya nunawa Dan uwansa komaiba,
Shi Bai taba yi musu wata maganar bare nuna wani abin daban kaman yanda suka Basu taba cewa komaiba bare nuna shakka fargaban yasan wani abin kawai dai kowa na nesa da Dan uwansa duk dubaru da nuna kaunarsu Bai Bata zuwa inda suke ba kaman yanda ya toshe hanyarsu ta zuwa inda yake iya Hulda da zumuntar waya sukeyi tareda nunawa juna kauna da kulawa a iya wayar sai yanzu da wannan kyakkyawar Daman ta taho musu wadda baida kowanne uzuri ko dalilin Badawa na qin zuwa auren Haroon Wanda sune ma ya kamata ace sinje Neman auren nasa batareda anje dashi Mam dinba Dan shine iyayensa.

*****Ta bangarensu Amarya Ameenatou kuwa suna fama da kadaici da bakuntar sabon guri Amma irin rayuwar da suka samu kansu a ciki ta wadata ta Saka bakuntar zuwan musu da sauki ga Kuma hidiman da aketa kokarin farawa gadan gadan.

Su mum Atee dasu mummy Sarat da jamaarsu sun kawo lefen auren Wanda ya amsa sunan lefen gaske na auren masu abun duniya Dan kuwa sosai dadah da umman fadila datazo tarbon lefen sbd Jamaal da siddeeq harma da Haroon din suka girgiza da tarin kayan da aka kawo din tareda wasu mahaukatan sarkokin Dalma(zinari/gwal/gold).

Da dadah da umman fadila sai Jamaar amanar dadah biyu da suka taho bikin Tim daga Nasarawa Dan lasa arzikin Suma da Kuma tabbatarda amanarsu Dan idan Basu taho auren budurwan gidan Babbah ba yar gaban goshin dadah dasu Hafiz ai basuyi komaiba.

Duk da basuda wani karfi Saida Babbah ya fidda kudi masu Dan kauri a Dan abinda suke Tarawa na bikin ya Bada tukuicin da sedai masu aikin da sukai shigo da kayan ne suka karba Amma mum Atee Sam kin karba sukai suna nuna ai ba komai bazasu karba tukuicin ba bayan a cikin ransu dukkaninsu qyanqyamin taba kudin ma sukeyi sbd Yan dari biyar biyar ne a hade dubu hamsin cif.

Su umma anan duka wuni sunata duba kayan har dare suna sake Saka

albarka da adduar fatan farin ciki me dorewa a auren.

Washe gari masu gyara na musamman aka turowa Ameenatou wadda za'a fara gyarawa Tin daga satin har satin auren Wanda ya rage saura sati biyu cif.

Ranar farko da aka fara yimata gyaran ta fara sauyawa abinta sbd fatarta irin me santsin Nan ce dake karban komai da wuri,

Farin ciki da dokin datake ciki itada Haroon ya wuce duk inda ake tinani sbd karfi da yaji duk yanda Babbah da Dadah suka Kai basa ganin laifi ko illan komai datakeyi Saida suka ringa Jin kunya da mamakin irin son datake wa Haroon Wanda ya Sakasu shiga tsoro da duqufa da adduar Allah yasa irin girman son dayake mata ya tabbata a rayuwar auren nasu yakuma barsu tare har karshen rayuwarsu.

Haroon a wannan lokacin yana cikin kwanakin farin cikin rayuwarsa me tsananin gaske da Bai taba samun kansa a cikinsu ba Wanda Hakan ya sanyaya zuciyar 'dan uwansa da mahaifiyarsa akansa wadda Bata isoba har lokacin Amma ta sheda farin cikin Da Haroon dinta yake ciki Wanda takejin a matsayinta na uwa a garesa tayi missing Daman basa wannan farin cikin dasuke Gani tareda shi sedai tana Jin dadi har ranta daya samesa sanadin macen dayakeson.

Jamaal tausayin dan uwan nasa ne ya Sanyaya zuciyarsa bata cikin farin ciki ko walwala kwata kwata Dan Bai taba ganinsa a irin wanna kyakkyawar yanayinba tsawon rayuwarsu Dan haka yake tayasa farin cikin Samun abinda shi Bai samuba Dan kuwa a nasa labarin Bai taba samun farin soyayya a tareda wadda yaso din ba, duk lokacinda suka dauka a tare lafiyanta koyaushe itace abinda take gaban soyayyarsu Dan haka har suka rabu Basu taba samun kansu a cikin irin wannan farin cikin ba Dan haka baisan Menene yanayinba da yanda ake samun Kai acikinsa.

Koda yaushe a waya suke maqale da juna suna magana tana nuna masa duk abinda akai mata na gyaran Amarya Wanda kullum take sake sauyawa sosai tana fita budurwan datake cikin Hutu da gyara sosai Dan tinda suka taho Lagos din Bata sake fita ko gate ba daga gyara sai Hutu da AC datake Sha da lafiyayyar abinci me gyara jiki take ci.

Har lokacin Bai dawo ba Haroon din Yana Nasarawa n Abuja aikinsu gap yake da kammaluwa Wanda yake Jin kaman Yana Neman rasa kansa kafin gama aikin ya koma Lagos din.

******Su Dad so biyu suna turawa Omar jeden gayyatarsa a matsayin Wanda

zai karbanwa Haroon din auren Amma Yana toshe buqatansu ta Hakan sai gashi hankalinsu Yana Neman tashi da Hakan Dan haka Kai tsaye Mam yayi masa maganar Amma still dai ayyukan gabansa bazasu basa Daman zuwan ba ya sake Bada uzurinsa sbd Koda suke maganar ba Baya Nan Yana Japan Dan haka Kai tsaye ya Saka Ahmed ya tura musu zunzurutun kudi a matsayin gudunmawarsa data Saka su Dad din shiga mamaki da baqin gaske me tsanani.

Tsaban kudin suka kalla suna sake shiga qyashin gaske da bakin cikin irin yanda ya debo kudi irin wannan me yawa ya Basu kusan 500m as gudunmawarsa.

Shiru Dad Lameenu yayi lokacinda suke cikin tinanin abinyi gameda baqin cikin da Omar yake Neman sakasu Dan kuwa idan har zaayi auren Nan Bai tahoba tabbas Babu amfanin yin auren babba a garesu Dan duka kudi da dukiya me yawan da aketa zubarwa ana Shirin auren da akeson duniya ta sheda auren SEELAHs duk Dan sbd Omar din yazo ne Amma Kuma komai Yana Neman lalacewa a daidai lokacinda Babu time na Neman mafita ko gyara.

Mam da hankalinsa ya rabu biyu a yanzu akan yanda komai na ayyukansu ke tafiya daidai da Kuma sauyin Haroon Daya fara Sakasa Jin so da kaunan Dan nasa me tsanani na cikeda sedai Kuma Yana shakkar Shima yazo yayi auren mace ta sauya masa shi yazo Kuma baida abinda zaiyi masa barazana dashi Dan tankwarasa Dan haka gaskia gwara ya kama dukiyan dayake son kamawa Koda yayansa sun juya masa Baya yanada abinda bazai taba Jin zafi ba.

Lameenu wani numfashi ya sake Yana dagowa ya Kalli Mam da Shima yake Nisa cikin nasa tinanin ya sauke numfashi Yana ajiye wayar hannunsa daya gama da BB akan a Turo Yan jarida gidan Babbah zasu tafi Kai masa ziyara Yana son a yada abinda ya hadasu din sbd Omar yaga abinda sukeson ya Gani.

Mam da Baisan me Lameenu ke nufi ba yace

"Kayi duk yanda zakayi Omar yazo kasar nikuma wanna Karan nayi alkawarin cike aikin komai da hannuna batareda matsala ko dayaba wannan alkawarina ne."

Murmushin Daya tsaya iya fuska lameenu ya sake Yana Jin dadin Hakan Dan yasan aikin da Mam yasaka hannunsa da kansa aciki kaman cikan alkwarine Da Baya tashi cikar wannan aikin Dan haka ya sake murmusawa Dan shi a nasa bangaren ya gama yadda da indai akwai abinda Babbah ya sani gameda

Omar da abinda ya Haifa to tabbas Omar Saiya taho wannan auren idan yaga Babbah a tareda su din.

****Da yamma a gidan Babbah Dad Lameenu yayi Sallah tareda su a masallaci bayan sun Dade suna tattauna maganar daurin auren ya bawa Ameenatou kyautan motan da ita aka taho gidan wadda ta tareda katin gayyatan da aka bugo na musamman me tsadan gaske.

Yan jaridan da BB ya turo sun dauko bayanan da yiwa motar hotuna da Kuma yiwa Babbah da Alh Lameenu din hotunan da suka fito da kyau.

Babbah Bai karbi motan ba ya Saka aka mayar akan bayan auren idan Ameenatou ta dawo hannunsu an Bata acan.

Dayake ba damuwa Daman sukai da lamarin ba Yana dawowa da ita aka ajiye kawai sedai a Daren aka hada labarin dasukeson a hada dauke da hoton Babbah Dana Dad Lameenu suna dariya cikin farin ciki dayake nuna shakuwansu da kusanci sosai.

Washe gari bayan Dad Lameenu din ya gama karantawa kallan fuskanta Babbah yayi wadda ta fito da kyau akan

"mahaifin Sirikitar Seelahs Mal Nuhu babbah ya nuna farin cikinsa da Jin dadinsa ga kyautan motar da sirikansa da kansu suka kawiwa yarsa har gida amatsayin tukuicin auren dansu"

Kai tsaye tareda invitation dinsu na musamman na auren da hoton dayake dauke da wainnan bayanan ya Saka aka yada kafin kace me labarin ya fara yaduwa har inda basa zato.

****
Greece

Dattijo ne Dan zaka zama confused akan shekarunsa and Hutu da wayayyar ilimin data gama ratsa rayuwansa Tako wanne Sako ya koma half bature kwatakwata.

Zaune yake a cikin lafiyayyar balcony din gidansa Mai tsananin yalwa da tsari irin na masu kudin gaske dayake Shan iska Yana sanye da farin glass Daya qarawa farar fuskansa kyau sosai da qara fitarda sirrin kyau da Kwanciyar hankalin da Allah ya wadacesa dashi yana karanta mahimman

bayanai a Apple iPad datake hannunsa kafarsa Daya na kan Daya hakama gabansa table ne da laptop take Akai a Bude da alama itama wani sakon ya karanta kafin daga gefe qaramin tea cup ne Daya Sha coffee yabari a gurin.

Ahmed ne da Shima ya sauya sosai kaman wani lafiyayyan dattijon bakin bature Shima Hutu da kudi sun ratsashi ya iso gurinsa Kai tsaye da tasa iPad Shima a hannunsa.

Yana isowa kafin yace komai iPad din ya jiye a gaban Omar jeden Kai tsaye Yana cewa

"Ya kamata kaga abinda yake faruwa" ya nuna masa screen din iPad din.

Idanuwa Omar ya juya akan iPad din yana zare farin Glass din idanuwansa idonsa Kai tsaye akan fuskan Babbah da suketa azaban nema ya sauka a tareda Lameenu a gefensa suna dariya cikin farin ciki da shaquwa.

Hannuwansa Dake rawa ahankali yakai ya dauki iPad din a hannunsa Yana kafe hoton da ido kafin idanuwansa suka gangara akan abinda yake rubuce Wanda shine yake Saka Ahmed zufa da motsawan zuciya cikin tashin hankalin da Bai taba tinanin samun kansa ba.

Alh Omar Dayake Neman kasa gane komai saurin miqa hannu yayi Yana Neman ruwan Sha sbd yawunsa da suka qafe take.

****
SEELAHs sun shiga satin farin cikinsu Dan aikin project ya kammala an kaddamar
Fadan farin cikinsu Baya yiyuwa musamman Dad Lameenu dayake ganin sun tsallake rijiya da Baya Dan haka sune cikin farin ciki sosai.

Haroon sosai ya samu lambar yabo da karramawa tareda burge abokan huldodinsu da yawa ciki hadda turawa da yawa da suka yaba da aikin Dan haka take SEELAHs suka ringa samun manyan proposals masu zafin gaske Daya Saka su Jin duniya ta sake dawowa hannunsu Kuma a cikin satin suka samu sabuwar babbar Hulda daga Ashalawa wadda ta sake Saka kan Lameenu gigicewa shi Kuwa Mam a yanzu alfaharin gaske yakeyi da Haroon Wanda yake cikin farin ciki Shima sosai ya ringa Jin kaunar Dan uwansa na sake kere dukkanin abinda yakeso a rayuwarsa.

Dan haka a Lagos aka shirya hadaddiyar lafiyayyar dinner da aka barar da mahaukatan kudin gaske ta kammaluwan aikin.

Kusan duk wani babba dayaci ya tayar da Kai dayake mu'amalantar seelah ko sanatayya ya halarci dinner din wadda aka sakawa matakan tsaro da securities sosai.
Karfe goma Sha biyu da kusan Rabi aka gama dinner din wadda tsarinta yake na asalin Yan boko da masu kudin da muqami sai business tycoons kowa ya watse.

A daidai wannan lokacin da aka gama dinner din seelahs a wannan lokacin ne jirgin Omar jeden ya sauka a Abuja Nigeria.
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
47
Sabon drivern da suke tareda shi tin Baya Wanda dashi kadai Ahmed ya

yadda yayi contacting Tin kafin zuwansu ayau din aka tanadi lafiyayyar motan da zata daukosu daga airport har Mansion dinsa Dayake jere Dana Yan uwan nasa.

Babu amfani ko kadan ga gujewa zama gidansa dayake hade da masu tinda abinda yafi so da kauna duniyarsa fiyeda komai ta riga ta shiga hannunsu Dan haka ya yanke shawaran tinkaransu kaman yanda suka tinkaresa Dan yasan Nemansa ne sukeyi Kai tsaye shiyasa suka bayyanawa duniya fuskan Babbah Dan ya Gani duk da baida tabbacin sun gane asalin waye 'yarinyar da suke Shirin aurawa dansu din Hakan yake son tabbatarwa Dan baida ikon kowanne irin motsin da zai Saka babynsa a hadarin da zai illata masa ita sbd a yanda aka kawo sauran kwanaki ne kadai suka ragewa auren bayajin Babbah zai fahimci abinda yake son ya fahimta Amma dai Kuma bayajin har abada zai iya bayarwa ko barin 'yarsa da ita kadaice jininsa Kuma Jaden daya data rage ta shiga hannunsu Mamman.

A cikin Daren su dukkanin iyalan seelahs da suka dawo suka tararda koina na wutar mansion din Jden a kunne ta haskaka koina na zagayen gidan Wanda Hakan ya tabbatar musu da an kunna switch na wutan gidan gaba Daya dayake kashe hakama securities ne na musamman koina zagaye da gidan Wanda Koda suka fita hidiman bikin Babu ko Daya a mansion din.

Babban abinda ya sake raya mansion din shine matar Ahmed da yayansa biyu dasuke tareda su duka a cikin gidan Dayake kusan tsarin Mansion dinsa na can Greece Dan haka a cikin Daren ma'aikatan da duka aka Riga aka tanadar musu suka iso gidan cikin abinda Bai wuce awanni ba aka hau aikin gyaran gidan kafin su iso shiyasa Koda suka iso komai tsaf Babu abinda yake tashi sai kamshin freshners dana manyan humidifiers dana burners dayake tashi a duk inda ka Saka kafafunka da sanyin ACs da Suma suke aiki.

Ma'aikatan kusan guda biyar ne aka kawo dukkaninsu mata sai namiji Daya da shikuma harabar Mansion din itace tasa.

Mum Noor matar Omar da har lokacin ta riga ta rasa cikakkiyar lafiyanta akan abinda ya faru Bata Gani sosai hakama Bata iya tafiya sai akan wheelchair itama hakanan suka taho sbd yazo da niyar zama ya fuskanci wainda suke son fuskantarsa Amma zuwan na yarsa ne Daya danne dukkanin abinda yake ji akanta tsawon shekarun ya nesanta da ita sbd Bata kariya da rayuwar Kwanciyar hankali batareda tsoro ko fuskantar hatsarin dayake tattareda wata dukiyar ba,

Taimako da kyakkyawar rayuwar dayaso Basu itada su Babbah duk ya danne kansa ya janye daga garesu sbd koma huldan dazaiyi dasu a boye su Mam zasu iya bibiyan Hakan su mata illa.

Yayan Ahmed ba wani shekaru ne dasu ba sbd ya Dade sosai sosai baiyi aureba har Saida ya fara manyanta ma Dan haka suke Yara daidai kusan Ameenatou din Amma tama girmesu da shekaru biyu zuwa uku haka Dan babbar kenan sai namijin Wanda duka duka yanzu yakeda 10yrs zuwa 11 Dan haka masu aiki tini suka fara kokarin kaisu dakinsu Dan taimaka musu dasu wanka da sauransu.

Mai aikin da itace kaman babba a cikinsu sunanta Zahida itace ta Kai kayan kowannensu dakinsa ta fito ta nufi dakin yar budurwan wadda batasan sunanta ba Saida taji mom dinta ta ambaci sunanta da Fatmah kafin ta kama itama.

Abincin alfarma marasa nauyi irin Wanda sukasan zasu iya ci ne dayake dukkanin masu aikin kwararri ne aka dauko wainda albashinsu ma na musamman ne suka jere a makeken dining din Wanda Babu abin buqatan ci da Sha da baa jere ba cikin tsari.

Alh Omar ne a sama gaba Daya da mum Noor
A qasa Kuma Dayan bangaren Ahmed da nasa Iyalin ne dakin Fatmah daban hakama dakin Arfat daban.

Dukkaninsu Babu Wanda zai iya cin wani abinci a Daren sbd gajiyan dasuke tattare da ita,basa wani Jin yunwa sbd sunci snacks dasu tea da sai sauransu a jirgi so basa wani Jin yunwa Hutu kawai suke buqata.

Arfat da Bai Saba da koina ba hasalima shi Bai taba zuwa Nigeria ba tinda aka haifesa Dan haka kwata kwata qin yadda masu aikin su kusantosa yayi wanka yayi abinda ya shirya cikin kayan bacci ya fito ya nufi dakin Fatmah ya kwanta tareda ita itama duk da Bata san Kwanciya dashi Amma sbd bakuntan gidan ya Sakata kyalesa bayan sunyi sallah tea me zafi ta buqata daga masu aikin kawai Tasha ta kwanta.

Duk yanda Mam suka shiga mamakin abinda yake faruwa Basu nemesa ba sbd dare yayi Suma Kuma a matiqar buqatan hutun suke sbd hidiman da aka Sha Dan haka suka bari zuwa da safe Dan tabbatarda idan Omar jden dinne ya sauka Nigeria.

******Washe garin ranar da mamaki kowa ya wayi gari da ganin dawowan Wanda baa taba tinanin Gani ko yaddar zai dawo din ba wato Alh Omar jeden seelah wadda tini labarin ya fara yaduwa.

Mam da Lameenu da kansu suka taho yi masa barka da sauka cikeda farin ciki Mai tsananin gaske da nuna yabawarsu batareda nuna komai a fuska ba, Shima Bai nuna komaiba cikin farin ciki da nuna kewan juna ya bayyana farin cikin ganinsu.

Fira suka zauna sosai cikin kewa da murnan kasancewansu tare da juna a yau din bayan tsawon lokaci sun Hadu a matsayin brothers da aka Sansu.

Mum Noor Bata nuna komai ba sbd ba komai ma ta sani ba Dan haka sosai aka Hadu anata murna da farin ciki musamman dasu mum Atey suka shigo hakama su mummy Sarat ma duk sun shigo hadda su Aliyah anata murna harma da matar Ahmed Aunt Didi Wanda take wayayyar mace sosai Kuma ta waye ga ilimi Dan haka ta saki jikinta ta sake acikinsu.

A tare duka ahalin sukai breakfast qatuwar dining din gidan Dad Omar ana sake tattauna bayan rabuwa da Kuma murnan auren Haroon Daya sake hada auren.

Bayan breakfast shigewa su Dad suka sake yi Babu Wanda yake jinsu suna palonsa anata maganganu.

Su mum Atee ma sun jima sosai kusan a gidan aka wuni gaba Daya sai daga baya kowa ya koma masu fita Kuma irinsu Aliya tini ta qara gaba duk da Dad Omar tana yinsa sbd Yana kaunarsu sosai hakama wasu lokutan idan ta Kalli tazarar dukiya Dan rayuwan dayake da shi da 'yannansa su Dad dinta sai take Jin inama shine ya haifeta gashi a waye fiyeda Dad dinda da ilimin da kallansa kadai zakai kasan ya gama shigarsa Tako ina.

Sai dare Jamaar gidan suka samu Hutu da gidan yayi tsit sukaci abinci gaba dayansu a dining kafin kowa ya shige dakinsa yayi wanka ya kwanta Dan samun hutawa.

Washe gari Haroon ne da Bai samu zuwa ba jiyan ya taho yayiwa Dad din sannu da zuwa cikin farin ciki sosai.

Zuba masa idanuwa Dad Omar din yayi Yana karantarsa cikin nutsuwa da kulawa a matsayinsa n Wanda zai auri yarsa ta cikinsa.

Haroon sosai yake kauna da girmama Dad Omar shima Amma Kuma kusanci da kaunan Dake tsakanin Jamaal da Dad Omar din Babu Wanda zai iya shiga ko samun irinta Dan haka Shima Omar yake kaunar Haroon har ransa sbd kaunar dayakewa Jamaal da Dr Aleena Amma Badan mahaifinsa ba.

Haroon ya Jima a gidan Shima kafin ya fito Kai tsaye ya nufi ganin

amaryansa.

A Daren Ahmed da Omar suka fita sedai Bai nufi gidan Babbah Kai tsaye ba Wanda suka samu bayanin komai nasa da gidansa,
Zuwa gidansa Kai tsaye yanada hadari Dan haka masallacin da babban yake sallah ya nufa Dan yin sallan ishai acan.

Babbah tareda Abdul da Hafiz suka fito daga gida suka nufi masallaci kowanne da sauran ruwan alwala a fuskansa Hafiz na latsa wayarsa Babbah na masa maganar meyasa yake zuwa da waya masallaci Hakan baida amfani tinda ba dadewa zaiyiba a masallacin.

Shiga masallacin sukai Babbah ne a gaba kafin su a bayansa suna shiga suka shiga sahu
Ana kokarin tayarwa Ahmed da Dad Omar suka shigo masallacin Kai tsaye gefen Babbah Omar ya tsaya Yana gyara tsayuwansa Dan tayarda sallan Ahmed ma gefen Omar din ya tsaya Yana gyara nasa tsayuwar.
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
48
https://chat.whatsapp.com/K3rO5UonX4GDVxtQbA5mZl

Assalamualaikum wa rahmatullahi ta'ala wa barakatuhu!!! Wannan group din dai na komai da komai ne. A taiqaice
*Farashin mu na daban ne compared to sauran Yan kasuwa
*Kaya masu kyau da quality. Abinda kika zaba shi za a Baki
* Swift delivery.watau waybill a sauqaqe da Yardar Allah
* Muna sake New Arrivals ka fin su cika Gari
* Muna iya duba maku kaya a good price ko da ba namu ba ne idan kuka Aiko da hoton kayan
Allah sa mu qaru da juna Ameen

****
Babbah da baisan waye a gefensa ba sbd ya riga ya tayar da sallansa Dan haka hankali kwance da nutsuwa yake sallan hakama suma kowa ya natsu a cikin jam'in.

Dun Yana sallah ne Babu filin tinanin komai a zuciyarsa Amma dai Kuma ya tabbatarda ko waye a gefensa bako ne a masallacin Kokuma babban mutum ne sosai Dan qamshinsa me sanyi da nutsuwa ya tabbatarda Hakan kusan a duka sahun Babu Wanda qamshin me sanyi Baya shiga hancinsa.

Ana sallame sallar Babbah yana juyowa zai gyara zamansa idanuwansa suka sauka akan fuskan Wanda yake kusa dashi din take salatin daya debo daga bakinsa ya bace masa bat.

Juyawa gefensa Daya dasu abdul suke zaune yayi yaga hankalinsu Baya kansa adhkar kawai sukey,
Juyawa yayi bayasan yaga kowa abinda yake gabansa yakeyi da sauri ya sake dawo da kallansa gefen nasa ya sake kallan fuskan Omar ya kasa yadda da idanuwansa Gani sukeyi daidai Dan haka ya ambaci sunan Hafiz a hankali cikin nutsuwa yace

"Wannan bawan Allahn Dake gefena ka taba ganinsa a kuwa??"

Kallan Omar Dake zaune hankalinsa kwance Yana addua yayi yaga kwata kwata idanuwansa basa kansu hakama da alama lafiyayyan Mai abin duniya ne dan daga nutsuwansa da motsin jikinsa kadai zaka gane Hakan.

Girgiza Kai Hafiz yayi ahankali Yana dauke kallansa daga kan Dad Omar din Daya Burgesa Kai tsaye sbd wani sanyayyan kwarjininsa Daya cike idanuwansa dama duk Wanda ke kallansa Dan kaman kusan yakusa zama bature Dan fari ne sosai farin ma na Hutu.

Numfashi me dumi Babbah ya sake saukewa a karo na kusan biyar kafin ya juyo idanuwansa da suka sauya take ya Kalli Omar din baice komaiba Shima Omar din baice komaiba sai hannu Daya miqawa babban Yana Dan sake fuska da muryansa me Kamala yace

"Assalam alkm"

Cikin karfin hali babban ya miqa masa hannun Yana amsa sallamar Kai tsaye batareda ya kallesa ba kafin ya miqe tsaye Yana wucewa yabar masallacin.

Su Abdul cikin girmamawa sosai suka gaida Dad Omar din Wanda ya miqa musu hannu Shima Daya bayan Daya sukai musabaha Yana kallansu cikeda kauna da kulawa kafin suka bi bayan Babbah sedai suna fita suka tarar da ya bace musu da alama ya kama hanyar gida.

Hanyar gidan suka kama Hafiz na fidda wayarsa daga aljihu Dan Saka kira Abdul kuwa Kai tsaye hanyar gidan ya kama sbd zai fita da Dadah siyayyar turarukan wutan da zasuje yi itada umman fadila na MEERAH B PALACE masu fitinanniyar kamshin da duk amaryan datai amfani dashi Babu ta yanda bazata Hana zuciyar duk Wanda ya shaqa zaman lafiya ba Dan qamshine da a iya gurinta ne kadai ake iya samunsa.

Dayake washe gari ne kadai bazaa daura auren ba Dan haka Gyaran da akewa Ameenatou din ya koma so Daya a wuni maimakon so biyu sbd sauyin datai yayi yawa gaba Daya bazaka taba ganinta Kai tsaye ka dauka budurwan Babbah bace.

Babbah daga cikin masallacin Kai tsaye wani gurin ya nufa yaqi nufar gidansa Dan Bayaso abinda zai Kai Omar gidansa Kokuma abinda zai Saka a gansa da Omar ko a mafarkinsa kuwa Dan har abada baida alaqa dashi,
Alaqan Dake tsakaninsu sun Riga sun yanketa sbd shine kadai abinda ya Saka Ameenatou dinsu take raye,

Aurenta shine abinda zai sake Bata tabbatacciyar tsari daga mahaifinta da

masu bibiyansa sbd zatai aure gidan arzikin da zasu Bata kariyan da duk take buqata Dan haka yaji Inama gobe ne daurin auren...

Aurenta kadai zai Hana Omar amsarta daga hannunsa duk da Shima Koda Babu auren bazai taba basa ita ba sedai bayan ransa kuwa Dan haka yaji tsananin dadin Daya kasance auren ya raba musu gardaman yaqin da zasuyi akanta.

Mema ya dawo dashi bayan tsawon shekarun da sukai Basu San inda yake ba baisan inda suke ba kowa na tasa rayuwar?
Tayaya Ameenatou zatasan bashine asalin mahaifin Daya haifetaba?bama zata San wannan gaskiyar me rugusa farin cikinta ba a yanzu datake cikin tsananin farin cikin aurenta da Wanda take mutuwan so.

Tafiya yakeyi batareda ma yasan inda yake jefa kafafunsa ba sbd tinani da tashin hankali harma da tsananin bacin ran dayake Jin Yana tasowa Yana rufe dukkanin zuciyansa na bayyanar Omar gabansa.

Tafiya Mai Nisan gaske yayi batareda yasan yayi ba har Saida yaji kafafunsa suna Neman kasawa kafin ya tsaya Yana duba inda ya kawo kansa Bai saniba.,
Kafin ya sauke numfashin zafin zuciyar Dake cinsa lafiyayyar motan dake daukan idanuwansa ta tsaya gabansa Batareda an sauke glass ba Ahmed ya Bude motar ya fito ya Bude kofar Baya inda Omar yake zaune Yana kallan Babbahn Ahmed yace

"Bismillah"

Jajir idanuwan Babbah sukai Yana yiwa Omar wani kallo abinda ya danne shekara da shekaru Yana taso masa Mai tsananin zafi da radadin gaske harma ciwo me nauyi.,

Shima Omar Babbah din yake kallan gashi anguwar tsit Babu mutane sosai Kuma akwai duhu Dan haka Babu Wanda zaisan waye suka tsaya dauka.

Ahmed ne ya sake kallan babban Kai tsaye yace

"Ko zaa taimaka Maka ne gurin shigan??"

Maganar Ahmed ta Saka Babbah dagowa ya kallesa Jan idanuwansa na karuwa sbd yasan me Hakan ke nufi,

Ahmed shine Wanda ya kawo sakon yafe Ameenatou da Omar yayi tin tana kwana Daya da haihuwa a duniya Dan haka tsana da zafin Omar Dayake ji

daidai yakejinsu akan Ahmed.

Shima Ahmed a nasa bangaren zuciyarsa a shirye take da duka dangin Omar dana matarsa sbd Bai yadda da kowa ba akan Omar hakama zai iya taka kowa Babu ruwansa akansa,
Idan rayuwar Omar sukeso to tabbas saisun shirya daukanta Dan ba sauki ya shirya musu.

Abinda yake ji a zuciyarsa tsananta ta yanda ko numfashin iskan da Omar yake gurin Bazai iya shaqaba,
Hakama tayaya zasu fuskanci juna da Omar din?
Me zasu tattauna?
Meye a tsakaninsu?
Ameenatu ce Kuma ta rasu Dan haka ba sauran abinda ya rage Dan wannan Ameenatou din ya yanzu tasa ce Babu abinda zaisa ya tsaya ya sauraresa, idan ma zasuyi magana to yabari sai bayan daurin aurenta.

Takawa yayi a raba gefen Ahmed ya wuce Yana Jin kirjinsa na tsananta nauyi kaman numfashinsa ma zai toshe.

Motsawa Ahmed yayi zai bisa Omar ya dakatar dashi sbd Shima tasa zuciyar datai nauyi.

Tayarda motar sukai suka bar gurin sbd ganin kaman wata motar tafe Wanda Sam bayason asan Yama San Babbah sbd abinda ya lura ya karanta a tsakanin zuwansa zuwa yanzu shine su mamman basusan Ameenatoun itace Ameenatou Jden ba da suke tsananin nema Dan haka yanada Daman Hana auren ko dauketa kafin sanin nasu Wanda kowanne time zasu iya sanin Hakan sbd yasan sarai ana biye da takunsa da lamuransa shiyasa bayason bayyanarda sanayyarsa da Babbah.

Suna wucewa Babbah ya Nemi guri ya zauna Yana rintse idanuwansa sbd zufan Daya jiqasa me zafi,
Baisan ta inda zai fara barin Ameenatou tasan ba sune suka haifeta ba,
Idan ta sani kwata kwata bayason duniya tasan ita 'yar Omar Jaden ce sbd hatsarin da rayuwarta zata shiga me girma,
Ba Dan bayason Omar ya Hadu da 'yar tasa ne ba sai Dan barin su Hadu din asan yarsace komai zai iya lalacewa,
Ameenatou zata iya shiga hadari sbd ko bayan aurenta zata iya shiga hadarin duk da acikin masu arziki sosai zatai auren Amma Shima Omar din me kudin gasken gasken ne Amma aka tafi har cikin gidansa aka kashe Ameenatunsu tana cikin nakuda ba Dan Allah yasa Ameenatou rabo bace da yanxu baisan a wane matsayi rayuwarsa take ba Babu Ameenatunsa Babu abinda ta Haifa.

Ya jima a gurin zaune cikin tsananin damuwa da tashin hankalin da Bai Saka masa Rana ba Dan kuwa duk Jin yayi Lagos din fitar masa a Rai hankalinsa ya fara tashi matiqa.

Daqyar ya dawo da kansa gida sbd kirjinsa dayake wani irin ciwo da nauyi hakama zufa yake hadawa sosai ya kasa denawa.

Yana isowa gida ya shige daki batareda kowa yaga halinda yake ciki ba Dan sunacan sunata hayaniyar bikin da zaayi gobe Wanda Seelahs suka hada.

Omar ma yana komawa gida kusan damuwan tabasa tayi Saida likita yazo ya Danyi checking BP dinsa kafin ya shige cikeda damuwa Dan bayason nunawa Babbah karfinsa yanason ya aminta dashi suyi maganan Daya kamata kafin lokaci ya kure sbd idan ya nuna masa power kaman yaci mutuncinsa ne bayan Tsananin gata da son dayasan Yanawa 'yarsa fiyeda yanda yake son nasa yayan na cikinsa.

Ahmed dayaji shikam baida hakuri ko lokacin batawa akan lamarin Yanke shawaransa yayi Babbah dole ya saurare abinda ake son fada masa Dan Jin Wanda akeson aji daga garesa.

A cikin Daren jirgi ya sauke Jamaal tareda siddeeq a Lagos batareda sanin kowa ba Kuma a Daren yayi magana da Ahmed Wanda basusan Jamaal na qasar ba Shima Dan haka da safe siddeeq ne yaje mansion din Mam seelah ya dauko Haroon Wanda a ranar yake cikin farin cikin dayafi na kullum sbd daga ranar sai ranar daurin aurensa da mutanensa da yawa Shima suna Lagos Dan halarta daurin auren goben.

Wata lafiyayyar tsadaddiyar Lodge din da Jamaal yake siddeeq ya Kaisa Yana shiga Jamaal dayake jiransa ya fito tareda siddeeq din suka barsa acan sbd Jamaal din na buqatan ganin Dad Jden.

A rumfar hutawan Dake bayan mansion din ta gurin garden suke wadda ta hada kofofin gidajensu uku batareda saika zagayo ya gate ba kake shiga tanan Dan haka yasa familys din suke kaman a gida gade guri daga daga baya Baya gaban mansions din ba.
dukkaninsu ne a zaune su uku sai Ahmed na hudu suna zaune cikin Hutu da nutsuwan Wainda arziki da Hutu ya ratsa fira sukeyi Hakama table dayake gabansu tea ne kusan kala hudu a different tea set masu kyau da tsada sai healthy snacks na Manyan mutane sai wayoyinsu da Kuma jaridan yau.

A Jden mansion baa yadda motar kowa nene ta shigo gidan ba iya ta masu gidan ce kadai take shiga ta Kuma fita Dan haka siddeeq baima nufi gidan Kai tsaye ba mansion din Dad ya shige sbd securities ma na ganin motar

Haroon ce ta dawo suka wangale gate din ya shige da ita yayi parking.
##MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
49
https://chat.whatsapp.com/K3rO5UonX4GDVxtQbA5mZl

Assalamualaikum wa rahmatullahi ta'ala wa barakatuhu!!! Wannan group din dai na komai da komai ne. A taiqaice
*Farashin mu na daban ne compared to sauran Yan kasuwa
*Kaya masu kyau da quality. Abinda kika zaba shi za a Baki
* Swift delivery.watau waybill a sauqaqe da Yardar Allah
* Muna sake New Arrivals ka fin su cika Gari
* Muna iya duba maku kaya a good price ko da ba namu ba ne idan kuka Aiko da hoton kayan

Allah sa mu qaru da juna Ameen

****

Fitowa Jamaal yayi daga motan sanye da sweatset ash na Ralph Lauren wandon mara tsayi da kadan ya sauka gwiwansa kafarsa sanye da sneakers na Louis Vuitton Ash fuskansa sanyeda fcap da glass na Versace Kai tsaye hanyar garden din ya nufa sbd siddeeq Daya sanar masa securities since su Dad na can garden din gidan Sir Jden.

Cikin nutsuwa ya nufosu Kai tsaye idanuwansa na kallan irin zaman Hutu da bayyanarda kusanci,so da shaquwan da sukai Amma abin baqin cikin dukkaninsu ba Hakan ne a cikin ransu ba Dan haka yaji tausayi da tsananin son Dad Jden na sake shigan zuciyansa sbd mutum ne dayake da tabbacin Babu tsatsa a zuciyansa.

Dad Lameenu ne yafara Ankara da tahowansa ya gyara zamansa Yana zuba masa idanuwansa da Shima suke cikin farin glasses Yana kallan fatan kafafunsa Dake bayyane sbd wandon Dake jikinsa sai daukan ido takeyi a fili karara sirkin bature da Nigeria.

Mam ma juyawa yayi ahankali ya Kalli Jamaal din Yana sake fuskan Dan yanzu Haroon ya zama hasken idanuwansa,
Sedai murmushin nasa Neman sauyawa yayi sbd idanuwansa Jamaal suke nuna masa Dan kuwa tafiyan da class da kamewan duk na Jamaal ne yake Gani Amma ya kasa yadda da abinda idanuwansa ke nuna masa da sauri ya juya ya kalli inda lameenu yake shima Lameenu din shi ya kalla kafin suka Kalli Omar a tare Wanda idan Jamaal ne sun tabbatarda zai fisu ganewa sbd shine ya taso Dashi a gabansa har girma Kuma sun tabbatarda suna tare haryanxu din,
Idan har Omar zaizo auren Haroon sun tabbatarda Jamaal ma duk inda yake Yana cikin Nigeria Kokuma Yana hanyar sauka cikinta ayau din tinda gobe ne daurin auren.

Omar da kallo Daya yayiwa Jamaal ya gane waye ke tahowa a natse cikin kulawa da bayyanarda kauna ya saki fuska murmushinsa me kyau Yana fitowa idanuwansa akan Jamaal din Wanda Shima shi yake kalla murmushinsa daya kusan Saka shayin Lameenu biyowa ta hancinsa Ya saki ahankali da nutsuwa..

Yana isowa gurin Omar ya ajiye cup din hannunsa tareda miqewa tsaye ya ware masa hannuwansa suka rungume juna.

Qamshin Jamaal din Mam ya shaqa da kyau yaji bana Jamaal din bane sbd yasan Babu wani qamshi da a duniya zai Saka Jamaal sauya nasa.
Lameenu ma qamshin Haroon Daya shaqa din ya Saka zuciyarsa Dake tsallen rawa Dan daidaita Yana miqa hannu ya zari tissue din gabansa ya Dan goge goshinsa Yana kallan Mam Wanda yake a natse hankali kwance sedai tasa zuciyar aciki tafi ta lameenu shiga wani irin firgita da karyewa Dan ya dauka Jamaal ne ya bayyana gabansa.

Cikin nutsuwa Jamaal Daya dago yana kallan Dad Omar bayan sun saki juna da sauti mara karaje ko sauri yace

"Dad Omar barka da dawowa"

Muryan ya Saka Dad Omar sake kallansa sbd Haroon ne da sauran yayansu ke kiransa Dad Omar Amma Jamaal Dad J kadai yake ambatarsa dashi.

Yanda Jamaal ya fuske bayan maganar Yana rungume Ahmed Wanda ya miqe cikeda farin cikin ganinsa da kaunan dayake masa Shima Mai tsananin gaske Yana cewa

"JAMAAL my man"

Murmushi Jamaal din yayi Yana Dan janyewa yace

"Haroon ne, JEEY Bai isoba tukuna Banda tabbacin ma idan zaizo din"

Dad Omar dayake kallan fuskansa wani murmushi me kyau ya sake Yana dauke kallansa daga Jamaal din Yana cewa

"Haroon Yaya hidiman?farko daya iso Nima na duka Jamaal dinne sai daga baya na gane,
Kamannin nasu nata sake rudarwa haryanxu dai."

Ahmed ma Yana zaunawa yace

"Ni haryanxu bana banbance su,
Barr Yaya hidiman?
Inshallah zaka samu farin ciki da zaman lafiya da Kwanciyar hankali me dorewa bayan auren,my wishes kenan.

Murmushi Jamaal yakeyi Yana cewa "thank you, thank you"

Bai tsammanin tararda su Dad tareda Dad j dinba Dan haka dole ya sake Yana murmushi da sakewa sosai kaman yanda Haroon yakeyi sbd har lokacin

Daya gaida su Dad din idanuwansu dai a kansa suke sun kasa tantance mema suke Gani ko ciki,
Dad Lameenu idan ya shiga wani hali Baya iya boyewa da wuri ake gane Hakan a tareda dashi sbd tinda jamaal din ya taho gurin duk da sun shiga shock a farko Amma ganin dai da gaske Haroon dinne Amma kwata kwata ya kasa Dena hada zufa karshe dai haka ya ringa Neman rikicewa a zance.

Mam kuwa hankalinsa kwance yake ci gaba da maganarsa suna tattauna ci gaban da Haroon din yake samu sosai ayanzu akan manyan ayyukan dayake handling da yanda zai karbi babban nauyi akansa bayan auren.

Sun jima sosai a gurin kowa da abinda yake zuciya da cikinsa hakama kowa a tsananin mace yake Daya tashi yaje ya tattauna abinda yake ransa Amma hakanan kowa ya fuske suke cigaba da fira cikin walwala da farin ciki.

Sallan azahar ne ya rabasu bayan sunyi sallah kowa ya wuce Dan hutawa a gida.

Suna rabuwa Mam da lameenu office suka nufa,

Suna shiga Dad Haroon ya kira a waya Kai tsaye yace masa

"Menene Dayan alkawarin daka mun bayan na project????

Haroon dayake zaune a dakin Jamaal Yana cin abincin dayayi order Yana Jin tambayar yasan me Hakan ke nufi Dad Yana zargin Haroon din dayake gabansa Dan haka Kai tsaye yace

"Alkawarin Nemo Maka duk inda Magajin Dad Omar yake Kokuma bayanin da zai nuna mana inda yake"

Numfashi Dad din ya sauke kafin yace

"Kazo yanzu Nan Ina office ka sameni Kuma ka zo da takardun aikinsu Chris Jeremy."

Kashe wayar yayi Yan kallan kofa sbd ya ji abinda yakeson ji Amma Kuma idan har da gaske ne zai gane idan Haroon din ya shigo.

Haroon na kashe wayar siddeeq yafara kira ya sanar masa inda takardun suke ya dauko Kai tsaye yakaiwa Jamaal Daya fito sallan tareda Dad Omar sunason magana Amma dai dama Dan haka address kawai Ahmed ya bawa Jamaal Kai tsaye ta waya da time a yau din zuwa dare.

Haroon Kiran Jamaal din yayi hankalinsa tashe tsoro na ciked zuciyarsa ya sanar dashi abinda sukai magana da Dad din a waya kafin Jamaal din ya nufi office din Dad din.

Koda ya shiga Dad Lameenu Yana tsaye Yana Kaida kawo sbd haduwan Jamaal da Omar su nasu yazo karshe Dan Basu iya da Omar dinba shi kadai bare Jamaal da kaman ma su da suke iyayen sune suke tsoronsa sbd zai iya ruguzasu tinda yasan hanyoyin yin qasa dasu.

Mam kuwa Jamaal din na shigowa ya miqa masa hannu Yana kallansa yace

"Takardun Menene wannan din?

"Chris Jeremy's" ya Bada amsa Kai tsaye Kansa a kasa.

Dad na Jin Hakan ya jefar da takardun kan table Yana fuskantar Jamaal din yace

"Menene kake Jira haryanxu akan alkawarin daka dauka?
Kana ganin Dan gobe ne daurin auren Nan bazan iya dagasa fa har Sai abinda mukeso ya tabbata"

Dagowa Jamaal yai ya Kalli Dad din Kai tsaye Shima yace

"Ni nafara cika nawa farkon alkawarin komai ya tafi daidai sauran alkawarin da kayi na tabbatarda ka auramun yarinyar a gobe.....

Wuta Mam ya dauke Dad Lameenu kuwa dakatawa yayi daga Kaida kawon dayakeyi cikin rudewan zuciya da Kai Daya dauki zafi ya dawo gaban Jamaal din ya tsaya ya juya ya kalli mam dayake Jin kansa Shima Yana daukan wuta kafin ya sake dawo da kallansa Kam Jamaal kafin yayi magana cikin tsananin zafi da bacin Rai daya rufe Mam idanuwansa na rufewa zaiyi magana Lameenu yayi saurin taresa da cewa

"Ba lokacin fada bane muna tsananin buqatan sanin wani abu gameda magajin Omar ko yayane Kamun gobe a daura auren Nan,

Ana daura auren Nan zai juya ya tafiyarsa yabarmu batareda mun sani sani akan abinda ya sakamu tilasta masa zuwan na,

Jinina tafasa yakeyi Kuma bazai daina tafasa ba zuciyata bazata daina bugawan tashin hankali da baqin ciki ba idan bamu samu sanin abinda mukai shekarun Nan ba muna bibiyan son sani,

Rayukan da aka kashe duka an kashesu a banza,
Har matar Omar din dana yanka cikinta aka kashe duka an kashe a banza,
Hakama su kasim da jamilu da muka kashe da hannuwanmu duk da zamansu jini da Rabin jikinmu tin farko duk anyi a banza,
Duka a banza idan har daga karshen Nan bamu samu sanin abinda Omar ya haifaba da inda yake muka hadasa da Omar din muka kawar dukiyan ta shigo hannunmu,
Duka wannan komai da komai zai tashi a banza idan dukiyar Nan Bata dawo tamu ba,

Zamu rasa komai,zamu koma Asalin zero agaban Omar....."

Maganganun cikin tsananin zafi da radadi tareda tafasar zuciyar yake fadansu idanuwansa jajir Dan kuwa an daura auren kaman yanda suka samu labari Haroon kasar zai bari Dan su BB sun kawo masa tabbacin Haroon din yakai Ameenatou anyi mata passport ba tareda saninsu ba bayan sun San ko garin Lagos Haroon Baya bari Saida izininsu.

Jin wannan maganar a bakin Lameenu ya Saka Mam Jin kansa ya qarasa daukan zafi Shima zuciyarsa wani zafi takeyi a quntace ya kalli Jamaal da idanuwansa sukai wani irin mugun jajir hannuwansa na wata irin rawa ya dunqule hannuwan sbd rawan da sukeyi tayi yawan dayake Jin zai iya raba Dad Lameenu Kamanninsa na asalin mutum Dan haka juyawa yayi kirjinsa na nauyin da Saida yayi saurin dafesa Yana dafa table din gabansa sbd wani mummunan jiran Daya dubasa kansa ma Neman kasa daukan abinda kunnuwansa suka ji masa yakeyi sbd sunayen dayaji suna ambatar sun kashe da hannuwansu,

Mutuwan granny dinsa Dayake matiqar kauna yaji a bakin Lameenu cewan Dad ne.....wani irin sarewa kafafunsa sukai take ya durqushe a Gurin Yana riqe hannuwansa Dake tsananta rawa da zufa me tsananin gaske amma har lokacin Babu Wanda ya tsaya lura da yanayinsa sbd a rikice suke Suma da tashin hankalin Dan sun tabbata Jamaal na tafe wlh.

Lameenu ne yafara tahowa gurin Jamaal din da sauri Yana cewa

"Ka tashi kaje kaman yanda ayau ka rudar dashi da kamannin Jamaal kaje ayau a matsayin Jamaal ka tabbatarda kaji wani abu gameda inda 'dansa yake...

Mam Dayake kasa kallansa sbd baqin cikin halayen Haroon din wasu lokutan yace

"Alaqarsa da Babbah nakeson fara sani komai rintsi a Daren Nan kafin daurin

auren gobe sbd kada mu daura aure da Wanda bamusan me muka Saka kanmu a ciki ba Dan Omar din Shima zai iya komai Dan ganinmu a qasa Dan haka a yau ka tabbatarda kasan alaqar Babbah da Omar idan ba haka ba wlh bazan daura Maka auren Nan gobe ba"
##MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
50

https://chat.whatsapp.com/K3rO5UonX4GDVxtQbA5mZl

Assalamualaikum wa rahmatullahi ta'ala wa barakatuhu!!! Wannan group din dai na komai da komai ne. A taiqaice
*Farashin mu na daban ne compared to sauran Yan kasuwa
*Kaya masu kyau da quality. Abinda kika zaba shi za a Baki

* Swift delivery.watau waybill a sauqaqe da Yardar Allah
* Muna sake New Arrivals ka fin su cika Gari
* Muna iya duba maku kaya a good price ko da ba namu ba ne idan kuka Aiko da hoton kayan
Allah sa mu qaru da juna Ameen

****
Jamaal take yaji Yana Neman samun attack na zuciya sbd bugawan datakeyi Daya wuce kaida da sauri ya miqe sbd iska datai masa karanci
Saiga BB ya shigo office din Yana kallan Mam yace

"Ranka ya Dade P.A din Chris Jeremy ne ya iso karban Sako gurin Barr" ya qarasa fada Yana kallan Jamaal Dake kokari da yaqin Neman iskan Data kasa wucewa cikinsa.

Cikin zafi da bacin ran dayake cinsu ya fizgo takardun Daya zubar a table dazu ya miqawa Jamaal Kai tsaye yace

"Yi signing ka miqa masa ya basa"

Siddeeq Daya shigo office din Shima a lokacin shine ya karbi takardun cikeda girmamawa daga hannun Dad din ya kawo gaban Jamaal Wanda dakyar ya iya riqe pen din da aka basa yayi signing ya fice daga office din.

Miqawa BB file din takardun yayi yace yayi yace yayi scanning nasu a tura masa copy din ta email dinsa ko na Lameenu.

Karba BB yayi Shima ya fice daga office din ya Satan kallan jamaal Daya fice zuciyarsa na shiga shakku Dan kuwa shidai yau JAMAAL idanuwansa suka nuna masa ayau din ba Haroon ba Dan haka ya shiga shakka da tsinkewan zuciya Dan wancan Karan a abinda Bai wuce daqiqa nawa ba ya kakasu prison din da aka gana masu azabar da take tayi kusan sanadin rayukan yaransa biyu.

Bayan ficewansu Dad Lameenu da sauri ya dauki wayarsa Yana sake hada gumi ya kira likitansa Dan Jin yakeyi kaman hawan jini zai sake kama sa.

Mam kuwa zaunawa yayi Babu abinda yake tafasa zuciyarsa da sake cike ta da baqin ciki da zafi sai murmushi da nutsuwan dayake cikeda rayuwan Omar tareda Kwanciyar hankali Dan sun tabbatarda ko crisis na business Baya samu idanma ya samu a take Ahmed ke handling nasu batareda da Omar y samu ciwon Kai ko damuwa ba a wuce gurin.

Amma su gasunan gaba Daya rayuwarsu kullum cikin tashin hankali da fargaba suke da shakka da baqin ciki duk da suna cikin arzikin Amma kwata kwata basuda nutsuwan zuciya Dana fili Dana boye musamman shi Baya tareda 'dansa dayake cikin zuciyarsa fiyeda komai.

***Jamaal na fitowa siddeeq ne ya taimaka masa ya Isa mota yana shiga ya rufe masa ya zagaya da sauri yaja motar suka fice daga Mansion din cikin mugun speed siddeeq na saukan masa da dukkanin glss din motar sbd ganin yanda idanuwansa da sukai wani mugun ja ya rintse su numfashinsa na fita ba adaidaiba.

Suna isa Haroon da tinda Dad ya kira hankalinsa ya kasa Kwanciya Yana ganin Jamaal yaji gaba Daya gashin jikinsa ya tashi da tsananin tashin hankali sedai Jamaal kwata kwata Baya son komai face shiga dakinsa ya fasa abinda yakejin ya tsaya masa a kirji sbd yau yaji abinda ya jijjiga jarumtarsa da karfin halinsa.

Rufe kansa yayi a daki Wanda ya Saka Haroon juyowa da Sauri ya Kalli siddeeq kafin yayi magana siddeeq din ya girgiza masa Kai Kai tsaye alaman baisan komaiba tukuna.

Sake tashi hankalin Haroon yayi ya Isa kofan da Jamaal din yake ciki yayi knocking Yana Kiran sunansa cikin tsananin kulawa da fargaba.

Ganin ba alaman sauki ya Saka Haroon din karban key dinsa motarsa hannun siddeeq ya fito Kai tsaye gida ya ko zai fahimci wani abin.

Koda ya Isa gidan duka a hargitse da Yan biki da hayaniya sbd evening event din da zaayi a ranar mutane sun halarto manyan motoci Tako ina da securities Dan haka baima yi cikin gidan ba da Ayeesha ya Hadu ta sanar masa Dad Baya Nan duka matane cikeda da gidan anata Shirin tafiya event din wadda aka kashewa kudi bana wasa ba dan ita kanta amaryan kayan da zata Saka a ranar daga Dubai mum Atee Tayo odansa da duk abinda zaka Saka a event din hakama masu makeup dinma professionals aka aika na musamman Dan shirinta.

******Dad Baya gidan ya fita Dad Lameenu kuwa Yana samansa Yana hutawa sbd jininsa daya Dan hau likita ya basa shawaran hutawa jinin ya daidaita.

Hakan ya Saka Haroon komawa side dinsa Yana sakawa da warwara cikin matsuwa da kaguwan dawowan Dad ga mum dinsa ma ta kirasa Bata samu s

Jirgi ba aranar sai washe gari zata iso kusan ma ba zata samu aurenba Dan Koda zata iso kilama amaryan ta tare.

Bangaren Jamaal dayafi na Haroon din girma sosai aka gyara tareda zuba komai na Jin dadin rayuwa masu kudi sabo a cikinsa Nan amarya zata tare su umman fadila ne suka taho suka sake gyara komai tareda Saka abinda suka kawo na turarukan wuta da duka abubuwan da aka Siyawa Ameenatou din suna gamawa suka koma Dan nasu Shirin na tafiya bikin ranar.

Har lokacin event yayi Dad Bai dawo ba Dan haka dole Haroon ya fita yabar gidan Dan zuwa dubo Ameenatou wadda tana can ana shirinta Kuma ladies event ne kawai Dan haka tace saiyazo yaga kwalliyanta kafin kowa ya Gani.

Yana barin gidan Dad na dawowa lokacin duka an tafi bikin Babu kowa a gidan sai masu aiki Dan haka abinci kawai yaci a dining din palonsa ya huta sosai kafin ya fito ya nufi office dinsu Dan Kiran duba sakon da Chris Jeremy yace ya turo ta email ayi gaggawan dubawa.

Yana shiga office din BB ya shigo ya sanar masa tin jiya suke bibiyan Omar Kuma tabbas sungano alaman magana yakeson yi da Babbah sbd a masallacin anguwan babban yayi sallan magrib Dan ishai jiyan hakama yau acan yayi azahar da laasar yanzu ma daga can suke.

Mam na Jin hakan ya dago idanuwansa ya zubawa BB din Yana Jin kansa na shiga tinani.

Wayarsa ya dauka ya Saka Kiran Lameenu Wanda Shima ya gama hutawan zaune yake Yan amsa wayoyi saiga kiran Mam din ya dauka Yana Jin Abinda Mam yace ya kashe wayar tareda miqewa tsaye ya fito sanyeda jallabiya fara qal da wayarsa a hannunsa sai farin glass dinsa Dake fuskansa.

Mam na shigowa kafin yace komai Kiran Chris Jeremy ya sake shigowa wayar Mam Dan haka iPad dinsa ya dauka Dake kan table ya kunna Ya shiga duba sakon.

Abinda yagani je ya sakashi ajiye iPad din gefe ya miqawa BB hannu ya dauko masa glass dinsa na qara Gani dakyau ya miqa masa ya karba ya goge da tissue da kyau kafin ya Saka ya sake daukan iPad din ya sake dubawa dakyau.

Numfashi ya sauke ahankali tareda rintse idanuwansa ya Bude fes akan iPad din hannunsa zufa na tsatsafowa daga goshinsa Wanda Hakan ya Saka Lameenu daga Kai sama ya shaqi iska me zafi sbd ganin abinda ya Saka Mam zufa daga gashi to ba qaramin balbalin balai bane Dan haka hannuwansa

suka jiqewa da zufa Yana zuba dukkanin idanuwansa da Kunnuwansa akan Mam din Yana jiran Jin Abinda zai fada.

Mam dago jajayen idanuwansa dasukai jajir din a take ya Kalli BB yace bani copies na takardun file din Chris Jeremy.

Da sauri BB ya juya ya nufi locker dinsu ta takardun sirri ya Saka pin ya Budeta cikin sauri ya Nemo takardun Daman sune a sama Dan shine ya ajiyesu bayan yayi scanning da photocopy dinsu.

Yana kawowa Mam da sauri ya karba hannuwansa na rawa ya budesu zufansa na karuwa ya jefa idanuwansa a inda signature din Jamaal take wadda tabbas tabbas da gangan Daman Jamaal yake Saka signature dinsa a duka aiyukan masu mahimmanci sbd signature din Haroon daban tasa daban Dan haka aiki bazai taba yiyuwaba Saida Wanda Saka hannunsa yake ciki shikuma Baya Nan Dan haka sunaji suna Gani zasu ringa rugejewa Daya bayan Daya.

Sakin file din Mam yayi da sauri Yana miqewa ya nufi locker din da kansa ya fizgo dukkanin files dinsu dake ciki na aikin miliyoyin da biliyoyin kudin da zaayi bayan auren dansa
Hannuwansa na wata irin rawa da jijjiga ya ringa budesu Daya bayan Daya Yana duba signing din dayake cikinsu duk na Jamaal Seelah ne ba Haroon seelah ba.....

Kasa tsayuwa yayi ya zube a kujeran datake gurin zufansa na tsiyaya kaman ya hadiye kunama da ranta.

Lameenu dayake tsaye Yana kallan Mam zufansa Tama Fi ta Mam din Dan kaman ana gobara a cikin jikinsa haka yakeji dakyar ya iya tattara yawu ya hadiyewa makoshinsa Daya Bushe yace

"Jamaal ne ko??
Jamaal ne ba Haroon ba,
Signatures din duka na JAMAAL ne ko??
Shine yake tareda mu duk tsawon lokacin Nan?
Shine yake tsaye a gabanmu da bakinmu mum sanar dashi har abinda Haroon Bai saniba ayau din sbd Haroon baisan dukkanin wainnan da na lissafo ayau mune da hannuwanmu muka kashesu ba.....

JAMAAL me mukai Maka??
Wane balai da masifa ne wannan?
Wace masifa Haroon ya sakamu bayan tarin wadda take gabanmu...

BB ma da tini zufan ta katse masa cikin fargaba da shakkar abinda zai iya biyowa Baya kallan Mam yai Wanda zuciyarsa ke Neman bugawa sbd zufa yakeyi sosai hakama zuciyarsa Bata bugawa daidai.,

Lameenu kujeran datake kusa dashi yayi saurin zaunawa Yana cewa

"BB yi sauri kirawo likita ya dawo bana Gani zuciyata Bugawa zatai jinina ya mummunan hawan da baa so yi sauri kirawosa"

Daga Mam din har Lameenu jininsu mummunan Hawa yayi dole Akai gaggawan Kiran Dr Koda yazo Lameenu yafi Dad shiga Mummunan hali Dan haka shi aka fara dubawa kafin Dad Wanda shi zuciyarsa bugawa take Neman yi kawai.

Dr na fita Haroon da BB ya sanar da Dad na Nemansa Yana shigowa BB ya rufe kofar.

Haroon dayake kallan Dad Lameenu dayake numfashi ahankali ahankali alaman ba cikakkiyar lafiya mayar da kallansa yayi gurin Dad dinsa Wanda ya dago jajayen idanuwansa yayi masa kallo Daya na tsaftan gaske ya tabbatarda Haroon ne a gabansa take ya daga hannu ya sauke masa wani mahaukacin Marin Daya Saka gefen bakin Haroon din fashewa da jini.

Dagowa yayi bakinsa na jinin ya Kalli Dad din sedai wani Marin Dad ya sake saukar masa Mai zafin dayafi na farko.
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400

Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
51
Radadin Marin Kai tsaye a zuciyarsa yake sauka wadda take tarwatsewa aduk lokacinda mahaifinsa ya Saka masa hannu duk shekarun dayake dasu Wanda da yayi auren wuri da tini ya Tara Yara biyu ko uku.

Jajir idanuwansa sukai a karo na farkon dayaji zuciyansa na tabbatar masa da shidin ba komai bane a Gurin Dad Kuma har abada bazai taba zama komai ba a gurinsu,

A zero yake gabansu Kuma a haka zaici gaba da zama..

Yanda zuciyarsa ke radadi da qunan dayake tafasa jininsa haka ta Dad dinsa ke tafasa ya kallesa da jajayen idanuwansa yace

"Ayau nayi baqin kasancewa Wanda ya haifeka,
Nayi baqin ciki da Dana sanin barinka a qarqashin inuwata sbd har abada bazaka taba zama me amfani ba,
A yanda Aleena ta haifeka ba komai cikin kanka haka ka girma Babu komai a cikin kan naka dayekeda amfani ko buga Maka lissafi Mai amfani.....

Tsananin 'dacin maganganun ya Saka Haroon rintse idanuwansa dasuke tsananin radadi sbd Jan da suke qarawa hannuwansa na rawa kansa na sarawa ahankali ahankali Yana qara qarfi.

Dad Lameenu da ayau tsaban shock baida karfi ko kadan a zaune yake Yana Jan numfashin wahala da 'dacin zuciya Bude Baki yayi yace

"Ban taba daukan karshenmu a hannunka zai faro ba Haroon sai ayau din,

Ban taba sanin jinin kafiran dayake yawo a jininku na mahaifiyarku zai taba aiki a kanku ba wataran sai yau,
Haroon Ashe bakada Imani bakada ha nkali???
Tin yaushe ne Jamaal yake acikinmu batareda mun saniba???
Tin tsawon yaushe muke kirari muna dabawa kanmu wuqa a gabansa batareda mun saniba??
Jamaal da yayi alkawarin saiya mayar damu mabarata kafin ya San sirrinmu kenan yanzu Daya San hatta yanda muke kalan numfashinmu kana tinanin a mabaratan zai barmu yanzu???
Wlh Jamaal Saiya tabbatarda ko Baran idan munyi bazaa bamu sadakar ba..... innalillahi wainna ilaihirrajiun,. innalillahi wainna ilaihirrajiun,

Kallan Mam yayi jininsa na sake hayewa a rikice yace

"Wlh mamman Jamaal bazai rasa hada kwararan shedu akanmuba,
Bazai rasa recording na wasu maganganunmu ba.....

Kirjinsa ne ke Neman rikewa Dan haka BB Dake tsaye Yana jiquwa da zufan Shima yowa kan Lameenu Yana masa fifita duk da sanyin AC Daya cike office din tsaf Amma dukkaninsu a jiqe suke da zufa.

Mam dayakeji zuciyarsa na tinkudo masa baqin cikin duniya da bacin Rai kallan Haroon yayi Wanda jikinsa keta tsananin rawan Dayake nuna da ciwonsa yafara tasowa Daman gashi tinda ya dawo mum Atee ta Dora daga inda ta tsaya.

"Haroon kaman yanda ka ha'ince ni kabi shawaran Dan uwanka da mahaifiyarsa kuka sakani wannan baqin cikin wlh saina nin ka masa Wanda yafisa Dan bazaka auri wannan yarinyarba wallahi indai nine na haifeka,
Bazaka samu farin cikin dakake tinanin zaka samu ba idan ma ka gujeni ka komawa mahaifuyarka,

Kaman yanda kuka rusamu wlh dakai zamu dawwama acikin wannan baqin cikin da rashin Dan kuwa idan baka sani ba ka sani wannan ciwon haukan Daya kwakwalwanka Babu inda zan zaka Daya wuce na tattara ka na aikaka asibitin mahaukata Koda kanka zai Bude,

Idan har lissafina ya buga daidai Dan uwanka yanda yake kwararren likita na tabbata ya karanci yanayinka Kuma bazai rasa bincike akan abinda ya fahimta tareda Kai ba Dan haka zuwa yanzu yasan mummunan Nisan da qwaqwalwanka yayiba a Juyewa Dan haka ka Saka aranka Babu maganar aurenka gobe wlh....

Dad Lameenu dayake cikin mawuyacin hali har lokacin dagowa yayi yace

"Yanda Babbah ke son 'yarsa har abada bazai tabawa me tabin kwakwalwa auren yarsa ba kome zaayi kuwa Dan Haka takardun asibitinka kawai zamu basa a Daren ba sai gobe ba,
Maza ma ka fice ni ko ganinka Haroon a yanzu banason yi qaramin hawan jini yakeyi,
Ka cucemu Kaci amanar mu Kaci amanar kaunar da mahaifinka yake Maka.

Zuwa lokacin Haroon ba iya hannuwansa kadai ne suke rawa ba dukkanin jikinsa jijjiga yakeyi sosai hakama kansa tini yayi wani irin mugun nauyi Yana Neman inda zai fara bugasa bakinsa yakeson budewa Yayi magana Amma Dad Shima ko ganinsa bayason yi a lokacin sbd zai iya masa Baki idan Bai bar gurinba Dan haka Dad dinne ya fice Kai tsaye ko gabansa Baya Gani sbd Shima jininsa yayi mugun hawan Daya wuce misali.

Daqyar yakai kansa cikin gida yayi samansa ya shige bedroom dinsa Dan har lokacin Babu kowa a gidan Yan biki suna gurin bikin.

Dad Lameenu ma BB ne ya taimaka masa ya fice.

BB ne ya dawo office din ya kama Haroon daya qanqame gabaki Daya Yana rawan jiki sosai yakaisa har palonsa ya dawo ya rufe office din ya fice daga Mansion din.

Haroon rarrafawa yafara yi idanuwansa na ganin duhu da haske yafara kokarin Kai kansa bedroom Amma ya kasa sbd wani kifewa da yayi akan console mirror dayake hanyar bedroom din ya fado masa ya fashe.

Bugawa kansa keyi sosai hakama hannuwansa rawarsu ta tsananta sosai har tayi muni hakanan ya sake dafawa ya tashi cikin glass din Yana dafa Bango ya Isa kofar dakinsa yana shiga ya zube qasa Yana buga kansa sosai a tiles idanuwansa Dake rufe suna sake birkicewa.

Siddeeq kaman yasan abinda yake faruwa a mansion din ya dawo daukan Haroon sbd acanma Haroon jikinsa ya rikice zazzabi Mai karfin gaske da Bai taba yin irinsa ba ya rufesa Wanda ya bawa siddeeq tsoro hakama mum datake Kiran yayan nata Babu me dauka siddeeq din ta kira tanajin Jamaal ba lafiya taji hankalinta ya tashi Amma Kuma wannan Karan rashin daukan wayar Haroon yafi daga hankalinta fiyeda ciwon Jamaal Dan haka tace siddeeq ya dubo mata mansion din zuciyarta takasa samun nutsuwa.

Koda siddeeq ya Isa halinda ya samu Haroon yayi mugun girgizasa Dan Bai taba ganinsa a irin wannan mugun halinba duk tsananin ciwonsa kuwa.

Da gudun gaske ya qaraso inda yake ya tallafosa sedai Haroon din yayiwa kansa mummunan rauni jini Tako ina Dan haka a haukace ya daukosu gaba Dayansa ya fito dashi Bai tsaya wata wata ya Saka mota sbd ba qaramin munu lamarin yayi ba ya fice dashi zuwa asibitin SEELAHs din da gudun gaske.

Yana Isa aka karbi Haroon din da gaggawa Dan tini ya fice hayyacinsa Wani jijjiga kawai yakeyi sosai kaman me wani ciwon daban.

Fadan tashin hankalin da siddeeq ya shiga a wannan lokacin bamai yiyu bane sbd ya shiga tsoro Mai girma wannan Karan da ciwon Haroon din ga Jamaal a kwance ba lafiyan Shima.

Haroon sosai ya wahala cikin azaban ciwonsa Babu uwa Babu Uba Babu wani nasa sai siddeeq Wanda ya tsayu akansa har Saida ya dawo daidai sbd cikin qanqanin lokaci Allah ya mayar dashi kaman ba shine angon da zaa daurawa gobe ba.

Duk karfin zuciyarsa siddeeq sai dayaji tausayin Haroon ya karyasa sbd bayan dawowansa daidai Hawaye ne masu tsananin zafi da radadin zuciyan gaske suke gangaro masa batareda yace komaiba.

Sallan magrib siddeeq yake yaji daga can ya koma hotel ua dubo yanayin Jamaal Wanda ya Riga ya miqe haryayi wanka yayi Sallah
Siddeeq din na zuwa ya sanarwa da Jamaal halinda Haroon yake ciki.

Karban key Jamaal yayi shi kadai ya nufi asibitin gurin Dan uwansa.

Zuwansa asibitin Haroon na ganinsa hawayen tsananin kaunar Dan uwansa daya tabbatarda duk duniya ko mum dinsa Kila Baya kaunarsa yanda Jamaal din yake sonsa ne suka ciko idanuwansa suna gangarowa.

Jamaal Daya kasa masa maganar abinda ya faru ayau din sbd ganin yanayinsa daukansa yayi suka baro asibitin Babu me magana shiru kowa da abinda yake tinanin Amma dai shi Haroon zuciyarsa da jikinsa gaba Daya a Sanyaye suke sbd rayuwarsa yasan daga yau ta dena moruwa ne sbd aurensa dayasan har abada Dad bazasu taba barin ayi aurenba,

Rasa Ameenatou garesa tamkar zare control na tabin kwakwalwansa ne kaman yanda su Dad suka fada Dan haka idan har tabbas gobe ya tabbata ya rasa Ameenatou to ya cire Rai daga komawa daidai,

Yasan Jamaal da mahaifiyarsu zasu shiga tsananin qunci da baqin ciki akan Hakan Amma Shima kansa a yanzu yasan ko da auren Ameenatou ko Babu tabbas tabin kwakwalwa ne a tattare dashi me tashi Kuma me tsananin gaske.

Rintse idanuwansa yayi ahankali maganganun Dad da fushinsa da Bai taba Ganin irinsaba suna dawo masa a kunnuwansa take yaji ciwonsa na Neman sake dawowa ya dago jajayen idanuwansa ya Kalli Jamaal dayake tuqi a natse Shima zuciya da kansa duka a jagule da lissafi kala kala.

Cikin wata murya me sanyin gaske data Saka zuciyar JAMAAL sanyi akan fushi da bacin ran dayake ciki akansa
yace

"Jamaal,
Kayi mun alkawarin ganin na auri macen danake so matiqar ba Allah yariga yayi cewan ba matata bace,
Ko ban auri AMEENATOU a gobe ba Kai inason ka sheda itace macen danake so fiyeda komai a duniya bayan Kai da mum,
Son AMEENATOU wata jarabtace da Allah ya jarabceni da ita,
AMEENATOU itace macen da zanso har karshen rayuwata Kuma itace mace Daya da bayan ita Babu macen da Nima zan iya so.

Ko ban auri AMEENATOU ba bazan iya rabuwa da ita ba Dan haka Dan Allah Jamaal Karka bari su dadi su hanani samun farin cikin aurenta,

Aurenta shine Abu na karshe da zanzo kafin rayuwata tabar duniya.....

Shiru Jamaal yayi masa har suka Isa mansion ya shigo dashi har cikin harabar gidan wannan Karan shine da kansa ya fito motan tareda Dan uwansa dukkanin securities din gidan da sauran Jamaar dasuka dawo event suna harabar gidan mutuwar tsaye sukai ganin su biyun a tare Kuma kusan kamannin Babu Wanda zai iya banbancewa bayan raunikan Dake fuskan Haroon sai Kuma haske da jamaal yafisa sosai.

Mam da lameenu wainda suka Fito masallaci sallan ishai daqyar sbd radadin da zuciyoyinsu suke ciki mutuwar tsaye sukai lokacinda suka kawo su Jamaal dinma sun kawo cak kowannensu ya tsaya Mam ganin 'yayan nasa a gabansa tare sai yaji zuciyarsa na narkewa da tsananin kauna da kewan kasancewa inuwa Daya dasu.

Lameenu kuwa kallo daya yayiwa jamaal yaji jininsa na son Hawa da sauri yai gaba

Shima Dad kafin kowannensu ya motsa ya gaidasa gaba yayi batareda ya waiwayosu ba ganin Haroon kawai Yana tafasa ransa.

Jamaal ajiye Haroon kawai yayi ya juya yabar gidan Kai tsaye gidan da zai Hadu da Dad Omar a daren ya wuce Yana kallan time.

Suma acan bangaren tin ana sallan ishai Yana fitowa masallaci Ahmed yayiwa Babbah abinda baisoba waton nuna masa power Kai tsaye sojoji ne suka daukesa daga kofar gidansa suka wuce dashi shi kuwa Haroon da Jamaal na ajiyesa ko zama baiyiba Shima ya fice gidan yayi gidansu Ameenatou Kai tsaye Yana Isa motar na wucewa da Babbah Dan haka ko gidan Bai shiga ba Shima yabi bayansu.

Sun isa da Babbah motar Jamaal ma na Isa Dan haka kusan da Ahmed din da Babbah dayake kallan Jamaal da dukkanin Idanuwansa da tsoro da shakka harma da fargaba tare suka shigo palon da Dad Omar din yake zaune.

Dayake bayason asan da Yana gurin ko makamancin Hakan ko securities Babu a gurin sbd guri ne da bazata taba tinanin samunsa agurin ba bare a biyosa.

Su kansu su BB Dake bibiyar Babbah ganin sojojine suka daukesa sai basuyi gangancin binsu ba sbd yanzu a ankare suke tinda Jamaal ya bayyana komai zai iya faruwa juyawa sukai Dan sanarda dasu Mam.

Haroon da Shima ya shigo da motarsa gurin yayi parking Yana ganin motar Dad Omar data Jamaal a gurin bayan Kuma yaga lokacinda sojojin suka ajiye babba suka fice take kirjinsa ya sake daukan nauyi Yana bugawa Dan haka Kai tsaye ya wuto ciki Shima.

Babba ne yafara maganarsa Kai tsaye da cewa

"Meyasa ka gayyato Haroon anan??
Kanason yasan ko Kai din wanene?
Kanason yasan kaine asalin mahaifin AMEENATOU wadda ka tsallake ka bari ranar da aka haifeta????

Cak Haroon ya tsaya bakin Kofar batareda ya qasara shigowa ba sbd gagaruman kalaman Babbah da suka shiga kunnuwansa.
#MAMUH
#DR JEEY SEELAH
#AMEENATOU SEELAH
#UNEXPECTED

#CRAXYLOVE
#ROMANCE
#DEEP
#LA HOT

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!! _**_Arewabooks@Mamuhgee_*
52
Dip yaji jinsa Dan ganinsa na Neman daukewa sbd tsananin girgiza da rikewan abinda kunnuwansa suka ji.

Hannunsa Daya iya dagowa da kyar ya bubbuga kunnensa Dan Jinsa Daya dauke take ya dawo idanuwansa da Basu koma daidai ba suna sake rikidewa Dan Bai taba jinsa cikin mummunan tashin hankalin dayake Jin kansa a

daidai wannan lokacin ba idan har AMEENATOU dinsa itace jinin Dad Omar din dasu Dad da shi kansa suka ringa dakon nema a tsawon shekarun Nan.

Babbah kuwa da zuciyarsa har lokacin radadin gaske takeyi kallan Omar din yayi Yana cigaba da cewa

"Me kace akan Ameenatou din?
Zaka Nisanta damu sbd Bata kariya
To meyasa ka dawo?
Shin ka manta irin masifar da kusancin naka da ita zai iya jawowa?

Sanyi muryansa tayi jikinsa da bakinsa na rawa cikin mutuwar jiki yace

"Ameenatou itace hasken zuciyata da idaniyata,
Ameenatou itace walwala da farin cikin rayuwata data iyalina,
Ameenatou ita kadaice jinin jinina Danake Gani,
Ameenatou itace nake kallan tawa Ameenatu din a cikinta meyasa zaka dawo Omar?
Meyasa zaka dawo daidai lokacinda take gap da samun farin cikin rayuwarta?
Omar na rokeka da Allah ka koma inda ka fito batareda kowa yasan alaqar da muke da ita dakai ba,
Ameenatou batasan tayaya zata fara karban cewan ga mahaifinta ba a tsaye gabanta wani ne ba ni ba....

Su kansu sirikanta Babu ta yanda Rana tsaka a ranar daurin auren kawai ace musu wani ne mahaifinta ba Wanda suke tinanin sun karba auren a hannunsa ba,

Hakama sanar dasu Hakan dole muna buqatan yimusu qarin bayanin yanda Akai tabar hannun mahaifinta ta dawo nawa hannun,
A wannan gabar me zamu ce musu?
Me zamu sanar musu?
Cewa zamuyi anyiwa mahaifiyarta kisan gilla a gaban idanuwanmu aka yanka cikinta da cikin wata Tara a jikinta????
Ce musu zamuyi a hannuna jininta ya tsayaye Ina kallo ta sadaukar da rayuwarta ta haife cikin jikinta bayan yankan wuqar daya Huda cikinta da kirjinta???
Ce musu zamuyi a wannan ranar da aka haifeta ka tsallake ta ka barta duk akan ana bibiyar rayuwarka zaa hallaka ka??

Jamaal Da kusan Shima mutuwar tsayen yayi sbd shock da tarin mamaki da hada sauran bayanan dayaji a bakinsu Dad da bakinsu ayau din komai Yana haduwa acikin kansa Amma Jin irin kisan da Akaiwa Aminatu a bakin babban

ya Sakasa rintse idanuwansa Yana Jin kaman jiri zai daukesa,

Meyake faruwa a duniyar Nan da suke ciki ne?
Wane irin buri ne da son duniya ya Saka su Dad shiga wannan mummunan qazamiyar kaddarar ta kashe kashe irin na zallan rashin Imani????
Bayan irin kisan da sukaiwa Aminatu matar Omar din mahaifiyar Ameenatoun ahakan suke sake bibiyan rayuwarta Baji ba Gani Dan su qarasa aikin da Basu qarasaba shekaru..... innalillahi wainna ilaihirrajiun,
Innalillahi wainna ilaihirrajiun?

Omar shiru yayiwa Babbahn idanuwansa jajir Yana Jin zantukansa na shigarsa suna dawo masa da komai tareda yanka zuciyarsa.

Ahmed ne ya katse babban cikin radadin zuciya da kasa dannewa da cewa

"Duk wannan abin da kake fada akan rabuwarsa da gujewansa tareda bawa Ameenatou kariyan da Kai da tasa sadaukarwan zasu tashi duka ne a banza Dan da hannuwanka gasunan zaka miqawa wainda ke bibiyan rayuwar tasa da tata ita a bainar jamaa gobe..
Da kanka zakai kirari ka dabawa kanka wuqa sbd su sirikan da kake magana sune jinin Omar din Kuma sune masu Neman jinin nasa.

Wani kallo Babbah ya juyo Yana yiwa Ahmed kafin ya mayar da kallansa kan Jamaal da Daya kasa kallan kowannensu Idanuwansa jajir Yana rintse su sbd kunyar abinda duk ake fada ana magana ne akan rashin Imani da Barnar mahaifin Daya haifesa.

Kan Omar Babbah ya mayar da kallansa Yana Jin zufa na tsiyayowa har ta cikin kansa da kunnuwansa Dan haka ya zare hular kansa yayi wurgi da ita Yana cewa

"Omar me nake ji?
Me yake faruwa?
Menene yake Kuma Shirin faruwa?
Shin balain ne ya dawo da masifar kokuwa wace balain ce take Shirin dawowa??
Meye hadinka da SEELAHs???

Kallansu yakeyi Daya bayan Daya a rude Yana Neman Karin bayani Dan kansa Neman Juyewa yakeyi da tashin hankali da tsoron abinda zai iya faruwa idan wani abu ya samu Ameenatou dinsa.

Omar ne ya dago tareda tashi tsaye Yana fuskantar babban idanuwansa jajir yace

"SEELAHs shine Nima nawa asalin sunan ba Jden ba?
Mamman seelah, Lameenu seelah, Omar seelah da Yan uwanmu biyu da suka rasu kasim da jamilu seelah Yan uwan jini muke,
Dukiya itace ta lalata jinin dayake yawo a jikin kowannenmu na alkawarin tsira tare mu mutu tare,

jinin yan uwanmu ne Daya zuba akan dukiyar ya gurbata dukiyar ta Saka mu samun Kanmu a mummunan halinda muke ciki a yanzu na bibiyan rayuwar Yan uwanmu Amma ka sani har abada bazan iya rabuwa da yata ba a yanzu kaman yanda nayi alkawarin Bata kariyar da ban samu bawa mahaifiyarta ba,

Ameenatou a yanzu itace babban abinda duk wani maqiyana yake Neman samu,
Ameenatou itace mukullin dayake riqe da duk wani abinda Dana mallaka,
Ameenatou itace mamallakiyar dukkanin tarin dukiyar Jden a rubuce Dan haka samunta a shine mafi farin cikin cikan burinsu,
Sanin wacece Ameenatou shine babbar hatsari da tashin hankalin da dukkaninmu zamu fuskanta Dan haka Babu maganar aurenta a goben Dan har abada bazasu taba Dena Neman ba har sai ranarda suka samu sanin waye magajin dukiyar jdens gaba dayanta.

A rubuce dukkanin dukiyata da abinda na mallaka nata ne,
Ahmed ya sani ayau Kai da Jamaal inason Kuma ku sheda Hakan sedai ku sani barin asan wacece ita shine karshen komai.

Kallan babbah Daya gama jiqewa da zufan gaske hankali tashi yayi kafin ya Kalli Ahmed ya zaune dashi ahankali ya fara zayyano masa asalin tarihinsu da komai tin daga barowansu gaban iyayensu har zuwa yanzu da suke maganar.

Kuka wiwiwi Babbah keyi dukkanin jikinsa na rawa sbd shiga tashin hankali da tsoron rayuwar dasuka samu kansu dumi dumi aciki ta masifar da Bai taba ji ba...

Jamaal ma kusan silalewa yayi kan kujera wannan Karan da hannuwansa biyu ya Saka Yana rintse idanuwansa sbd kansa Dake Neman bugawa tareda zuciyarsa....

Ahmed ma da tinda yake da Omar din baisan asalin asalin mafarin komaiba sai yau din sbd kaf duniya yanzu Babu Wanda yasan ba uwa Daya Uba Daya SEELAHs suke ba sai yau din,
Ko Jamaal da Haroon dasuke yayan cikinsu da matayensu Basu taba sanin wannan sirrin ba sai yau din da Omar yake fada musu da bakinsa cewan ba

uwa Daya Uba Daya suke ba...

Dukkaninsu Dake palon silalewa sukai qasa kowa kafafunsu na kasa daukansu,

Duk tsananin jarumta da karfin halin Jamaal Hawaye ne suka ciko jajayen idanuwansa yanajin wani abu me nauyin gaske ya tsaya ya tokare kirjinsa sbd baqin ciki da radadi tareda kunyar abinda ake fada mahaifinsa na ciki,

Makashi ne ya haifesa?
Makashin Yan uwansa da wainda Basu da hakkinsu na komai shine mahaifin Daya haifesa,
Mahaifinsa shine makashin kakanninsa da macen da harya mutu bazai taba Dena Sonta ba.....
innalillahi wainna ilaihirrajiun,
Innalillahi wainna ilaihirrajiun

Babbah kuka yakeyi sosai hankalinsa da gashin jikinsa duka suna tashi,

Shi kansa Omar da sai yaune ya Bude Baki ya iya furta abinda yake ransa qunshe tsawon shekarun Nan Bai taba maganar dayake cin zuciyarsa Yana saukar masa da radadi mafi ciwo na yanda shi da Yan uwansa suka kasance,
Tin suna Shan nonon iyayensu suke tareda juna a guri Daya aka haifesu suka taso tare batareda ko a takalman sakawa iyayensu sun banbantasu sbd kauna junan datake yawo a jininsu tin
A iyayensu take acan ta samo asalinta har a nasu jinin,
Sun tashi da kauna me karfin gaske a tsakaninsu Amma yau rayuwar junansu suke nema,

Wannan abin ne yake Saka Omar baqin cikin Daya zauna zuciyarsa yake cinsa akowace daqiqan rayuwarsa Dan haka yau Daya samu furta sirrinsu hawayen ne suka gangaro masa a Karan farko sbd a yanzu bayan su ukun dasuke gabansa Babu Wanda ya yadda dashi Akan yarsa,

Su uku sune wainda yasan zasu tayasa bata kariya da rayuwarsu Dan haka ya juyo da idanuwansa akan Jamaal Wanda shi kadai ne Seelah Daya dayake Jinsa har cikin ransa Kuma ya yadda dashi fiyeda rayuwarsa kaman Ahmed a Sanyaye yace

"My son Ina tsananin baqin cikin hanawa Dan uwansa wannan auren sbd ba Kai bane,
Kai kadai ne namijin dana yarda na bawa aurenta na jefata cikin SEELAHs batareda naji shakka ko tsoron Hakan ba,
Kaine Wanda zan bawa amanarta ko Bada aure ba Amma kwata kwata

zuciyata Bazata taba samun nutsuwa ko Kwanciyar hankalin bawa Haroon aurenta ba Badan komai sai Dan rauninsa ga mahaifinsa Wanda ba ita kadaina akanta shi kansa tasa rayuwar a hadari take.....

Dago jajayen idanuwansa Jamaal yayi ya zubawa Dad Omar din tareda girgiza masa Kai bakinsa na sake daukan nauyi sbd tsananin son da Dan uwansa yakewa Ameenatou din idan aka rabasa da ita matsalar ciwonsa zata iya Maidasa cikakken mahaukacin dayake tsananin tsoron ya koma,
Bazai iya kallan Rabin jikinsa Haroon din ya koma Hakan ba,
Zai iya sadaukar da rayuwarsa akan lafiyan Haroon da Kuma samar masa macen dayake so fiyeda nasa ran Dan haka ya Bude Baki bakin cikin muryansa Daya shaqe sbd tsananin tashin hankali da baqin ciki harma da shock yace

"Dad Dan Allah Karka Hana Haroon auren Ameenatou,
Ameenatou itace farin Daya Kuma nutsuwa Daya rak Datake riqe da rayuwar Haroon,
Hana masa aurenta tamkar rabasa da lafiyarsa ne gaba Daya,.
Haroon Yana yimata tsananin son da bazai taba barin komai ya faru da ita ba Koda hakan na nufin zai gitta tasa rayuwar".

Kuka Babbah ya sake fashewa dashi sbd gano gaba Daya su rayuwarsu acikin seelahs din da aurenma gaba Daya a duhu suke Babu Abu Daya dayake gaskia sai soyayyar da Ameenatou dinsa takewa Haroon sbd Jamaal da Haroon dai mutum biyu n mabambamta da suka ringa wasa da zuciyar Ameenatoun,

Tayaya zai bari Ameenatou tayi aure a cikin wainnan mutanen da yanzu ma tsoro suke tsananin basa bayan Omar din da Ahmed sai Jamaal din Wanda yaji yamafi samun nutsuwa dashi.

"Bazan taba bawa Haroon ko Daya daga cikin zuriar seelahs din auren Ameenatou ba gaba Daya har abada" babban ya fada Yana dagowa jajayen idanuwansa Yana kasa kallan Jamaal Daya cike masa ido har lokacin Hawaye ne ke zubowa daga idanuwansa.....
#MAMUH#
#THE SEELAHS
#THE JDENS
#LOVERS
#MARRIAGE
#AMEENATOU JDEN SEELAH

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOUH_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee
#ZafafaBiyar
#BestLove

53
Maimaicin fasa aura masa Ameenatou da akeyi ne ya Saka kansa kasa dauka hannuwansa suka fara rawa hakama kafafunsa,

Toshewa kirjinsa yakeyi Yana Jin kaman bazai iya Jan numfashi ba ga idanuwansa da suka fara ganin babbiyu Dan haka yafara bin Bango Baya Gani sosai ya juya Yana dafe gefen kansa da hannu Daya Yana kokarin Bude idanuwansa dakyau da basa Gani sosai bayan gasu a buden.

Tsananta rawa jikinsa yakeyi sosai,
Mummunan faduwa yayi Yana gap da Isa motarsa sbd tsananin da jikinsa yayi Dan haka da rarrafe ya nufi kofar ficewa ya fice yabar Motarsa a gurin Yana rarrafawa duhun gaske Yana qara rufe idanuwansa.

BB dayake nesa sosai daga gidan sbd bayan ya koma Mam sakashi dawowa yayi akan ya tabbatarda ya riqe tsawon lokacin da suka dauka a tare Dan haka ya dawo batareda ya tabbatarda su waye da waye a cikin gidan ba gashi Kuma Yana shakkar Isa gurin sosai ko shiga a samu matsala Dan baisan takun Jamaal ba.

Idanuwansa akan gidan da duk motsin dazai fito cikinsa yake Dan haka Yana hango motsi ya fito daga maboyarsa ahankali tareda Dan biyu duhun ya iso gurin daidai lokacinda Haroon yake fara buga kansa a Kan titin dayake tsit Babu kowa ko motsin komai..

Tareda yayi da sauri tareda rufe masa Baki ya janyesa da sauri daga gurin yayi cikin duhu dashi Yana Jin kirjinsa na harbawa Yana leqa hanyar gidan baiga ko motsin kowaba dazai fito daga ciki.

Sunkutar Haroon yayi gaba Dayansa duk girmansa sbd shi kansa BB din ba qaramin Mai qarfin gaske bane sbd a Bude yake kaman basamude.

Gurin motarsa Dake nesa da gidan ya nufa dashi ya Bude ya Sakasa ciki tareda rufe motar yana juyawa yaga har lokacin Babu kowa yaja motar yabar gurin da sauri sbd Baya buqatan cigaba da jiran indai Haroon daga ciki yake tareda su Omar din yasan me zai masa duk abinda suka tattauno zasuji koma Menene adaren Nan.

****Jamaal irin roko da tabbaci tareda alkawarin da yayiwa Dad da Babbah akan auren ya Saka jikinsu sanyi Jin irin halinda Haroon yake ciki da ciwon dayake cin kansa batareda shi kansa ya sani ba,

Sanar dasu yayi alkwarine ya dauka ana auren zai tafi tareda Haroon din da Ameenatou gurin mum dinsu acan zasu zauna duk wannan yaqin batareda ko dayansu cikin su biyun ba zaayisa wanna alkwarine yayi musu.

Kallansa Dad Omar da idanuwansa sukai jajir yayi sbd Babu abinda Jamaal zai rokesa a rayuwarsa yaji bazai iya basa ba Amma kuma yanzu ana magana ne akan 'yarsa da Bai hadata da kowaba hakama tafi komai na duniyar Nan Daya mallaka mahimmanci da daraja Mai girman gaske a zuciyarsa.

Babbah a nasa bangaren farin cikin Ameenatou ne kadai abinda yake tsaye a ransa,
Tsananin Son da Ameenatou kewa Haroon shine babbar matsalar Dake tayar da hankalinsa Dan kuwa Babu wani abu komai girmansa da zai ciresa daga zuciyarta...

Omar kuwa Jamaal Dayake cikin tsaka me wuyar gaske akan Dan uwansa ya kalla Yana Jin abubuwa da yawa a zuciyarsa gameda auren Wanda zaifi farin ciki da Jin dadin tareda samun cikakkiyar nutsuwa ko bayan mutuwa ace Jamaal ne igiyoyin auren 'yarsa suke hannunsa,

Auren Ameenatou tamkar wani babban nauyin da mutum baisan dashine ba zai dauka Dan kuwa dukiyarta gaba Daya nauyinta akansa zasu sauka,
Haroon bazai taba iyawaba sedai Kuma so yayi gaggawan shiga lamarin nasa da Ameenatou Amma Kuma aurenta ba abune Mai saukin gaske ba garesa,

"Jamaal kayi mun alkawarin zaka tsaya ka tsayu ka zama kariya ga 'yata?
Ka mun alkawarin zaka Hana duk wani cuta tarwatsa rayuwanta?
Kamun alkwarin ko Dan uwanka zaka tsayu gabansa ka zama katangar karfenta idan ya kasa Bata kariya da tsaron Daya kamata,
Idan na bawa Haroon auren 'yata ka sani shi auren na basa Amma Kaine na bawa Amanarta ta har abada,
Ni amatsayin mahaifin Daya haifeta Kaine na bawa aurenta da kaina kaikuma ka karbanwa Dan uwanka Dan haka idan har ka Aminta shi ka bawa auren tabbas bazan Hanaka ba sedai Kasani har abada ni Amanar 'yata na baka Kaine ka aura mata Dan uwan naka.

Jajayen idanuwan Jamaal ya dago Babbah ya fara kalla Wanda Shima shi yake kalla zuciyarsa na rawa hakama jikinsa amsarsa suke Jira Dan dai shi Kam Babbah bayajin zai aminta da auren sedai kafin yayi magana Jamaal ya fadawa Dad maganganun da suka hatta jikin Babbah yin sanyi baisan lokacinda Hawaye suka sake gangaro masa ba sbd yanajin tabbas Shima ya amince a aurawa Haroon din Ameenatou sbd Jamaal ya kashe musu jiki da alkawarin Daya dauka tareda Amanar Ameenatou Daya tabbatarwa dad din idan har su Dad dinsa sun samu damar taba ko suturar jikin Ameenatou da dukiyarta to bayan ransa ne Inshallah.

Ahmed Daya kasa riqe kansa akan tsananin kaunar dayakewa Jamaal rungumesa yayi sbd Daman yasan Jamaal namijin gaske ne ko Dad Omar baice komaiba jininsa yafi karfin ganin cutatarwa indai Jamaal Yana sane,
Kaunar datake tsakanin Jamaal da Omar kaunace irin ta asalin 'da da uban da suka hada jini,
Yanda yake Jin Dad Omar ko mahaifinsa Baya jinsa a cikin ransa Hakan,
Shi kansa Omar yanda yakejin Jamaal ko ransa ko cewa Yayi yaje da kansa ya

sanarwa su Mamman waye yarsa zaiyi sbd yasan bazasu iya komai Dan itaba.

Rungumesa Ahmed yayi Yana Jin nauyin dayake zuciya da kansa sun rage na alkwarin bawa Omar da 'yarsa kariya Koda da rayuwarsa ne.

Har lokacin Jamaal zuciyarsa wani irin nauyi da daci ne danne da ita Dan haka Dad Omar ma dayake Jin nauyi da tsananin dacin zuciya rungumesa yayi sai alokacin hawayen Jamaal din suka gangaro daga idanuwansa Shima Dad Omar sai alokacin nasa suka gangaro Dan Bai taba zubda Hawaye ga rabuwarsa da Yan uwansa ba sai yau din Badan abin Baya cin zuciya da ruhinsa ba sai Dan baisamu Wanda daidai irin radadin ne aransaba sai yau din Dan yasan radadin dayake ransa shine yake ran Jamaal.

A cikin daren Omar ya sanar dashi komai daya Dade a rubuce na sunan AMEENATOU dayake kan komai na Abinda ya mallaka Dan haka Babbah yaji hankalinsa ya sake tashi Dan kaman sun sake nutso ne shida iyalansu da Ameenatou din cikin wutar qaddarar da zata kona kowa Dan haka take yaji zazzabi da ciwon kirji na rufesa,

Jamaal ma ciwon kan ne tareda zazzabin gaske ya rufesa sbd kirjinsa Daya toshe Dan haka cikin karfin hali ya fito kusan su babban da Dad Omar na bayansa suka fito gurin sedai babban tashin hankalin da suka tarar a wajen ne ya Saka jiri diban Dad Omar da Jamaal lokaci Daya sbd tabbatarda motar Haroon ce a gurin pake.

Ahmed ma dayake cikin shock saurin tare Omar yayi Yana kallan motar da tashin hankali yace

"Haroon Yana gurin Nan??

Babbah na Jin Hakan jiri ya zubar dashi jikin motar Omar Dake gurin Yana ambatar "Qalu innalillahi wainna ilaihirrajiun.

Jamaal Daya ji kansa na sake daukan masifaffiyar zafi da sauri ya nufi motar yaganta a rufe

Ahmed da Shima cikin tashin hankalin ya zagaya Baya ya zagayo koina gidan baiga Haroon dinba ya dawo saiga key din motarsa a kasa gurin yashe.

Babbah na ganin Hakan yayi zaman Yan bori a gurin Yana cewa

"Shikenan haukarsa ta motsa zaije ya sanar WA mahaifinsa"

Zabura yayi da sauri ya nufi Omar Yana cewa

"Wallahi tinda baida cikakkiyar lafiya tsaf zai iya sanarwa ubansa,ku yi wani abu Akai ko wlh tallahi a cikin Daren Nan na tattara iyalina ku nememu ku rasa wlh ko zaka sake ganina sai qiyama idan mun hadu gaban Allah."

Dad Omar da Baya ma gane me Babbahn ke fada motarsa ya nufa Dan sauri Shima Jamaal tasa ya nufa Ahmed ne yasamu karfin halin Jan Babbah ya jefa mota ya rufe suka tayarda motacinsu kaman masu wasan tsere cikin mugun gudun Daya Saka Babbah sake shiga tashin hankali suka hau titi su sukai kudi shi yayi arewa kowannensu Yana Saka Kiran wayar Haroon din ba kakkautawa.

Jamaal kaman zai tashi sama haka ya figi motar Yana Saka Kiran Haroon din idanuwansa na rikidewa gaba Daya Dan kuwa kowannensu tsoronsa kada Haroon din ya nufi su Dad Dan haka tabbas yaji wani abu shiyasa ya bar gurin a halinda basuda tabbacinsa tinda ga key din motarsa yashe a gurin.
#MAMUH#
#JAMAAL JEEY SEELAH
#AMEENATOU JDEN SEELAH
#OMAR JDEN SEELAH
#MAM SEEELAH
#LAMS SEELAH
#THE SEELAHS
#WAR

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOU_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee
#ZafafaBiyar
#BestLove

54
BB kuwa Kai tsaye gidansa ya nufa Dan Haroon din Kuma harya Isa Bai Hadu da wata matsala ta jamian tsaro ba Dan haka Yana Isa yayi parking motarsa a harabar gidansa ya Bude ya fito ya zagayo ya Bude motar ya dauko Haroon din Wanda ciwonsa yakai kololuwan tashi sai fizga yakeyi Yana jijjiga kansa Yana buga kan a jikin hannuwansa idanuwansa a rintse.

Kai tsaye Dayan dakinsa yakaisa ya zubar a kasa tareda juyawa ya fice daga dakin Yana Ciro wayarsa ya Saka Kiran babban yaransa.

Yana daukan wayar Kai tsaye BB yace

"Killer ka kawomin Ps biyu yanzun Nan"

"Yes oga" killer ya fada daga bangarensa Yana kashe wayar tareda ture macen datake kansa tana lashesa kaman sweet har Saida kanta ya bugu da Bango ko a jikinsa ya miqe tsaye Yana kama dadar kansa datake a watse ya Saka Roba ya daureta tsakiyar Kai Yana nufar toilet ya wanko jikinsa ya fito, Underwear yafara sakawa kafin ya Saka Jean Akai ya Saka shirt ya dauki wayarsa da key din motarsa yafice bayan ya shiga dayar dakinsa da mugayen kwayoyin rayuwa suke ciki ya dauko wadda ogan ya buqata.

Koda killer ya iso gidan BB ya tube yayo wanka dagashi sai underwear Wanda kusan Babu abinda na jikinsa da baka Gani.

Dakin suka nufa Yana miqawa killer hannu ya amsa fitinanniyar kwayar wadda take hade da ruwan alluran ta,

Tsananin karfi da balain dayake tattareda ita uku ake tanata asha Daya alluran Kuma tafi komai balai da masifa Dan hadda tsananin azabar gaske ne da ita Dan haka suna shiga dakin ya daga allurar Bai tsaya wata wata ba ya kama wuyan Haroon ya soka masa ita tareda dure masa ruwanta gabaki Daya Wanda yayi daidai da budewan idanuwansa cikin tsananin azabar da Bai taba samun kansa aciki ba take ya qame kaman Sanda kafin jikinsa ya saki gaba Daya Hawaye na gangaro gefen Idanuwansa da sukai duhu gaba Daya Baya ganin komai.

Sakin kansa BB yayi gaba Daya ya yanke jiki agurin ya zube kansa na bugawa da bakin table Dake gurin gashinsa na fashewa jini na fitowa ahankali ya lumshe idanuwansa Yana Jin jijiyan jikinsa kaman suna tsinkewan hakama jinin dayake jikinsa yana konewa cikin wata sanyayyar azaba Mai radadin gaske ga ganinsa gaba Daya ya dauke Baya ganin komai Baya Jin komai.

Dad Lameenu ne da BB ya kira tin Yana hanya ya shigo dakin bayan BB ya Bude masa kofar Yana kallansa tareda basa tabbacin Haroon din bayaji Baya ganin Komai.

Tsayuwa Dad Lameenu din yayi akansa tareda kallan BB Wanda Shima killer ya kalla aka Ciro kwayar killer na kokarin rabawa uku BB yace ya basa a Hakan.

Cikin tsananin firgici da tashin hankali killer din duk rashin imaninsa ya Kalli BB din sbd ko ukun idan aka ranata akasha ba qaramin Neman kashe mutum takeyiba bare duka Kuma har gida biyu.

Karban kwayoyin Yan kanana dasu BB yayi baiyi wata wata ba ya Bude bakin Haroon dayake kwance kaman gawan data rasa gatan suturtawa ya zuba masa su duka tareda karban ruwan da Alh Lameenu yake miqa masa ya zuba masa take suka wuce maqoshinsa.

Suna shiga kafin ma su fara aiki BB ya bari fuskansa da karfi tareda tayar dashi zaune duk da jikinsa asake yake Babu abinda yake Aiko a jikinsa.

Cikin tsananin mawuyacin halin da ko mara Imani Saiya zubar masa da Hawaye ya Bude bakinsa kansa na masa wani hayaqin masifa da balai yafara jijjiga Yana cewa

"Ameenatou itace 'yarka Dad Omar, Dad Omar ka auramun Ameenatou sbd mutuwa zanyi idan na rasata, Ameenatou bazan taba barin kowa yasan itace 'yar da ake nemaba ko da Hakan zaiyi sanadin Raina Dad Omar,

Babbah ku bani Ameenatou,
Jamaal ku bani Ameenatou,
Dad Omar ka taimakeni ka cika mun burin auren Ameenatou....."""

Sakinsa BB yayi tareda ja Baya da tsananin karfi jikinsa na daukan wani rawa da tashin hankalin da Bai taba tinanin shiga ba sbd Jin Abinda Haroon ke fada,

Shi kansa Lameenu Baya yayi da sauri Saida killer ya tarosa sbd firgici da shock din abinda yaji din.

Haroon kuwa sanqarewa yakeyi jini na fitowa bakinsa da hancinsa sosai sedai Bai Dena magana ba hakama jikinsa Bai Dena jijjiga ba.

Da sauri cikin masifaffen tashin hankali da tsoron abinda yake Gani da Wanda yaji Dad Lameenu ya Kalli BB Yana cewa suyi sauri su gogewa Haroon din jinin su mayar dashi inda zaa samesa kada ya mutu a hannunsu.

Suma Dake cikin tashin hankali sake shiga sabon tashin hankalin sukai sbd sanin waye Mam idan 'dansa ya mutu a hannunsu Dan haka ba Bata lokaci suka daukesa suka Kai mota
Kusan motarsu data Lameenu a tare suka fice su sukabi wata hanyar Shima yabi wata.

Tafiya sukeyi suna gudu sosai suna kallan Haroon din Wanda yake zubarda jini sosai har lokacin cikin mafi tsananin azabar rayuwarsa da Bai taba jiba.

Tafiya me tsayi sukai kafin suka Isa inda BB din ya daukosa suka ajiyesa agurin suka gudu batareda kowa ya gansu ba.

Suna barin gurin motar siddeeq da shima ya shiga layin masu tsananin Neman Haroon din sbd zautuwan da Jamaal ke Neman yi gurin Nemansa Yana Sako Kai a layin Dan sake dubawa sai gashi kuwa yayi mummunan Gani Dan halinda ya samu Haroon din saura kadan ya buga zuciyarsa,

Bazai iya barin Jamaal ya gansa a wannan mummunan halinba Dan haka hankali tashe ya daukesa tsaban shiga rikici Kai tsaye Mansion din ya nufa dashi sedai Yan Isa ganin abin yayi muni Dad ya nema Kai tsaye sbd shi kansa jijjiga jikinsa yakeyi tsaban tashin hankali.

Mam na fitowa kallo Daya yayiwa Haroon ya Yanke jiki ya Fadi sbd zuciyarsa data buga irin bugun da zai iya kamuwa da shanyewan Rabin jiki mum Atee ce tayi saurin rikesa itama jikinta na daukan rawar tsoro da firgita sbd ganin abinda yafi karfin nata rashin Imanin.

Daukansa Akai aka nufi ciki dashi Kai tsaye bangarensa Akai dashi zuwa lokacin jikinsa sake sanqarewa yakeyi Dan haka suna Isa Kai tsaye toilet siddeeq ya wuce dashi ya Saka a bathtub din dayake cike da ruwan sanyi.

Dad kasa tsayuwa yayi ya qarasa gurin Haroon din dayake sanqare acikin ruwan jini har lokacin Yana fitowa ta hancinsa.

Wani irin kukan da baisan yanada shi bane ya fashewa Dad din Yana ihun ambatar Haroon din daidai Nan Lameenu yashigo Shima kafafunsa na rawar tashin hankali da tsoron abinda zai iya biyo Baya.

Kamo Haroon din yayi Shima Yana ambatar sunansa sedai Haroon Babu abinda yake ji a lokacin.

Sosai jinin yake sake gudu Wanda ya Saka siddeeq kasa riqe kansa ya kira Jamaal Wanda yaketa bulayi a titin Lagos Yana Neman Haroon din Yanajin abinda siddeeq ya fada Kai tsaye ya juyo motarsa kaman zai tashi sama yayo mansion din.

Isowansa yayi daidai da wani tarin jinin gaske da Haroon ya feso daga bakinsa Mai yawa jikinsa na qarasa sakewa gaba Daya a jikin Dad Wanda yake rungume da Haroon din qamqam Yana Jin Abinda Bai taba ji ba na ganin zaka rasa Wanda kake tsananin so da dukkanin rayuwarka.

Ganin Dan uwansa ya Saka Jamaal karasawa kafafunsa na Neman sarewa hakama zuciyarsa koina yankewa yaji tana yi.

Dad Lameenu da sauri ya janye daga Haroon din ya bawa Jamaal guri.

Hannuwansa duka biyu yakai cikin ruwan ya kamo Dan uwansa Yana fitowa dashi sbd gaba Daya jikinsa ya lalace da jini
Bai tsaya komaiba ficewa yayi dashi daga dakin ya fita dashi Dad Wanda ya kasa motsawa daga inda yake tsaban mutuwan dayakejin duka jikinsa yayi Babu inda ke motsuwa mum Atee ce ta kamasa suka fito suma suka marawa Jamaal din Baya.

Asibiti Jamaal ya nufa dashi cikin gaggawa aka karbesa sedai hadda Jamaal din aka shiga sbd samun damun tsayar da jininsa da ya zube sosai Dan take jininsa ya fara yin qasa.

Dayake da yawan manyan doctors din asibitin sunsan Dr Jamaal Seelah din baa hanasa shigaba Dan shine ya tsayar da jinin sedai ana buqatan jinin sakawa Jamaal din da gaggawa take ya kwanta aka fara diban nasa ana

sakawa haroon din Wanda ya koma daidai sedai Babu inda yake motsi a jikinsa yayi fari fayau a cikin kankanin lokaci ya koma abin tausayin da zaka dauka shekarunsa ashirin a kwance.

A waje kuwa Dad da mum Atee da siddeeq ne sai Dad Lameenu da mummy Sarat duka tsit gurin ya dauka bayan Kaida kawo Babu abinda siddeeq keyi su kuwa Dad aketa Neman Kiran likita ya dubasa sbd jininsa yayi mummunan hawan dayake buqatan maganin gaggawa Shima.
#MAMUH

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOUH_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee
#ZafafaBoyar

Dad Omar ma tin kafin a ga Haroon din jininsa yahau Shima har yana Naman zubewa dole Ahmed ya dawo dashi gida Shima aka Nemo likita.

Babbah ma a gida likitan aka Nemo sbd take ya rafke zuciya na ciwo sosai hankalin nasa Iyalin yayi mummunan tashi.

A cikin Daren abubuwa da yawa sun faru marasa dadi da tashin hankali tareda Saka hawan jinin mutane da dama,

Sai guraren asuba Haroon ya farka sedai cikin yanayin Daya Sakasa tsiyayo da Hawaye masu zafin gaske Yana kallan Dan uwansa Dake gabansa zaune Yana kallansa idanuwansa jajir
Ko baa fada ba yasan irin radadin dayake zuciyar JAMAAL bamai faduwa ne ba,

Wani numfashi Mai dumi ya sauke ahankali hawayen cikin idonsa na gangarowa yanason magana Amma ya kasa sbd baisan me zai fada ba,

Abu uku zuciyarsa a yanzu kadai take so sbd samun sanyin da sassaucin azaban dayake ji na cin jininsa,

Ganin mahaifiyarsa,ganin Ameenatou da Kuma Jamaal din Wanda shi gashinan a gabansa.

Ahankali ya Bude bakinsa cikin sanyi da karfin hali yace

"Nagode"

Sukan Jamaal kalmar tayi Dan haka ya miqe tsaye Yana kokarin danne tausayi da tsinkewan da zuciyarsa keyi tareda nauyin dayake ji a kirjinsa yace

"Ka manta yau daurin aurenka???

Murmushi Haroon din yayi Mai sanyi kafin yace

"Ban manta ba shiyasa nayi Maka Godia.

Magana yakeson yi Amma bazai iya ba sbd hakanan zuciyarsa da bakinsa

basa son furta komai bayan idanuwansa Daya zubawa Jamaal din Yana kallansa jikinsa na mutuwa hakama idanuwansa sunyi jajir.

Shima Jamaal Jin yayi bakinsa da zuciyarsa sunyi nauyi sosai bazai iya cewa komaiba bayan yin shiru suna sauraron numfashin junansu.

*******Mam a cikin Daren Lameenu daya kasa zama ya kasa tsayi yasaka BB ya kawo musu rahoton abinda yake Neman zautashi tinda yaji a bakin Haroon.

BB a cikin asibitin ya sanar da Mam wacece 'yar Omar Jaden da Kuma alaqarsa da Babbah akan cewa shine da kunnensa yaji lokacinda ya bisu.

BB na gama fada Lameenu ya sauke ajiyan zuciyarsa Dake cikin balai da masifa tinda yaji zancen shi kadai,

Maganar da farko kaman a mafarki Mam ya jita Saida ya dago idanuwansa da sukai jajir ya Kalli BB
BB din ya jinjin masa Kai alamar haka zancen yake.

Da hannu Mam yayi musu alama dasu kira masa likita numfashinsa tsayawa zaiyi.

Da sauri BB ya fice ya kirawo likita Wanda y dawo dakin tareda Mum Atee da itama tana asibitin Taki tafiya.

Tsaban tashin hankalin firgitan da Mam yayi Saida aka Saka masa oxygen na wucen gadi daqyar yakai asuba sbd tinane tinane da sakawa da warwarewa.

Asubar fari yaji dukkanin ciwonsa dayake ji a jikinsa ya warke,
Bai taba sanin Kowane 'da da baiwar da Allah yayi masa ba da kalan arzikinsa sai yanzu,

Haroon ayau ya tabbatar masa da Hakan sbd zai basa abinda yayi shekaru Yana nema tin kafin ya Saka ran haihuwarsuba,
Bai taba Saka ran duk wannan tashin hankalin da sukaita fama dashina karshen dukiyar Omar a gidansa zata dawo,
Wannan auren shine babbar taskar arzikinsa Daya Dade Yana kashe kashe gurin mallaka,
Wannan auren da yace bazaiyiba ayau Yana tabbatarwa kansa idan baayi auren Nan ba to shine Baya raye Amma wallahi tallahi Babu Wanda zai Hana auren Nan dauruwa ayau kaman yanda ayau din Omar Zai bar duniyar dukiyar tashiga hannunsa da dalili....

Lameenu da Mam din ya Sakasa zuwa asibiti gurinsa tin asubar fari gama tattaunawa sukai inda kansa ya shiga wani zafi da duhu ya shiga lissafin abinda zai faru Idan auren ya tabbata.

Wannan auren idan anyi sa Ameenatou Jden ta zama matar Haroon sirikar Mam ayau Kuma idan Omar ya mutu gadonta na dukiyarsa gaba Daya zata zama a karkashin mijinta wanda dukiyar gaban dayanta zata koma ne akan yanzu gadon sirikar Mam ce ba tasu ba da zasu mallake su Raba tsakaninsu.

Jin yayi kansa na Neman kuncewa da lissafi Amma Kuma ko yayane su Raba Omar din da duniyar tukuna zasu fuskanci juna shida Mam din akan dukiyar sbd tabbas dole kasonsu me tsoka Yana cikinta.

Mam ne ya shiga dakin da Haroon yake kwance sedai idanuwansa biyu har lokacin shida Jamaal Babu me magana sai da Dad din ya shigo Jamaal ya fice ya basu guri dad din ya Kalli Haroon Wanda Shima Haroon din shi ya kalla Yana Jin tausayin mahaifin nasa akan rayuwar Daya samu kansa Dan haka yake Jin inama zai iya sauya Dad din dayayi Hakan.

Sunansa Dad ya ambata cikeda kulawa da farin ciki shimfide a fuskansa Yace

"Haroon Allah ya albarkaci rayuwar da zaka fara daga yau dinnan har ranar tashin qiyama,
Allah ya haskaka zuciyarka yanda ka haskaka tawa,
Allah yayi Maka kyakkyawar karshe ya albarkaci zuriar da zaka Haifa."

Hawaye ne kawai suka silalo daga idanuwan Haroon sbd Bai taba samun wannan kyakkyawar adduar Mai dadin sauraro daga mahaifin nasa ba Dan haka ya rintse idanuwansa jikinsa gaba Daya na yin sanyi da mutuwa ahankali ya Bude bakinsa cikin kaunar Dad dinsa da har lokacin yakeji yace

"Amin Dad nagode Allah ya Saka da Khairan,
Allah ya tsarkake Maka zuciyarka ya wanketa Dad ya Kuma baka ikon gyarawa da tubar masa"

Shima Dad din cikin farin ciki da tsananin kaunar dansa yace "Ameen Haroon"

Jamaal ne ya dawo dakin daukeda takardun Haroon din Daya karbo dasu zai tafi akwai binciken da zaiyi akansu.

Duk da rashin karfi dayake jikin Haroon din hakanan Jamaal ya daukesa daga asibiti sbd bazai taba barin a daga daurin auren ba daga ranar sbd hakanan a yanzu zuciyarsa tafi ta Haroon cika da tsoron Da baisan na Menene ba Idan ba ganin yayi igiyan auren Haroon din sun rataya akan Ameenatou ba.

Dad ma bayajin akwai abinda zai Hana wannan auren ayanzu Dan haka gida suka dawo kowa na kokarin fara Shirin daurin auren Wanda zaayi da karfe goma Sha Daya na rana.

Dad Omar ma hankalinsa kwantawa yayi Daya samu tabbacin su Mam Basu ma samu damar magana da Haroon ba tin jiyan Dan haka yasan sirrinsu Bai fita ba Dan haka ya kira Babbah Wanda Shima yake a tsinke tini ya sake yafara Shirin daurin auren shi dasu Hafiz da zuciyoyinsu suke cikin farin ciki Mai tsananin gaske.

Amarya Ameenatou kuwa da batai waya da Haroon ba sai da safen Jin tayi kaman yayi mata caji Dan haka ta sake daga sanyin jikin datake fama dashi yin jiyan zuciyarta da kirjinta na nauyi.
Dan haka ta sake Wainda suka taho shirinta ta Basu Daman shigowa inda take Dan fara shiryata sbd daurin auren ma ya kusa ga gidan nasu a cike yake sosai da Yan bikin gashi Babbah yace bayan daurin auren zai sanar da ita abinda Bai taba sanar da ita ba Mai tsananin mahimmanci Dan haka duk ta sake zaquwa da ayi daurin auren ta zama ta Haroon ya zama nata.
Wannan tinanin kadai sake narkar da zuciyarta yakeji cikin farin ciki Mai sanyin gaske.

******A yanzu kusan dukkanin seelah Babu Wanda tin daga zuciyarsa yake cikin tsananin farin ciki da wannan auren ba Dan haka sosai ake cikin annuwan gaske Dan haka tini suka kammala nufinsu da komai akan Omar Wanda Shima yake cikin nutsuwa da farin ciki Dan ana daura auren zasu tafiyarsu hadda Haroon din da Ameenatou da Jamaal shiyasa ma suka dakatar da Dr Aleena daga zuwan tinda Nan zasu taho.

Ahmed ma Yana cikin farin cikin gaske Jamaal ne kadai yake Jin kirjinsa da zuciyarsa cikin nauyin Daya hanasa ko numfashin daidai.

Karfe goma saura kusan kowa ya gama Shirin daurin auren,

Haroon Wanda Jamaal ne ya tayasa shiryawa cikin kyakkyawar farar shaddar datai masa wani irin kyau haskensa da Bai taba sanin yana dashiba bayyana sosai.

Ayau hatta turare iri Daya sukai amfani dashi sbd komai dayake jikinsu iri dayane babu banbanci abinda Basu taba yiba kenan tin suna kanana har girmansu sai yau din.

Time Haroon ya kalla yaji jikinsa ya mutu da farin cikin wannan ranar Dan haka ya Ciro wayarsa ya Saka Kiran Ameenatou wadda itama kusan ankusa gama shirinta tana dauka ajiyar zuciya kawai ya fara saukewa kafin ya ambaci sunanta Yana ce mata Yana Sonta kawai ya kashe.

Murmushi kawai tayi tana damqe wayar a hannunta tareda cigaba da shiryawa.

Jamaal tsayuwa yayi bakin window ranar aurensa na dawowa sabuwa acikin zuciyarsa Dan haka nauyin kirjinsa yake sake karuwa Yana sakashi shiga yanayin tashin tsikar jikinsa idanuwansa na Neman sauya Amma ya kasa Hana zuciyarsa shiga wani irin tsoro duk jarumtarsa.

Matsowa Haroon yayi Yana kallan time da yayi yace

"Muje ko time yayi"

Juyowa Jamaal yayi ahankali ya zuba masa idanuwansa da suka sauya sedai Bai iya cewa komaiba.

Tsoro yakeji sosai Dan haka ya Dan dauke idanuwansa daga Haroon yanayin gaba Haroon din ya biyosa yana gyara zaman babbar rigar jikinsa.

Motar Mam da securities dinsa ce ta fara barin gidan ya wuce daurin auren zuciyarsa fes,

Fitowan su Jamaal yayi daidai da fitowan Dad Omar tareda Ahmed zasu shiga mota Dan haka Kai tsaye ya kofar harabar Daya hada gidajen suna nufa suka Isa gurinsa idanuwansa na kansu Yana kallansu a tare zuciyarsa na cika da farin ganin auren yarsa Dan haka Kai tsaye rungume Jamaal yayi kafin ya rungume Haroon da yau Shima yake cikawa kowa idanuwa da kwarjini Mai sanyi.

Cikin kulawa da kauna Dad Omar ya kallo Haroon yace su shiga motarsa suje daurin auren tare.

Cikin farin cikin Hakan Haroon ya juyo ya kallo Jamaal zaice da Dan uwansa yake son zuwa daurin aurensa sai Jamaal din Wanda ya kasa samun nutsuwa ya girgiza masa Kai Yana kallan fuskansa Yace yabi Dad din kawai.

Murmushi me sanyi Haroon yayi tareda gyada Kai kaman qaramin yaro yabi dad da Ahmed dukkaninsu suna murmushi suka shige mota.

Jamaal na kallo suka tada motar suka bar harabar gidan Shima ya juya yabar harabar gidan.

Dayake sun Dade da fita kafin ya fita Kai tsaye biyawa sukai suka dauki Babbah sbd Shi Daman da Omar zasu tafi daurin auren sai gashi Kuma sunzo da Haroon sai Hakan yayiwa Babbah dadi sbd zaiso ya sake bawa Haroon amanar Ameenatou
Babbah na shiga suka tada motar suka bar gurin.

Jamaal na kama hanyar zuwa gurin daurin auren siddeeq ya kirasa kaman bazai daukaba Saiya Isa sai kuma ya dauka
Abinda siddeeq din ke sanar masa yaji Yanzu daga bakin Lameenu da BB a Mansion shine ya sakashi juya kan motarsa ya kama hanyar gidansu Ameenatou sbd bazai taba barin wani abu ya samu matar Haroon ba aranar aurensu kaman yanda Shima ranar auren ya rasa tasa matar.

Wayar Dad Omar yake kira cikin gaggawa Amma Sam Bata shiga,
Ta Ahmed ya koma kira kwata kwata Bata shiga itama,
Ta Haroon ya kira ita Kuma Saiya jita a cikin motar dayake din Dan haka yayi wurgi da wayar seat din gefensa tareda qarawa motar tsananin gudu yana nufar gidan.

Yana Isa kofar gidan Hafiz da Abdul sun fito kenan cikin Shirin wucewa ko kashe motar baiyiba ya fito da sauri Yana kallan Abdul yace

"Yi sauri karbi bayansu Dad da Babbah ka sanar musu kada su bi ta Aneyam nzki road,
Ka tabbatarda Basu bi hanyar ba yi sauri, yi sauri...

Abdul na Jin Hakan da Kuma ganin yanda Jamaal din yake a zafafe ya sakashi fadawa motar Hafiz ma ya fada suka bi bayan su Haroon din da mugun gudun gaske.

Shikuwa Kai tsaye harabar gidan ya shiga daidai fitowan Ameenatou din zata bawa Hafiz agogonsa Daya manta gurin sauri cikin mahaukacin navy blue tsadaddiyar lace din Daya fidda kayanta da kuruciyarta akansa idanuwanta akansa suka sauka ta tsaya cak daga inda take tana masa kallan Daya Sakasa qin kallan fuskanta bare gane kamanninta.

Takowa tafara yi ahankali tana nufosa cikin sanyin da duka jikinta kawai taji yayi hakama kirjinta nauyi yayi mata take me tsananin.

Gap take da isowa gurinsa wayar hannunta tayi ringing daidai Nan tasa wayar Shima tayi ringing itace ta fara daukan tata tareda kaiwa kunnenta tareda tsayawa cak daga inda take.

Daga nasa Kiran yayi da siddeeq yayi masa sedai baima gama Jin Abinda yafara fada masa ba Ameenatou ta Yanke jiki ta zube a jikinsa kaman matacciya Shima Neman zubewan yakeyi siddeeq daya iso bakin gate din gidan a haukace sbd mummunan tashin hankalin da baa Saka masa Rana ba ya shigo da mugun gudu.ya taresu gaba dayansu.
##MAMUH#*_AMEENATOUH_*
Mamuhgee
#Arewabook@Mamuhgee
#ZafadaBiyar

56
A jikin Jamaal gaba Dayanta Ameenatou din ta zube Dan haka baida zabin Daya wuce riqeta da hannuwansa Shima nasa kafafun na gagararsa daukansa.

Siddeeq da idanuwansa ke rikice da wani mugun ja riqesa Shima yayi Yana Kasa kallan fuskarsa data fara gaba Daya.

Umman fadila ce tareda anti zulaihat cikin mutanen dadah da suka taho daga Nasarawa biki ne suka fito daukan kaya a harabar gidan suka tarar da wanna tashin hankalin da sauri siddeeq yace umman tazo ta dauke Ameenatou daga jikin Jamaal din.

Da sauri suka qaraso tare umman ta tattaro Ameenatou din daga jikinsa tana tambayar lafiya a rude Tana raba idanuwa a tsakanin Ameenatou din da Jamaal da Kuma siddeeq din.

Siddeeq Bai iya cewa komai bayan cewan suyi ciki da Ameenatou din shikuma ya kama Jamaal Wanda har lokacin kaman jiri yake Gani suka fito daga harabar gidan Kai tsaye motar da Jamaal din yazo da ita suka nufa shi siddeeq din yabar wadda yazo da ita a gurin.

Saida ya zaunar da Jamaal din a mota kafin ya zagaya da sauri ya shiga motar zai tayar Jamaal ya dago jajayen idanuwansa ya kallesa daqyar ya iya

Bude Baki yace

"Bani key ni zanje na dubo Kai ka Jira anan din Sbd A,dole Ina buqatan barin wani anan din incase.

Siddeeq kallansa yayi da nasa jajayen idanuwan Shima Yana girgiza Kai sbd bazai iya barinsa yayi tuqi ba a lokacin da kansa.

Bude motar Jamaal yayi tareda fitowa ya zagayo ko gabansa Baya Gani dakyau wani irin wuta da radadin azabar nauyi yake ji a kirjinsa Babu abinda yakeso kaman ganinsa gurin da ake maganar.

Karban key din yayi Bai tsaya komaiba ya fada motar Yana rufewa ya tayar Kai tsaye yayi mata wani irin mugun ja yabar gurin siddeeq na bin bayan motar da kallo hankalinsa na mummunan sake tashi sbd kaman zata tashi sama tsaban mugun gudun da Jamaal din keyi.

Jamaal na barin gurin yayi cikin harabar gidan Yana fiddo wayarsa aljihu Yana rasa a cikin wainda suka tafin waye zai kira tinda Babu me lafiyan dauka Kila.

Jamaal kuwa tuqin yakeyi idanuwansa na Neman rufewa Amma karfin hali Dana zuciyarsa Basu bar hakanba Saida ya hau titin da zai Kaisa Aneyam nzki road Wanda yake kaman bypass Babu mutune sosai.

Yana Jin Nisa sosai a kan titin
Tin daga nesa yafara hango mutane da Jamaan tsaro sun rufe titin hakama hadda masu daukan hotuna da wata katuwar mota a gurin datake kokarin kamawa da wuta anata ihu da hayaniya.

Tin anan Kunnuwansa sukai masa wani irin dim suna kokarin dauke jinsu,
Idanuwansa kuwa wani dishi dishi suke son fara masa Amma ya rintse su da karfi tareda budewa Yana budewa motarsa da sauri ya fito batareda ya kasheta ba hakama wani parking din tsakiyar Titi yayi Yana qarasowa gurin da gudun gaske ganin motar Dad Omar data Abdul sun hade guri Daya kaman kayan wankin da aka hada aka matse cikin mafi muni da tashin hankalin kallo a kusan karkashin babbar motar wadda da alama itace tayi musu hawan tela.

Daukewa ganinsa yafara yi da gaske hakama kunnuwansa Dan haka take yafara Neman kasa karasawa sbd jiri da rashin Gani,
Daidai lokacin Mam ya iso gurin da drivernsa tareda Lameenu cikin matsanancin tashin hankalin da Bai taba Shiga ba Shima nasa ganin da Jin kusan daukewa yayi can sama sama yakejin maganganun mutane da iska

suna kadawa hakama gabansa Baya Gani sosai Yana Sako Kai inda police din gurin janye masa shida Jamaal daidai lokacinda aka shimfide gawar Haroon da aka samu cirowa a gabansu cikin fararen kayansa da suka sauya take Babu ko dogon haskensu koina jininsa ne ya sauya kalar kayan gabaki dayanta.

Daga Jamaal har Dad lokaci Daya kafafuwansu suka sare a gaban gaban gawar suna zubewa Jamaal take ya qarasa zubewa qasa Yana rarrafowa gaban Haroon din Dan cetan ransa sbd Bai yadda da wani abin ya Riga ya faru ba da Haroon dinsa, Dad kuwa zubawa gawar idanuwansa yayi hannuwansa na wata irin rawar tashin hankali bakinsa na rawa yace

"Kuyi sauri ku kawo mota muje asibiti Dan uwansa likita ne kwararre gashinan zai taimaka masa kuyi sauri,
A kawo mota,
Me kuke Jira?
A kawo mota da sauri 'dana Yana buqatan taimakon gaggawa,
Yaro na Yana buqatan Isa asibiti,
Lameenuuuu a yi gaggawan kawo mota Dan Allah karku bari yarona ya mutu a Haka yanada raunin zuciyaa, HAROON,HAROON,
HAROON my boy,
Yarona 'dan Albarka Karka tafi ka barni Kai kadai nake dashi a cikin abinda nake tsananin so a duniyar Nan,
Haroon,Haroon..... innalillahi wainna ilaihirrajiun....

Dukkanin maganganun da Dad din keyi Baya hayyacinsa sbd Bai yadda da Babu Rai a jikin Haroon ba sbd jamaal ma kwata kwata ya kasa yadda da Babu Rai a jikin Dan uwansa Dan haka yaketa kokarin dawo da numfashi a jikinsa ya hanyar dubarunsu na likitoci hannuwansa na wani irin tsananin rawa hakama nasa fararen kayan tini sukai kaca kaca da jinin Yana rungumo Haroon din idanuwansa na qanqancewa Yana ihun su kawo ambulance Shima.

Lameenu rudewa yayi Shima yafara cewa a kawo ambulance Maza Maza daga SEELAHs hospital Yana Jin tsananin tashin hankali da tausayin halin da yaga Mam a ciki yau harma da tsoro da fargaba duk ya shiga sbd dukkaninsu Basu taba kawo tinanin Haroon zai shiga motar Omar ba,to mema ya shigar dashi,

Babban tsoro da tashin hankali da mugun firgicin dayake ciki shine bayan wucewansu Omar din tareda Haroon Saida ya Jira Jamaal ya gama wayoyinsa tukuna ya fice kafin ya fidda wayarsa ya kira Lameenu din Kuma daidai wannan lokacin ne siddeeq ya shigo mansion din Bai dauka su Jamaal din sun wuce ba sbd yanata Kiran wayarsa busy yake.

BB ya sanar da Lameenu cewan Haroon fa yabi motar Sir Omar a dakatar da aikin kokuwa a qaddamar dashi yanda aka tsara sbd Haroon na ciki,

Kai tsaye Lameenu Bada umarnin yayi ayi aikin kaman yanda aka tsara sbd Ameenatou bazata taba zama sirikar Mam ba ta yanda zai fisa Iko ko mallakar dukiyar gaba dayanta bayan wuyar da suka shawo akanta Dan haka gwara Bata zama sirikar tasaba tin farko suna gamawa da Omar itama su gama da ita shikenan sune magada tinda sune ake kallan uwa Daya Uba Daya dashi Kuma kada a kuskura duk tsanani bayan aiki a cewa Mam an sani su tsaya akan Basu San Haroon yabi motar ba.

Hakan da siddeeq yaji ne ya sakashi Kiran Jamaal Wanda ya gama wayarsa harya fara Nisa a hanya ya fada masa take shikuma ya sauya hanya yabi zuwa gidansu Ameenatou Dan cimma su Dad din da bawa Ameenatou kariya kafin ya samu a dauro auren a dawo yasan Dan uwansa ya samu mallakar macen zuciyarsa.

Wuto babbar motar ta fara ci dashi Dan haka Akai saurin Bude ambulance din data iso aka fara dauke gawar Haroon aka Saka kafin ta Abdul wadda itama kallo Daya zakai masa ka fashewa gawar da kuka sbd daidai lokacinda su Abdul din suka iso gap da motar su Dad sun musu magana kenan babbar motar data taho da mugun gudun ta haye kansu gaba Daya cikin rashin tausayi kuma Yana hayewa kansu da motar sedai kafin ayi wata wata drivern ya Bude motarsa yana kokarin guduwa a raunane Dan Shima ya raunana sosai

Sedai Yana fitowa motan zai gudu yaran BB Dake gurin a rarrabe suka taso suna rufesa da dukan mutuwa suna cewa ya kashe mutane zai gudu
Take mutane da Jamaar gurin suka tayasu aka rufesa da dukan da take aka kashesa a gurin Shima duk yanda Yan Sanda suka so samunsa da Rai tini Rai yayi halinsa cikeda baqin ciki suka dauki gawarsa Shima aka jefa wata motar daban.

Dad Omar da Babbah sune Basu rasu ba Amma sunfi wainda suka rasu kakkaryewa sosai tareda wahalalliyar azaba hakama gabaki Daya sun sauya daga mutanen da aka Sansu Dan Babu Wanda ake gane ko fuskansa sunyi mummunan raunana Tako ina Dan haka a cikinsu Babu ma Wanda alamun sauran Rai yake a jikinsa amma dai an duba suna raye din Dan haka Akai gaggawan daukansu zuwa asibiti,
Sai Ahmed da Hafiz da Suma sukai Mummunan kariya ta hannuwa da kafa hakama sun raunana sosai sedai su suna hayyacinsu sedai rikitacciyar azaba Da jininsu Dake zuba kaman ba daga jikinsu yake fitowa ba.

Suma kwasansu Akai zuwa asibiti gaba Daya,

Jamaal har acikin ambulance din rungume yake da gawar Dan uwansa ya kasa sakonsa duka jikinsa rawa yakeyi sosai kaman zai jijjige Haroon din Dan haka koda aka Isa asibitinma da qyar aka bambare gawar daga jikinsa Akai ciki da ita.

Dad Koda ya iso Lameenu na biye dashi sbd kada ya Fadi hakama su Mum Atee tini suka qaraso asibitin
Hakama su Aunt Didi matar Ahmed da Fatmah duk sun iso
Mum Nur kuwa Kuka kawai takeyi sbd tsoron dataji duk ya dabaibaiyeta.

Siddeeq Daya kasa hakuri wayoyin kowa kira yakeyi gashi itama Ameenatou din taqi farfadowan sai ruwa ake zuba mata Dan haka ya daukosu tareda dadah cikin sabon tashin hankali sukayo asibitin da ita.

Suna isowa itama aka karbeta sedai samun ahalin seelahs kaf a asibitin ya Saka su dadah cikin masifaffen tashin hankali kafin dukkaninsu su motsa daga inda dukansu suke tsaye Dr zayyan ya fito daga dakin emergency din da suke ciki da duka su Omar da Haroon din bayan fama da taqaddamar da sukasha da Jamaal kafin ya yadda Allah ya karbi ran 'dan uwansa ya koma garesa Dan haka kallansu Dr zayyan din yayi idanuwansa jajir hakama Shima hannuwansa yar rawa sukeyi idanuwansa na cikowa da kwallan Daya kasa riqewa ya kasa kallan Dad dake tsaye shi yake jiran abinda zai fada,mum Atee da Dad Lameenu na gefensa kowa Dr zayyan din yake kalla,
Su mum Sarat da Dadah ma duk a tsinke suke,
Sai su mum Nur da kukanta ya tsaya cak suna kallo bakin Dr zayyan din ya Bude cikin sauti me tsananin sanyin gaske yace

"Sai hakuri,sai hakuri, Haroon seelah da AbdulRasheed Allah ya Riga ya dauki ransu lokaci yariga yayi Babu abinda zamu iya sai hakuri da rungumar hukuncin ubangiji"
#MAMUH#

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*

Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k
Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

*_karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!_**_AMEENATOUH_*
Mamuhgee
#Arewabooks@Mamuhgee
#ZafafaBiyar

57
Ahankali Dad ya daga hannunsa da yayi masa wani irin mugun nauyi ya Dora a kirjinsa inda yaji wani abu ya tsaya masa Yana hanasa Jan numfashi kwata kwata kafin ma ya sake kokarin Jan numfashin ya yanke jiki a gurin Yana kokawa da numfashin Daya Yanke daga kirjinsa gabaki Daya idanuwansa na tsiyayo wasu zafafan hawayen masu radadi ahankali.

Mum Atee da Dad Lameenu ne suka durkushe gabansa suna ambatar sunansa cikin tsananin tashin hankali da rikicewa.

Dr zayyan ma cikin tashin hankalin me tsanani ya kira nurses da masu daukansa tini aka daukesa Akai ciki dashi Dr zayyan na cewa cikin sauri a kawo oxygen da gaggawa kafin numfashin nasa ya yanke.

Dadah kuwa da Karan farko Bata gane Abdul dinta ake nufi ba saida umman fadila ta rungumeta tana fashewa da kuka sbd dawo mata sabuwa da ranar rasuwar Taya 'yar tayi a wannan asibitin itama ranar aurenta.

Dadah sai alokacin ta fahimci me ake nufi Dan haka ta silale qasa tana Neman numfashin itama sbd kukan ma mantawa tayi da ana yinsa a duniya

iskan numfashi kawai take nema a kirjinta kafin ayi yunqurin Kiran likita ya some a gurin gaba Daya jikin umma.

Mum Nur dasu Aunt Didi kukan baqin cikin rasuwar Haroon din dana farin cikin mazajensu dake raye suka sake lokaci Daya tareda tausayinsu.
Fatmah ma kukan takeyi sbd ta dauka zaace Dad dinta da Dad Omar sun rasu suma sun barsu.

Mummy Sarat ma dasu Aliyah kuka sukeyi sosai musamman Ayeesha datafi kowa shakuwa dashi Kuma ita kadaice yakeda kauna mara sirki daga zuciya a tsakaninsa da ita duk cikin family Dan haka ta zube a gurin kasa tana fasa kukan Daya Saka gaba Daya gurin daukan shiru tana Kiran sunan Haroon din.

Emergency Akai gaggawan shigewa da Dad sbd oxygen din Neman gagararsa ja ma yakeyi Dan haka hankalin likitocin ya fara tashi Dan hak suka Taru akansa ana yaqin cetan numfashin nasa hankali tashe.

Su Lameenu Dake waje ma hankalinsu tashi yayi Dan haka kusan asibitin tayi tsit ba dogon motsi bare hayaniya sbd masu asibitin ne da kansu cikinta a mafi wahalan yanayi da tashin hankalin dasuke ganin Basu taba shigarsaba.

JAMAAL Babu Wanda yagansa har lokacin sbd Yana ciki inda gawar Haroon din take tareda ta Abdul a gefensa,
Gawar Haroon itace gawar datafi masa rayuwar duka Wanda yake duniyarma yake Gani,
Gawar Haroon itace abinda ya kasa dauke idanuwansa daka kansa,
Rabin jikinsa ya tafi yabarsa,
Haroon yasha wahala da baqin cikin rayuwa fiyeda komai,
Bai samu farin ciki ba tinda ya taso harya komawa ubangijinsa,
Yaso samun sauyin rayuwa a tareda Dan uwansa da mahaifiyarsa Dan matarsa bayan auren sedai Allah baiyi zaiga hakanba,

Meyasa suka kasance acikin zuria da jinin marasa imanin duk duniya da rashin tausayi?

Kasa riqe kansa yayi daidai lokacinda ya Tina maganar Dan uwan nasa ta karshe akan farin cikin dayake ciki a yau din sbd zai auri farin cikin rayuwarsa.....

Wani irin kuka Mai tsananin radadin zuciya ne ya fashe dashi Yana Dora goshinsa gefen kan gawar Haroon din duka jikinsa na rawa da jijjigan kukan da yakeyi Mai ciwo da baqin cikin ya rabu kenan da Dan uwansa shikenan.

"Innalillahi wainna ilaihirrajiun"

Kukansa ne sosai ya Saka siddeeq kasa riqe nasa kukan tausayin Haroon da irin rayuwar rashin kaunar da ake nuna masa Daya gudanar tareda wahalan ciwo Daya ringa fama dashi batareda kowa ya sani ba daga karshe ya tafiyarsa yabar duniyar da Babu komai a cikinta sai son zuciya da azaba a gurinsa.

Dadah da Akai gaggawan taimakawa tana farfadowa wani kuka Mai ratsa zuciyan duk uwar Datake da 'yaya ne da uban dayake da yayane ta fasa tana Jin kirjinta Yana kasa daukan radadin Datake Jin kanta acikinsa,

Rashin 'dan ta Babba tareda mummunan halinda mijinta yake ciki na tsakanin Rai ko mutuwa baa San wanne zai faru ba da Kuma Hafiz da Shima aketa kokarin ganin an ceta rayuwarsa sbd jininsa da kusan ya tsiyaye da kariyar datafi nawa a jikinsa.

Mum Nur ma da Aunt Didi lokacinda suka samu bayanin halinda su Dad Omar suke ciki mum Nur kasa dauka tayi dole Akai gaggawan mayar da ita gida tinda itama lafiyar tata sai ahankali,

Dadah tin tana iya kuka Dan idanuwanta har lamarin yaci karfina ta sake rikicewa jikinta ya rikice gaba Daya dole dai itama akai gaggawan Bata kulawa aka mayar da ita baccin dole da wahala sbd zuciyarta Dake Neman samun matsala sbd BP dinta yayi mummunan hawan daya fara Sakata kaman zatai jijjiga.

Daidai wannan lokacin ne Ameenatou ta farfado sedai umma kasa barinta tayi tasan meyake faruwa ta dawo gida da ita a taxi sedai Koda suka Isa gida gaba Daya gidan anyi cirko cirko kowa idanuwansa jajir masu kuka sunyi masu shiga tsananin damuwa da tashin hankali duk suna ciki Dan kuwa labarin wannan mummunan ranar ta ahalin SEELAHs ya isarwa kowa.

Duk yanda akaso taimakon Dad abin yaci tura sai da kyar suka samu damar daidaita numfashinsa sedai Kuma Bai San inda kansa yake ba Dan a cikin qanqanin lokaci Allah ya mayar dashi abin tausayi kaman Wanda yayi watanni a kwance take ya jeme.

Lameenu ma cikin tashin hankalin da jemewan yake sbd bazai taba son ya rasa Mam ba tinda a yanzu shi kadai ne yake dashi a rayuwarsa,
Idan ya rasa Mam bazai taba iya komai na rayuwarsa shi Daya ba Babu Dan uwan nasa,

Sun rasa sauran Yan uwansu Badan basa sonsu ba sai Dan son zuciya da

shedan tareda muguwar zuciya datake rinjayarsu,
A yanzu tashin Mam da ganin lafiyansa shine abinda yake cikeda zuciyarsa ya Sanyaya jikinsa Dan haka gaba Daya ya koma Kalan jemewan Shima yana cikin tsaka me wuya.

*******Hudu bayan la'asar aka iso da gawar Haroon da Abdul mansion din Dad Omar sbd jamaal Daya Bada umarnin anan zaayi janazah dinsu wadda tini mutane masu yawan gaske suka fara halarta sbd daurin auren da sukai Niya tafiya shine ya koma janazah din Dan haka manyan mutane da Jamaa Tako ina.

Saida aka gama suturtasu siddeeq yaje gida ya dauko Ameenatou wadda take gida ta rikice musu gaba Daya Babbah da Yaya Abdul da Yaya Hafiz kawai take ambata sbd wayarta ce numbern da aka fara kira a wayar Babbah cewan sun samu mummunan accident wanda Dayan police din Kuma numbern Jamaal ya kira da wayar Dad Omar.

Zuwan siddeeq gidan ya tararda sauyawan lokaci Daya da Ameenatou din tayi sbd duk abinda yake jikinta na adon auren da Akai mata ta ciresa ko Dan kunne Bata bari ba daga ita sai doguwar Riga mara nauyi da mayafi ya fito ko gabanta Bata Gani Saida umma ta riqeta suka shiga motar datake jin kirjinta na sake toshewa tana Jan numfashi kaman me asthma.

Suna isowa har cikin harabar Mansion din gidan tana fitowa mota kafafunsa suka sare ta kasa daukan kanta sbd ganin tarin mutane Tako ina.

Umma da Aliyah data fito ne suka kamata har cikin palon farko na mansion din Wanda gawar biyu suke a shimfide fuskan Abdul an Riga anrufe ta Haroon ce ake kokarin rufewa ta iso gurin idanuwanta akan fuskan ta fara sauka kafin ta kyafta idanuwata suka sauka akan dadah Dake gaban dayar gawar zaune kaman mutum mutumi take numfashinta yayi sama Yana Neman fita daga kirjinta jikin tsananin tashin hankalin da Bata taba shiga ba da mummunan shock kafin suyi yunqurin tarota tafara kokawa da numfashinta Wanda yake kokarin ficewa.....

Umma datai saurin Kiran sunanta Bata ma gama rufe Baki ba kwakwalwan Ameenatou din ta juye gaba Daya sbd rashin Babbah da Haroon shine abu na karshe da kanta zai iya dauka Yanke jiki tayi a jikin umma ta zube qasa umma na binta kasan tana Kiran sunanta da tsananin tsoro da tashin hankali sbd wannan yanayin nata ya banbanta matiqar gaske Dana farko data Suma.

Daukanta Akai akayi ciki da ita sedai ko qarasa shigewa da ita baayi ba aka dauke gawar Dan yi musu sallah aka fice dasu.

Ficewan da Akai dasu yayi daidai da sake Saka dadah mummunan halin Daya Saka ita Kam dole asibiti Akai da ita.

Daga gurin janazah din suna dawowa wayar Jamaal ta samu mummunan sakon Daya Saka kansa sake ciki fitinanniyar tashin hankali sbd mum dinsu data yanke jiki kasamakon Jin rasuwar 'danta Kuma likitan ya tabbatar masa data samu paralyze suke tinanin Amma dai Bata farfadoba Dan haka suna tsananin buqatansa da gaggawa kafin ta farfado din.

Wannan mummunan labarin sabon tashin hankalin ya kusan Saka zuciyar JAMAAL bugawa take yafara kokarin tafiya sedai Kuma hankalinsa na rabuwa biyu da barin Ameenatou baa hannun kowaba,.

Babu Haroon,Babu Babbah,Babu Dad Omar,Babu Abdul Babu Hafiz bare Ahmed Dan haka barinta a daidai wannan lokacin kaman barin nama ne a tsakiyar damisoshi.

Babbar tashin hankalin sabo shine Ameenatou din gaba Daya anyi anyi taqi farfadowa dole Akai asibiti da ita itama aka jere su kowa da dakinsa Babu Wanda yasan inda kansa yake tsakanin ita da Dad da Dadah ga su Babbah da sai yanda hali yayi Suma.

Ahmed Daya Dan samu kansa cikin karfin hali ya sanar da Aunt Didi ayi gaggawan shirin fitar da Omar zuwa gurin dangin Didi din Dake Angola sbd jinyarsu acan tinda shi baida lafiyan basa kariya ko jinyarsa Dan haka su tattara su tafi can hankalinsa zaifi Kwanciya sbd zaa iya tinanin qarasa Omar din daga Nan tinda Yariga ya shige coma shi da Babbah sai yanda Allah yayi dasu.

Mum Nur Daman Batada niyar barin mijinta a Nigeria din ayi jinyarsa sbd ko zai tashi dukkaninsu sunsan ba yanzu ba ko duba da yanayin niqan da mota tai masa Dan haka a take washe garin ranar suka hada komai suka bar Lagos zuwa Abuja sbd acan zaa tashi.

Kaman abin da ake Jira qanqanin lokaci aka rufe mansion din suka tafiyarsu batareda sun tafi da Babbah ba kaman yanda Ahmed yaso sedai Shima ba qaramin Jin jiki yakeyiba tinda ya Bada umarnin tafiyar Bai sake sanin inda kansa yake ba shima har suka bar qasar.

Jamaal Neman haukacewa yakeyi a Nigeria din sbd duk yanda yaso wucewa yabar qasar da Ameenatou lamarin ya gagara sbd Babu abinda take dashi na barin qasar hakama acan kiransa akeyi mahaifiyarsa na tsananin buqatansa da gaggawa sbd tsoron sukeyi wani abu ya faru Jamaal din Baya kusa sunsan bazai taba yafewa kowa ba..Dan haka Jamaal din yake cikin tsananin

mawuyacin hali da Neman mafitan yanda zai Hana su Dad taba ko farcen Ameenatou din Tako ina.

Washe gari da wucewansu JDENS Dad dinsa ya farfado Dan haka ya sake Jin kansa ya dauki zafin da Bai taba dauka ba Dan haka Kai tsaye karfe biyun Rana ana fitowa sallahn azahar aka daura Aurensa da Ameenatou wadda ita Kuma karfe biyu da rabi ta farka sedai abinda bai taba tinanin zaiwa wani ba a rayuwarsa shine juyar Maka da hankali shine abinda yasan kadai mafita a garesa kafin yaje ya dawo ya tafi din sbd matiqar tana cikin cikakkiyar hankalinta Koda igiyoyin aurensa Dake kanta bazasu Bata cikakkiyar tsira daga su Dad da Lameenu ba sai Hakan,

Kasancewanta mara cikakkiyar hankali a yanzu shine kadai zai Hanasu mallakar ko tsintsiya daga dukiyar Omar kaf datake kasar duka sun bari daga gareta,

Babu maganar kudi ko wani gado tinda Omar yana raye ayanzu Amma sbd tsoron Omar din zai iya rasa rayuwarsa daga can ya sakashi yin Hakan sbd alluran duka duka wata Daya zatayi tana mata aiki zata dawo daidai Wanda yake Saka ran kafin can ya dawo gareta.

Siddeeq kuka yakeyi sosai jikinsa na cira sbd tausayin kansa,Dana Ameenatou din Dana Jamaal din Wanda ya kasance a tsaka me wuyar gaske gashi ya kasa yadda da kowa akan Ameenatou tinda wainda ya yadda dasu gasucan a kwance asibiti Babu Wanda yasan ranar tashinsu.

Hankalin lameenu tashi yayi mummunan yi da samun labarin juyewan kan Ameenatoun Daya fara Jin farin ciki da tsananin Jin dadin an tafi anbarta a hannunsu sune iyayenta sune sukeda cikakkiyar ikonta da dukiyarta.

Bai shiga Mummunan tashin hankalin Daya Sakasa faduwa ba Saida akayo asibitin dashi Shima Saida yaji AN DAURA AUREN JAMAAL DIN DA ITA, AMEENATOU OMAR JEEDEN SEELAH DIN A YANZU CIKAKKIYAR MATAR JAMAAL SEELAH DINCE HALAK MALAK..... Innalillahi wainna ilaihirrajiun.

Dad ma da farfafowansa kenan zancen girgiza yayi har Saida Shima jikin ya sake Neman rikicewa.

Sunaji suna Gani Jamaal ya dauke Ameenatou din ya Kaita wani tsadaddiyar asibitin masu matsalan kwakwalwa na wani abokin aikinsa acan Poland kwararre Shima ya Bada Amanarta gasu da wani irin tsananin tsaron gaske a asibitin wanda acan ne kadai zai samu nutsuwan barinta,
Hakama radadi da tashin hankalin da zatai ta shiga akan rasuwarsu Haroon da Babbah datake tinanin shine ya rasu bazasu taba dawo mata ba sbd

bazata taba tinawa ba sai ta dawo daidai zasuyi mata saukin gaske.

Da zai tafi haka ta zaune a dakinta da Babu abinda ya rasa tana kallonsa da fararen idanuwanta da suka rame lokaci Daya harya fice aka rufe mata dakin.

A ranar jirginsa yabar kasar bayan yabarwa siddeeq komai da zai kula dasu Babbah da Hafiz harma da Dadah da umma ke dawainiya da ita.

END OF PART 1
DAN ALLAH DUK INDA NAHI KUSKURE A DAUKESA A MANTUWA KO AJIZANCI,
Insha Allah bayan sallah zamu Dora part 2
Allah ya bamu ikon ibada cikin aminci da yardar Allah
Allah Kuma ya nuna mana kaman yanda mukaje hutun Nan ayau lafiya mun dawo lafiya.
##MAMUH
#AMEENATOU JDEN SEELAH
#JAMAAL SEELAH
#BABY ARFAT SEELAH
#LOVE
#DEEP
#ROMANCE
#THE SELAHS
#WARISCOMING
#ZAFAFA BIYAR

*_ZAFAFA BIYAR_*

1 *_Ameenatou!!_*
Mamuhgee

2 *_Tsutsar Nama!!_*
Billyn Abdull

3 *_Gudun Kaddara!!_*
Safiya huguma

4 *_Kwankwason Jimina!!_*
Miss xoxo

Guda Daya 400
Guda biyu 700
Guda uku 1k

Guda hudun 1200

*_6019473875 MUSAA ABDULLAH SAFIYAH keystone bank_*

*_ATURA SHEDA ZUWA 09166221261_*

*_MTN/VTU 09134848107_*

*Al'ummar NIJER kuma ku nemi wannan number don yin naku payment din 09033181070*

karki bari ayi tafiyar ZAFAFA BIYAR BABU KE!!!